😩😩😩😩

ZAWARCI😉

😩😩😩😩

LoVe aNd HoRrOr StOrY

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman.

_____

21/10/24

1-2

#Damagaram

Kʻarfe uku na dare agogon ɗakin ya nuna,a sa'ilin da mutane ke kwance suna hutawa a daidai wannan lokacin ne Hajara ta hana idonta bacci saboda yawunta da suke tsinkewa tsabar yadda suke kwaɗayin ɗanɗanon jini.

Idonta ta fara rikiɗarwa tun farko kafin ta tura ƙofar ɗakin wacce ta yi sa'a ba a kulle ba,ɗakin cike yake da duhu amma bai hana idon Hajara hango Safeenat ba wacce ke kwance ta tallabe ƙaton cikinta tana sharara bacci.

Yawun Hajara suka ɗiga ga ƙasa lokacin da ta yi tozali da ɗan jinjirin da ke kwance a marar uwarsa,ta ɗaga ƙafa da niyyar isa gare ta kawai sai ga wani haske da ba ta san daga ina ya fito ba ya luluɓe Safeenat.Da wani mugun sauri ta yi baya tana zarar idonta da suke jawur kamar wuta kafin kuma ta fice daga ɗakin gaba ɗaya,ba wai don ta haƙura ba sai don ƙara yin wani sabon shirin.

“Hajara lafiya kika zo kika tsaya tsakiyar falo?” muryar mijinta Dayyabu ta daki kunnenta,da mugun sauri ta lumshe idonta gudun kar asirinta ya tonu,ba tare da ta amsa masa tambayar ba ta yi gaba ta koma ɗakinta ta ja ƙofa ta rufe.Sai a lokacin ta ja wani numfashi haɗi da buɗe idon, ƙarƙashin gadonta ta je jawo wata tukunyar laka.Banda baƙin hayaƙi babu komai a ciki,wani yare ta yi sai ga shi ta rikiɗe ta koma tsakaka haka ta fito ta fara bin bango ba ta zame ko ina ba sai ɗakin Safeenat a karo na biyu.Har yanzu hasken bai ida gushe wa ba,wannan dalili yasa ta sauka kan dressing mirror ta fiddo harshenta tare da fara zuba yawunta cikin man shafawa da Safeenat ta bar shi a buɗe . Bayan ta gama ne ta ƙara bin bango ta fito mijinta ta gani ya buɗe ƙofar ɗakinta ya shiga ya kuma fito da alamu rashin ganin ta ne yasa haka.

Da sauri ta koma ta je ta ɗauki siffarta ta bil'adama,gefen gado ta zauna tana jin har yanzu kwaɗayinta bai kau ba.Haka wannan dare ya kasance daren rashin sa'a gare ta,sam ba ta yi wani baccin kirki ba.

Washegari

Tun safe Safeenat ta yi wanka ta shafa mai da turare sannan ta shirya cikin doguwar riga kasancewar cikinta ya tsufa ba ta da wata sutura mai yi mata in ba doguwar rigar ba.

Cikin sanyin jikin da ya zama tabi'arta ta fito,a falo ta tarar da ahalin gidan kan table suna cin abinci.

“Daddy ina kwana?” ta gaishe da mahaifinta,ya amsa cikin sakin fuska yana cewa “ lafiya lau Feenat ya ƙarfin jikinki?”

“Alhamdullah!” ta amsa tare da maida dubanta gefen Hajara ta ce “ina kwana Gwaggo?”

Hajara ta haɗe rai ta ce “ da ban kwana ba za ki gan ni ? Tsabar munafurci ba ki tashi fito wa ba sai da baiwarki ta gama girki kin fito ki kwashi banza to ban girka da ke ba”

Feenat ta sunne kai tana jin wani irin zafi na tasowa daga ƙasan zuciyarta,babban takaicinta kuma da ta ji Daddy yayi shiru bai ce komai ba.Yaran Hajara Munir da Munira suka shiga yi mata dariya,ba ta kula su ba ta wuce kitchen ɗin ta nema wa kanta abin da za ta ci.Ƙasan tile ta zauna dirshen ta soma tunanin bayan ta gama cin abincin,hawaye suka zubo mata ba ta shirya ba da sauri kuma ta dafe ƙaton cikinta da ke faman juyawa tana jin muguwar ƙaunarsa don a yanzu shine kawai zai rage mata raɗaɗin rashin masoyinta Bashir.

“A yi dai mu gani in tusa ta hura wuta! Yo wannan kukan shi zai maido miki mijin? Ai dama duk abin da aka yi shi da cin amana ba zai je ko ina ba.Yanzu da kika yi sanadin hana Bashir auren Murjanatu ina ce ya mutu ya bar ki,kuma ita Murjanatun na can Saudi Arabia cikin gata tana auren farin ciki” Goggo Hajara ta faɗa lokacin da ta tarar da Feenat a kitchen tana kuka.Ta yi kutufo da ƙafafunta ta ce “ ja ki ban wuri na wuce ko kuma na sabanta ki muguwa mai halin uwarta” da mugun sauri ta janye ƙafafunta wani sabon kukan na ƙwace mata.

Cikin masifar nan Goggo Hajara ta ci gaba da balbale ta da masifa,“ ki tashi ki fitar min daga kitchen zan ɗora girki ,ki koma can ɗaki ki ci gaba da munafurcinki”

Daga bakin ƙofa Daddy ya ce “Hajara ki zo ina son ganin ki ɗakina”

Idonta kamar za su faɗo ƙasa tsabar yadda take hararen Feenat,haka ta wuce ta je ɗakin Daddy a tsaye ta tarar da shi ya ba ƙofa baya.

“Daddyn yara ga ni ” ta faɗa cike da ladabi.

“ Haja ki kiyaye ni,bari gani na ƙyale ki ɗazu kin ci mutumcin yʻata,na yi shiru ne kawai don in nunawa Feenat ba ta kyauta da ta bar ki ke ɗaya ki ka yi aikin gida ba .Amma ba zan lamunci ki tozarta min yʻa ba,nan gidana ne don haka tana da yʻanci sake wa yadda take so.Mine ne na yi mata gori? Maimakon ki rarrashe ta akan halin da take ciki shi ne za ki tsiro mata da wata sabuwar masifar? Ta rasa mijinta wannan kaɗai abun tausayi ne,sannan ga tsohon ciki.Na san tun bayan da Feenat ta auri Bashir ki ka tsane ta,kin manta cewa matar mutum kabarinsa tun can farko Allah bai nufa Murjanatun ce zai aura ba”

Cike da munafurci Goggo Hajara ta soma kuka har da jan majina kamar wata yarinya,da mugun sauri Daddy ya juyo tare da jawo ta jikinsa yana cewa “mine ne kuma na kuka? Ke fa uwa ce bai kamata sai an faɗa miki abin da ya dace ba,ɗa na kowa ne ba ka san mai taimakon ka ba”

“Amma Daddyn yara ka fi kowa sanin yadda na riƙe Safeenat da zuciya ɗaya amma rana tsaka ta ruguza alaƙar nan don kawai ta ga banda burin da ya wuce Murjanatu ta yi aure”

“To ai yanzu komai ya wuce,ba ga shi ta yi auren ba? Jiya ma mijinta ya min magana kan yana so ta dawo gida ta haihu ”

Jin yʻarta za ta dawo sai ta manta da zancen kuka ta washe baki ta ce “au ! Madallah! Yaushe za ta zo?”

Daddy ya murmusa ya ce “a'a yʻarki ta ce kar a sanar da ke za ta yi miki bazata kawai ki zamana cikin shiri” da wannan Daddy ya fice ya bar gidan zuwan can Company wurin aikinsa.

Goggo Hajara kuwa kitchen ta koma sai ta tarar da Feenat ta ɗora girkin rana sai gumi take saboda zafin wutar gas,ta taɓe baki kafin ta fito.

Ita kuwa Feenat baiwar Allah sam ba ta ƙaunar tashin hankali wannan ya saka ta ɗora girkin duk don a zauna lafiya.Kafin ta gama jikinta ya soma ƙaiƙayi, soshe-soshe ta fara yi ganin abun na ta yin gaba yasa ta kashe gas ɗin ta fito.Ɗakinta ta

je,direct toilet ta shiga ta soma yin wanka sai dai ba ta canza zane ba sai ma wani ja da fatarta ta yi.Dakyar ta daure ta je ta ida girkin ta zuba a kuloli ta jera kan table,da ta koma ɗaki sai ta ɗauki hoton hannunta inda alamun jan ya fi yawa ta tura wa ƙawarta Sakeenatu tana tambayarta ko mene ne wannan kasancewarta likita .Babu jimawa ta kira ta bayan sun gaisa ne take cewa “ sai dai ki zo asibiti a duba ki ta waya ba a ganewa,kuma ni ba aikina ba sai dai na haɗa ki da likitan fata”

Feenat ta ja ajiyar zuciya ta ce “ KEENAT kin san Daddy ba zai bari na fita ba,kuma dama bai dace mace mai takaba ta fita ba”

Cike da tausaya wa KEENAT ta ce “ na sani amma ai lafiya ta fi komai ,ƙila kuma kin ci wani abu ne da ya haifar miki da hakan”

“Ban ci komai ba fa,ya aikin ana ta fama ko?”

“Wallahi kuwa,in sha Allah in na sauka zan biyo nan gida na duba ki” sosai suka yi hira kafin su yi sallama.

Daga inda take zaune ta fara kallon hotunan Bashir inda yake sanye da Kakin soja,nan ta lalace wurin kallonsu har sai da Munira ta shigo kiranta .Ta miƙe dakyar ta fita,a falo ta tarar da Goggo Hajara tun da ta fito ta lura idonta na kan cikinta.Ta sunne kai tana mai karanta ‘ Hasbunallahu wani'imal wakil ’ a can ƙasan zuciyarta,cikin nata ne ya soma yin motsi kamar zai fito mata ta cibiya.Tsabar yadda take jin ciwon juyinsa yasa ta kai hannu ta dafe ƙasan mararta tana mai fitar da nishin wahala,ido rufe ta ci gaba da sauraren azabar da ke ratsa duk sassan jikinta.

Goggo Hajara ta yi wani makirin murmushi tana mai cewa “ Safeenat lafiya kuwa?”

Sai a lokacin ta ware idonta da suka yi wani mugun ja,bakinta sam ba zai buɗu ba ballantana ta iya yin magana.Bayanta da ƙugunta suka ƙage lokaci guda wanda ya haifar mata duƙawa ba ta shirya ba,tuni idonta sun fara ganin dishi-dishi duk da wannan ne cikin farko tuni ta fahimci haihuwar ce ta zo bilhaƙi.

Goggo Hajara ta ce “ Haihuwa ce kam,Munira fita waje bari na ɗauko leda ”

“Mama in kira mai taxi ku wuce asibiti ko?” Munira ta faɗa tana kallon Safeenat wacce tuni ta fara wani gurnani mai haɗe da nishi.

“Uwar mai taxi za ki kira ,fice na ce” Goggo Hajara ta faɗa tana mai shiga ɗakin Safeenat ta ɗauko robar da aka tanadi duk wasu kayan haihuwa.

Da kanta ta shimfiɗa leda ta ɗora wasu zannuwa akai kafin ta ce “ Safeenat ki cire rigar nan mai haihuwa ina ruwanta da wata sutura” tsabar azabar da take ji yasa ba ta yi yunƙurin hana Goggo cire mata kayan ba.

Yawun Goggo Hajara har wani dalala suke suna tsinkewa lokacin da ta ga kan ɗa ya sawo kai.Jikinta har rawa yake wurin taimakawa yaron ya fito ,babu wani jinkiri ko ɓata lokaci ta fara juya ido tare da soma kai wa kurwar jinjirin hari sai dai ba ta ida cin galaba ba nishin Safeenat haɗi da kukan wata babyn ya dawo da ita hayyacinta.

Kirjin Goggo Hajara ne ya kusan ɓallewa zuciyarta ta faɗo tsabar firgici,jaririyar da faɗo cibinta a yanke yake sannan kuma babu marakiya saɓanin shi namijin da har yanzu take masa reto.

Sai a lokacin ne ma ta samu zarrar yanke mahaifar,ba tare da kuma ta san dalilin kawar mata da mugun nufinta ba ta soma kimtsa Safeenat wacce babu laifi ta dawo hayyacinta.

Goggo Hajara ta wanke kayan da kuma gyara ɗakin ta saka turaren wuta,ita ce kuma ta zaɓo wa Safeenat riga da zane.Har da haɗo mata tea mai zafi ta sha,gefe ta koma bayan ta gama komai tana tunanin zuci ‘ mi ya shiga kaina ni Hajara? Kamar ni kamar ba ni ce ba’ kukan jariran ne ya katse mata tunani ,ta ce “ ki ɗora su ga abincinsu” sai kuma miƙe ta soma nuna mata yadda za ta yi.Namijin kawai ya sha ita kuwa macen baya ga kuka babu abin da take,Goggo Hajara na ɗaukar ta sai kuma ta yi shiru kamar ba ita ce ke kukan ba.Muƙut ta haɗiye wasu yawu hango wani baƙin kallo daga cikin ƙwayar jaririyar da ko minti talatin ba a yi ba da haihuwarta.....

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

22/09/24

3

Sannu a hankali Gwaggo Hajara ta soma jin wani sanyi na ratsa ɓargo da tsokarta,kamar wacce aka yi wa doli kuma ta ƙi kawar da dubanta daga cikin idon Babyn.Idonta suka soma kafewa saboda wata irin shaƙa da ta ji an yi wa wuyanta,babu shiri ta buɗe bakinta na maita kurwar jaririn da ta soma cin galaba kansa ta fara fitowa daga can cikin hanjinta tana fitowa ta bakinta .Wani koren hayaƙi ne ya soma shiga cikin jaririn wanda daga bakin Gwaggo Hajarar yake fitowa,wata irin atishewa ya soma yi kafin ya tsala kuka.

Da mugun sauri ta yi baya ta zauna kan kujera,idonta na kan babyn wacce tuni ta soma bacci.

“Gwaggo ya ƙi yin shiru ko cikinsa ke ciwo?” Safeenat ta faɗa kamar za ta yi kuka tana ririga yaron,ran Gwaggo Hajara ne yayi mugun ɓaci sai yanzu tunaninta ya dawo a tunzure ta ce “ uban mi zan yi masa to? Lokacin da na yi haihuwata uban wa ya kama min wurin rainon ? Ki riƙe abin ki” ta faɗa tare da ajiye mata babyn kusa da ita,jikin Safeenat sai yayi sanyi dakyar ta samu yayi shiru bacci ya ɗauke shi.Ta shimfiɗe shi kusa da Baby girl ɗin kafin ta je ɗakinta don ɗauko wayarta,tana dawowa sai ta hangi maciji kan jaririyar duk ya naɗe jikinta da shi ba ta san lokacin da ta saki wata ƙara ba wacce ta yi daidai da ɓacewar macijin.Safeenat ta zo da mugun sauri ta ɗauki yaranta ta mayar da su ɗakinta,sai da aka ɗauki lokaci kafin nutsuwarta ta dawo ta soma kiran mutane tana shaida musu zancen haihuwar.Hatta Daddy sai da ta kira shi ta sanar da shi,babu jimawa kuwa sai ga ƙanwarsa Habiba ta zo gidan sosai Safeenat ta ji daɗin ganinta musamman da ta ga har da ƙullin kayanta ta zo da alamu za ta jima.

Ruwan zafi ta je ta ɗora cikin ƙatuwar tukunya kafin ta dawo,“ Safeenat ya zama doli ki kula da yaran nan musamman namijin don na ga shi ne mai rauni” Habiba ta faɗa tana shafar twins ɗin.

“In sha Allah Gwaggo Habibah zan yi,da alamu ma ya fi kuka dakyar na samu yayi baccin nan” cewar Feenat.

“Hum! Baccin wahala ne,ah to ai doli ma yayi Allah dai ya kyauta”

“Amen!" Feenat ɗin ta amsa ba tare da ta san dalilin Gwaggo Habibah na faɗar haka ba.Bayan ruwan sun tafasa ta juye su ta yi wa yaran wankan,namijin ana saka shi a ruwa ya farka tare da canyara kuka amma ita hajiya babba har aka gama wankan tana bacci tamkar wacce ba ta rai.Gwaggo Habibah kuwa sai murmushi take tana jin wani farin ciki ƙasan ranta,dama ita Allah bai taɓa bata haihuwa ba .

Safeenat ma sai da ta yi wanka da ruwan zafin ta gasa kanta da kyau ta fito ɗaure da towel,sai kuma yanzu ne Gwaggo Habibah ta lura da yadda fatar Safeenat ta yi ja.Da wani mugun sauri ta tashi ta cabke hannunta da ke ƙoƙarin ɗaukar kwalbar mai,“ jira na duba na gani” ta faɗa tana mai duba man ba tare da ta ce komai ba sai kuma ta fita direct ɗakin Gwaggo Hajara ta wuce ko sallama ba ta yi mata ba kuwa ta yi tsaye kai gare ta tana mai cewa “ an gaishe da uwar mugaye ta

duniya,wato baƙar zuciyarki na nan daram babu canji .To asirinki ya tonu na ga bala'in da kika zuba cikin man shafawar Safeenatu,sai dai ki sani sai dai ki ci kanki amma Twins sun fi ƙarfinki ”

Da wani mugun sauri Gwaggo Hajara ta tashi zaune,dama tun bayan da ta shigo ɗaki take jin duk jikinta babu daɗi dalilin kwancin da ta yi kenan sai kuma yanzu da ƙanwar mijinta ke feso mata kalaman rashin mutumci.Wani makirin murmushi ta yi kafin ta ce “ da alamu dai kin manta wace ce ni ko Habibah? Amma za ki gani”

“Babu abin da zan gani sai alkhairi...”

“Eh lalle wuyanki ya isa yanka” Gwaggo ta faɗa tana juya ido,Habibah ta tuntsire da dariya ta ce “au kin zata guntun tsafinki zai iya yin tasiri a kaina? To ki canza shawara tun wuri bai ƙure miki ba don yanzu daidai nake da ke”

Ganin alamun tabbas ba Habibar da ce ke tsaye a gabanta ba yasa Gwaggo Hajara haƙura da surkullen,idonta masu cike da mugunta ta tsura mata ta ce “ mi ya kawo ki ɗakina?”

“Ina so ki fita sabgar Safeenat da yʻayʻanta,in kuma ba haka ba....” sai kuma ta yi shiru tana cije baki haɗi da jinjina kai.

“Ki tona min asiri? A tunaninki akwai wanda zai yarda? Hahaha! Yaro man kaza,Habibah kar ki manta hatta gyatumarki a tafin hannuna take....” ta yi saurin katse ta da “sai dai shi wanda kike tutiyar da shi mugun tsafinki bai yi tasiri kansa ba ,na san kin san haka”

Ran Gwaggo Hajara ne ya ƙara yin baƙi,duk duniyar nan Habibah ce kawai ta zame mata ciwon ido duk yadda take son gudanar da lammuranta to muddin tana ga wuri sai ta roga su.

Kʻarar buga ƙofa ce ta maido ta daga guntun tunanin da take,ta bi bayan Habibar da mugun kallo tana jin baƙin cikin da ba ta da MAITAR IDO (MRS SADAUKI,duk mai son complete book ɗin nan zai iya tuntuɓa ta kai tsaye ta lambar da na rubuta a can sama) da tabbas ta jefa wa Habibah ƙwayar cutar da za ta zama ajalinta.

SAKEENATU

Tana tashi daga aiki ta fito don samun adaidaitar da za ta kai ta can gidansu Safeenat kwatsam sai ga kiran wayar mijinta Abbas .

“Mamuh ta ce yau ba ki bar mata abin da za ta ci ba ina son sanin dalili?” shi ne abin da ya fara cewa ko sallama babu,ran Sakeenatu ya ɓace amma ta haɗiye shi ta ce “ na samu yʻar aiki fa kuma kafin na fito na shaida mata kan ta girka mata abin da za ta ci”

“Yʻar aiki za ta kula da uwata? Keenat mi ya shiga kan ki ne? Yanzu dai na baki minti goma ki tabbatar kin yi mata girkin abin da take so” yana gama faɗa ya yanke kiran.

Tamkar za ta fashe haka take ji,mai ɗan sawu ma dakyar ta faɗa masa inda zai kaita.Tana shiga gidan ta tarar da Mamuh zaune kan kujera ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya tana wani yamutsa fuska,gaban Sakeenatu ya faɗi kamar kullum muddin dai za su haɗa inuwa ɗaya da surukarta ta.

“Barka da yamma Mamuh” ta faɗa murya na rawa,Mamuhn ta ce “ in kin gama yawon tanbaɗar sai ki shiga kitchen ki girka min wake da shinkafa”

Idonta tab ƙwalla ta shiga kitchen ɗin ta ɗora tukunya ko kayan ba ta cire ba haka ta tsaya sai da ta tabbatar ta gama sannan ta zuba a plate ta kai wa Mamuh.

Da zafi da komai ta saka hannunta tana ci mai na bin hannunta sai wani lumshe ido take alamun yana yi mata daɗi, Sakeenatu wacce ta tsaya don ganin ko yau ma Mamuh za ta yi irin yanayin nan sai kuwa ta ga ta yi.Idon Mamuh sai wani haske-haske suke fitar wa kamar kullum muddin dai wake da shinkafa ta girka mata.

A tsorace ta nufi ɗakinta ,kayan jikinta ta rage sannan ta shiga toilet.Shower ta sakar wa kanta,kamar abun almara haka ta soma jin yanayin jikinta na canzawa tana jin feeling wanda kuma abu ne mai wuyar faruwa da ita muddin dai ba Abbas ke a wurin ba.

Abu kamar wasa amma sai yin gaba-gaba yake,kafin Sakeenatu ta farga tuni ta hankalinta ya soma gushewa ta dumulmiya duniyar son kasancewa da mijinta.Tamkar a mafarki ta soma jin kamar ana wasa da sassan jikinta,sai dai idonta sun yi nauyin da ba za ta iya buɗe su ba ballantana har ta ga shin zahiri ne ko kuwa? Sama da minti goma tana cikin wannan yanayi kafin ta dawo hayyacinta,a doli ta tsarkake jikinta ta fito tana mamakin al'amarin.Bayan ta shirya tsab cikin riga da zane sai ta fito falo,Mamuh ta gani sai sharar bacci take kamar matatta .Dining ta je ta zauna ta buɗe kulolin da yaɗar aikinta ta yi girki,shinkafa ce da miyar kaji haka ta zuba ta soma ci tana mamakin yadda aka yi Mamuh ta zaɓi cin wake da shinkafa akan lafiyayen abincin nan .Bayan ta gama ta ɗauki waya ta kira Safeenat ta shaida mata za ta zo yanzu ,sai kuma ta koma ɗaki ta saka hijabinta ta ɗauko jaka ta fito.Tana fita ba ta wani wuya ba ta samu ɗan sawu ya kaita,da sallama ta shiga gidan har ta wuce can ɗakin da Safeenatu take wanda ya cika da mutane kusan dangin Bashir ne.

A mutumce take gaishe da kowa amma yanayin jikinta na bata ana kallonta,tana juyawa suka haɗa ido da Habibah wacce ta kasa ɗauke idonta kan Sakeenatu har sai da ta ji ta tsargu.Ta zauna kusan Safeenat tana mai cewa “waccan wace ce sai kallona take?”

“Kanwar Daddy ce fa ba ki gane ta ba?” Feenat ta faɗa tana mai miƙa mata boy bayan ta shafi kansa sai kuma ta ajiye shi aka miƙa mata girl ɗin.Wani irin shock ne ya ratsa Sakeenatu har sai da ta zabura,yayin da gabanta yayi mummunar faɗuwa ganin Babyn ta buɗe idonta tana kallon ta alhalin lokacin da aka miƙo mata ita tana bacci.Sakeenatu ba ta ida shiga tashin hankali ba sai da ta ga tamkar Babyn na yi mata murmushi.....

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

23/09/24

4-5

Wani irin abu ne marar misaltawa ke ratsa Sakeenatu tun daga kan babban yatsan ƙafarta har zuwa kwanyarta da ta soma toshe wa .Lamarin da take ji a al'aurarta kuwa kusan girme wa hankalinta ya yi,tamkar wacce ake fitar wa da wani dafi haka take jin ana yi mata motsi gami kuma da samun sassauci a doli ta lumshe ido ba ta shirya ba.Ita kuwa Gwaggo Habibah da ke can gefe sai murmushi take tare da yin zancen zuci don duk tana ankare da abin da ke faruwa.‘ Tabbas a duk inda ke da mugunta da cutar wa Allah sai ya kawo mai ceto mai magani,na zo kenan a gidan nan mutuwa kawai za ta fitar da ni zan saka ido sosai akan jaririyar nan zan raine ta da hannuna ta yadda zan taimaka mata wurin fahimtar baiwar da Allah ya yi mata da yadda za ta sarrafa ta’ sai kuma ta miƙe tana yin wani murmushin nasara.Babyn ta ɗauke daga cinyar Sakeenatu wacce gumi ya jiƙa ta har goshinta na ɗiga,babu

kuma wanda hankalinsa ke wurin hatta ita Safeenat sai hira take da dangin mijinta waɗanda suke cewa shi namijin a saka masa suna Bashir a yi madadi.

Sakeenatu ta ware idonta jikinta na ɗan rawa kamar wacce ta farka daga mummunan mafarki.Idonsu ya sarƙe cikin na juna,Gwaggo Habibah ta ce “ sannu! Bari na nemo miki ruwa masu sanyi” sai kuma ta shimfiɗe babyn wacce tuni ta koma baccinta.

Kitchen ta nufa don samo ruwa masu sanyi,sai suka yi kiciɓis da Gwaggo Hajara yar kallon-kallon suka yi kowacce na hararen yar uwarta.

“In tusa za ta iya hura wuta a yi mu gani mana,sai shegen kinibibi da nuna isa kan an san ɓoyayyar duniya nan kuma ba asss ” Gwaggo Hajara ta faɗa don kuwa a goshin Habibah ta fahimci sun karya wata muguntar tsafi.

Ita kuwa Habibar murmushi ta yi don ta fahimci mi take nufi wato in ta isa ta yi wa kanta maganin damuwarta.“ Nan gishirinki zai ƙare a dafuwar ƙaho,yadda bacci ya bar ido haka za ki gaji ki bar Habibah saboda kabewar kan kabari nake baƙin cikin masu taushe”

“Aikin banza sai aukin cika baki ,a hakan kuma na yi sanadin hana ki baccin kullum cikin kukan kin ƙi haihu ba”

“Haihuwa ai ta Allah ce,kuma alhamdullah yanzu na samu irina wacce tsoron samun ta yasa kika jefo min mugun nufinki ” Habibah ta faɗa tana wani murmushi,Gwaggo Hajara ta kasa cewa komai yayin da ita kuma ta ci gaba da cewa “ ko ba ki gane abin da nake nufi ba? To Safeenatu ta haifi wata Habibar sak irina ce ko na ce ma ta fi ni don ita murucin kan dutse ce ba ta fito ba sai da ta shirya” muƙut! Gwaggo Hajara ta haɗiye wasu yawun tsoro don kuwa ta fi kowa sanin babyn Safeenatu ba normal jaririya ce ba tun da ta ga zahiri.

Ta ja wani irin numfashi jin saukar ruwan sanyi kan fuskarta,dakyar ta ware ido tana kallon Habibah wacce tuni ta juya ta yi tafiyarta tamkar ba ita ce ta gama zuba mata ruwan a fuska ba.Cike da baƙin ciki ta koma ɗakinta,a yadda take jin jininta ya hau in ba jini ta sha ba ƙila zuciyarta sai ta buga.Tukunyar tsafinta ta ɗauko ta yi yɑn surkullenta kafin ta ɗauki mayafi ta fita waje,yara ta gani suna wasa daga inda take a tsaye ta soma kiran kurwar wani yaro cike da ƙwarewa wurin maita tsafi.Yaron ya dafe gefen wuyansa inda ya ji kamar an tsikare shi da allura amma bai bar wasar ba haka yake ci gaba da gudun yana son kamo wani,idonsa ne suka soma rufe wa kafin bugun zuciyarsa ya tsaya cak kawai sai ya faɗi ga ƙasa.Ita kuwa Gwaggo Hajara da wani mugun sauri ta rufe ƙofa,tuni yara sun fara ihu suna faman kiran sunansa.

Ɗakinta ta koma ta ci gaba da tsotse jinin yaron ko jira ba ta yi ba,don ta san sarai in ta jinkirta ajiye kurwarsa Habibah za ta iya fahimtar haka.Tsawon lokaci ta ɗauka cikin siffar mugunta kafin ta dawo normal,zuciyarta ta ji fayau babu ƙunci.Tana nan zaune sai ga Munira wacce rabon ta da gidan tun lokacin da aka ce ta fita.Kusa da mahaifiyarta ta zauna ta soma bata labarin yadda yaron maƙwabciyarsu ya faɗi suna tsaka da wasa,“ je ki nemo min Munir ya dawo gida ” shi ne kawai abin da ta ce tana jin wani daɗi a ranta ba don komai ba sai don ta yi mugunta.

Habibah na shiga ta miƙa wa Sakeenatu gorar ruwa mai sanyi haka ta shanye su tasss tana sauke ajiyar zuciya.“Ki dinga kula da kan ki mana,ko barin kai a buɗe ai yana sa maƙiya su yi galaba kanka”

“To in sha Allah ” Sakeenatu ta faɗa tana mai ɗan satar kallon jaririyar ƙawarta,ido ɗaya babyn ta buɗe ita ma tana kallonta babu shiri Sakeenatu ta miƙe tsaye tana cewa “ Feenat zan tafi sai kuma gobe in sha Allah zan zo da safe tun da babu aiki”

“Na gode sosai Keenat wai ina Ma'idah?”

“Tana wurin Mama tun wancan satin na kai ta kin san Komandan ta zo”

Safeenat ta waro ido ta ce “ ki ce dai a takure kuke yanzu,kai tsohuwar nan an yi yʻar masifa mine ne na zuwa hutu ke ba yʻar makaranta ba”

Sakeenatu ta tuntsire da dariya ta ce “ kar a yi babu ita mana,duk gani take wasu kuɗi ne da shi ba ta san rabin hidimar gidan ni ke yi ba a haka kuma za ta dinga tsiro da abubuwa tana saka sharaɗin abin da take so”

Safeenatu ta ce “ ah lalle ta ci sunan Komandan ɗin” nan dai suka yi sallama Sakeenatu ta fito.Kafin ta isa gida sai da ta saya wa Mamuh kifi don ta san tana son shi,da sallama ta shiga amma ta ƙi amsa mata sai ma tambaya da ta jefo mata “ daga gidan uban wa kike? Wato kin matsu na koma ƙauye shi ne kika je gidan malamai da bokaye a yi min asiri na tafi ban shirya ba”

Jikin Sakeenatu banda rawa babu abin da yake yi,kanta ƙasa ta soma rantse-rantse tare da sanar da ita inda ta je.

“Ita ƙawar taki ce ta baki magani kika yi wanka da shi ta yadda zan ji tsoron ki? Sakeena lalacewar taki har takai ki dinga faɗawa ƙawarki ƙarya da gaskiya akan ta baki magani? In maganin za ki nema mi yasa ba ki ce a baki na haihuwa ba sai na korar maƙiyiyarki”

“Wallahi Mamuh babu wani magani da aka bani,na faɗa miki barka kawai na je” Keenat ta faɗa cikin muryar kuka.

Mamuh ta tsure ta da ido,sam babu tabon duk muguntar da ta ajiye a jikin Sakeenatun komai ya rushe ta koma normal.Sannan a baccinta aka nuna mata ta yi wanka da ruwan magani duk mugun nufinta ya fita daga jikinta,jin shiru yasa Sakeenatu ta ɗago ido da zumar kallon Mamuh mugun ganin da ta yi ne yasa zuciyarta kusan faso allon ƙirjinta ta faɗo.

Idon Mamuh sak irin na maciji yanayin fuskarta ma ya canza duk ta yi baƙi,“ in kin gama gulmar sai ki wuce ki ɗora min wake da shinkafa” Mamuh ta faɗa tare da yin gaba,Sakeenatu ta ce “ akwai sauran na ɗazu bari na zubo miki ”

Ba tare da ta juyo ba ta ce “ ban so wani nake so ki dafa min”

Jakarta ta ajiye ta shiga kitchen ta ɗora girkin,wannan karon ko waken ba ta wanke ba kamar yadda tsarin dafa shi ya zo mata daga Mamuh ɗin ,dama ita shinkafar ba irin wacce ake wankewa ce ba.Cikin plate ta zuba bayan ta tsalala mai dayawa,sai ta fito ta nufi ɗakin Mamuh da sallama ta shiga duk da ta san ba za ta amsa ba.

Cike da ladabi ta duƙa har ƙasa ta miƙawa Mamuh plate ɗin wake da shinkafar amma ta ƙi karɓa sai ido da tsura mata.Tuni gaban Sakeenatu ya fara dukan uku-uku,“ ba zan ci ba!”

“Amma ke kika ce na girka miki ” ta faɗa murya na rawa.

“Tun zuwana gidan nan na faɗa miki sai an dirje wake an waken shi da hannu sannan ake girka min mi yasa yanzu ba ki yi ba?”

“ Na zata kina jin yunwa ne sosai shi yasa na yi haka don na yi sauri”

“To sai ki je ki sake dafa wani” Mamuh ta faɗa tana mai miƙe wa tsaye,cikin dakiyar zuciya Sakeenatu ta ajiye plate ɗin ta ce “ ki yi haƙuri Mamuh akwai aikin da nake son yi yanzu,ki ci wannan ɗin gobe in Allah ya kai mu sai na yi miki irin wanda kike so ɗin”

Sam ko kaɗan Mamuh ba ta yi mamakin furucinta ba ,don dama da tsafi ne ta ci galaba har Sakeenatun ke mugun tsoronta yanzu kuma komai ya karye.Ita kuma tana gama faɗar haka ta fice,da ta fito har sai da ta ja ajiyar zuciya tana mamakin yadda yau ta cire tsoron Mamuh.

Tana shiga wanka sai ta ga period ɗinta ya zo,wanda kuma ba komai ya haifar da haka ba sai gwagwarmayar fitar da sihirin jikinta.Cikin ƙananan kaya ta shirya sannan ta haye bed tare da kiran Abbas,cike da nishaɗi suka yi hirar soyayya nan ne kuma ya shaida mata gobe zai zo sannan a karɓo Ma'idah don ita yake son fara cin karo.Har ƙasan ranta ta ji daɗin furucinsa , wannan yasa suna gamawa ta kira can gidansu ta ce a kawo mata Ma'idar.

Washegari

Kuwa tun safe Sakeenatu ta soma gyaran gida ita da yar aikinta wacce ba za ta wuce shekara ashirin ba mai suna Fa'iza.Mamuh dai na ta kallonsu ba ta ce komai ba don fushi take da Sakeenatu,da kanta ta yi girki Fa'iza na kama mata.

“Shi kuma waken nawa sai yaushe za a girka?” Mamuh ta leƙo kitchen ɗin tana mai faɗar haka.

Sakeenatu ta ce “ yanzu zan yi” ba ta ƙara cewa komai ba ta tafi.

“Fa'iza wanke min waken nan da kyau sai ki girka wa Komandan ban son ta kawo min cikas ina cikin farin ciki”

Yar dariya Fa'iza ta yi kafin ta soma wanke waken kamar mai wankin kaya,ita ce ta girka shi kuma.Sakeenatu ta zuba a plate da kanta ta kai wa Mamuh jikinta har rawa yake ta soma ci tana lumshe idonta waɗanda tuni suka soma yin hasken nan.Ita dai Sakeenatu Allah na gani tsoron yanayin nan take ,da sauri ta wuce ɗakinta ta yi wanka ta shirya cikin wani rantsatsen less tana tsaka da fesa turare Ma'idah ta shigo da gudunta ta na kiran Ammyna.Ita ma sosai ta yi kewar yarinyar sai ta rungume abarta tana cewa “ ke da wa ne?”

“Anty” ta bata amsa.

A ɗan firgice Nafisa ta shigo tana cewa “ anty Sakeena wace ce waccan a kitchen? Zo ki ga abin da take”

“Yʼar aikina ce lafiya?”

“Zo dai ki gani” cewar Nafisar tana mai yin gaba Sakeenatu na take mata baya har suka shiga kitchen ɗin.

Fa'iza suka tarar duk ta cire suturar jikinta tana fitar da wani nishi idonta a rufe suna tsiyayar da hawaye.....

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

24/09/24

6-7

Tamkar wacce ke wata mu'amala da namiji haka Fa'iza ke yi ,hankalin Sakeenatu in yayi dubu to ya watse.Ta kalli ƙanwarta ta ce “ Nafisa ko iskokai ne? Dubi abin da take yi”

Nafisa ta ce “ anty Sakeena tun da nake ban taɓa ganin mai kalar iskokan nan ba,hatta masu aljanin soyayya ai sai in suna bacci ne suke zuwar musu dubi ita wannan fa tamkar idonta biyu fa”

“Yanzu dai don Allah ki taimaka mata tun da ke Malama ce kin ga Ma'idah har ta soma kuka” cewar Sakeenatu tana mai jan yarta zuwa waje.Nafisa ta cika kofi da ruwa ta tofa ayatul ƙursiyu da amanar rasulu sannan ta shiga watsa ma Fa'iza ruwan,a sannu a hankali ta soma barin abin da take daga ƙarshe ta buɗe idonta waɗanda suka kaɗa suka yi ja.Nafisa ta shiga yi mata sannu kafin ta taimaka mata ta mayar da kayan jikinta,“ dama kina da aljanu?” Sakeenatu ta tambaya wacce ta dawo.

Fa'iza ta girgiza kai,“ to tashi ki yi wanka sai ki zo ki zuba abinci ki ci”

Da “ toh” ta amsa kafin ta fita zuwa Toilet ɗin tsakar gida kamar yadda Sakeenatu ta shaida mata da ita za ta dinga amfani.

Wanka ta soma sai da ta saɓa jikinta har sau biyu sannan ta fito,wasu kayan Sakeenatu ta bata ta saka abincin ma da ta zuba gidansu ta wuce da shi.

Su kuwa a falo suka zauna suna hira Nafisa na bai wa Ma'idah abinci a baki,Abbas yayi sallama da gudu ta nufe shi tana “ Daddyyy” ya caɓe ta tare da cira ta sama yana yi mata wasa haɗi da kai mata sumba.

Cike da farin ciki ya ƙarasa ya zauna,Nafisa ta gaishe shi yayin da suke aikawa juna wani kallon so shi da Sakeenatu mai cike da kewa.

“ Mu je ka fara yin wanka ko?”

“A bani abinci tukuna don Allah ” ya faɗa yana wani murmushi,Ma'idah ta ce “ Daddy ni ma ina ci” sai aka zuba musu ya dinga bata a baki ita kuma sai surutu take yi masa.Suna tsaka da nishaɗinsu sai ga Mamuh ta fito,fuskar nan kicin-kicin,“ ita kuma wannan farar tinkiyar?” ta yi tambayar tana zunɗen Ma'idah wacce ta tsorata da ganin Mamuhn.

“Ina wuni Mamuh? Fatan na same ku lafiya?” Abbas ya faɗa cike da ladabi.

“Ka bani amsa ta”

“Ma'idah ce fa yʼar wurin Keenat” ya bata amsa a sanyayye.

“Shegiya za ka ce wacce ba a san taƙamaimai wane ne ubanta ba,kai da ka iya kwashe-kwashe ka rasa wacce za ka auro sai wadda ta gama yawon duniya ta tsiyayar da duk ƙwayaƙwayin haihuwarta a titi.To ban yarda ban lamunce wannan tinkiyar ta zauna a gidan nan ba” Mamuh ke faɗa cikin masifa ita kuwa Ma'idah tuni ta soma kuka musamman irin abin ban tsoron da take hangowa a fuskar Mamuh.

Abbas ya sunne kai ya ce “ a dai yi haƙuri Mamuh dukkan bawa bai wuce jarabawa,Ma'idah ita yarinya ce ba ta san komai ba”

“Wallahi sai ta bar gidan nan” Mamuh ta faɗa cikin ƙaraji, Sakeenatu kuwa banda kuka babu abin da take yi .

Hannun Ma'idah ta kama da niyyar jawo ta,ita kuwa baiwar Allah cike da tsoro ta ɗauki cokali mai yatsu ta caka ma Mamuh ita a ido da zumar ceton kanta ga dodo.

Wani uban ihu Mamuh ta yi tana cewa “wayyo idona! Yʼar daba ta kashe ni” jikin Abbas na rawa ya je ya kamo Mamuh wacce tuni idon ya soma fitar da jini,hankali tashe ya soma goge jinin wani na zubowa a doli ya kama ta zuwa asibiti.

Bayan tafiyarsu ne Nafisa ta soma tofa ma Ma'idah addu'o'i saboda yadda take wani irin kuka tana firgita,cikin kuka Sakeenatu ta ce “ Nafisa ki ɗauke ta ku wuce gida don Allah”

“Ke kuma a nan za ki zauna? ”

“To ina zan je Nafisa? Haƙuri zan yi dama aure ya gaji haka sanin kan ki ne a can gidan ba wani jituwa muke ba ni da Mama ta ɗauki ƙiyayyar ɗan farin ta ɗora min”

“To amma dai ki kula da kan ki,in kin ga abin ya yi yawa kawai ki tawo gida”

Kuɗi ta basu sannan suka bar gidan,ita kuma ta ɗauki waya ta kira Abbas don jin asibitin da suke shi da Mamuh yana shaida mata ita ma ta fita ta je.Tuni Mamuhn ma ta yi bacci an naɗe idon nata da bandeji ga kuma ƙarin ruwa an saka mata.

Jikinta a sanyayye ta ce “ ka yi haƙuri” Abbas ya kamo hannunta ya ce “ dama haka Allah ya tsara,ina Ma'idah?”

“Nafisa ta koma da ita can gida”

“Don me? Zan rarrashi Mamuh na san za ta amince ta zauna da mu”

Ta sakar masa murmushi ta ce “ na gode sosai da kawaicinka gare ni” wani kallo yake aika mata yana mirza tafin hannunta,da ido ɗayan mai lafiya Mamuh ke kallonsu tana jin wani irin haushi da takaici.

“Mine ne haka? A asibiti fa muke ka bari har mu koma gida” Sakeenatu ta faɗa tana janye jikinta daga nasa ganin abin zai wuce gona da iri.

“Mu je gidan to tun da kin ga Mamuh ta samu bacci ,sai mu dawo daga baya” Abbas ya faɗa yana langwaɓar da kai saboda ba ƙaramar kewar ta yayi ba.

“To ai na farka” cewar Mamuh tana mai tashi zaune haɗi da hararen Sakeenatu,da ɗan sauri ya miƙe yana tabayarta jiki.“ Ka kira likita ya cire min ƙarin ruwan nan sai mu wuce gidan tun da uwarka ba za ta barin ka cikin salama ba” cewar Mamuh a zafafe,Abbas ya fita don kiran likita.

“Duk tsiyarki dai ba za ki iya canza ma tuwo suna ba,Abbasi ɗana ne ba naki ba don haka ni ke da iko da shi ba ke ba.Kuma wannan shegiyar taki sai ta san ni ta caka da cokali sai na shayar da ke mamaki”

Da wani mugun sauri Sakeenatu ta je gaban Mamuh ta tsuguna ta ce “ don girman Allah Mamuh ki yi haƙuri , Ma'idah yarinya ce ba ta da wayo ko me za ki yi to ki yi min amma kar ki taɓa yaƴata” ta ƙarashe maganar hawaye na zubo mata saboda zuwa yanzu ta yarda Mamuh muguwa ce.

Kafin ta kai ga bata amsa Abbas ya shigo shi da likita,ya ce “ sai kin yi kwana uku sannan za mu sallamar ki”

“To ka sanar da uwarmu wacce ta matsa mu je gida” Mamuh ta faɗa a zuciye tana hararen Sakeenatu.

Likitan yayi murmushi ya ce “ yanzu yadda za a yi sai ka nemo wacce za ta zauna da Mama,amma gaskiya ba za mu sallame ta ba yau” sai yayi wa Mamuh allurar bacci,duk yadda masifa ke cin ta haka ta haƙura saboda ƙarfin allurar.

Shi kuwa Abbas Gwaggonsa ya kira wacce ke nan Damagaram ita ke bi ma Mamuh,babu jimawa kuwa ta zo .Ya ja matarsa zuwa gida,cike da zallar soyayya suka gamsar da junansu.

SAFEENATU

Tun bayan da kowa ya watse aka bar su ita da Gwaggo Habibah sai ta nutsu sosai kafin ta ce “ Gwoggo ni kam ɗazu wani abin ban mamaki ya faru,maciji na gani ya naɗe Baby girl ɗin nan ina yin ihu ya ɓace kamar aljani ”

Gwaggo Habibah ta yi murmushi ta ce “ kar ki wani ji tsoro,sannan ina so ki kwantar da hankalinki duk wani abu da za ki gani ki yi shiru da bakinki.Duk kusan yan biyu suna da wannan baiwar,to ke macen ce ke da shi don haka ki shirya ganin abubuwa iri-iri wasu na tsoro wasu kuma na almara”

Safeenat ta ja wani numfashi kafin ta ce “ to Allah cire min tsoron” ba ta ida rufe bakinta ba hasken ɗakin ya ɗauke duhu ya turnuƙe shi kai ka ce dare ya tsala.Duk

tsit suka yi babu wanda ya ce wani abu,sai kukan jaririyar da ya soma tashi sannu a hankali tsawon minti biyu kafin ta yi shiru.Hasken ɗakin na dawowa Safeenatu da Gwoggo Habibah suka yi yʼar rige-rigen ɗaukar babyn duk suka yi tsaye suna kallon yadda goshinta ke fitar da wani haske yana ƙyalli a gaban idonsu ya ɗauke sai ga shatun haƙoran maciji ya bayyana raɗau .Safeenat ta kai hannu ta shafi wurin sai kuma ya ɓace,ta ja ajiyar zuciya tana mai ɗaukar jaririyar ta soma shayar da ita.

Daddy ya yi sallama ya shigo,duk suka gaishe shi kafin a basa babys ɗin ya gani.Sosai yayi musu addu'a sannan ya fita,haka suka ci gaba da yin hirarsu har dare ya tsala.Duk sun yi shirin bacci za su kwanta amma ita Baby kamar ɗiyar aljanu ta ƙi baccin sai ma wani kuka-kuka da take yi.

“Safeenat ki bata abincinta mana” Gwaggo Habibah ta faɗa tana shirin tashi ta kunna wuta.

“Ina ta ƙoƙarin bata ta ƙi karɓa” cewar Safeenar.

Kusa da ita ta zauna tana shirin ɗaukar babyn sai ta lura da yadda hannunta na hagu ke fitar da wani zane mai hasken wuta kamar ta murhu.Wani irin murmushi ne ya suɓuce wa Gwaggo Habibah ba tare da ta shirya ba cike da murna ta jawo hannun jaririyar ta riƙe sannu a hankali har zanen ya fito raɗam letter M ta fito sai a lokacin kuma jaririyar ta yi shiru sai ajiyar zuciya da take saukewa.

A ɗan ruɗe Safeenatu ta ce “Gwaggo mine ne kuma wannan?”

Sam Gwoggo Habibah ba ta bata amsa ba sai safar hannu da ta je ta binciko cikin kayansu ta saka wa hannun mai zane.“Daga yau kar ki ƙara barin hannunta a buɗe ki dinga saka mata safar hannu ”

“Gwaggo ina tambayar ki mine ne ba ki bani amsa ba”

“Alama ce ta prophétie/prophecy,da yawan yʼan baiwa tana soma aiki ne in sun kai shekara sha takwas amma ke yarinyarki tun farkon dirowar ta duniya tata baiwar ta fara aiki.Ta ceci ɗan uwan tawaicinta sannan kuma ta ceci ƙawarki Sakeenatu ”

Ba don ta fahimci zancen da kyau ba ta ce” mi ya samu Keenat ɗin?”

“An yi mata ajiya cikin ruhinta ta yadda esprit zai samu damar yin yanda ya so da gangar jikinta har ya cutar da ita”

“Ya aka yi kika sani to?”

“Safeenatu yi bacci in lokacin fahimtarki yayi babu buƙatar ki yi tambaya”

Da wannan duk suka yi bacci, Safeenatu na tsaka da yin mafarki akan goben yarta Gwaggo Habibah ta tashe ta daga bacci.“Ruwan wankan ki na can toilet ta tsakar gida,ki je yi wankan sabulu kafin na zo na gasa miki jikinki da towel”

Ta yi miƙa ta tashi a gajiye saboda kwana dare ta yi tana shayarwa,sai da ta ɗauki wani zane da hijabi sannan ta fita ta bar Gwaggo Habibah za ta yi wa Twins wanka.

Sakeenatu na fitowa suka yi kiciɓis da Gwoggo Hajara ta gaishe ta sannan ta wuce toilet.Ita kuwa tsabar mugunta yasa ta koma ɗakinta ta yo shirin mugunta yau ma siffar tsakaka ta ɗauka ta yi tsinke can toilet inda Safeenatu ke wanka tun tuni.Da ga can saman katanga Gwaggo Hajara ke ƙarewa surar Safeenat kallo,cikin salon mugunta ta mayar da harshenta dogo sannan ta zuro shi tun daga can sama har ƙasa yana taɓa tile.

Safeenatu ta yi wani ihu wanda bai sauka ko ina ba sai cikin kunnen yarta jaririya,kwacaaaa Gwaggo Hajara ta faɗo cikin ƙatuwar robar tafasasshin ruwan zafi.....

Ga masu son fara yin payment su yi min magana ta lambata na basu detail na sabon account number da za a tura kuɗin ba waccan na Ecobank ba.DM +22795045822

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

25/09/24

8

Da wani mugun sauri Safeenatu ta yi tsalle ta koma jikin ƙofa tana kyarma ,idonta ƙur cikin robar wacce tsakakar ke ta ƙoƙarin fitowa daga ruwan .Ganin ta soma yin girma sosai yasa Safeenatu ta buɗe sakatar toilet ɗin zane a hannu ta fito Allah yayi sa'a babu kowa a tsakar gidan,dakyar ta yi ɗaurin ƙirji kafin ta nufi can ciki da gudu.

“Ke lafiyar ki?” Gwaggo Habibah ta yi tambayar .

Feenat ta dafe gefen zuciyarta da yake mugun bugawa ta ce “ tsaka...ka ce ta faɗa cikin ruwan da nake wanka”

“Shi ne kike wannan haƙin? Kai Allah ya shirya min ke ban san lokacin da za ki girma ba”

“Gwaggo ba normal tsakaka da kika sani ba ce, wannan ƙatuwa ce inda kin ga yadda halshenta ke da tsayi ya fi pampo fa”

Shiru Gwaggo Habibah ta yi tana kallon Baby girl don kuwa a gaban idonta da tana yi mata wanka wani mugun haske ya fita goshinta tamkar an jefa kibiya.

“Allah ni dai ba zan sake shiga toilet ɗin waje ba ƙila ma aljani ne” muryar Safeenatu ta katse mata ɗan guntun tunaninta.

“Bari na je na gani ” cewar Gwoggo Habibah kafin ta miƙe ta fita zuwa Toilet ɗin tsakar gida,tun kafin ta ƙarasa ciki take jin nishin wahala .

Ido huɗu suka yi da Gwaggo Hajara wacce zuwa yanzu tuni ta galabaita ta yi wani tsamo-tsamo cikin ruwan zafin ta kasa fita . Gwaggo Habibah ta yi wani murmushi tana kallon yadda ruwan suka yi baƙi tsabar yadda muguntar da ta shiryo ma Safeenatu ba ƙarama ba ce.

“Kʼarshen alawa ƙasa! Yanzu wa gari ya waya? Shi dama ramen mugunta an ce ka gina gajere in kuma ka gina dogo kai za ka faɗa .Ai wallahi ba zan taimaka miki ba sai dai ki dawwama a ruwan zafin nan,in kuma kin ga na taɓa robar nan to wallahi cikin masai ne zan zubar da ku ke da ruwan” Gwaggo Habibah ta faɗa tana wani murmushin jin daɗi.

Kamar daga sama tsakaka ta soma magana wacce ta kasance Gwaggo Hajara ,“ ki taimaka min Habibah na yi miki alƙawarin daga yau na zubar da makaman yaƙi”

“Kar ma ki zubar ki yi ta riƙon su har sai Mahadi ya bayyana,ba dai maita ita ce jarinki ba? Ki ci gaba da yi wata rana mutuwarki za ki ci” tana gama faɗar haka ta fito daga toilet ɗin,sai kuma ta tuna duk wanda ya mutu a ruwa yayi shahada da sauri ta koma ba tare da ta ce komai ba ta ɗauko robar ta fito da ita tsakar gida tare da juye ruwan ga ƙasa.

Tamkar acid haka turɓayar ta soma yin bori tana fitar da kumfa tsabar bala'in da ke tattare da ruwan,a kunyace Gwoggo Hajara tsakaka ta soma jan ciki ta nufi hanyar ɗaki.

Ita kuwa Gwaggo Habibah ji ta yi kamar ta sa ƙafa ta laɓe shegiya kowa ya huta.Tana komawa ciki ta cewa Safeenatu “Ki shiga toilet to kafin na juye ruwan yi miki wankan” sai kuma ta fita ta ciko ƙaton bokiti da ruwan zafi,da ɗan ƙaramin towel ta soma yi wa Safeenatu wankan jego ita kuma tana ihu kamar wata ƙaramar yarinya.

Macijin jiya ne ya sake bayyana a jikin macen yana wani naɗe jikinta,ita kuma ta buɗe ido taram tana kallonsa kamar mai wayo.Tsawon lokaci ya ɗauka tare da ita yana yi mata wasa kafin ɓace jin motsin su Safeenatu za su fito.Gefen gado ta zauna ta soma shayar da yaran kafin ta kimtsa cikin riga da zane,sai da Gwaggo Habibah ta gama wanka ita ma ta fito ta shirya sannan ta je ta kawo masu abinci suka ci daga nan suka wuce asibiti bayan sun karɓi kuɗi wurin Daddy.Lafiyarta da ta babys aka duba kafin su dawo gida,tuni kuma yan Barka suka fara zuwa in waɗannan sun fita wasu sai su shigo.

SAKEENATU

Tana rungume jikin Abbas ta ce “ Yau tana ɗaya daga cikin ranakun ovulation ɗina,yau na gama period ” cikin tsokana ya ce “ period ɗin ɗaya rana ” ta ja

hancinsa ta ce “ eh na dai ji,inda ina jimawa kafin ta ɗauke ai da yanzu ba ka kasance da ni ba don jiya ne na gan ta”

Ya gyara mata kwanciya kan ƙirjin nasa yana mai cewa “ Keent don Allah ki dinga bin Mamuh a hankali kin san ta tsufa,ban so kina yin abin da zai ɓata ranta ki guji ɓata mata don farincikina.Ina yi miki wani mugun so ne wanda na san ke ko rabin shi ba ki yi min”

“To in sha Allah na yi ma alƙawari zan kiyaye,ai Ma'idar ma an tafi da ita”

“A'a za ta dawo,sanin kan ki ne yadda nake mugun sonta ba zan iya yin nesa da ita ba”

Wani daɗi ne ya luluɓe zuciyar Sakeenatu,ita ce shaida kan son da yake yi wa ƴarta duk da ta fito ba ta hanyar aure ba.Za ta iya cewa halarcin bai nuna mata ƙyama ba ne ya ɗunguza ta ga aurensa,soyayyarsa ma ba ta jima da samun gurbi a zuciyarta ba.

“Ina son ki Keenat!” furucinsa ya katse mata tunani,ta yi murmushi mai ɗan sauti ta ce “ na gode”

“Ke ba za ki faɗa kina sona ba? Keenat sai yaushe zan ji furicin so daga bakinki?”

Ta laƙace masa hanci ta ce “ sai ranar da na haifo ma kyakkyawan Prince mai kama da kai” sai kuma ta miƙe ta je ta shiga toilet,shower ta sakarwa kanta tana tunanin saurayinta mahaifin Ma'idah.Ruwan hawayenta haɗi da na pampo suka haɗu wuri ɗaya suna zuba.Daga bayanta ta ji an rungume ta,da sauri ta juyo suna fuskantar juna kallo guda yayi mata ya hango damuwa a shimfiɗe a ƙwayar idonta.Zuciyarsa kuma ta basa ta yi kuka,bai tsaya tambayar ta ba ya ɗora bakinsa kan nata a wannan rana a kuma daidai lokacin nan Abbas ya shayar da ita zumar ƙauna mai haɗe da yayafin kalaman soyayya masu nuni da sadaukarwa.Ba tare da ta shirya ba ta ce “ I love You Abbas!” numfashinsa ne ya kusan tsaya wa tsabar murna da farin ciki,kamar wani ƙaramin yaro ya soma yi mata kuka saboda kawai ta ce tana sonsa.

Shi yayi musu wanka ya shirya su,a ranar a gida ya ja su sallah har ta isha'i .Bayan sun salamce sun yi dogayen addu'o'i ya dube ta da kyau ya ce “ Keenat fatan bayan tafiyata duk salloli kin yi su kan lokaci kuma kin tsare su?”

Da sauri ta sunne kai ba tare da ta basa amsa ba,yatsun ƙafarta ya soma ja mata tare da soma yi mata nasihar da ya saba game da mai wasa da sallah a ƙarshe yake cewa “ in kuma na ga kin ƙi yi zan kawo miki ƙanwa ustaziya” a shagwaɓe ta faɗa jikinsa ta ce “ to ai ina yi ko”

“Kina yi ko za ki dinga yi?”

“Duka biyun! Ba za ka koma asibiti ba?”

“Tare za mu koma tashi ki shirya” da “ to” ta amsa kafin ta canza kaya suka fito,sai da ya tsaya ya saya musu fruits sannan suka isa asibitin.Da sallama suka shiga ɗakin Gwaggo Rahamu ce ta amsa yayin da Mamuh ta juya musu baya tana jin wani irin baƙin ciki ya turnuƙe ta saboda a yadda ta gansu cikin farin ciki suna nishaɗi ta san sun keɓe da junansu.Abbas ya ƙarasa yana mai cewa “ Mamuh ya jikin naki?”

“Ka damu da ni ne ka sa ƙafa ka yi tafiyar ka? Wato Abbasi matarka ta fi ni ko?” ta faɗa cike da masifa tana juyowa.

“Ki yi haƙuri Mamuh Allah dai ya baki lafiya ” ya faɗa kansa ƙasa.

Tsabar fitina ta Mamuh sai cewa ta yi “ ina wakena?” Abbas ya ɗago da sauri yana kallon ta yana mai cewa “ wane irin wake kuma Mamuh yanzu da daren nan? Ga ayaba nan da lemu da apple na sayo ”

“Na yi da kai na ce ka sayo? Ita waccar abar ai ta san wake nake ci mi yasa ba ta dafo ba?”

“Yi haƙuri Mamuh gobe sai a daf....” bai rufe baki ba Mamuh ta saka kuka yana cewa “ shinenan tun da mata ta fi uwa”

Da mugun sauri Sakeenatu ta ce “ bari na koma gida sai na dafo mata”

Abbas ya ce “ to ki yi sauri” ta yi tunanin shi zai kai ta amma sai kuɗin ɗan sawu ya bata,tana zaune tana hawaye har suka iso gida ta biya shi kuɗin kafin ta wuce ciki.

A gaggauce ta soma aikin tana mita “ an yi tsohuwa kamar mayya kullum wake yanzu nan in ban wanke shi ba sai ta sani mtsww ” ta ja tsuki tana dirje waken amma jin ita ma an ja mata tsuki yasa ta zabura tana dube-dube sai dai babu kowa.Watsar da tunanin ta yi ta ci gaba da aikinta wani tsukin ta kuma ji sannan ana magana ƙus-ƙus,gabanta ya faɗi jin tamkar ana tafiya cikin falo.Tana shirin fitowa aka ɗauke wuta,lalubo ta soma yi cikin duhu ko Allah yasa ta ɗauko wayarta ta kuwa yi sa'a ta samu jakarta hannunta har rawa yake ta zuge zip ta ciro wayar sai ta ga saura ƙiris batirin ya mutu alhalin a cike ta bar ta.Tana ƙoƙarin ganin ta kunna fitilar ta ji tamkar saukar huci kusa da ita,ta wani juyo da sauri ta inda take jin abin tare da haska hasken screen babu kowa sai ƙafafuwan ƙofato da ta yi arba da su babu kuma gangar jiki.....

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

26/09/24

Babu shiri Sakeenatu ta saki wayar ta arta a guje,sai dai ta nemi ƙofar fita ta rasa saboda mugun duhun da ya mamaye gidan baki ɗaya.Cikin ƙanƙanan lokaci duk ta firgice,dakyar ta iya samu ta fito tsakar gida da lalabe zuciyarta sai ƙara tsananta gudu Waige-waige ta fara sai ta ga ashe kaf unguwar ne babu wuta,ba ta gama daidaita numfashinta ba wata baƙar mage baƙa ƙirin ta soma yin kuka miyau! miyau! Kukanta duk ya cika gidan.

Ta ɗaga kai dakyar ta dubi inda sautin kukan ke fitowa,ido huɗu suka yi da magen wacce hasken idonta yake kamar na lantarki sai canza kaza suke.A hankali ta sauko daga katangar ta soma nufo inda Sakeenatu ke tsaye da gajiyayun ƙafafunta,Allah ya gani ba ta wani ba wai karatun addini muhimmanci ba dukkan lokacinta da hazaƙarta ta zuba su ne a harakar boko wannan ya sa ba ta iya wasu addu'o'i ba .A halin yanzu da take tsaye ta yarda kuma ta aminta rayuwarta na cikin haɗari,tabbas ta san wannan magen ba normal ba ce muguwa ce cutar da ita za ta yi.

Ta na dab da ta kawo kusa da ita ta samu bakinta na furta “ la haula wala ƙuwata illa billah!!!” ƙiiii magen ta wani ci burki tana mai canza salon kuka zuwa na jarirai amma sam Sakeenatu ba ta yi gigin yin shiru da bakinta ba sai ma ƙaimi da ta fara wurin maimaita addu'ar.A gaban idonta magen ta soma mayar da idonta kamar na mutane kafin ta ruga a guje ta yi tsalle ɗaya ta haye katanga,daidai nan kuma aka maido wuta yaran unguwa suka hau ihun murna.Sakeenatu ta ja ajiyar zuciya tana mai yin hamdala ga Ubangiji,bakinta bai gushe ba yana ta furta lahaula wala ƙuwata illa billah a haka ta koma can ciki.Gas ɗin ta kashe saboda muguwar gajiya da ta saukar mata wacce ba ta san dalili ba,wayarta ta ɗauka Allah yayi sa'a babu abin da ya same ta abun mamaki kuma yanzu cajin wayar a cike yake saɓnin ɗazu da aka nuna mata ta kusa mutuwa.

Lambar Nafisa ta kira,tana ɗauka babu wani tsaya wa gaisuwa ta ce “ Nafi ki turo min karatun nan da kike saurare don Allah duk dare”

“Anty Sakeena lafiyar ki kuwa?”

“Ki turo min karatun dai don Allah ina son saurare ”

“Ok to bari na hauda data yanzu zan turo miki”

“Yawwa ina jira” ta faɗa tare da kashe kiran,ita ma datar ta kunna babu jimawa kuwa karatun ya shigo suratul Baƙara ce ta turo mata sai Yasin .Tamkar abun tsiya network ɗin ya ɗauke ɗif ko ɗaya babu wanda ya buɗe,juyin duniya ta yi amma sun ƙi buɗewa har wayar ta kashe ta kunna amma network ɗin ya ƙi yi.Cike da damuwa ta sake kiran wayar ƙanwarta,tana ɗauka sai ta rasa abin da za ta ce mata kawai ta fashe da kuka.Daga can ɓangaren Nafisa ta ce “ subahanallah! Anty Sakeena don Allah mike faruwa? Mike damun ki?”

Cikin muryar kuka take cewa “ Nafisa tsoro nake ji! A tsorace nake ji nake kamar ba ni ɗaya ba ce cikin gidan nan tamkar ina ….inaaa” ta kasa ida maganar saboda motsin da ta gani ana yi can cikin labule wanda ta tabbata kuma ba ɓera ne ba saboda girman halittar.Ihu ta fasa ganin ƙatuwar gafiya ta faɗo timmm da ƙasa,yayin da kuma wata ta biyu ita ma ta sake fitowa a guje ya kama waccan wacce ta faɗo a gaban idonta suka soma faɗa suna cizon junansu.Babu shiri Sakeenatu ta haye ɗaram kan bed ta na kuka,Nafisa na jin haka ta ziri hijabi ta fito ko Mamarsu ba ta sanar ma ba ta fito ta samu ɗan sahu.Allah yayi sa'a ba wani nisa ne sosai a tsakaninsu ba,da gudu ta shigo gidan tana ambaton sunan Allah daidai nan gafiyoyin suka yi ɓatan dabo hatta.

Nafisa ta je ta rungume yar uwarta wacce da ace tana da cutar asuma da tuni numfashinta ya fita,“ yi shiru don Allah ya isa yi min bayanin mike faruwa? Ina shi Abbas ɗin?”

“Yana asibiti wurin Mamuh,na dawo na dafa mata wake da shinkafa ne shi ne ake ta firgita ni” nan ta kwashe duk abin da ya faru ta shaida wa ƙanwarta.

Nafisa ta ja dogon numfashi bayan ta saurare ta,sannan ta ce “ wannan duk sharrin miyagu ne shi yasa a kullum ake son bawa ya keɓe wani lokaci don nemawa kansa kariyar ruhi da gangar jiki ba wai gyaran duniyarka ba kawai.Ni wallahi na fara zargin Mamuh ɗin nan,kina dai ganin yadda Ma'idah ta caka mata cokali da dukkan alamu ta hango abin da idanunmu basu gani.In ba masifa ba cikin daren nan za ki dafa mata wake kamar mayya,ke ƙila ma ita ce.Tashi mu je ki yi alwala ai zama bai gan ki ba tun da kin ji kin gani aure a inda ba a ƙaunar ki”

Da taimakon Nafisa ta yo alwala dama ita Nafisar kusan kowanne lokaci tana da alwala mace ce mai riƙo da addini ba ta da sake,hasali ma malamar makaranta ce a wata islamiyya.

Karatun Alkur'ani ta soma koya wa Sakeenatu kamar wata ɣar yarinya haka take biyawa inda ta yi kuskure kuma ta gyara mata.

“ Ki kasance kullum cikin tsarki bima'ana alwala saboda tana da muhimmanci sosai wurin bada kariya,ko sheɗanu suna shakkar mutum mai zama da alwala a koyaushe,ke ko period kike to ki yi abarki sannan ki riƙe azkhar na safe da maraice”

“Amma ai kin san ban iya su ba ko?”

“Ki koya mana anty Sakeena ,shi ilimi ai bai da ƙa'ida shekaru ko tsoho ɗan shekara ɗari zai iya shiga makaranta ballantana ke da ko talatin ba ki kai ba”

“ Ni rubutun larabcin ne ke bani wuya ”

“Zan nemo miki littafi mai fassarar Hausa ,sai na dinga koya miki yanzu bari na tura miki app ɗin Alkur'ani sai ki dinga saurare ”

Ta karɓi wayarta ta tura mata tare da saita mata komai ta kunna sautin ya soma tashi,ta ce “ to ni zan tafi gida ko Mama ban sanar ma ba”

“ Don Allah Nafisa kar ki tafi ki bar ni ki jira har Abbas ya dawo,bari na kira Mamar na shaida mata” haka suka yi kuwa,tun suna jiran Abbas har ƙarfe sha biyun dare bai zo ba a tare suka fito suka rufe gida da ko ina sannan suka je suka kwanta.

A can asibiti kuwa bayan fitar Sakeenatu,Gwaggo Rahamu ta yi wani kishingiɗa ga kujera kamar mai bacci nan kuwa ruhinta ne ta soma fitar wa daga gangar jikinta.Sawun Sakeenatu ta bi,hasali ma ta rige ta zuwa gidan duk abin da take yi

akan idonta hanyar farko da ta soma bi shi ne tafiya ta shiga tunanin mai kula da nepa na unguwar ya ɗauke wuta ba tare da shi kansa ya san dalili ba a cikin wannan duhun ne ta yi ta yi wa Sakeenatu mugunta.Da ta koro ta da addu'a shine ta biya wurin wasu miyagun ƙawayenta ta basu address suka je a siffar gafiya,su ma ba su bar gidan ba sai zuwan Nafisa.

Abbas na daga can gefe Mamuh na yi masa hira tana murmushi saboda duk abin da ke faruwa ita tana gani saɓanin shi Abbas ɗin.Bayyanar esprits biyun yasa yanayin shaƙar iskan ɗakin ta sauya saboda tsabar muguntar su, wannan karon hatta Abbas sai da ya ji wani iri.Har yanzu Gwoggo Rahamu ba ta farka daga baccin ƙaryar da take ba,cikin hirarsu ta yɜan duniyar ɓoye suke bata labarin yadda suka firgita Sakeenatu tana ta yin kuka.

“Na gode sosai ƙawayena,kar ku manta in kun gama yawon Maitar dare ku biyo ta nan mu sake komawa mu uku mu haɗa ƙarfi mu shayar da ita mamaki” baƙin ruhin Gwaggo Rahamu ya faɗa ,suka yi dariyar mugunta tare da ɗaukar mata alƙawari kafin su bar wurin.Cikin ƙwarewa ta dawo da ruhinta a gangar jikinta,ta dubi Abbas tana mai cewa “ bacci ya ɗauke ni duk yau ban rintsa ba,ina sauran waken ni ma na ci yunwa nake ji”

Shi Abbas sam ya manta da wani zancen wake saboda yadda Mamuh ke masa hira,sai yanzu ya tuna Sakeenatu ta je gida dafawa.Da ya duba agogon hannunsa ransa ne yayi mugun ɓaci,“ uwar tamu ai ba ta dafo ba tana can tana gantalin da ta saba,ah to dama su likitoci ba su da kamun kai tsakaninsu da abokan aikinsu suke neman juna in aka ce miki tana can asibiti wani ƙato ya taushe kar ki yi gardama” Mamuh ta faɗa ,yayin da Gwaggo ta karɓe “ i sosai ita ma wannan shegiyarta ta ai shugabansu ne ya ɗirka mata cikin ya bar yaronmu da wahala,wai Abbasi wai ya ƙaƙaba maka aurenta?”

Kasa cewa komai yayi,haushi goma da gomiya tara ya rasa da wane zai ji abin ka kuma da zuciyar namiji sai ya ji zargi ya ɗarsu a ransa.Da ya nuna zai je gida Mamuh ta hana shi tafiya ta hanyar amfani da tsafinta,haka suka dinga kwaso sharri iri-iri suna yaɓa ma Sakeenatu sosai kuma suke samun gurbi a zuciyarsa.Can waje ya koma ya kwanta kan wani banci yana ta tunanin rayuwa baya yadda neman aurensa ya kasance yadda sam Sakeenatu ba ta samu shaidar ƙwarai ba ga mutanen unguwa amma ya rumtse ido ya ce sai ita .

Ƙarfe biyu da rabi na dare ƙawayen Gwaggo Rahamu suka biyo mata,kafin su yi tsinke gidan Sakeenatu.Sai da suka shiga kitchen suka cinye kaf abincin da ta dafa sannan suka dawo falo suka fara shawarar abin da za su yi mata,suna dariyar mugunta suka tura ƙofar falon sai dai da zarar sun yi niyyar ɗora ƙafarsu a tile ɗin bedroom sai su ji tamkar cikin garwashin wuta ne suke ɗora su.Gwaggo Rahamu ta ƙanƙance ido tana kallon gefen Nafisa inda kusan kanta ta ɗora wayarta ne sautin karatun Alqur'ani na tashi a hankali wanda ba ma a jinsa sosai,kamar ta san suna nan kuwa sai ta kai hannu ta ƙara volume a tare suka saki wani ihu wanda sai da gidan ya girgiza a firgice Sakeenatu ta farka tana zarar ido

My book is only 500 via 6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank DM +22795045822

My book is only 500 via 6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,DM +22795045822

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

28/09/24

10

A wahalce Gwaggo Hajara ke bin bango don isa ɗakinta,fatar nan tata ta tsakaka duk ta yi wani taushi ta fara fitar da wani fanko.A yadda bango ke zuzar fatar cikinta ji take kamar ta yi ta ƙurma ihu sai dai ba dama sata lahira! Tana isa ɗakinta ta ɗauki siffa ta mutum nan ne fa ta yi tozali da yadda duk jikinta ya kumbura yayi ja kamar wacce aka soya,mai ta ɗauko ta shafe jikinta da shi tana matsar ƙwalla tare da jin tsanar Safeenatu na sake feso mata daga can ƙasan zuciyarta.

A fili ta furta “ sai na wulaƙanta rayuwarki,sai na saka kin tozarta a duniya,sai na shayar da ke gubar azaba wacce sai kin gwammaci mutuwa akan rayuwarki. Ke kan ki Habibah ba zan bar ki ba zan ɗora miki karatu da alamu har yanzu ba ki ji jiki ba shi yasa kike taimaka wa wata wurin ruguje plan ɗina” shiru ta yi jin an turo ƙofa.Daddy ne ya shigo da sallama a bakinsa,ba ta amsa ba sai ma saurin jawo hijabi da ta yi ta saka duk ta luluɓe jikinta.

“Ni kam Hajara lafiya kike? Kin ga yadda fuskarki ta yi suntum sai huci take kamar ƙullun wainar da ya ji yis?” Daddy ya faɗa yana ƙare mata kallo.Wani ƙululun baƙin ciki ne ya ƙara turnuƙe Hajara ta ce “ uwar waina ce….” ba ta ida kai aya ba ta ji yatsun Daddy biyar kan kuncinta,shaye da mamaki take kallonsa nan ta hango wani

baƙin tauraro tsakiyar goshinsa wanda ko shakka babu aikin Habiba ne ta tura masa shi.

Ba ta gama dawowa daga duniyar mamakin da ta je ba Daddy ya soma magana cikin masifa,“ wato abun naki ya fara zama iskanci,daga tambaya shine za ki zagin uwata saboda kin san yau za ta zo.To tsaya ki ji Hajara duk wata tijararki ki tattara ta ki ajiye wuri guda muddin Hajiya ta koma da baƙin cikinki gida to wallahi akan aurenki.Ki tashi ki ɗora girki tsabar lalaci muna da mai jego a gida amma kin zo kin shige ɗaki kin haye gado tare da saka hijabi kamar matar liman kowacce za ta yi aikin ƙwarai” yana gama faɗa ya nufi ƙofa,sai kuma ya juyo ya ce “ Murjanatu na kan hanya sai ki fara shirin tarben ta” kawai ya fice.

Gwaggo Habibah da ke zaune kan kujera a falo ta saki wani irin murmushin nasara,tun da uwarta ta haife ta yau ce ranar farko da ta juya taurarinta na baiwa ta yi aiki da su.Tun bayan da ta yi wa Twins wanka ta shirya su sannan ta bai wa uwarsu abin da za ta ci kawai ta fito falo ta zauna,Daddy na fitowa ta soma yi masa transfer ɗin tauraron ta hanyar kallonsa tsakiyar ido da farko har ya tambaye ta lafiya sai kuma yayi shiru jin sabon abu a tattare da shi.

Duk abin da yake faɗa wa Gwaggo Hajara sarai ta ji alamun aikinta yayi kyau,ta saki murmushin nasara tana mai cewa ‘ mijinki zai zame miki kumurci,da haka zan raunata muguwar zuciyarki’

“Habibah karɓi wannan ko kuna da buƙatar wani abu sai a ɗauka ciki” Daddy ya faɗa yana mai katse mata tunanin zuci.Ta karɓa tana mai cewa “ Yaya Ɗayyabu na ce bayan biki sai Safeenatu ta koma can gida wurin Hajiya ko?”

“Saboda me? Ba a nan za ki zauna ba?”

“Eh to ni ma da haka na ce ɗin amma sai na ga kamar anty Hajara ba ta son zamana tun da na zo idonta kamar za su faɗo tsabar yadda take jifana da mugun kallo”

Ran daɗi ya ɓace, yanayin fuskarsa ya canza tuni tauraron goshinsa ya ƙara yin baƙi ba tare da ya ce komai ba ya ƙara komawa ɗakin Gwaggo Hajara ita kuwa Habibah har da wata dariyar mugunta ta yi tare da tashi tana taka rawar murna.

Daddy na shiga ɗaki ya yi wa Hajara wankin babban bargo,ko ina ana jin muryarsa yadda yake yi mata masifa in ta je yin magana kuma sai ya gwaɓe bakin.Da wannan baƙin cikin ya fita ya bar ta,sai da ta sha kuka wiwi sannan ta fito ta ɗora girki babu jimawa kuwa sai ga Hajiya ta zo .A ladabce Gwoggo Hajara ta gaishe ta wanda sosai ita hajiyar ta yi mamaki don rabon da ta yi mata irin wannan ladabin tun ranar da Ɗayyabu ya kawo mata ita a matsayin matar da zai aura.Cikin sakin fuska ta amsa tare da cewa “ to barkarmu Safeena an sauka Allah raya kan sunnah,kin samu mai taya ki aiki da kuma miji” Hajiya ta faɗa tana murmushi a doli ita ma ta yi murmushin yaƙen a can ƙasar zuciyarta tana cewa ‘ an haifo mana masifa dai aljanar jaririya muguwa wacce ta yi gadon jaraba ’

“Zan shiga daga ciki” hajiyar ta faɗa tare da nufar ɗakin Safeenatu,cike da murna ta zauna tana kallon jariran Gwaggo Habibah ta ɗauki namijin ta bai wa Hajiya ta karɓa tana mai kai masa sumba haɗi da yi masa addu'a sannan ta miƙa shi.Ana ɗora mata macen jikin Hajiya ya ɗau kyarma kamar mazari,murya na ɗan rawa ta ce “ wane suna za a saka musu?”

“Basheer da Baseerat ” Habibah ta bata amsa tana murmushi tana kallon mahaifiyarta wacce kambun muguntar Gwaggo Hajara duk ya dabaibaye ta yanzu kuma ya fara barazanar tarwatsewa.

Hajiya ta ce “ karɓar ta” tana mai miƙo Baseerat don ruhinta ya soma yin rauni, Habibah ta ce “ Hajiya don Allah ki riƙe t...” ba ta kai ƙarshe ba Hajiya ta miƙe ta je ta shimfiɗe Baseerat a shimfiɗa,sai aka yi rashin sa'a safar da aka saka ma hannunta na hagu ta fita wani mugun haske ya fito ya shiga ƙirjin Hajiya saura ƙiris ta faɗi saboda yadda fitilun idonta suka rufe jiri kuma ya ɗebe ta.

Safeenatu dai na daga gefe tana kallon abubuwan ban al'ajabi , Gwaggo Habibah ce ta kamo Hajiya ta taimaka mata ta zauna.Kamar mai cutar huka haka numfashinta ke fita,ruwan sanyi ta nema da sauri aka bata ta shanye ƙatuwar gora.

“Habibah bani pilow bacci nake ji” cewar Hajiya ,da sauri ta ɗauko ta miƙa mata ita kuma ta kwanta babu jimawa bacci mai nauyi ya ɗauke ta .

Safeenatu ta ce “ Gwaggo Habibah ni fa na fara jin tsoron lamarin Baseerat kina dai ganin abin da ya faru, wannan ai ba zan fita da ita unguwa ba gudun ta jawo min masifa ace mayya ce ma”

Da mugun sauri Habibah ta katse ta “ kar na sake jin kin faɗi haka,saboda yɗarki ba mayya ce ba yɗar baiwa ce”

“To amma ai wasu ba za su ganin haka ba ko? Tun yanzu tana jaririya tana haka ina ga ta girma?”

Gwaggo Habibah ta yi murmushi ta ce “ Safeenatu bari dai na soma ɗan guntsira miki labaran duniyar ɓoye, kowane mutum da kike gani a duniyar nan yana da matriculation na sama.Ko kuma lambar sirri ta samaniya,da wannan ne in aka sayar da ruhin mutum daga lokacin matriculation ɗinsa ta saminiya sai ta canza.Duk wani ɗan Adam kasance yana da taurari iri-iri waɗanda suke taimakawa wurin gudanar da al'ammuran duniyarsa.Ya zama doli kowa ya kare taurarinsa ya basu tsaro,muddin ka yi sakaci da su kuma to wannan mutumin zai iya zama cikkaken maƙasudi wurin tallafawa masu sayar da taurari su ƙwace masa su.”

Safeenatu ta katse ta da cewa “ ta ya za a ƙwacewa mutum taurarinsa alhalin mallakinsa ne?”

Gwaggo Habibah ta bata amsa da “ ba ki taɓa jin labarin wata ma'aikaciyar saloon ba mai gyaran gashi? Ki nemi littafin Mrs Sadauki na MAITAR IDO a nan duk za ki samu cikakken labarin.Ki sani cewa matsafa don su kama ruhinka ma abu ne mai sauƙi,abin da suke buƙata shi ne kawai keɓaɓen abu na gaskiya ta atomatik da ke fitowa daga mutumin da ake son cutarwar,kamar gashinsa,sunansa,date ɗin ranar haihuwarsa,zufar jikinsa wato tufafin da ya saka ba a wanke ba,ko kuma jinin jikinsa.Daga lokacin da matsafi ya riƙe ɗaya daga cikin waɗannan abubuwan zai iya buɗe katinka na samaniya kuma ya karɓe ƙarfin ikonka wato power daga nan sai yayi abin da yake so”

A sanyayye Safeenatu ta ce “ duk Baseerat za ta iya yin wannan? Gaskiya ni dai ban so in kin san hanyar da za a toshe wannan baiwar tata ni dai ki taimaka min don ina ji a jikina muddin aka bar ta da ita a gaba za ta zame mana masifa”

Gwaggo Habibah ta yi mata wani irin kallo irin na ba ki da hankali kafin ta je ta ɗauki safar hannun ta saka ma jaririyar wacce ta buɗe ido sai kalle-kalle take kamar mai wayo,kafin kuma ta kafe idonta ga madubi Gwaggo Habibah ta yi kasaƙe tana

kallon Baseerat a sannu a hankali ta ga idon yarinyar na sauya kala har suka zama farare tasss babu ɗigon baƙi,wani abu kuma ya soma fita daga bakinta yana bin direction ɗin madubi.Habibah ta ja wani dogon numfashi don kuwa ta fahimci Baseerat za ta yi tafiya ne ko kuma yawon buɗa ido wanda dayawan mutane na yinsa ba tare da sun san mine ne ba.Sai ka ji tamkar jikinka ya zama gawa kana son tashi daga bacci amma ka kasa tamkar an danne ka da dutse,har kwatanta buɗe ido ake amma baka iyawa saboda ruhinka da yayi balaguro ya bar gangar jikinka a kwance.

#SAKEENATU

Gefen da Nafisa ke ta sharar bacci ta duba kafin ta ɗaga kanta sama tana kallon yadda rufin ɗakinta ke wani lomaƙawa tsabar yadda ake tafiya a guje.Kukan jaki da na kare ga kuma na mage duk a lokaci guda,gefe guda kuma wata siririyar murya take ji tana kiran sunanta.Idonta ya ciko da hawaye,fitsari take ji amma tsoro ya hana ta tashi.Nafisa ta soma tayar wa,ita kuwa dakyar ta buɗe ido ta ce “ mine ne ?”

“Fitsari nake ji” ta bata amsa kamar wata ƙaramar yarinya,cikin magagin bacci Nafisa ta ce “ ki je ki yi mana” sai ta koma baccinta.A hankali Sakeenatu ta zuro ƙafafunta ƙasa a tsorace ta shiga toilet ko Bismillah ba ta yi ba ballantana karanto addu'a,a tsorace ta je ta haye WC ɗin ta soma fitsari sai kuma jikin ya soma kyarma ganin ruwa na ta ɓulɓulowa ta ƙasan tile suna cika toilet ɗin ko kafin ta ƙyafta ido sun kawo mata a wuya ta yunƙura za ta tashi amma sai ta ji tamkar an saka super glue an manna ta a jikin WC ɗin ta ƙurma wani uban ihu wanda dama su mugayen shine suke jira ai kuwa suka tsaga rufin ɗakin ji kake ƙiiiiii kamar suna yaga zane.Idon Sakeenatu duk a waje take kallon yadda bindi mage,na kare da kuma idon wata baƙar mujiya a daidai wurin da suka tsaka.Cike da mugunta suka diro toilet ɗin wanda yayi daidai da tsinkewar numfashin Sakeenatu.....

My book is only 500 via 6042551755 Hassana Ibrahim Keystone bank DM +22795045822

□□□GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA□□□

□□*BACK TO VIRGIN KIT* *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin ku♀♀ga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame ☹

□□Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤

□□Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba

□□Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko

□□Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

29/09/24

11

GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA

BACK TO VIRGIN KIT *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin kuƤƤga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame ☹

□□Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤□□Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba□□Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko □□Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

Duk da Sakeenatu ta suma hakan bai sa mugayen nan sun ƙyale ta ba,haka suka ajiye mata cutar a jikinta kafin su bar ta nan yashe a toilet.Cike da murna suka koma asibiti suka dinga bai wa Mamuh labarin abin da ya faru,cike da mugunta ta ce “ gobe da safe da hannunta za ta dafo wake ta kawo min ,daga nan kuma zan datse alaƙar farin cikinsu ita da Abbas zan maye mata gurbinsa ” duk suka sa dariya suna ƙara tsara mata wani salon muguntar.

Washegari

Kiran sallar asuba ya tashe da Nafisa,ta sauka daga bed ta shiga toilet nan ta ci karo da Sakeenatu a yashe babu numfashi.Hankalinta a tashe ta cika bokiti da ruwa ta zuba mata,ta ja ajiyar zuciya kafin kuma ta soma kuka cikin firgici.Nafisa ta kamo ta tare da fiddo ta haɗi da tambayar ta,duk a tsorace take wannan yasa ta kasa yi wa ƙanwarta bayani.Ganin haka yasa ita kuma ta je ta yo alwala ta yi sallah,bayan

haka ne ta matsa wa Sakeenatu ta je ita ma ta yi sallar.Ko wanka ba su yi ba ta ce “ Nafisa tashi mu je gida wallahi tsoro nake ji” haka suka runguɗa suka je can gidan Mama wacce ke ta ƙoƙarin hura wuta domin ta ɗora ɗumame,tana ganinsu ta san ba ƙalau ba.Kamar wata ƴar yarinya haka ta je ta rungume mahaifiyarta tana wani sabon kukan,“ Subahanallahi! Nafisa mike faruwa?”

“Wallahi Mama ban sani ba ni ma na yi ta tambayar ta amma ta ƙi faɗa min,alamu dai sun nuna tsorata ta ake yi a can gidan nata” Nafisa ta bata amsa.

Mama ta ce “ to Allah ya sawwaƙa,ku wuce ciki bari na kira malam na shaida masa ”

Can cikin mitsitsin ɗakinsu suka shiga,Ma'idah na kwance sai bacci take ba ta farka ba.Sakeenatu ta ɗauki abarta ta rungume ƙam kamar an ce za a raba su,mugun mafarkin da ta yi kan Ma'idar ya dawo mata a kai.Ta lumshe ido ruwan hawaye na kwaranya a kumatunta,ta yi tunanin kakarta ta yanke saƙa,ba ta taɓa tunanin za ta sake yin ƙunci a rayuwa bayan wanda ta yi a baya ba tun lokacin da Abbas ya shigo rayuwarta komai ya dawo mata normal ashe da sauran kallo a sama.Tsohuwar shuɗaɗiyar rayuwarta ce kwanyarta ta soma yi mata tariya,cikakken sunanta shi ne Sakeenatu Abubakar,ƴar gwagwarmayar rayuwa mai zuciya cike da burin zama wata aba a duniya.Karatun boko shi ne abokin da ta riƙa sannan kuma tubali don gina rayuwa mai inganci,sai dai ƴan magana na cewa rashin sanin ya fi dare duhu.Sakeenatu ba ta taɓa sanin cewa ba sanadin boko ne za ta zubar da mutuncinta ba,zuwanta jami'a shi ya ƙara buɗe mata ido sosai ta waye ta zama ƴar gayu,ƙwazonta a wurin karatu shi yasa ta ciri tuta a wurin malaman makaranta kusan duk maganarta suke suna yabon baiwar da Allah yayi mata banda malam Agali wanda tun ranar da ya ɗora idonsa kanta yake jin mugun sha'awarta saboda ta haɗu ta kowanne fanni.A wata rana Laraba ce wacce ta kasance ranar farko da ya fara ɗana mata tarko da kuɗi,“ki hau taxi” ya faɗa cikin taushin murya a gaban ɗalibai ba tare da ya ɓoye ba kuma ya sakar mata murmushin nan nasa wanda yake haukata ƴan matan makaranta da na wajensu .Ba za ta cewa tana sonsa ba,amma ita ma tana cikin waɗanda yake burge su saboda yadda yake da kyau kamar Balarabe ga baƙar sumar kansa ko wata macen ya fi sannan ɗan gayu ne kullum cikin shiri mai kyau yake.Ƴan matan ajin suka hau yin shewa suna taɓi tare da cewa yau dai an samu wacce ta sace zuciyar Dr Agali,da ido ta bisa kawai lokacin da yake fita daga ajin yayin da ɗalibai duk suka dawo kusa da ita kowacce na tofa albarkacin bakinta.Sakeenatu ta ji wani irin girman kai ya zo mata tare da alfaharin ita ce ta ciri tuta,cours ɗin da aka yi musu na gaba sam ba ta fahimci komai ba saboda tunanin malam Dr Agali.Ba ta buɗe ƴar enveloppe ɗin kuɗin ba sai da ta je gida, kuɗi ne ƴan jika-jika sabbi da su har guda goma.Ta kai su kusan

hancinta ta shaƙi ƙamshin turarensa,tuni jikinta ya mutu murus ta na shirin saka kuɗin a jaka ne ta lura ɗaya daga cikin takardun kuɗin an rubuta lamba a jiki.Kamar wacce ake tsikara ta ɗauki wayarta ta loda lambar sannan cike da waswasi ta tura masa saƙo babu jimawa ya kira ta,kamar wani mutumin ƙwarai har da yi mata sallama ta amsa tare da ce masa “ fatan ka je gida lafiya?”

Cikin muryar nan tasa ta buzaye waɗanda ba su ida iya Hausa ba ya amsa mata da “ a'a ina wata asibiti an kira ni in tiyata”

Ta saki murmushi mai sauti ta ce “ ina son ganin ranar da za a ce Sakeenatu na yin tiyata”

“Lokacin zai zo ke dai ki ci gaba da dagewa wurin yin karatu,na ji malamai sai yabon ki suke ashe ba a cours ɗina ne ba kawai kika ƙware” nan ma murmushi mai sautin ta yi kafin ta ce “ burina shine zama babbar likita wacce duk duniya za ta yi alfahari da ita,ana dinga nuno ni a TV”

“Kina iya barin Nijar Keenat?” Dr Agali ya tambaye ta,kai tsaye ta basa amsa da “ eh sosai sai in gwamnati bai ɗauki nauyin karatun nawa ba”

“To ki fara shiri in sha Allah ni nan zan sa burinki ya cika”

“Keee Sakeenatu keee!” Mama ta faɗa tana mai kamata dundu wanda shi ya katse mata tunanin shuɗaɗiyar rayuwarta,da sauri ta dawo hayyacinta tana mai kallon Mama wacce ta janye Ma'idah da sauri tana mai ci gaba da cewa “ kawai ki kama yarinya ki riƙe gam tana kuka da ranta amma kin ƙi sakin ta”

Sam ita ba ta san riƙon da ta yi wa Ma'idar ya cutar da ita ba,cike da takaici da zugin da zuciyarta take yi ta tashi ta fita ta cika bokiti da ruwan ta shiga banɗaki.Wanka take son yi amma tunanin Dr Agali sai ƙara kawowa kwanyarta farmaki yake,abin da ya faɗo mata a rai a yanzu kuma shi ne ranar da ya kira ta ya shaida mata Visa ɗinta ta fito ta zo ta karɓa bai jin daɗin jikinsa.Ba tare da wani tunani ba ta je gidan nasa kamar yadda yayi mata kwatance,duk a tunaninta yana da mata amma sai da suka shiga ciki ne ta ga shi ya bata ruwa sannan ya kawo mata lemu wanda ya zubar da shi a jikinta da gayya har tufafinta suka ɓace.Ta wani rumtse ido don takaicin ganin video yadda Dr Agali ya ɓalle maɓallan rigarta ya cire ta ya bar ta daga ita sai bra ya je wanke mata ita duk ta yi tunanin ƙauna ce ta kawo haka sai bayan ya dawo ne ya soma yi mata wasu zafafan romance.“ Ni fa dama ba zan yi miki komai ba, wannan ɗin ma ban san ya aka yi ya faru ba ki yi haƙuri ba zan sake ba sai bayan aure” Dr Agali ya faɗa lokacin da ta sakar masa kuka.

“Anty Sakeena don Allah ki aje tunanin nan gefe ki yi wanka ki fito ga malam nan ya zo” Nafisa ta faɗa daga bakin ƙofa.Sai a lokacin Sakeenatu ta fara wankan ,bayan ta fito ta je ta gaishe da malam wanda ya kasance ƙanen Mama ne.Cikin garwashin wuta ya zuba yaƴan habbatu sauda hayaƙi ya turniƙe ɗakin,idon Sakeenatu duk suka fito waje ta soma tari kamar ranta zai fita shi kuwa karatu ya soma nan lamarin ya ƙara yin gaba don tuni ta soma yin kuka .Tsawon lokaci kafin ya bar ta haka nan,magani ya bada wanda za ta dinga shafawa da hayaƙe jikinta da kuma gidan.Bayan tafiyarsa ne ta samu ta ci abinci,wunin ranar dai Mama haka ta ƙare shi wurin yi mata nasiha dab da magrib Nafisa ta yi mata rakiya zuwa gidanta.A tare suka yi gyaran gidan da girki kafin ta yi wanka ta shafa man da malam ya bata ta kuma yi turare.

A can asibiti kuwa tun safe da Abbas ya bar su bai koma ba,kuɗi kawai ya bar musu hakan bai yi wa Mamuh daɗi ba.Ana yin sallar magrib ba tare da likita ya sallame ta ba Gwaggo Rahamu ta haɗa tarkacensu suka fito a ɓoye.A bakin hanya suka samu adaidaita wacce za ta kawo su gida ,suna tafe suna hira “ ai tun da kika ga bai dawo ba to tabbas babu makawa da ya koma gida karuwanci ta yi masa kin san halin namiji kan mace sakarai yake zama” Gwaggo Rahamu ta faɗa .

Mamuh ta tsuke bakin nan nata ta kasa cewa komai saboda baƙin cikin da ke addabar baƙin ruhinta,gani take yi ma tamkar adaidaitar ba ta gudu.

Suna isa gida tun a bakin ƙofa suka canza kalar idonsu daga na mutum zuwa na mugunta,sai aka yi rashin sa'a Nafisa na tsakiyar falo tana hayaƙa hantiti da tazargade .A tare suka shigo,a tare kuma suka saki ihun azaba suna masu faɗuwa ƙasa suna yin wani irin huci a gaban idon Nafisa suka rikiɗe suka zama jibga-jibgan macizai kowa yace shi ba ma matsoraci ne ba to bai ga abin tsoron ba .Da wani mugun sauri Nafisa ta mangal ɗin hannunta mai cike da garwashi,da azama ta nufi hanyar ɗakin Sakeenatu sai dai kafin ta isa Gwaggo Rahamu ta yi wani uban tsalle ta naɗe handle ɗin ƙofar da bindinta tana mai buɗe ƙaton bakin,Nafisa na shirin komawa baya ta ji ana bin ƙafafunta wanda kuma tunaninta da ruhinta tuni sun shaida macijiya Mamuh ce.....

My book is only 500 via 6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank DM +22795045822

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam empire takawo muku babbar gara basa

Duka akan 5500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 5500 na 1. Kaza rabi 2. Ciccibi 3. Gumba 2 4. Gari 1 5. Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k 2. Matsin maganin infection 300 3. Dripping pills 1pcs 300 4. Matsin dare daya wanka goma 400 Total total gift 2k 😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 5500 dinki ki mallaki kayan da ko 10k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam empire

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1000 kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

ZAWARCI

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

01/10/24

Last free page 13-14

Wani irin mugun ƙishi ne ya wanzu a maƙoshin Gwaggo Hajara saboda Maitar shan jini ta motsa.Dakyar ta iya sakin Murjanatu ta koma gefe tana kallon ta,sai kuma ta kasa haƙuri sai da ta shafi ƙaton cikin da mugun sauri Murjanatu ta kai hannunta ita ma kan cikin saboda mugun juyawa da yayi.

“Washhh! ” ta furta a wahalce kafin kuma ta dafe ƙugu jin kamar ta soma naƙuda ne,“ sannu Murjanatu ki zauna mana” Gwaggo Hajara ta faɗa tana haɗiyar yawu don tsaf take kallon jaririn wanda sai juyi yake a ciki.

Kan gwiwanta ta zube tana mai ci gaba da yin gumurzu,tuni ita Hajara ta san da yau in ba wani iko na Allah ba sai yaɗarta ta haihu.Da sauri ta shiga cikin ɗaki ta fito kafin ta ce “tashi mu je asibiti” a wahalce ta ɗago ta dubi mahaifiyarta ta ce “ wallahi Mama ban iya tashi”

“To haka za ki zauna? Sai nake ganin kamar haihuwar ce”

Ba ta rufe bakinta ba Murjanatu ta fasa wani uban ihu wanda ya jawo hankalin Gwaggo Habibah da saurinta kuwa ta fito tana tambayar lafiya sai kuma ta yi tozali da Murjanatu a cikin mawuyacin hali.Da taimakonta suka samu suka Murjanatu ta miƙe tsaye,Munir ne ya je ya nemo musu mai ɗan sahu.Kayan robar Safeenatu aka yi aro aka kai ta asibiti,sai uban ihu take tana kururuwa tana faɗin za ta mutu.

Daga nan waje kuma inda mutane ke zauna wa,ran Gwoggo Habibah ya ɓace sosai tun tana ɓoyen abin har ta kasa ta ce “ yanzu ke hatta yaɗarki ba ki bari ba? Wannan mugun hali naki bai yi ba.Wato babu babban makunyaci a duniya irin maye,tun da har jininsa bai bari ba”

Gwaggo Hajara ta ƙanƙance idonta da suka kaɗa suka yi ja kafin ta ce “ ina ruwanki da ni ? Ke kika haifa min Murjanatun? Kanwar uwa ko ta uba?”

Gwaggo Habibah ta miƙe ta ce “ kina fa da gaskiya,amma ki yi haƙuri farar zuciyata ta taimakon jama'a tasa na zo na tsoma hannnuna inda ba a gayyace ni ba.Tabbas Murjanatu yaɗarki ce in kina so ki haɗa har da ita duk ki cinye” tana gama faɗa ta yi tafiyarta ta bar Hajara a zaune babu jimawa kuwa Murjanatu ta haifo ɗanta namiji.

Ɗakin hutu aka kai ta,murya na ɗan rawa Gwaggo Hajara ta ce “ yo ina jaririn?”

“Nurse na duba shi ne don tabbatar da lafiyarsa” ta bata amsa.

Tsawon lokaci kafin a kawo shi jikinta har rawa yake ta karɓe shi,nurse ta ce “ a basa abincinsa ya sha da alamu yunwa yake ji”

“Toh! Toh” cewar Hajara tana wani kafe yaron da idon mugunta,ya soma kuka Murjanatu ta tashi zaune babu kunya ta ce “ Mama kawo shi” ba don ta so ba ta miƙa mata shi ta koma gefe cike da ƙwarewa ta damƙe kurwar yaron .Da ta fita wankin kayan da suka ɓace ta samu wuri ta haƙa rame ta binne ,duk da zuciyarta babu dadi amma ji take ya zama doli ta cinye jikanta na farko ko yawunta sun koma.

Daren nan dai ba su yi bacci ba jariri nata yin kuka hatta likitocin sai da suka shigo suka duba shi,sai asubahi ya rumtsa wuraren ƙarfe tara na safe aka basu takardar sallama bayan sun biya.Hajara ce ta je ta taro ɗan sahu,bayan ta saka kayansu Murjanatu ta shiga sannan ita ma ta shige tana kallon wurin da ta binne kurwar jariri can ƙasan zuciyarta ta furta ‘ zuwa dare zan zo na tone’ haka suka isa gida.

Ta kuwa ci sa'a Daddy bai fita ba,Murjanatu ta gaishe shi ya amsa tare da yi mata barka kafin ya maida dubansa ga Hajara wacce sai raba ido take kana gani ka san ba ta da gaskiya.

“ Hakan da kika yi daidai ne? Don dai ba ni ne na haifi Murjanatu ba shine kika koro Habibah daga asibiti? ”

“Ka yi haƙuri ba koro ta na yi ba,na dai ce ta dawo gida tun da ba za a barin mai jego ita ɗaya ba a gida”

“Mi yasa ba ki kira ni kin shaida min zancen haihuwar ba? Ban cancanta ba ne ko me?”

“Ka yi haƙuri Daddyn yara,yanzu dai ka kira shi mijin nata ka shaida masa zancen haihuwar ”

Bai amsa mata ba ya fice,sai a lokacin Habibah ta fito idonta kan jaririn wanda ke baccin wahala.Cike da tausayinsa ta ƙarasa ta ce “ barka Murjanatu Allah raya shi kan sunnah”

“Amen na gode” ta amsa tare da miƙa mata jaririn,Habibah ta karɓe shi tana mai zaunawa kan kujera ta shafi sumar gashinsa tana kallonsa da kyau ta tabbata kurwarsa na gidan yari ba a cinye ba sai dai ba ta san a ina aka binne ta ba.Haka ta gaji da binciken ta miƙa shi ga uwarsa ta miƙe suna ɣar kallon-kallon ita da Hajara wacce idon nan nata suke wiƙi-wiƙi na maras gaskiya.

A sanyayye Habibah ta koma ɗakin Safeenatu,“ ya dai Gwaggo Habibah lafiya na gan ki duk kin yi wani iri?” Feenat ta tambaya.

“ Babu komai Safeena,bacci Baseerat take?”

“Eh ba ta jima da rufe idon ba”

“Mu gan ta” Habibah ta faɗa tare da yin zama, Safeenatu ta ɗora mata jaririyar kan cinya.Hannunta mai safa ta kamo ta cire sannan ta soma shafa shi ,zuciya cike da rauni ta soma yin magana “ ki tausaya ki ceto jaririn da bai san komai ba,ki sani shi ma tamkar Basheer yake mai rauni ne.In kuma har yanzu kuna cikin fushi ne shi yasa kuka hana ta ɗauki mataki ku yi haƙuri,amma dai a duba lamarin” tana gama

faɗa Baseerat ta buɗe idonta taram cikin na Habibah,ita kuwa ta shiga kallon abubuwan da suka faru bayan ta bar asibitin a cikin ƙwayar idon jaririyar ta ga komai har inda Hajara ta binne kurwar.Tana gama gani Baseerat ta maida idonta ta rufe, Safeenatu dai na gefe a yanzu ma kallonsu take ba tare da ta ce komai ba.

Habibah ta ja ajiyar zuciya ta sakar mata murmushi ita kuwa kai ta ɗauke,tana mai jawo wayarta ta kunna data so take ta yi bincike don gano shin abubuwan da suke faruwa zai iya kasancewa ko kuwa yƴarta ce kawai ke da shi.

Tunanin ta watsar ta shiga WhatsApp ta fara duba saƙonnin mutane masu yi mata barka kafin kwatsam ta ganta cikin wani group.A hankali ta soma biyayar abubuwan da ke faruwa sai ta ga amsoshin tambayoyinta kan wani posting.

```“M” CIKIN TAFIN HANNU,MAUME HAND/PAUME DE MAIN

Chiromancy wata daɗaɗiyar hanya ce ta hango makomar mutum da kuma fassarar halayyar mutum daga dalilin layukan hannu. Wani lokaci waɗannan layuka na iya samar da lambobi da haruffa. Ɗaya daga cikin waɗannan wasiƙun na iya zama wasiƙar M, ma'anar wacce mystics da dama suka yi nazari a kanta.

Kamar yadda mutane da yawa suka yi imani, layukan da ke kan tafin hannunmu suna bayyana halinmu da ƙaddararmu. La lettre M est attribuée à des personnes vraiment spéciales(The letter M is assigned to truly special people). An ba su kyakkyawar fahimta kuma suna wakiltar abokan haɗin gwiwa akan dukkan wasu kasuwanci.
```

Idan mutanen da kake so suna da wasiƙa ta musamman M a cikin tafin hannu ya kamata ka sani cewa ba za ka iya raina masa hankali ba kuma ta wata hanyar ba za ka iya yin ƙarya ko yaudarar wannan mutumin ba. Kasancewar shi mai dubara da hankali da tsantsar lura sosai, mutamin da ke da harafin M a tafin hannu cikin sauƙi zai fahimci cewa ana yi masa ƙarya ne ko yaudara.

``Matan da suke da harafin M a tafin hannunsu suna da zurfin tunani fiye da maza, har ma da waɗanda suke da wannan wasiƙar. Ana yi musu baiwa da ikon sarrafawa da shawo kan duk wani cikas a rayuwa, kuma sun san yadda ake amfani da albarkatu da damar da ake da su.

Harafin "M" a kan tafin hannu ma na iya nufin:

• Ƙwarewar shugabanci

• Iko wato power/pouvoir```

Zuciyar Safeenatu banda bugawa babu abin da take yi har sai da ta ajiye wayar ta je ta ɗauki ruwa masu sanyi ta sha .Ta dawo ta zauna don ƙara duba saƙon sai dai hatta shi kansa group ɗin ya ɓata a wayarta babu shi sam .Kamar mahaukaciya haka ta miƙe ta je ta yi wani gurwanau a gaban net ɗin da aka saka Baseerat,ta zuge zip ɗin ta kalli ƙofar toilet inda motsin ruwa ke ta zuba da alamu Habibah wanka ta shiga ba tare da ita ta san yaushe ta shiga ba .

Murya a ɗan kasalance ta ce “ Baseerat ni ce mahaifiyarki,ni na haife ki.Duk wani wanda bai son ganin kin cutu to tabbas sai dai ya biyo bayana,don haka kar ki ga kamar ban son ki a'a wallahi zuciyata raunk ne da ita.Magana nake son yi miki game da abin da na gani cikin wayata,shin kina da masaniya? In dai tabbas ke yar baiwa ce kamar yadda saƙon nan ya bayyana to ki buɗe idonki ki kalle ni” ko rufe baki ba ta yi ba kuwa Baseerat ta buɗe idon sai da Safeenatu ta dafe ƙirji saboda tsoro.

“Mine ne wai?” daga bayanta Habibah ta tambaya ,zip ɗin net ɗin ta mayar tana mai cewa “ babu komai Gwaggo Habibah,na yarda na aminta da lamarin nan gaske

ne ana samun yɑ̈n baiwa to Allah bata ikon yin amfani da ita ta hanyar ƙwarai” ruwan sama ne suka fara sauka a daidai lokacin da Safeenatu ta rufe bakinta.

Gwaggo Habibah ta yi wani ɗan ihun murna tare da rungume Safeenatu ta ce “ kin ga ko? Yɑ̈rki ta musamman ce ancestor/ ancêtre suna tare da ita”

A wannan daren cike da zullumi da tunani Safeenatu ta yi shi,da ta samu bacci ya ɗauke ta mafarkai ta yi barkatai akan goben Baseerat.

Washegari tun da safe kukan jaririn Murjanatu ya cika gidan kamar wanda ake cirewa rai.

“Jaririn can ba dai kuka ba” Safeenatu ta faɗa .

Habibah ta ja baki ta yi shiru tana tuna jiya irin gumurzun da suka yi ita da Hajara akan kurwar yaron.Dakyar ta yi nasara ta tone ta tare da saka Hajara don doli ta mayar masa abarsa wacce tuni ita kanta kurwar ta yi rauni,kukan da yake yi kuma saboda ciwon jiki ne.

★A kwana a tashi babu wuya wurin Allah yau ne sunan Twins ɗin Safeenatu waɗanda dangin Bashir suka yi bajinta sosai wurin yankan manyan raguna uku biyu na BASHEER ɗaya kuma na BASEERAT .A wannan rana ta farin ciki Safeenatu ta rakuɓe wuri guda tana ta yin kuka,ga shi dai ta sha ƙunshi da kitso ga kuma gizner ta gani ta faɗa amma rashin masoyinta ya dawo mata daram musamman yadda ake ta faɗar an yi masa madadi da kuma addu'o'in da mutane ke yi.

Da wannan damar Gwaggo Hajara ta shirya mugunta wacce take kambacin fansar da ta yi niyyar ɗauka akan Habibah da hana ta rawar gaban hantsi.Sai da ta bari duk hankalin mutane ya ɗauku,sannan jarirai duk an fitar da su can tsakar gida saboda zafin da ɗakin ya ɗauka sannan ta nufi ɗakin Safeenatu.Duk da akwai mutane hakan bai hana ta gwada sa'arta ba,“ ungo Safeena Gwaggonki Habibah ta ce ki ci abincin nan kafin ta zo ta yi miki ta ƙarfi tun da dai ke ba ki jin magana kina jego amma kin ƙi cin abinci ” Hajara ta faɗa tare da miƙa mata plate mai cike da

nama ya sha jar miya,ta karɓa tana turo baki tare da soma ci don ita duk a tunaninta gaske dai Habibar ta bata.Cike da murna Hajara ta bar ɗakin ta je ta kasa kunne tana jiran sakamako.

Da rana mutanen arziki sun cika gida, Safeenatu ta shiga Toilet ta yi wanka da canza kaya daga shadda zuwa less.Kamar wacce aka yi wa wankin ido haka take ganin yan biki tsirara tamkar babu kaya jikinsu,zuciyarta ta yi wani mugun bugawa ganin ta soma ganin hanjin cikin mutane yayin da kuma take jin wani abu a bakinta da ba ta san mine ne ba.A daidai nan free page ya ida,duk mai son ci gaba za ta biya kuɗi domin shiga PAID GROUP.

FREE PAGE/ PAGE NA KYAUTA YA IDA

Detail 500 via 6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank DM +22795045822

In kin san ba ki shirya saya ba kar ki min magana,ga detail nan kawai ki tura kuɗin ki turo min evidence ta WhatsApp.

NB: daga lokacin da ya kammala ya zama complete zai koma 1000.

01 octoba 2024

#CHAMSIYA LAOUALI RABO

MRS SADAUKI

```MRS SADAUKI✍```
```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

03/10/24

□□□GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA□□□

□□*BACK TO VIRGIN KIT* *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin kuƤƤga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame 😢

Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤

Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba

Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko

Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

Tashin hankali wanda ba a saka masa rana,jikin Safeetu na yin rawa ta nufi wata ƙawarta wacce take fara sol da ita jikinta ɓulɓul da shi.Ba ta san ta yaya ba ko kuwa ya aka yi ba ta ji bakinta na son sarrafa yadda ake damƙe kurwa,sai kuma aka yi rashin sa'a Gwaggo Habibah ta shigo hannunta riƙe da baby Baseerat na canyara kuka.Bugun numfashi Habibah sai da ya kusan tsayawa lokacin da ta yi tozali da idon Safeenatu ga ƙanƙarar maita nan tsakiyar maƙoshinta ko cikinta ba ta shiga ba kamar yadda tsarin yake sai ranar da ka sha jinin farko sannan za ta faɗa ciki ta kuma game gangar jiki .

“Don Allah duk kowa ya fita falo ina son yin magana da mai jego” Habibah ta faɗa cikin wata irin murya ,duk kuwa suka fice sanin ita ɗin ƙanwar mahaifin mai jegon ce.Wata irin shaƙa ta kai wa wuyan Safeenatu,duk idonta suka fito waje yayin da harshenta ya zazzalo waje koren yawu na ta zuba dalalaaa.

Tsabar azaba Safeenatu ta zube kan gwiwanta,sai a lokacin Habibah ta sake ta tare da ɗauko Baseerat ta cire safar hannunta ta kamo shi ta ɗora bisa goshin Safeenatu nan ta soma kakarin amai kafin ta tashi da gudu ta shiga toilet,duk abin da ta ci sai

da ta maido shi.Habibah na gefe tana kallon ta har sai da ta ga ƙanƙarar Maitar ta faɗo hankalinta ya kwanta.Ta ja wata irin ajiyar zuciya kafin ta kamo Feenat wacce ta galabaita,wani wankan ta sake yi ta zo ta shirya cikin doguwar riga ta atamfa.

“Ina Baseerat?” Safeena ta tambaya tana kallon daidai inda aka shimfiɗe ta babu komai sai zanenta ,ko kafin Habibah ta bata amsa sai kuma ga jaririyar ta dawo kamar ƙyaftawar ido.

“Hajara ta baki abinci ko?” Habibah ta tambaya ,ita kuwa ta gyaɗa kai.Ta ci gaba da cewa “ yaushe kika fara yarda da ita har haka? Ko kin san da cewa ba don na shigo ba da ke ma yanzu kin bi jerin Mayu ? Daga yau kar na sake ji ko ganin kin ci abin hannunta ko yunwa za ta kashe ki”

Idon Safeenatu taf da hawaye take tuna irin tashin hankalin da ta gani yanzu ,hanjin mutane hanjin mutane terere kamar a Film ɗin zombies.Ta ce “ in sha Allah Gwaggo Habibah na fahimta sosai,ina shi Basheer ɗin ? Gwara a kawo shi nan kar ta je ta kame kurwarsa”

“Bari na je na karɓo shi” cewar Habibah tana mai ficewa.

Safeenatu kuwa ta zauna ta ɗauki babynta tana jin wata sabuwar ƙaunar Baseerat na ratsa ɓargonta.Ta kai baki ta sumbaci goshinta,abun mamaki sai ta ga yarinyar na yi mata murmushi.

Babu jimawa yɗan bikin suka ƙara dawowa ciki musamman ƙawayenta duk sai tambayar Sakeenatu suke ita ma mai jegon tana mamakin abin da ya hana ta zuwa tun ranar da ta zo ta yi barka ko waya ba su sake yi ba.

Safeenatu na rungume da yɗayɗanta ta ji wata irin kururuwa a can tsakar gida,hankali tashe duk suka fito sai ta yi turus tana kallon wata ƙatuwar mace yadda ta haye Gwaggo Hajara tana jibgar shegiya babu kuma mai yin magana ballantana a janye ta da dukkan alamu ma lamarin ya basu citta.

“Za ki saki kurwar mutane ko kuwa sai na sheƙa ki lahira? Muguwa,munafuka, azzaluma yau sai na kashe ki na yi ajalin baƙin ruhinki mai cike da mugunta” shine abin da matar ke faɗa tana bugun Gwaggo Hajara ta ko ina ita kuwa sai ƙoƙarin kare fuskarta take,wuyanta matar ta tuƙe sai ga Hajara ta soma aman wasu ƙwari sun fi goma baƙaƙe ƙirin da su suna tashi sama duk suka dira kan ɗaiɗaikun mutanen da ke wurin tare da ɓacewa wanda hakan na nuni ne Gwaggo Hajara ta damƙe kurwar mutane dayawa da suke wurin,cikin rashin sa'a ne yasa ta fito don ƙara yin farauta da kuma ganin halin da Safeenatu ke ciki sai kuma matar nan ta shigo wacce manyan iskokai ne a kanta.

Sai a lokacin ta tashi daga kan Hajara ,ita kuwa ta miƙe tana zarar idonta da suke jawur da su.Duk yɗan biki ai sai suka fara tafiya,yayin da ita kuma matar ke cewa “ duk ku kwantar da hankalinku babu wanda za ta cutar muddin ina wurin nan da ikon Allah,saboda Allah wannan wane irin cin zalun ne? Muguwar mata duk ki kame kurwar al'umma ki haɗiye?”

Habibah ta ce “ har da fa mai jego ta damƙe kai maye bai ji daƈi ba” sai ta harari Hajara wacce gwiwanta suka yi sanyin da ta kasa taka su.

Murjanatu na daga can jikin ƙofa tana goge hawaye don a gaban idonta duk komai ya faru,kunyar duniya ce duk ta rufe ta babban takaicinta shi ne da Hajara ta kasance uwarta.Da sauri ta koma ciki ta soma haƈa kayan jikinta,don kuwa ba za ta zauna ta kame mata jariri ba ,duk Flashback ƈin abin da ya faru ne ya soma dawo mata.Tana cikin haƈa kaya Hajara ta shigo,“ mine ne kike yi?” Hajara ta tambaya tana tsure ta da ido .

A firgice ta juyo tana kallon mahaifiyarta ,murya na ƈan rawa ta ce “ babu komai”

“Su kuma trollyn nan fa ina za ki kai su?” Hajara ta tambaya cike da masifa tana ƙanƙance ido.

Murjanatu ta fashe da kuka ta ce “ don Allah Mama kar ki cutar da mu ki yi haƙuri”

“Wato Murjanatu ke ma kin yarda da ƙazafin da aka yi min ko? Sharrin Habibah ne fa duk ita ta tsara wannan saboda kawai na bar gidan ƈan uwanta.Kina dai ganin yadda suka haƈa baki da aminiyarta suka tozarta ni a gaban jama'a,shine ke ma za ki goyi bayansu ki yi tafiyar ki? Kenan kin yarda? To babu matsala za ki iya tafiya tun da ana canza uwa uwa” Hajara na gama faƈa ta shige Toilet ta kunna pampo ruwa suka soma dukan jikinta. Wani irin maƙoƙon baƙin ciki ne take ji yana yi mata yawo a maƙoshi,ta sani sarai asirinta ya gama tonuwa wanda kuma hakan barazana ce da tsinkewar igiyar aurenta.Tsawon lokaci ta ƈauka kafin ta cire kayanta ta soma wankan sabulu,bayan ta gama ne ta fito gefen da Murjanatu ke zaune ta rabka uban tagumi ta duba wani irin takaicinta take ji ba don tana ƙaunarta sosai ba da yau babu abin da zai hana ta yin romon kurwar Murjanatu ta cinye.

Cikin wasu kaya na riga da zane na atamfa Hajara ta shirya tsaf,har da fesa turare sannan ta ƈauki hijabi kamar wata Malama ta fice.Tafiyar ƙasa sosai ta yi kafin ta

samu ɗan sahu ta shaida masa inda zai kai ta,tafiya ce mai shegen tsayi kafin su isa,ta biya shi kuɗinsa kafin ta gangara can cikin wasu manyan dutsuna.

Daga bayanta ta ji an ce “ Hajo? Ke ce da uwar ranar nan?”

Ta juyo suka haɗa ido ita da wani farin tsoho wanda tsabar tsufa fatarsa har ta tamuƙe,ta ɗan murmusa ta ce “ Eh Baba ni ce”

Tsakiyar idonta ya kalla da kyau kafin ya ce “ to zo mu zauna na ji ta bakinki”

Haka tsakiyar rana kamar abun tsiya suka zauna,Hajara ta koro masa irin tozarcin da aka yi mata a yau a bainar nasi.

“Yanzu me kike so a yi kenan ?”

“So nake na sani in akwai wata hanya da zan bi na adana Kambun Maitata na ajiye ta zuwa wani lokaci,don kuwa ina da tabbacin Habibah ba za ta yi shiru ba dole da abin da ta tsara nan gaba”

Baba ya dube ta da kyau ya ce “ akwai sai dai ki sani in kin cire ta wa'adin mayar da ita bai wuce kwana uku in kika saɓa doka kuma duk abin da ya biyo baya ki sani ke kika saye shi da hannunki ”

Hajara ta washe baki ta ce “ ni ai ba ma zan iya yin haƙurin kwana ukun ba,kawai dai yanzu ka taimaka min ka nuna min yadda zan cire Maitar daga jikina ”

Cike da ƙwarewa ya nuna mata,nan take Hajara ta cire kambun maita ta dawo normal mutum.Cikin wata yar buta ce mai kamar ta shayi aka ɓoye ƙwayar cutar .“ Yanzu ina zan ajiye ta?”

“ Ko a nan za ki iya barin ta” Baba ya bata amsa .

Hakan kuwa aka yi kafin Hajara ta baro wurin,ko da ta isa gida tuni yamma ta yi yɗan biki sun watse tuni an share gidan an wanke komai.

Tana shiga falon ta tarar da Hajiya,da Daddy da kuma sauran yɗan gidan.Munir da Munira sai kuka suke,Daddy ne ya soma yin magana ya ce “ zan iya sanin daga ina kike mai girma Madam?”

Cike da makirci Hajara ta yi ƙasa da kai tare da soma shafar ido ta ce “ ba su faɗa ma ƙazafin da suka yi min ba ne? Na bar musu gidan ne har su gama cin bikinsu ”

“Ba ki bani amsar tambayata ba,daga ina kike na ce?”

“Gidan Salmu” ta basa amsa kai tsaye.

“Yaushe kuka fara shiri ke da Salmun?” Daddy ya tambaya cikin tsare gira,Salmu babbar ƙawar Hajara ce duk wanda ya santa to tare zai gansu sun samu saɓani da ita tun lokacin da Daddy ya auri Hajara .

Kame-kame ta fara yi,Habibah wacce tun shigowar Hajarar ta kafe ta da ido ta ce “ hum! Shi munafuki ko saman doki sai yayi ɗingishi,wato mu za ki rainawa hankali….” ba ta ƙarasa ba Daddy ya katse ta “ Habibah ya isa haka ,ki bari na yi magana da ita” ran Habibah ya ɓace don kuwa ita ta fahimci Hajara ba ta tattare da kambun maita a wannan lokaci kenan ko Sarkin Mayu ya zo ma aikin banza ne.

Daddy ya gaba da cewa “ tun da ba za ki bani amsa ba,bari na shigo da Sarkin Mayun don tabbatar mana da gaskiyar lamarin” da sauri Hajara ta ce “ babu matsala kirawo shi”

Daddy ya fita ya je can ɗakin waje ya yi wa Sarkin Mayu iso,yana sako ƙafarsa ya ji tabbas da alamu akwai Maitar cutarwa a wurin daidai nan Munira ta miƙe tsam ta bar wurin ta koma ɗaki.

Turare da wasu abubuwa Sarkin Mayun yayi amma tsit babu alamun maita a jikin Hajara ,“ gaskiya ba mayya ce ba sai dai in ƙazafi ne aka yi mata” ya faɗa yana mai baza ido ko Allah yasa ya ga wani daga cikinsu mai ɗauke da ƙanƙarar maita wacce ba a soma yin aiki da ita ba amma babu.Daidai wurin da Munira ta tashi ya ƙure da ido,amma bai ce komai ba.Daddy ne yayi masa rakiya waje tare da sallamarsa,ko da ya dawo ya tarar Hajara na ta yin kuka tana faɗin “ tun ba yau ba na san da Habibah ba ta ƙaunata,kullum cikin son ganin ta tozarta ni take in na yi magana kuma ace mata sun tsani dangin mijinsu”

“Ya isa haka ki tashi ki koma ɗakinki” cewar Daddy,Hajara ta miƙe tana yi wa Habibah wani kallo haɗi da makirin murmushi.Tana tafiya Habibah ta ce “ ka yi haƙuri Yaya Ɗayyabu na yi kuskure ,bari ita ma na je na bata haƙuri ban kyauta ba gaskiya da na yarda da zancen mutane” sai ta mara wa Hajara baya.

A tsaye ta tarar da ita ta cire hijabi,ita kuwa tana ganinta ta sheƙe da dariya ta ce “ wato ke ga mai wayo za ki tona min asiri? Hahaha! Bari ki ji Habibah wutsiyar raƙumi ta yi nisa da ƙasa,ko a yanzu kin fahimci ruwa ba a sa'an kwando ba ne.”

Habibah ta yi wani murmushi ta ce “ Hajara ai duk komai gudun Zomo ba zai ƙure dawa ba,kuma duk nisan dare gari zai waye.Ki sani tun daga ranar da na sako ƙafa ta gidan nan na yanka miki ticket ɗin ZAWARCI ,shi ɗin dai ne ba ki son yi ko? To ki shiryar tarben shi nan da ɗan ƙanƙanen lokaci zai baƙunce ki” tana gama faɗa ta

fice ta bar Hajara da baƙin ciki,a ƙofa ta gamu da Murjanatu za ta shiga ciki ta ce “ ke kuma kar wannan yasa ki yarda da mahaifiyarki ki riƙe addu'a matsayin makami ki dinga shafe yaronki da ke kan ki” Murjanatu ba ta amsa ba ta shige ciki.

Ban kwana suka yi da Hajiya wacce Daddy zai mayar gida,sannan ta wuce ɗakin Safeenatu wacce ta saka yaranta gaba tana kallo.Ba ta ce mata komai ba ta shiga Toilet ta sakar wa kanta shower,yau ce ta tsara barin Hajara gidan nan sai dai plan ɗin ta bai yi ba sam don ita ce ta shaidawa Daddy a kirawo Sarkin Mayu .Tsabar baƙin ciki sai Habibah ta hau yin kuka kamar wata ƙaramar yarinya.

#GIDAN ABBAS

Mamuh

Tun lokacin da Nafisa ta barta nan tsakar ɗaki ta zaɗa dakyar cikin siffarta ta macijiya ta shige ƙarƙashin kujera.Ta gaji sosai duk jikinta ya galabaita,ga kuma takaicin yɑar uwarta Rahamu da na Nafisa duk ya haɗe mata wuri guda.Duk wani motsinsu a falo tana gani,babban baƙin cikinta guda shine yadda ta ga Abbas ɗanta ƙwaya ɗaya till yake rawar jiki akan mace wacce kuma ba ita ba.Tun a falo suka fara tattaɓa juna,don Abbas na ɗaya daga cikin mazan da kullum suke buƙatar son kasancewa da matansu.Tana jin lokacin da Sakeenatu ke ce masa su wuce can bedroom zai fi armashi,Mamuh na daga kwance ƙarƙashin kujera ta ga Abbas ya ɗauki Sakeenatu kamar wata Baby ya nufi bedroom da ita.Tsawon lokaci tana nan kafin ta yi ƙarfin hali ta fito,ta ƙarƙashin ƙofar bedroom ɗin ta zira kanta tana hangen yadda suke mu'amulantar junansu.Irin yadda Abbas ke yi mata alƙawarin abubuwa dayawa da kuma yadda yake bayyana tsantsar gamsuwar da yake samu shi ya tunzura Mamuh ta bar wurin tare da komawa ɗakinta.Dakyar ta maida suffarta ta mutum,duk jikinta yayi baƙi kamar wacce boom ta tashi da ita.Rahamu na ganinta ta soma murna amma ita Mamuhn ta yi biris da ita,a haka suka kwana cikin jin haushin juna.

Washegari kuwa wuraren ƙarfe takwas na safe Fa'iza ta iso gidan .Falon dama a buɗe Abbas ke barinsa in ya dawo daga sallah, wannan yasa ta shigo ta gyara shi sannan ta gyara kitchen ta ɗora girki.Daga bayanta ta ji tsayuwar mutum tana juyowa suka haɗa ido ita da Mamuh,murya na ɗan rawa ta gaishe ta da “ina kwana Komandan?”

Mamuh ta waro ido ta ce “Komandan?”

Cikin i'ina ta ce “eh na zata haka ne sunanki” ran Mamuh a matuƙar ɓace ta koma falo tare da buɗe murya ta ƙwala kiran sunansa “Abbasiiiii?”.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

05/10/24

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki
```

mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

Cikin magagin bacci Abbas ya ji muryar Mamuh na ƙwala masa kira kamar wacce Allah ya aiko .Ya janye Sakeenatu da ke lafe a ƙirjinsa sannan ya saka jallabiya ya fito yana mai cewa “ Mamuh lafiya? Yaushe aka sallamo ki?”

“Wato Abbasi ban taɓa sanin tantirancin matarka ya kai har haka ba sai yau,ni za ta yi wa sunan banza ?”

“Ina kwana Mamuh ? Ya ƙarfin jikin?” Abbas ya faɗa don kawar da maganar,ta saki baki tana kallonsa kafin tace “ wato maganar tawa ce ba ta da muhimmanci? To na ji na gode sai ka tashi matar gold ta zo da dafa min wake in kuma shi ma ba za ta yi ba sai na ji”

Abbas ya ja ajiyar zuciya kafin ya koma ɗaki ya tashi Sakeenatu,dakyar ta iya buɗe ido saboda yadda gajiya da kuma bacci suka yi mata mugun kamu.A ɗan shagwaɓe ta ce “ mene ne kuma hubby?”

Ya sosa ƙeya ya ce “ ki tashi ki dafa wa Mamuh wake”

Gaban Sakeenatu sai da ya faɗi jin sunan Mamuh kawai,amma haka ta sauko daga bed bayan ta kimtsa suka fito ita da Abbas ɗin.Mamuh na tsaye kamar haure ta ƙi zama saboda yadda masifa ke ciciyarta,“ina kwana Mamuh ya ƙarfin jikin?” Sakeenatu ta faɗa cike da ladabi,Mamuh ta saka idonta cikin nata kafin ta ce “ ki tabbatar kin wanke waken da kyau,yau shi kaɗai nake so ban son shinkafa”

Da “to” ta amsa kafin ta nufi kitchen,“ ki turo min yarinyar nan ta zo ta yi min tausa” Mamuh ta sake faɗa tare da zama kan kujera.Sakeenatu na shiga kuwa ta turo mata Fa'iza sannan ta ɗebo waken ƙaddara wanda dama Mamuhn ce ta zo da abin ta daga can ƙauye.

A gaggauce ta fara wanken shi tana dirza shi kamar mai wankin kayan dauɗa kafin ta zuba a tukunya,hankalinta biyu ta raba shi wurin ƙarasa girkin da Fa'iza ta ɗora tun da ta san dai Mamuh da gayya ta kira ta don yi mata tausar.

A can falo kuwa Fa'iza kan gwiwanta ta zube tana matsa ƙafafun Mamuh waɗanda suke da mugun taushi da santsi,ga wani uban sanyi kamar halittar ruwa.Cike da mamaki dai Fa'iza ke tausar a zuci tana cewa ‘ dube min jikin tsohuwa luwai-luwai da shi kamar na wata budurwa,ƙafa ɗas da ita ko ta wasu matasan albarka’

Kamar daga sama ta ji muryar Mamuh cikin dodon kunnenta,“ ko kina sona ne mu caskale?” da wani mugun sauri ta ɗaga kai ta dube ta,sai dai abun mamaki hankalin Mamuhn na kan TV wacce Abbas ya kunna suna kallo.Fa'iza ta ja wata ajiyar zuciya tana mai maida hankalin kan farcen ƙafar Mamuh na babban yatsa,in dai ba idonta ne ke yi nuna mata ba daidai ba tabbas tamkar motsi ta ga yana yi irin na maciji yana wani ƙara tsayi.Ido ta lumshe tana jin wani bacci na shirin figar ta,amma ta yi saurin buɗe idon.Mamuh kuwa cike da mugunta take sarrafa yatsan ƙafarta,a haka har ta yi galaba kan Fa'iza ta kwanta nan kan capet ta fara baccin doli.Mamuh ta

tura babban yatsan ƙafarta a bakin Fa'iza ita kuwa kamar wata yarinyar goye ta fara tsutsar shi,banda lumshe ido babu abin da Mamuh ke yi tana jin daɗin abin da ake yi mata.

Ta shagala sosai cikin wannan yanayi Sakeenatu ta fito tana cewa “ ga shi Mamuh na kammala” dakyar ta ware idonta da suka rine suka yi ja tsabar maita ta zube su cikin na Keenat.

Karɓar plate ɗin ta yi ta soma ci da zafinsa yana tiriri,idon Sakeenatu ya sauka kan Fa'iza tana shan yatsan Mamuh ba ta ce komai ba ta wuce ɗakinta mamaki fal zuciyarta.Bakin bed ta zauna tana tunani,‘ mi yatsan Mamuh ke yi a bakin Fa'iza? Ko dai ni ce ban gani da kyau ba? To ƙilan haka ne’ ta ƙarashe zancen zucin tare da tashi ta leƙa falo don ƙara gaskata hakan sai dai tuni Mamuhn ta bar falon.

Wani irin tsammm Sakeena ta ji a jikinta,duk tsikar jikinta ta tashi .Toilet ta wuce tana mai cire suturarta,yau ma kamar waccan ranar haka ta ji ana sarrafa gangar jikinta sai dai wannan karon idonta a buɗe suke duk dai ba wani gani take sosai ba.Dukkan jikinta rawa yake tana karɓar sabon al'amarin,ta jikin ɗan madaidaicin madubin da ke can manne ga bango ta hango wata jar halitta mai ɗauke da ƙaho biyu tana tsaye tana kallon ta.

Yadda ake sarrafa jikinta ba ta taɓa samun kanta a haka ba,ihunta shi ya ja hankalin Abbas wanda shigowarsa kenan bedroom ɗin.Ya buɗe toilet ɗin,nan yayi tozali da Sakeenatu a tsaye gaban shower yanayinta da tabi'unta tamkar wacce ke tare da namiji ga kuma idonta da suka kafe wuri guda .Hankalinsa ne yayi mugun tashi ya soma yin karatu daga inda yake tsaye,halittar nan ce ta jikin madubi ta fara guduwa a gaban idon Sakeenatu ta juya baya sai a nan ne ta ga har da bindi gare ta.

Daɓas ta faɗi ƙasan tile tana jan numfashi,Abbas ya shigo ya ce “ Keenat?” yana ƙoƙarin taɓa ta da mugun sauri ta buge masa hannu ta ce “ kar ka taɓa ni ban so na gaji,wallahi ban yi haba dai”

Sai yayi tsaye yana kallon ta,shi sam bai da niyyar yi mata wani abu taimaka mata kawai yake son yi ta tashi.“ Babu fa abin da zan yi miki,bari na yi miki wankan ” dakyar ta bari ya taimaka mata,bayan sun fito ya tsure ta da ido yana kallo na tsawon lokaci kafin ya sauke huci ya ce “ Keenat mine ne damuwarka? ”

Ba ta ce masa komai ba sai kuka da ta soma yi tana jin zuciyarta ta yi nauyi,ka ƙunci na dabaibaye mata ruhi.

“Yi haƙuri don Allah kwanta ki huta,ko na haɗo miki tea?” ta girgiza kai tare da yin kwanciya.

Tana ji ba wai mafarki take ba lokacin da wani hannu ke dadaɓa ta yana buga bayanta alamun ana son saka ta bacci,ga kuma idonta da take jin ana jan jijiyoyinsu a dole ana son rufe su ta ƙarfi da yaji don kawai ta yi bacci a cutar da ita.

Halittar nan dai ce take gani ta ɗazu, wannan karon tana iya tantance ta.Mace ce har da ƙirjinta,amma don rashin tsoron Allah esprit ɗinta ya zo yana shafar jikinta,duk yadda Sakeenatu ke ƙoƙarin ta farka daga baccin nan abu ya faskara saboda mugun ɗaurin da aka yi wa raunatacen ruhinta mai ƙaramci imani da kuma bautar Ubangijinsa kan lokaci.

A can ɓangaren Mamuh kuwa tsutsu biyu ta jefa da dutse ɗaya,cike da iya tsafi ta saka Fa'iza bacci don kawai esprit ɗin da ke bata kariya ya kasance da Fa'izar.Tamkar yadda in abin murna ya samu ɗanka kake jin farin ciki fiye da shi haka ita ma Mamuh take jin daɗin ganin protector ɗinta na kusantar Fa'iza wanda tun wancan karon da Mamuh ta yi wa Fa'iza fyaɗe ya nuna yana mugun son ta kuma ta bar masa shi.

A gaban idonta protector ɗinta ya samu gamsuwa,wanda a tsarin duniyar ɓoye ya kasance mai bada kariya ga mamalakinsa.Cike da makirci ta tashi ta koma can ɗakinta,jakarta ta zuge ta fiddo wani garin magani ta zuba cikin waken tana mai ambaton sunan Sakeenatu cikin ƙanƙanan lokaci Mamuh ta je wa Sakeenar a esprit ta mori gangar jikinta.Lokacin da Abbas ya soma yin karatu ji ta yi kamar ta shaƙe masa wuya,don har yanzu ba ta gama warkewa daga illar da Nafisa ta yi mata ba.

Falo ta dawo ta laɓe a bayan wani hoton Sakeenatu da Abbas da aka manna a bango,wannan karon protector ɗinta ne ya sakar wa da Sakeenatu da muguwar kasala ya kuma taya Mamuh saka ta bacci.A cikin baccin nan Mamuh ta ƙara yin yadda ta so da Sakeena,sannan ta zuba mata gubar tsafi a duk illahin jikinta.

#GIDAN DADDY

Munira yarinya ce da ba za ta wuce shekara takwas ba a duniya,tana da wayo sosai hakan yasa ta fahimci kamar sabon al'amari na faruwa da ita tun daga lokacin da ta shiga ɗakin Safeenatu don karɓo alawar biki sai kuma ta ga plate da nama ba tare da tambaya ba ta ɗauko shi ta cinye tass ta sha ruwa.Duk abin da ke faruwa na zancen maita duk tana ji tana kuma gani,amma ba ta san dalilin da yasa sam ba ta ji tsoro ba kamar sauran yara.Ambatar sunan Sarkin Mayu yasa ta yi tsam ta tashi

ta bar wurin saboda haka kawai ta ji tsanarsa,ɗaki ta shige kamar wacce ake fizgar ruhinta haka ta shige ƙarƙashin gado ta kwanta luf idonta a rufe ruf.Duk zantukan Habibah da Mamarta Hajara sarai ta ji su,amma ko motsi ba ta yi ba ballantana a san da zamanta.Tana nan kwance babu jima wa kuma sai ga Murjanatu ta shigo, wannan karon hancin Munira ne ya soma shaƙo mata ƙamshin jikin ɗan jinjirin da ko kwana bakwai bai yi ba da haihuwa.Bakinta da ruhinta ta ji suna muradin jini sai dai ba ta san ya za a yi ta sha shi ba,da tunanin nemawa kanta mafita bacci ya ɗauke ta sai kawai ta tsinci kanta a wata duniyar.

Tsaye ta yi tana kallon duk mutanen wurin,kusan rabinsu duk tsofi ne shagali suke suna cin jan nama .Wani tsoho ne ya zo ya kamo hannunta tare da yi mata iso tsakiyar jama'a,kowa sai kallonta yake cike da mamaki don dukkansu sun shaida ta sannan kowa ya san Hajara ta lashi takobin daga gare ta kambun maita kawai zai tsaya ba za ta bayar da gajiyarsa ba ga ƴayƴanta.

Ba tare da kowa yayi magana ba tsohon nan ya ɓallo wani jan goro ya miƙa wa Munira ,ita kuwa ta karɓa ta tauna shi nan wani abun mamaki ya ƙara faruwa da ita duniyar bil'adama ce ta gani a can ƙasa mutane na ta harkokinsu.

Tsohon ne ya katse mata tunani ta hanyar cewa “ ungo wannan shi ne protector ɗinki,da zarar kina son damƙar kurwa, ko ɗana tarko,ko kuma shan jini sai ki saka ta a baki”

Ƴar jaririyar tsutsar Munira ke kallo,tsutsa ce irin wacce in aka tona ƙasar pampo ake gani.Ta na shafarta sai kawai ta shige cikin akaifarta ta yatsanta manuniya.Wani murmushi ta yi,tace “ amma wannan ɗin mine ne amfanin ta?”

Tsohon ya shafi kanta kafin ya ce “bari na yi miki fashin baƙi game da protector Mystic na Ruhaniya,shi protector yana nufin mai kariya,Ruhaniya kuma na nufin duk wani abu da bai cikin tsarin zubinsa na naturel,shi ɗin yana ɗaukar ma'anar tsafi,sihiri,bokanci,ko siddabaru.Protector zai iya kasancewa dabba ko ruhin aljan mai ɗauke da alama da mahaluzi ko rai na wanda ya riƙe shi,sau tari shi wannan protector da kuma mariƙinsa ruhinsu a manne yake da na juna.Kusan duk wani mutum da kike gani yana da dabbar da ya fi so a duniya da ta kasance protector

ɗinsa,amma an fi samun wannan wurin tagwaye....” Munira ba ta ida jin zancen tsohon ba sakamakon gangar jikinta da ta fuzgo ruhinta ta dawo hayyacinta.A hankali ta fito daga ƙarƙashin gadon,ɗakin bai da wani haske sosai amma tana ganin shimfiɗar kowa.Jikinta har rawa yake ta isa ga jaririn Murjanatu,kamar wacce za ta yi masa huɗuba haka ta saka harshenta a kunnensa bayan ta lashi yatsanta manuniya.Kamar a mafarki take jin jinin yaron na shiga bakinta ita kuma ta sha,ta lumshe ido tare da tashi ta je bayan Hajara ta kwanta wacce duk abin da ya faru kan idonta.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

06/10/24

19-20

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa
```

kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

Jikin Hajara banda kyarma babu abin da yake yi daga nan kwance,tabbas zuciyarta ta yarda ta aminta da abin da ta gani ko tantama babu Munira maita ce ta gama yi yanzu nan.Tana jin yadda Munira ke ta faman haɗiyar yawu daga nan bayanta,tsoro ne fal zuciyar Hajara ji take kamar ta tashi zaune ta tuhumi yarta ta akan abin da ta yi yanzu,sai dai ɗayan ɓangaren zuciyarta na yaudarar ta akan cewa ta yiyu fa kawai zargi ne amma ba gaskiya ba ne.Sam daren nan kasa bacci ta yi har aka kira sallar asubah,ta tashi kamar wacce ke jin tsoro ta kunna hasken ɗakin.Ta hangi Munira na ta sharara bacci, toilet ta shiga ta watsa ruwa ta zo ta yi sallah sannan ta fita ta ɗora ruwan zafin da Murjanatu za ta yi wanka.

A can farfajiyar gidan suka yi kiciɓis da Habibah wacce ita ma nata ɓangaren sam ba ta yi bacci ba.Suka kalli juna kawai kowacce ta ɗora tukunyar ruwan zafinta,har Hajara za ta koma ciki Habibah ta yi saurin tsayar da ita ta hanyar cewa “ ƙin dawo da cutarki a gidan shine mafita a gare ki,amma ki sani muddin kika yi kuskuren karɓo sharrin maitarki wallahi Hajara sai kin yi da na sanin da ba ki taɓa yi ba a duniya”

Hajara ta ja tsuki ta wuce ,sai bayan wani lokacin kafin ta fito ta cika roba ta kai banɗaki sai a lokacin ta tashi Murjanatu ta kai ta banɗaki ta soma yi mata wankan hego.A can ɗaki kuwa Munira na farkawa daga bacci ta ƙara zuwa ta saka harshenta a kunnen jaririn tsawon lokaci tana zuƙar jininsa ta ji muryar Munir na cewa “ mi kike yi haka?” ta ɗago kai ta dube shi da jajayen idonta na mayya waɗanda suka rine suka yi ja,shi kuwa hankalinsa sam ya kasa ɗaukar ganin wannan mummunar siffar kawai sai ya fasa ihu ko kafin sautin nasa ya fita Munira ta damƙe maƙogoronsa ta yadda sautinsa ya ɗauke ɗif ya zama kamar kurma.

Munira ta fi kowa sanin wane ne Munir wurin surutu, wannan yasa ta yi amfani da kambunta ta saka shi bacci tare kuma da mantar da shi abin da ya faru.Daga nan ta shiga toilet ta yi fitsari,idonta a lumshe suke sai faman buɗe ƙofofin hancinta take saboda ƙamshin girkin maƙota da yake kawo mata.

Kamar wata mahaukaciya haka ta fita ko wanke fuska ba ta yi ba ta fito,har inda ƙamshin ke fitowa ta shiga wato gidan Lantana mai balangu da waina.Munira wata irin Maitar cin nama ce ta sauko mata,babu tambaya ba komai ta je gaban tukunyar ta buɗe.Duk da uban tiririn da ke tashi haka ta saka hannu cikin miyar tana tsamo nama tana ci,wanda a zahiri protector ɗinta ne take ciyarwa .

Lantana kuwa tana fitowa daga ɗaki ta hangi Munira a bakin murhu tana tsamen nama wanda sau ɗaya kawai ya tafasa.“ Ke uwar mene kike a nan?” Munira ta wani juyo da mugun sauri suka haɗa ido da Lantana wacce tuni ta dafe saitin zuciya ganin abin da ya girgiza tunaninta.

Daga inda take tsaye ta damƙe kurwar Lantana ,ita kuma ta faɗi nan a sume.Munira kuwa da gudu ta baro gidan ta koma can nasu ,a bakin pampo ta tona ta rufe kurwar maƙwabciyarsu tana ai lumshe ido tare da komawa normal.

“Ke mi kike yi nan ?” ta ji muryar Habibah ,Munira ta ce “ ina kwana Gwaggo? Ina wasa ne”

“Tashi ki wanke ido kika wani zo kina wasar ruwa,ai Yaya Ɗayyabu na cikin takaici tun da ya auro mana masifa baƙar uwa wacce ba ta san tarbiyyar yaranta ba.Yanzu a ce ɗanka ya shekara takwas amma ba ka damu yayi Sallah ba,to amma wa ya sani ko uwar na yi”

“Habibah ki fita idona na rufe,wato ƙiyayyar taki har ta wuce kaina ta koma ga yayan da na haifa ko?” Hajara ta faɗa lokacin da take fitowa daga bandaki.

“To ai kin san an ce shi jini ba ya ƙarya,wa ya sani zuciyarki ta mugunta tasa kina koyawa yayan naki butulce wa umarnin Allah ”

Hajara ba ta ce komai ba ganin Daddy na shigowa da motarsa,yana gama parking ya fito idonsa kuwa kanta cike da munafurci ta sakar masa murmushi shi ma ya mayar mata da martani daga jiya zuwa yau wani keɓaɓen wuri ya sake cusa Hajara don ya fahimci kawai Habibah ba ta son matarsa ne ta yi mata ƙazafi amma duk da haka ko yaji ba ta yi ba ballantana ta yi masa zancen sai ya sake ta.

“Lafiya mike faruwa a nan?” ya faɗa yana mai isowa gare ta.Hajara ta langwaɓar da kai kamar wata yarinya ta ce “ babu komai Daddyn yara na ce yaushe shi mijin Murjanatun zai zo?”

Bai bata amsa ba ya nufi ƙofar shiga falo ta take masa baya tana yi wa Habibah gwalo wacce ta yi tsaye shaye da mamaki tana tunanin ko ina tauraron ta tura wa Daddy ya nufa.

Suna shiga ɗaki Daddy ya samu gefen gadonsa yayi zaune yayin da Hajara ke tsaye tana ɗan nazarinsa,ta lura da magana bakinsa wannan yasa ta yi gyaran murya ta ce “ Daddyn yara ya dai? Ko akwai abin da ke damun ka?”

Daddy ya ja wata ajiyar zuciya kafin ya ce “ eh to kusan zan ce ba damuwa ce ba,wani yaro sojawanmu suka take mahaifiyarsa shine nake ta tunanin yadda za mu yi da shi tun da ita uwar tasa ma mahaukaciya ce”

Cike da kissa ta ƙarasa ta zauna gefensa ta ce “ mi zai hana to ka kawo mini shi tun da ɗa ai na kowa ne”

Wani irin daɗi ya luluɓe Daddy har bai san lokacin da ya rungume Hajara ba ya na godiya,ita ma da biyu ta yi hakan tana son ƙara cusa kanta ne wurin Daddy ya yarda da ita ɗari bisa ɗari kan ita mutumniyar kirki ce.Ta fahimce shi da kyau zuciyarsa na da rauni wurin taimakon al'umma da saurin yarda da mutane,a gabanta ya ɗauki waya ya kira kan cewa a kawo yaron nan gidansa.

Babu jimawa kuwa aka kawo wani kyakkyawan yaro ba zai wuce shekara takwas ba kamar Munir yake.Baƙi ne shi da wata irin sumar kansa ta masa yawa ko ta wata mace albarka,kana ganinsa ka ga baƙin buzu.

Kyawunsa da yadda kuma aka yi masa gayu shi ya ƙara saka ma Hajara ƙaunarsa,ta jawo shi tana mai cewa “ mine ne sunanka?”

Cikin muryarsa wacce babu Hausa sosai ya ce mata “ Khaleed” ta shafi sumar kan nasa kafin ta rungume shi ta ce “ daga yau ni ce Mamarka ka ji ko?” ya gyaɗa mata ta ce “ yawwa ce Mama na ji?” ya kuwa maimaita.

Daddy ya saki murmushi ya ce “ina Munir yake? Ya zo na yi masa aboki” sai a lokacin Hajara ta ja shi zuwa ɗakinta,tana zuwa ta tashi Munir kallo guda ta yi masa ta gane tabbas Munira ta taɓa shi.Ba yau take maita ba shi yasa ta gane duk da kuwa kambunta bai tare da ita,“ wane ne wannan Mama?” Munir ya tambaya,ta basa amsa da “ ɗan uwanka ne shi ma ɗana ne.Ina Munira ?”

Bai bata amsa ba sai hannun Khaleed da ya kama suka fara wasa,ita kuwa Hajara tsakar gida ta fito tana duba inda za ta ga Munira.Kafin ma ta kai ga tambayar Murjanatu wacce sai yanzu ta gama wankan sabulu,sai jin kururuwa suka yi irin ta mutuwa a maƙwabtansu ana cewa Lantana ta rasu.Ita kanta Hajarar sai da ta ji mutuwar ta dake ta, wannan ya saka ta ɗauki hijabi ta tafi gidan makokin a yadda ake bada labarin yadda aka samu gawar Lantana kawai ya tabbatar mata da tabbas irin jinsunsu na Mayu ne ya damƙe ta.

A haka dai aka yi mata wanka aka kaita gidan makokinta,hatta Habibah sai da ta shigo ta yi ta'aziya saboda kusan kowa ya san Lantana mutumniyar kirki ce.Ana zaman makoki Hajara ta kwashi jiki ta sulale ta je ta karɓo kambun maitarta sannan ta dawo,daidai wurin da aka ce Lantana ta faɗi ta je ta damtsi ƙasar a ɓoye ta kai kusan hancinta.Sai da zuciyarta ta kusan tsinkewa jin ƙamshin jikin Munira,hankali tashe ta dawo gida sai ta tarar da ita da Khaleed suna faɗa da junansu saboda ta gwada kame kurwarsa amma ta kasa saboda jininsa ya fi ƙarfinta.

Hajara ce ta raba su tana kallon Khaleed,gabanta banda bugawa babu abin da yake a yadda take hango taurarin haske na kariya tattare da Khaleed tabbas ta san nan gaba in ya girma zai iya zama ajalinta sam ba za su iya shan inuwa ɗaya da shi ba.A nan take kuma wata muguwar ƙiyayyarsa ta feso mata a zuciya har ta manta abin da ta shigo yi,ido ta ƙanƙance cike da rashin mutumci ta ɗauke shi da wani gigitacen mari wanda ya haifar masa da zubar jini a hanci.Aka yi rashin sa'a Daddy shi ma ya shigo a gaban idonsa,“ innalillahi wa'inna ileyhi raji'un! Hajo mi nake gani? Dama soyayyar ƙarya ce kika bijiro ba ƙaunar yaron kike ba?” Daddy ya faɗa

yana mai jawo Khaleed wanda tuni ya soma kuka ga jini kuma ya ƙi tsayawa.Daddy ya ja shi zuwa can ciki,Habibah da ke can cikin kitchen ta yi saurin fitowa tana ganinsa ta wani zo da sauri ta kama Khaleed tare da sa gefen zanenta ta kai tana goge masa jini.

Daddy ya koma gefe yana murmushi sai yanzu ma ya tuna babu wata uwa da Khaleed ya cancanta irin Habibah .Yana nan tsaye yana kallon ta sai zarya take tana kai da komowa har sai da ta samu jinin ya tsaya,ta ja wata ajiyar zuciya tana mai kallon Daddy ta ce “ yaron wane ne?”

Kai tsaye Daddy ya bata amsa da “ ɗanki ne!” sai da ta ji wani irin halbawar zuciya jin an danganta wani a matsayin ita ce uwarsa.

“Ki riƙe shi a wurin ki,na baki shi Habibah na san za ki zamo uwa ta gari a gare shi daga baya zan yi miki bayani”

Habibah wacce ke rungume da Khaleed ido kawai ta tsurawa yayanta,a jikinta wani wahaltacen bacci ya ɗauke shi sai kuma a lokacin Daddy yayi mata bayanin komai.Wasu hawaye suka zubo mata a kumatu tana kallon kyakkyawar fuskarsa kafin kuma ta saki murmushi ta ce “ Yaya Ɗayyabu ka tuna na sha faɗa maka ni ma wata rana zan zama uwa? To alhamdullah Allah ya cika min burina ” Habibah ta faɗi haka ne jin an ce mahaifiyar Khaleed mahaukaciya ce tana da ɗan yaƙinin ba ma za a ga danginta ba ballantana su raba ta da shi.Ɗaukar shi ta yi ta wuce ɗakin Safeenatu,kan gado ta shimfiɗe shi kafin ta juyo ta yi wa Safeenatu bayanin da Daddy ya yi mata sosai ita ma ta yi mata murna.

“ Gwaggo yanzu kin ga shikenan za ki iya komawa ɗakinki” cewar Safeenatu.

Habibah ta ce “ wallahi ba zan koma ba,gorin haihuwa matansa ke yi min shi kuma bai cewa komai kamar ba ni ce na soma aurensa ba.Ina nan zai gaji ya kawo min takardar sakin ,kin ga bari na koma kitchen na ida girkina kafin Khaleed ya tashi ”

Safeenatu ta yi ɗan murmushi ganin farin ciki shimfiɗe a fuskar Gwaggo Habibah wanda ba sai an faɗa maka ba tana ƙaunar Khaleed.Tana fita kitchen ta wuce ta ci gaba da yin girkinta, muryar Hajara take ji tana tambayar Munira “ don ubanki a ina kika ɓoye abin da kika yi farauta?” ita kuwa Munirar na cewa “ Mama na fa ce miki babu abin da na kama”

“Kar ki yi min ƙarya Munira,ni mahaifiyarki ce na san komai da ke faruwa don haka zo ki gwada min sai mu raba mu biyu” Hajara ta faɗa cikin sigar rarrashi,Habibah na jin haka sai ta leƙa ta window tana kallon su.

“ Mama kenan da gaske ke ma mayya ce? ”

“Zo mu je kar na sake jin kin faɗi haka” cewar Hajara ,Munira ta mata iso bakin pampo ta tono kurwar Lantana a tare su biyu suka cinye ta a gaban idon Habibah wacce ta ƙara jin tsoron Allah.Kasa haƙuri ta yi sai da ta fita waje,cikin dakakiyar murya ta ce “ amma dai Hajara kin yi faɗuwar baƙar tasa,wato maita kika baiwa yaɗarki? ”

Munira wacce ta tunzura ta wani buɗe baki za ta kai wa Habibah farmaki,da sauri Hajara ta riƙe ta tana cewa “ zo nan kar ki kuskura ki taɓa ta”

Habibah ta yi murmushi ta ce “ da dai ki bar ta in ƙarar kwananta ne ya zo” sai kuma ta tafi ta bar su nan.Kitchen ta koma bayan ta gama girki ta kwashe ta nufi ɗaki,a plate guda ta zuba ita da Safeenatu suna ci.

Khaleed ya tashi daga bacci ya zo kusan Habibah yana mai cewa “ Ammy yunwa nake ji ” zuciyar Habibah kusan tsayawa ta yi da bugawa,ta miƙe ta kai shi toilet ta wanke masa fuska da baki sannan suka fito da hannunta ta soma basa abinci sai ta lura kamar ma dama an yi masa irin wannan sabon.Da ya ƙoshi ta basa ruwa ya sha ,ya jingina da bayanta yayi lamo ita sam sai ta ji yunwar ma ta ɓace mata.

Ta maido shi gabanta tana cewa “ mine ne Khaleed ? Mi kake so?”

A shagwaɓe ya ce “ ki rungume ni” ta saki murmushi ta jawo shi ta rungume tsam a ƙirjinta,muryarsa can ƙasa ya ce “ Ammy duk yau ba ki ce kina sona ba”

Ta kalli Safeenatu kafin ta shafi sumar kansa ta ce “ ina sonka yarona” ya saki murmushi mai sauti ya ce “ ni ma ina sonki Ammyna”

Kukan Twins ne ya fargar da Khaleed cewa akwai jarirai a nan,da wani mugun sauri ya fita daga ƙirjin Habibah yana kallon yadda Habibah ta ɗauki BASHEER tana shayar da shi yayin da kuma take jijiga Baseerat.

“Ammy ina son Baby ” ya furta yana murmushi,Habibah ta ɗauko Baseerat ta ɗora masa kan cinya shi kuma ya fara shafar gashin kanta .

“Ya kamata ma a yi musu aski” Habibah ta faɗa .

“To ko zuwa yamma ai sai ki yi musu da reza” Safeenatu ta faɗa .

“Allah kai mu”

“Ameen”

“Kawo ta ita ma a bata ta sha” cewar Safeenatu tana mai aje BASHEER,dakyar Khaleed ya bada ta da aka ɗora masa namijin sai ya ture shi Habibah ta soma yin dariya .Tsam ya miƙe ya je ya zauna kusan Safeenatu tana shayar da Baby Baseerat shi kuma ya na wasa da gashinta ana gama bata tuni ta koma bacci.

#GIDAN ABBAS

Cikin kwana biyu zuwa uku ta ci galaba sosai akan Sakeenatu da kuma Fa'iza,kullum sai ta je musu a esprit ta musu fyaɗe.Hatta aiki Sakeenatu ta kasa zuwa saboda muguwar gajiyar da jikinta ke ɗauka,kusan a kwance take sai in Fa'iza ta gama girki ta bata ta ci.A ranar bikin gidan Safeenatu har sai da ta shirya za ta je amma Mamuh ta tsiro da zancen sai in ta dafa mata wake wanda a ƙarshe kuma ta buge da tattaɓa jikin Keenat ɗin har ta fasa zuwa.

Yau suna zaune a salon Abbas na gefe yana kallon duk wani motsin Sakeenar yadda take wani juye-juye kamar wacce ke tare da namiji.Lamarin nan ya ishe shi,kawai sai ya danna kiran Nafisa bayan ta ɗauka sai ya koma can bedroom ya ce “ Nafisa wai don Allah dama Sakeenatu na da iskokai?”

Nafisa wacce ke cikin aji tana koyar da ɗalibanta ta ce “ mike faruwa?”

“Wani abu take yi ga dai shi nan”

“Ka samu garwashin wuta ka yi mata turare akwai magungunanta na nan cikin aljihun dressing mirror ɗinta” godiya yayi kafin ya kashe,gawayi ya samu irin na zamani ya kunna sannan ya ɗauko maganin ya zuba a ciki ya dawo falo bakinsa ɗauke da karatun Alqur'ani.

Daga can ɗakin Mamuh ya ji an saki wani mugun ihu haɗi da gurnani yayin da kuma Sakeenatu ta faɗo kan capet tana rawar sanyi kamar yar bori.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via
```

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

07/10/24

21-22

□□□GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA□□□

□□*BACK TO VIRGIN KIT* *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin kuɣɣga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame ☹

□□Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤

□□Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba

□□Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko

□□Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

Abbas ya nufi ɗakin Mamuh da mugun sauri amma ya tarar da ƙofar a rufe,jijiga ta ya soma yi jin har yanzu na runtuma ihu.Ta ƙasan ƙofa ya leƙa nan ya hangi wani lakaɗeɗen maciji na wani irin motsi yana kaɗa bindin,nan take hankalinsa yayi mugun tashi don kuwa ya yarda ya sadaukar macijin ne ya sari mahaifiyarsa.A guje ya fita don nemo mabugi don ya ɓalla ƙofar,dakyar ya samu gatari amma ko da yake dawo wa sai ya tarar ƙofar a buɗe ga Gwaggo Rahamu a tsaye kai ga Mamuh wacce ta lumshe ido sai zufa ke tsatsafo mata.

Murya na ɗan rawa ya ce “ Mamuh? Mamuhna babu dai abin da ya same ki ko? Ina macijin? Gwaggo ina macijin yake?”

Gwaggo Rahamu ta wani haɗe yawu ta ce “ maciji kuma?”

Abbas ya ce “ eh! Na gansa ai”

“A'a sai dai ko in idonka ne amma babu maciji nan,ka ga nemo min ruwa masu sanyi na bata ta sha ƙila ta ji dama”

“To” ya faɗa tare da fita ya kawo ruwan,sai a lokacin Mamuh ta tashi zaune.Idonta da aka naɗe da bandeji ya kumbura saboda azabar da ta ci yanzu,dakyar ta iya shan ruwan kafin ta ce “ ƙaurin mi nake ji haka?”

Abbas ya bata amsa da “ turare ne na yi wa Sakeenatu iskokanta ne suka tashi,amma Mamuh ihun mene na ji kina yi?”

Gwaggo Rahamu ta yi caraf ta karɓe da cewa “ ba ka san tana da jinnu ba? To wannan baƙin hayaƙin ne ya motsa su”

Sai Mamuh ta ɗora da “ kar na sake ji ko ganin an yi turaren maganin jinnu nan gidan,a bari har na koma ban son warinsa ”

“To Mamuh in sha Allah,sai me kuma?” Abbas ya tambaya cike da ladabi.Mamuh ta yi wani murmushi ta ce “ ina alfahari da kai Abbasi,yadda kake yi min biyayya ya zama doli na faranta maka.Allah baku zaman lafiya kai da matarka ya kawo ƙazantar ɗaki,yanzu dai kana iya maido yarinyar Sakeena tun da na ga ita ce ke baka farin ciki”

Cike da munafurci Gwaggo Rahamu ta ɗora da “ ai ɗa na kowa ne kin kyau gaskiya sai ki ga ma ta dalilinta Allah ya ji tausayinsu ya basu haihuwar nan kusa”

Shi kuwa cike da murna yake yi wa Mamuh godiya ba tare da ya san gadar zare ce ta shirya ba .Ya fita ya koma can ɗakin Sakeenatu sai ya tarar da Fa'iza a tsaye ta kama mata kai wanda da alamu ciwo yake mata“ ya jikin? ” ya tambaya,da sauri Fa'izar ta fice ta bar su nan.

“Da dama,kaina ne ji nake kamar zai tsage”

“Allah ya sawwaƙa! Amma tun yaushe kika fara sanin kina da iskokai?”

“Ni lafiya ta lau ”

“To na ji ! Yanzu mi kike so?”

“Babu komai ka kira min Nafisa ina son a kawo min Ma'idah”

Ya saki ɗan murmushi kafin ya ce “ zan je da kaina na ɗauko ta”

Sosai ta ji daɗin haka kuwa,kayan jikinsa ya canza kafin ya fita zuwa gidansu.A mutumce suka gaisa shi da Mama inda ta shaida masa Ma'idah na makaranta ita da Nafisa,nan ya zauna sai da suka dawo.

“Malama Nafi ” ya furta yana murmushi yayin da kuma Ma'idah ta rugo ta faɗa jikinsa.

“ Ya Abbas an tashi lafiya? Ina anty Sakeena?”

“Tana can gida,ya karatu?”

“Alhamdullah!” nan suka yi sallama bayan ya ajiye wa Mama kuɗi.A kan hanya ya tsaya ya saya wa Ma'idah kayan wasa da kuma biscuits da chocolat kafin su wuce gida.Tana ganin Mamarta ta je ta faɗa jikinta tana dariya, Sakeenatu ta rungume yarta tsam a ƙirji tana sauke ajiyar zuciya.Ma'idah ta kasance farin cikinta duk da kuwa ita ɗin tukuicin zina ce,amma tana saukar mata da farin ciki musamman in tana surutu.

“Wa ya saya miki babyn roba?”

“Daddy ne,kin ga har da ball ya saya min .Kina cin cakuleti na baki uhum Mama?” Ma'idah ta faɗa tana murmushi wanda ya fito da zallar kyawunta da kuma tsantsar kamarta da mahaifinta.Sakeenatu ta rumtse ido tana tuna baƙar rana wacce ta yi wa rayuwarta pentin da ba zai gogu ba.

“Kukan kuma na mine ne?” ta ji muryar Abbas ,da sauri ta goge tana ƙaƙalo murmushi ta ce “ babu komai yaushe ne za ka koma a bakin aiki?”

“Gobe in sha Allah ”

“Zan bi ka”

Ya dube ta da kyau kafin ya ce “ aikin naki fa?”

“Zan tambayi hutu,dama tun jiya na yi wa shugabanmu bayani kan banda lafiya ne.Abbas ina buƙatar shaƙar iskan wani garin ƙila zan samu natsuwa ”

Ya zo ya sumbaci goshinta tare da cewa “ in sha Allah komai zai wuce ki haɗa kayanku,zan je na karɓo wani saƙon a ma'aikata” da wannan suka rabu ya fita, Sakeenatu kuwa ta haɗa kayanta da na Ma'idah hatta abubuwan da Abbas ya sayo mata yanzu.

A ɓangaren FA'IZA kuwa sai da ta tsarkake jikinta,yayin da mafarkin da ta yi ya kasa barin kwanyarta.Sam ko kaɗan ba ta kawo a kanta tana cikin matsala ,kawai dai ta ɗauki wannan a normal mafarki da kuma ƙila don saurayinta yana yi mata zancen soyayyar aure .Yau a mafarkin a siffar saurayin ya zo mata,hakan yasa ba ta wani ma damu ba.Tana gama aikinta ta gyara ko ina kafin ta je ta samu Sakeenatu “ zan tafi gida”

“Ok to kin zuba abincinki?”

“Eh na zuba”

“Yawwa ungo wannan ki riƙe,gobe in sha Allah zan yi tafiya in na dawo zan je can gidanku na faɗa miki ” Sakeenatu ta faɗa tana mai bai wa FA'IZA kuɗi,ta yi godiya tare da yi mata fatan alkhairi sannan ta bar gidan bayan ta ɗauki abincinta a kitchen.

Sai a lokacin Sakeenatu ta fito,ɗakin Mamuh ta bi da ido kafin ta zuba abinci ta je su ci ita da Ma'idah.Har dare ba su haɗu ita da Mamuh ba,kuma ba ta tsiro da zancen dafa wake ba sosai hakan yayi mata daɗi.Tun cikin daren Abbas ya saka trollynsu a mota, washegari tun da safe ta yi wanka ta shirya yaɗarta sannan suka fito.A falo suka tsaya yayin da shi kuma ya shiga ɗakin Mamuh don yi mata sallama,cike da girmamawa ya gaishe ta tare da sanar da ita zancen tafiyar.

Cike da masifa Mamuh ta ce “ ai inda cewa ta yi Mamuh fita ki ban gida ban son ganinki da ya fi wannan kora da halin.Wato ba ta son ganina gidanta shine ta tsiro tafiya tare da kai? ”

“Yi haƙuri Mamuh duk abun ba haka yake ba,kawai duba da yanayin jikinta ne shi yasa na ce zan tafi da ita tun da ke kin ma kusa komawa ”

“To na ji Allah tsare hanya ” Mamuh ta faɗa ,duk da cikin salon jin haushi ta yi furicin amma Abbas ya ji daɗi da ba ta hana tafiyar ba.

Sakeenatu na daga falo duk tana jin abin da ke faruwa,tana nan zaune sai ga Abbas ɗin ya fito shi da Mamuh.Cike da girmamawa ta gaishe da surukarta,Mamuh ta ƙanƙance ido tana kallon Ma'idah wacce a duk duniyar nan babu wacce ta tsana kamar ita da uwarta .“ Ki riƙe abarki,da ban kwana ba za ki gan ni ? Tun can ba ki je gaishe ni ba sai yanzu da fito?” Mamuh ta faɗa tana kwaɓe fuska, Sakeenatu dai ba ta ce komai ba har ta gama surutunta suka fice zuwa mota.

Cike da iya munafurci Mamuh ta shafi kan Ma'idah wacce sumar kanta ke a buɗe babu kitso ta ce “ Allah tsare hanya ya kuma bada tsarabar yarinya mai kyau mai kama da ke” da haka ta samu ta tsigo gashin yarinyar.

Abbas yayi murmushi ya ce “ Amen Mamuh” yayin da ita kuma Sakeenatu ta ce “tubarkallah lahaula wala ƙuwata illa billah ” duk da ƙasan maƙoshi ta yi magana sai da Mamuh ta ji,da wannan baƙin cikin ta ja baya tana jin takaicin Sakeena na dabaibaye mata zuciya.A gaban idonta motar ta fita daga harabar gidan,ba don ta na son Abbas ba da tabbas ta yi wani surkulle motar ta kife ko ta huta da baƙin ciki.

Sai da ta gaji da tsayuwa kafin ta koma ciki,a falo ta samu Gwaggo Rahamu.

“Shikenan kin bar ta? ”

“A'a ai kin san an ce kada mage ba yanka ta ba ne,zan ɓullo mata ta hanyar da za ta fi jin ciwo da takaici.Wato ita guduna ne ta yi,hum ba ta san tsiyar da na shirya mata ba” Mamuh ta faɗa tana murmushi haɗi da nunawa Rahamu gashin Ma'idah .Ita ma murmushin ta yi kafin su koma ɗakin Mamuhn,wani akwati ta buɗe ta fiddo jan ƙyalle ta ɗora gashin a kai haɗi da yin wani surutu tana mai ɗiga wasu ruwan tsafi a nan take hoton motar Abbas ya bayyana wanda ya ɗauki hanyar Maraɗi.

A ɓangaren Sakeenatu kuwa suna fita daga gidan sai ta ji tamkar an cire ta ne daga cikin wuta har sai da ta ja ajiyar zuciya.Abbas yayi murmushi tare da kunna AC,babu jimawa kuwa bacci ya ɗauke ta wannan.Ma'idah da ke zaune kan cinyarta kuwa ido kawai ta ƙurawa ɗan ƙaramin mirror ɗin mota inda take hango fuskar Mamuh tana yi mata murmushi,ido ta rumtse don ita tsoronta take a haka ita ma baccin ya ɗauke ta.Sai da suka kawo sannan Abbas ya tashe su,Sakeenatu ta fara ƙarewa gidan kallo bai da wani girma amma akwai kyau duk ta ko ina shuke-shuke ne ga kuma wani ƙaton saƙaƙon Zaki a tsakiya yana aman ruwa.

Duk suka fito,shi yayi musu iso har ciki kafin ya fita nemo musu abinci yayin da Sakeena kuma ta hau gyaran gidan ta share ta goge ta saka turare .Da ya kawo

abincin su uku suka ci cike da nishaɗi,shi kansa Abbas sai ya ji wata natsuwa ta saukar masa duk wunin ranar bai fita ba a tare da su yayi shi .Da dare yayi sai ta yi wa Ma'idah shimfiɗa a ƙasa yayin da su kuma suka hau bed,cikin salon soyayyarsa yake romance ɗin Sakeenatu ita ma yau hankalinta a kwance yake jinta take kamar wata amarya wannan yasa cike da so da ƙauna ta soma mayar masa da martani.Sun lula sosai cikin duniyar ma'aurata sai Sakeenatu ta ji a jikinta tamkar ana kallonsu ne,kallo irin wannan na ƙurilla marar daɗi .A hankali ta ɗan saita kanta tare da ware ido cikin ɗan hasken da ya rage a ɗakin amma ba ta ga komai ba,murya na ɗan rawa ta ce “ Abbas ji nake kamar ana kallonmu” shi kuwa jin furucinta sai ya jawo blanket ya rufe su .Ma'idah wacce Mamuh ta shiga tunaninta da sauri ta fito daga jikin labulen ta koma kan shimfiɗarta ta kwanta.

#GIDAN DADDY

Bayan sallar isha'i Daddy ya shigo gidan,har ɗakin Safeenatu ya shiga suka gaisa ya ɗauki twins waɗanda aka yi wa aski.Gefen da Khaleed ke zaune sai cika yake yana batsewa ya kalla yana mai cewa “ yarona zo nan na ji wa ya taɓa ka?” kamar jira yake ya je ya zauna kan cinyar Daddy yana mai nuna masa Habibah ya ce “ Ammy ce ta fidda gashin SEERAT ” Daddy yayi murmushi ya ce “ wani zai fito ai,sannan musulunci ne ya ce a yi hakan”

Khaleed ya saki ransa yana mai cewa “ dole ne kuma mu yi biyayya da duk abin da Manzon tsira ya umarce mu da shi,Allah ƙarawa Annabi daraja ”

Duk suka amsa da “amen” murmushi kan fuskarsu,nan fa Khaleed ya soma zuba kamar yayan kanya sai suka fahimci duk yadda aka yi gidan girma na malamai ya fito don yan magana na cewa jini ba ya ƙarya.

Khaleed ya ja hankalin DADDY sosai har ta kai shi da yi masa tambayoyi dangane da karatun Addini,yadda yake basa amsa daki-daki da kuma yadda ya ji yaron ya

kusa sauke alƙur'ani sai abin ya basa sha'awa da kuma mamaki .Ya saka hannu a aljihu ya ciro wata sarƙar azurfa ya saka wa Khaleed wacce ita wannan sarƙa a wuyan mahaifiyarsa aka cire ta lokacin da za a yi wa gawarta wanka.

DADDY yayi musu sai da safe ya fita, Khaleed ya je jikin Habibah ya zauna yana yi mata karatu tana saurare tare da alfahari da yaronta.A kan cinyarta yayi bacci,ta yi masa shimfiɗa tana tsure fuskarsa da kallo,tasbihi kawai take yi saboda zallar kyawunsa.

Safeenatu cikin raha ta ce “ Gwaggo ni dai na yi wa ƴata kame”

Cikin rashin fahimta Habibah ta ce “ na me fa?”

“Na hafizin ɗanki mana”

Ta yi murmushi ta ce “ ai kuwa dai da abin ya bada citta,amma ai kin ga ma kamar Khaleed ɗin na son ta”

Safeenatu ta yi dariya sosai ta ce “ haba dai sai ka ce wani babba,amma na ce mi zai hana gobe ki kai shi makaranta sannan kuma a rubuta sunansa har a ta boko tun da an kusa komawa?”

“Zan yi wa Yaya Ɗayyabu magana in sha Allah ” da wannan zancen suka ta yin hira har suka kwanta.

A can ɓangaren Munira kuwa yau ma dare na tsalawa ta miƙe ta je ta saka harshenta a kunnen ɗan Murjanatu ta tsotsi jininsa kafin ta je ta kwanta.

Washegari tun da safe da kukan yaron gidan ya tashi kamar abin tsiya duk yadda Murjanatu ke son ganin yayi shiru amma abu ya cuttura.

Falo ta fito rungume da shi tana kuka,wanda ya ida jawo hankalin dukkan yan gidan suka fito har da Daddy.

Gwaggo Habibah ta dubi jaririn sannan ta maida dubanta ga Hajara wacce gabanta ke mugun bugawa.Da ido take roƙon Habibah don Allah ta yi mata rai kar ta cutar da Munira,amma sam Habibah ba ta san da haka ba.Cike da mugunta ta koma ɗaki ta ɗauko turare ,jikinta har rawa yake wurin zuba shi a garwashin wuta ɗakin ya turniƙe da hayaƙi.

Cike da tashin hankali Munira ta nemi hanya tsira amma ina ƙarfin maganin duk ya wuce yadda suke tunani,tamkar wacce aka sakawa dabaibayi haka ta kasa gusawa sai wani gurnani da take yi .

“Habibah mine ne wannan kuma kin ga za ki tado wa da Munira ciwon asuma ɗinta” Daddy ya faɗa tare da zuba wa wutar ruwa, Gwaggo Hajara ta saki wani murmushi wanda bai je ko ina ba ta waro ido jin Munira ta soma yin magana “ Ni mayya ce,Mamana ce ta bani kambun ita ce ta koya min yadda ake kama kurwa.Zan tsotse jinin ɗan anty Murjanatu saboda na samu ƙarfin power Mama...” da wani mugun sauri Hajara ta je ta rufe bakin Munira.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .
```

_____

08/10/24

23-24

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

Munira ta gantsara wa hannun Hajara cizo da haƙoranta da suke kamar na Zombie har sai da wurin ya fasa jini ya fara zuba.A gaban dukkan jama'a Munira ta wani ziro halshe tana lashe jinin da ya ɓata kusan bakinta ,yayin da kuma Hajara ta fasa uban ihu ta yi gefe tana yarfa hannu.

Cikin muryar nan ta fita hayyaci saboda maganin da Habibah ta turara duk ya hargitsa kwanyarta ta ci gaba da cewa “ ni ce nan na ɗamƙe kurwar Lantana mai balangu da waina,tare da Mama muka ci ta kuma yi min alƙawarin bani hanjin cikin anty Safeenatu da kuma jinin shegiyar yarta Baseerat.Daddy ma ta ce za mu kashe shi mu cinye mu kwashe dukiyarsa sai mu koma wata ƙasa”

Safeenatu da Murjanatu sai kuka suke yayin da kuma Hajara ta soma rantse-rantse tana cewa “wallahi sharrin Habibah ne ,so take ta tozarta ni ta kora ni daga gidanka shine ta yi wa Munira turan Aljanu.Allah ya isa tsakanina da ke Habibah kin cuce ni,kuma wallahi ƙarshen ki ba zai yi kyau ba muguwa .....” kafin ta kai ƙarshe Munira ta yi caraf ta ce “ eh Mama duk toshe mahaifarta da kika yi bai ishe ta ba shine yanzu take shiga lamurranki,kawai ki sadaukar da ita ga aljanun maita kowa ya huta.....”

“Ya isa haka!” Daddy ya faɗa cikin ƙaraji yana jin zuciyarsa na tafasa kafin ya dube ta da idon takaici ya ce “ ki je na sake ki saki ɗaya,Hajara ba zan iya zama da ke ba” yana gama faɗa ya nufi hanya fita ya shige mota ya bar gidan gaba ɗaya yana jin duniyar na juya masa yayin da kuma abubuwan da suka faru shekaru goma cif suka dawo masa a kai .

Wata ranar Laraba ya dawo daga mission a gajiye ya zo ya buga ƙofar gidansa , Safeenatu ce ta fito cikin ruwan saman da ke ta shatata kamar da bakin ƙwarya ta zo ta buɗe gidan.Tana ganinsa ta rungume shi cike da murna “ Daddy!”

“Yi sannu kar ki faɗi mana,ina mai gadi ya je ne da kika fito cikin ruwan nan?”

“Babarsa babu lafiya shine ya tafi ƙauye” ta basa amsa suna mai ratso hanya suka isa cikin haɗaɗen falon su.Wata kamalaliyar mata ta so murmushi kan fuskarta ta ce “ Barka da shigowa Daddyn yara,ya hanya?”

Kafin ya amsa ne kuma suka ji ana buga gidan da mugun ƙarfi kamar za a ture ƙofar.

Da sauri Daddy ya fita da tunanin ko yaransa da suka ajiye shi a mota suka dawo,amma yana buɗe ƙofar sai yayi tozali da wata mata duƙunƙune cikin bargo da yɤarta sai rawar sanyi suke.Da ido yake ɗan nazarinta,akwai gajiya sosai a tattare da ita idonta duk sun zurma alamun yunwa .

“Wace ce wannan?” Momah ta tambaya wacce ganin shiru bai dawo ba yasa ta biyo bayansa.

Daddy ya juyo ya dube ta yadda take ƙanƙame jiki saboda ruwan da ke bugun ta duk da ba ta jima da fitowa ba amma har jikinta ya soma jiƙe wa.Da sauri ya cire rigar ledar jikinsa cikin kulawa yake cewa “ haba dai abar ƙauna ya za ki fito cikin ruwan nan ai sai ki yi mura” ɗan murmushi kawai ta yi tana wani lafewa a jikinsa tare da cewa “ wace ce wannan ba ka bani amsa ba?”

“Sunana Hajara ni baƙuwa ce,taimako nake nema don ku bani abinci na baiwa yɤata yunwa take ji tun safe ba mu ci komai ba”

“Subahanallah! Shine kuma ka bar ta a tsaye ? Ku shigo mana ” Momah ta faɗa,Hajara ta ja yɤarta suka bi bayan su Daddy har tsakiyar falo.

“Feenat kawo wa Gwaggonki abinci ,ki haɗa musu shayi mai zafi su sha” Momah ta faɗa tana goge lafiyayar sumar kanta irin ta Bugajen asali.Idon Hajara ƙurrr kanta musamman da ta ga DADDY na taya ta goge jikin .

“ Mu je ki cire kayan nan kar mura ta kama ki” Daddy ya sake faɗa .

Sai a lokacin Momah ta juyo ta dubi Hajara wacce ke tsamo-tsamo cikin jiƙaƙun kaya har tsiyaya suke,“ oh Allah! Bari na kawo miki kaya ki canza,Feenat ki bai wa wannan kaya ita ma ta canza mi sunanki yɗan mata?”

“Murjanatu” ta bata amsa cikin sanyin murya,wani ɗakin Momah ta kai su sannan ta basu kaya suka canza Safeenatu ta kai musu abinci .

Duk uban yawansa haka suka cinye shi tass sannan suka sha ruwa,sai a wannan lokacin Hajara ta dawo hayyacinta ta soma ƙarewa ɗakin kallo tsaf da shi da alamu na saukar baƙi ne.

Ta taɓe baki tuna yadda Daddy ya dinga yi wa Momah,sai kuma ta tuna Idi mijinta wanda shine yayi mata tonon silili a bainar jama'a ya tona mata asiri akan ita mayya ce.Da ta ji haushi ta kashe shi cikin dare sannan ta ja yɗarta suka baro ƙauyen tun cikin duhun dare.

Tunaninta ne ya tsinke lokacin da Momah ta shigo bakinta ɗauke da sallama.Farantin da suka ci abinci ta duba kafin ta ce “ in ba ku ƙoshi ba a ƙaro muku”

“A'a alhamdullah mun ƙoshi mun gode,yanzu za ma mu tafiya” Hajara ta faɗa tana wani sunne kai.

“Ruwan sama har yanzu zuba suke ku jira har a ɗauke”

“To Hajiya ”

Momah ta koma can sashenta,kusa da mijinta ta zauna tana mai ɗora kanta a kafaɗarsa ta ce “ Daddyn yara na ce ya za mu yi da matar nan?”

Ya ɗan dube ta ya ce “ ban gane ba? ”

Ta ja ajiyar zuciya ta ce “ sun bani tausayi ne,ga shi ta ce ita baƙuwa ce da dukkan alamu kuma ba ta san kowa a garin nan ba”

“Kina ji na? Kar ma ki soma tunanin za ta zauna a nan gidan don ba zan yarda ba,sanin kan ki ban son hayaniya kuma ni da gidana ba za a hana ni sake wa da matata ba.Kar ki so ki ga yadda take wani kallonmu kawai don ina goge miki ruwa”

Momah ta saki murmushi ta ce “ yʻar ƙauye ce fa doli ta ga abun wani iri,ni dai don Allah ka bani dama na yi mata tambayoyi in ba ta da wurin zama sai na ɗauke ta aiki.A kodayaushe mahaifina na cewa jama'a sune mutum,ki dinga taimako a duk lokacin da kika ga mabuƙaci” ya ja dogon hancinta yana mai cewa “ don Allah ni zo ki bani abinci yunwa nake ji” tana murmushi ta jawo farantin da tun ɗazu yake ajiye.

Abincin ta zuba kamar wani yaron goye haka ta wanke hannu tana basa a baki har sai da ya ƙoshi ta basa ruwa.Daga nan kuma tausa ce ta biyo baya,haɗi da hira soyayya yana faɗa mata irin yadda yayi kewarta.

Safeenatu kuwa tana falo tana kallon tv don a nan ta fi ƙwarewa sai ga Murjanatu ta fito ,leƙenta take yi kamar wata sabuwar halitta.Sosai take sha'awar kasancewa a matsayin Safeenatu,daga bayanta Gwaggo Hajara ta zo ita ma ta yi tsaye tana ƙarewa falon kallo tsaf.

“Zo ki yi kallo” Safeenat ta faɗa murmushi kan fuskarta, Murjanatu ta mayar mata da martani kafin ta dubi Hajara .“ Je ki mana” ta faɗa ,da sauri ta je ta zauna ƙasan capet suna kallon a tare.

Hajara ta yi wani murmushi tana jin a zuciyarta ta ga wurin zama,don a duniya babu wanda aka fi saurin cuta irin mai kirki da taimako.

Kiran sallar magrib ya fito da su daga ɗaki,sosai Momah ta ji daɗin yadda Safeenatu ta saki jiki da murjanatu.“ Ku tashi ku yi sallah” ta umarce su,nan ne fa farkon shigar Murjanatu a ɗakin Safeenatu ta ga uwar dukiyar da aka zuba a ciki da kayan ado.

Alwalar kirki ma ba ta iya ba haka ta wanke jiki ta fito suka yi sallar, Feenat ce ta bata hijabinta.Bayan sun gama Murjanatu ta je gaban dressing mirror duk wani da ke wurin sai da ta tambaya mine ne,ita kuma tana bata amsa.Sai da suka yi sallar isha'i ne Safeenatu ta shafa wa Murjanatu hoda ta yi mata kwalliya,duk da ba wani ƙware wa ta yi ba amma ta yi kyau sosai.Har kayan jiki sai da ta bata wasu ta canza kafin su je falo,nan suka tarar da Hajara ta karkace baki tana bada labarinta wanda ita Murjanatu ta san ƙarya mahaifiyarta ke yi.

Mijina ya rasu a gidansu kuma ba su ƙauna ta,kullum sai na yi sirfe nake samun abin da zan ci ni da yaɗata ana haka ne kuma suka tsiro za su yi wa Murjanatu auren dole shi yasa ni kuma muka baro musu garin muka zo birni da zumar neman aikatau sai dai duk inda na je kora ta ake.Yunwa da ƙishi kamar za su kashe mu wannan ne ma yasa ina ganin Alhaji da kayan sojoji sai na buga gidan tun da a can ƙauyenmu na ji ana cewa su sojoji taimakon rayuka suke”

Momah ta yi murmushi ta ce “ Allah sarki dama ita rayuwa sai a hankali,yanzu dai ki yi zaman ki a nan sai ki dinga yi min aiki.Nawa za a dinga biyan ki a wata?”

Wani irin marayan kuka Hajara ta fashe da shi ta ce “ haba Hajiya ai ba sai kin tambaye ni ba,duk abin da kika bayar Allah sa masa albarka na gode! Na gode sosai matuƙa”

Kamar da wasa sai ga Hajara ta zama yar aikin Momah,ita ke yin shara ta wanke kwanuka da kuma kayan jikin Momah da na Safeenatu.Tamkar cc camera haka idon Hajara suke ankare da komai na gidan,yadda Daddy ke kula da Momah yake tausayinta shi ya fi komai baƙanta mata rai,wanda ke sata farin ciki kuwa bai wuce yadda Momah ba ta nuna banbanci a tsakanin yaran ba ita ce ma ta umarci Safeenatu da ta rinƙa kiran Murjanatu da anty tun da ta girme mata.Makarantar islamiyya a tare suke zuwa,yayin da ta boko kuma Murjanatu ba ta zuwa sai dai Momah ko Safeenar su dinga koya mata abin da ba a rasa ba.

A shekara ɗaya currr da Hajara ta yi gidan Momah ba ƙaramin haƙuri ta yi ba wurin kawar da laminta na maita ba .Sai dai fa iya adadin yara yan makaranta masu bi suna wuce wa waɗanda ta kame kurwarsu Allah kawai ya san iyakarsu.Ko kaɗan ba ta buɗe wata ƙofa ta zargi ba,zaune suke ƙalau da duk mutanen unguwa don tuni an san ta saboda kirkin ƙarya da take nuna wa.

Ranar Laraba tana ɗaya daga cikin ranakun sa'a ko sharri a wurin Mayu da matsafa.

A gurguje yau Momah ke yin girki don kullum ita ke yin abin ta,Hajara na ta kallon ta .Can ta kasa haƙuri ta ce “ ni kam Hajiya lafiya yau na ga sai sauri kike?”

Momah ta yi murmushi ta ce “suruka ta ke zuwa,tsawon lokaci da Daddyn yara ke ta roƙonta kan ta dawo nan garin da zama amma ta ƙi.Yau dai Allah ya nufa za su dawo ”

Haka kawai Hajara ta ji babu daɗi,ta ce “ har su nawa ne?”

“Su biyu ita da autarta ”

Ta ɗan ɓata rai ta ce “ Hajiya na ga sai murna kike halan ba ki san zama wuri ɗaya da suruka ba akwai matsala”

Momah ta murmusa ta ce “ ai gidanta daban wanda ya gina mata,a can za su sauka girkin dai ne nake yi musu.Kina ji Hajara don Allah ki manta rayuwarki ta baya ki soma wata sabuwa.Dubi fa yadda maza ke sintiri a kanki amma kin ƙi kula su,ko mai gadi sai da ya ce yana son ki amma kin yi biris ”

Tsabar takaici Hajara ji ta yi kamar ta shaƙe Momah,ita da take da burin auren Daddy shi ne za ta wani yi mata zancen mai gadi.

Safeenatu ta shigo tana cewa “ Gwaggo Hajara wai ba dai ba ki wanke min uniform ɗin makaranta ba? Duk fa sun yi datti”

Cikin masifar da take cinta ta ce “ ke masaka ce da ba za ki wanke da hannunki ba? Yʻar uniform ɗin ma….” kallon da Momah ke yi mata ne yasa Hajara yin shiru tare da fita daga kitchen ɗin ,nan ne fa ƙiyayyar Safeenatu ta soma yi mata tsiro a zuciya.Uniform ɗin da sun fi kala biyar ta ɗauko ta wanke su tana kukan zuci,tana tsaka da wankin ne Safeenatu ta fito sanye da riga da wando jeans ta saka takalmi masu tsini,can ƙasa-ƙasa ta ce “ shegiya Allah sa ƙafar taki ta ruɓe a guntule sai na ga ta hawa takalmi mai tsini kamar wacce za ta leƙo bangon duniya”

Cike da baƙin ciki dai Hajara ta wuni,a gaban idonta Momah da yara suka fita bayan sun kwashi abinci.

A mutumce Momah ke gaida Hajiya yayin da Habibah kuwa ta ƙure ƙafar Safeenatu da kallo,kasa haƙuri ta yi ta ce “ zo nan yarinyata na ga ƙafarki” Safeenatu ta zo ta faɗa jikinta tana dariya,cikin sigar wasa Hajiya ta ce “ kar ki karya min auta”

Feenat ta ce “ ai dai Mamata ce” gefe ta koma yayin da Habibah ke shafa ƙafar na tsawon lokaci,Hajiya dai na kallonta .Bayan tafiyarsu ne ta dubi Habibah ta ce “ auta ban son tsiyar gumi fa,ɗazu na ga sai faman shafa ƙafar Safeenatu kike to mine ne kuma kika gani? Kin sani sarai saboda wannan canfin yasa na yarda muka baro garinmu muka dawo nan.”

“Mama babu fa komai,sanin kan ki ina da baiwa ne ta wankin ido duk wata …”

“Ya isa haka ban son jin komai” Hajiya ta bar ta nan falo ta shiga sashen da aka tabbatar mata da shi ne nata.Habibah kuwa shiru ta yi tana nazarin lamarin da ta gani a ƙafar Safeenatu,ga kuma Murjanatu da ta gani wai yʻar mai aikinsu ce .Da

wannan zullumi ta kwana tare da ƙudirin in sha Allah gobe za ta kai wa gidan yayan nata girgiza.

A can gidan Daddy kuwa bayan dawowarsu sarai Hajara ta ji hayaniyar su amma ta ƙi fitowa har sai da Momah ta aika aka kira ta.

Fuskar nan a ɗan haɗe ta fito tare da cewa “ Barka da dawowa Hajiya”

“Yawwa ! Ki zauna ina son yin magana da ke” bayan Hajara ta zauna ne sai ta ci gaba da cewa “ ki yi haƙuri in maganar da na yi miki ta ɓata miki rai,sanin darajar mace ɗakin mijinta shi yasa na yi miki sha'awar haka.To ina amfanin ZAWARCI? Kullum a takure,yanzu yadda nake da Daddyn yara bai baki sha'awa? Don Allah Hajara ki nutsu ki gane ƙaunarki nake da rahama shi yasa nake so ki raba hanya da ZAWARCI ki tsaya ku sasanta ke da baba direba yanzu ma sai da yayi min zancen har kuɗi ya bada na baki ”

Wannan karon hawaye suka zubowa Hajara ta ce “ to in sha Allah Hajiya zan yi tunani” da wannan suka rabu ta koma ɗakinta,a cikin wannan daren ne Hajara ta fitar da ruhinta ya zaga duniyar ɓoye ta samo sirrika sosai na cimma burinta.

Washegari da farin ciki ta farka,ta shaidawa Hajiya ta yarda baba direba zai iya zuwa su fara yin zance.Sosai Momah ta yi farin ciki har ta bari Hajara ta kama mata girki wanda a yau take son fara zuba mata magani,sai dai haƙarta ba ta cimma ruwa ba Habibah ta yi sallama a gidan.Gaban Hajara ya faɗi rasss lokacin da suka haɗa ido.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim
```

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

09/10/24

25_26

□□□GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA□□

□□ *BACK TO VIRGIN KIT* *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin kuɋɋga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame ☹

□□Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤

□□Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba

□□Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko

□□Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

Ido cikin ido suke kallon juna kafin Habibah ta kawar da kai ta maida dubanta ga Momah ta ce “ ina kwana anty?”

“Lafiya lau alhamdullah ya gajiya ya baƙunta?” Momah ta amsa tana mai nuna wa Habibar wurin zama,“ gajiya ta bi jiki,ina yɗata Feenat?”

“Tana ɗaki tana shirin makaranta,Hajara kawo wa baƙuwa drink ki haɗo mata da abin motsa baki” Momah ta faɗa .

Hajara ba ta ce komai ba ta wuce kitchen hannunta na rawa ta haɗa komai a ƙaton faranti kafin ta fito ta dire gaban Habibah ,aka yi sa'a kuwa sun ƙara haɗa ido.Habibah ta sakar mata murmushi ta ce “ anty wannan fa?”

“Yɗar aikina ce”

“Oh ita ce ashe Mamar Murjanatu ”

“Eh wallahi”

“Ina kwana Ummu Murja” Habibah ta faɗa tana tsure ta da ido tana tantance ta,Hajara ta yi murmushin yaƙe ta ce “ lafiya lau alhamdullah,Hajiya ko ita ce ƙanwar Alhaji ?”

Momah ta ce “ i ita ce”

“Allah sarki ai ga ma kama nan ” Hajara ta faɗa tare da ƙoƙarin barin wurin Momah ta tsayar da ita “ ki kaiwa baba direba abincinsa ko”

Ran Hajara ne ya ƙara ɓacewa,Momah ta yi murmushi ta ce “ a dai yi haƙuri a je a saurare shi”

Haka Hajara ta ɗauki abincinsa ta kai masa,ba don ta so ba ta zauna suna tattaunawa dangane da maganar auren nasu.Tun Hajara na jiran ganin Habibah ta

fito domin tafiya har ta gaji wannan yasa ta miƙe ta koma ciki,sai ta tarar da Safeenatu zaune kusa da ita suna hira wai ta fasa zuwa makarantar ma.

Sai dab da magrib Habibah ta yi musu sallama direba ya mayar da ita.Sai a lokacin kawai Hajara ta ji sukuni,bayan sallar isha'i Daddy ya kira ta cike da kulawa ya ce “ Suley mai gadi yayi min bayanin komai,sannan ya buƙaci a kai kuɗin sadakinki can ƙauyen naku sai a ɗaura auren.Hajara kin ga dai ke ba yarinya ba ce da za a tsaya a yi ta jan magana wannan yasa na yanke shawarar gobe da safe sai ki shirya za mu wuce can ƙauye”

Da wani mugun sauri ta ɗago kai ta ce “ don Allah Alhaji a ƙara min lokaci,kuma in dai aurena kai ma za ka iya ɗaura min shi ba sai an wani je can ƙauye ba”

“To babu damuwa zuwa juma'a in sha Allah sai a ɗaura”

“Allah kai mu” Hajara ta faɗa tana wani murmushi wanda ita kaɗai ta san ma'anar shi.Daddy da Momah kuwa sun zata na farin ciki ne,haka ta miƙe ta koma ɗakinta ta fara shirya wa Suley mugunta.

Tsakar dare Suley direba na zaune yana sauraren radiyo kamar yadda ya saba kullum a nan yake cika dare yana aikin gadi.Yana dab da tashi sai ya ji tamkar wata murya na yin magana,da farko can ƙasan maƙoshi ne ƙasa-ƙasa kamar wanda ake yi wa raɗa a kunne.A hankali ya miƙe yana kallon can nesa da shi wurin lungu inda Daddy ke ajiye motarsa,da tunanin ko ɓarayi ne suka shigo ba tare da ya sani ba ya doshi wurin sai ko kafin ya isa sai kuma ya ji motsin faɗuwar bokiti a toilet ɗin tsakar gidan.A lokacin da ya yo baya sai ya ji muryar nan na sake yin magana cikin raɗa surutu ne sosai amma ya kasa tsintar mi ake cewa,a haka ya ƙarasa ga ƙofar yana buɗewa kuma muryar ta yi tsit babu kowa a ciki amma yana jin tamkar an saka wani abu ana fuzgo ruhinsa.

“Oh wato yau na cika dare ne sosai bari na je na kwanta tun da har kwanyata ta soma juy….” zancen da bai ida ba kenan jin wani abu sulululu cikin ƙafar wandonsa yana tafiya,jikinsa tuni ya ɗau kyarma bai kai ga ida shiga tashin hankali ba sai da ya ji haƙoran halittar da yake kyautata zaton maciji ne ya gantsara masa cizo a al'aura.

A nan take ya suma ,sai a lokacin Hajara ta fito daga wandonsa tana juya idonta na maciji da suke fitar da wani haske.Cike da iya mugunta ta naɗe shi da bindinta sannan ta yarƀa shi can ga bangon ɗakinsa,muguwar buguwar da yayi ta dawo da shi daga suman da yayi.A rikice ya shige ɗaki ya saka sakata tare da zumbule wandonsa nan yayi mugun gani yadda al'aurar shi ta wani bushe tare da ƙanƙancewa kamar ta yaron goye.Dirshen ya zauna kamar ƙaramin yaro yana kuka,har aka kira sallar asubah Suley bai kwanta ba.

Washegari dakyar ya iya zuwa masjid,bayan an gama sallah suka jero shi da Daddy ba tare da ya lura kamar ba a hayyacinsa yake ba ya shiga basa labarin yadda suka yi da Hajara .

Murya na ɗan rawa ya ce “ da dai an bar zancen auren nan har zuwa gaba,ka san gaggawa aikin shedɗan ce”

Daddy yayi murmushi ya ce “ kar ka wani damu shi aure lokaci gare shi ai” duk yadda Suley ya so botsare wa amma Daddy ya ƙi yarda haka suka rabu.

Gari na wayewa Hajara na ta jiran ta ji zancen an janye aurensu amma shiru,ta tabbata kuma aikinta ya tafi daidai.Bakin window ta yi tsaye tana hangen Suley ya rabka uban tagumi yau ko rediyon babu a kusa da shi,ta saki murmushi tana juya kambun maitarta ta damƙe kurwarsa a zuci tana cewa ‘ wato duk da ban yi niyyar kashe ka ba amma ka tunzura ni zan yi haka’ tun a gabanta ya fara kelaya amai tare da ɗaukar buta yana zaryar shiga toilet yana gudawa.

Sai da ta bari ya galabaita sannan ta fito da gudunta zuwa falo, Momah da ke zaune tana yi wa Safeenatu kitso ta ce “ Hajara lafiya?”

Kamar wata yarinya ta soma yarfa hannu ta ce Suley ne wai babu lafiya,amai da gudawa.

“Subahanallah” Momah ta faɗa a tare duk suka fito,halin da ta gansa ciki ne yasa ta kira Daddy ta shaida masa babu jimawa ya aiko wani yaronsa da mota suka wuce asibiti,Hajara haka ta yi ta kuka ta bi bayan su.

Ana zuwa asibiti aka soma duba shi duk wani gwaji sai da aka yi masa kafin result ta fito.Hajara sai murmushi take a ɓoye,a nan aka kwantar da Suley tana jin sojan nan na yi wa Daddy bayani da fa matsala.Babu jimawa sai ga Daddyn,da ya karɓi takardar sai da ya ɗago kai ya dubi Hajara kafin ya ce “amma ni ko lokacin da zan ɗauke shi aiki bai ce min yana da HIV ba,ko ke ya sanar da ke?”

Kai ta girgiza tana sharar ƙwalla yayin da kuma can ƙasan ruhinta a sannu a hankali take cinye kurwar Suley.Ba ta son mutuwarsa ta zama abar zargi wannan yasa ta shirya plan ɗin nan ta jefa masa ƙwayar cuta ta ƙarya wacce da ace an sake yin wani gwaji za a ga ƙarya ce.

A wannan ranar Suley ya bar duniya, faɗar irin kukan da Hajara ta yi ɓata lokaci ne cikin son kwantar mata da hankali Momah ke cewa “ki gode wa Allah ma da ya toni asirinsa ai da tuni ya liƙa miki cuta” kamar wacce za ta yi wani abun arziki haka ta faɗa jikin Momah tana mai ci gaba da yin kukan ,gefe guda kuma ta na sakar mata da gubar cuta don ta ga alamu in ta yi wasa garin kallon ruwa kwaɗo zai yi mata ƙafa.

★Kwana uku ana zaman makoki duk jikin Momah yayi wani iri, sannu-sannu ciwo ke ratsa duk wata gaɓa ta jikinta kafin a farga tuni Momah ta soma ciwon jiki da kuma na ƙafa.Kullum cikin shan magani take da kuma na shafawa wanda Hajara ce ke bata su,hakan ya kwashe wata ɗaya currr kafin ta faɗi kwanciya .

Hankalin Daddy a tashe ya kwashe ta zuwa asibiti,suna zuwa aka bata gado.Ƙarin ruwa aka saka mata don kawo sauƙin raɗaɗin azabar da take ji yayin da kuma Hajara ke gefe ta ƙure ledar ruwan da ido tana sauya musu kala daga fari zuwa gurɓatacen jini.A wannan ranar ne kuma ta yi nasarar garƙame zuciyar Hajiya ta yi mata mugun kamu,da ta gwada yi wa Daddy sai kuma ta kasa juya shi saboda yana da yawan bautar Ubangiji.

Momah na daga kwance ranta ya kawo gargada ta buɗe ido ta kalli Hajara ,da hannu ta yi mata nuni da ta zo.Ta kuwa taso ,murya na ɗan rawa ta ce “ in kin koma gida ki taimaka ki haɗa kayan Safeenatu wuri guda a kai su wurin Habibah ”

Hajiya da ke gefe ta ji sarai abin da ta ce sai ta goge ƙwallar da ta ciko mata ido don duk mai hankali zai fahimci Momah wasiyya ce take bayar wa.

“Habibah tana Maradi wurin biki wata ƙawarta ke aure” cewar Hajiya .

Momah ta ce “ babu komai sai ta zauna wurin ki kafin ta dawo”

Hajara ta ce “ haba Hajiya ya kike magana haka? Ni mine ne amfani na da ba zan kula da Safeenar ba kafin ki dawo?”

Momah ta girgiza kai ta ce “ ba zan tashi ba,ciwona ba mai warkewa ba Hajara ....” sai kuma ta hau yin tari daidai nan Daddy ya shigo,da sauri ya isa ya tallabe ta bakinta sai fitar da gurɓatacen jini yake amma a haka ta shiga maimaita kalmar shahada sai da ta yi wajen goma sha kafin ranta ya ɗauke cak.Hawaye suka sirnano daga idon Daddy,yayin da Hajara ta fita a guje tana kuka ta kira likita .Cikin abin da bai wuce minti goma ba aka fitar da gawar Momah daga ɗakin zuwa can mutuware ,tuni aka fara shaida wa mutane zancen mutuwar.Habibah wacce ke tsaka da shagalin biki labarin mutuwar matar yayanta ya zo mata,haka tana kuka ta biyo Bus ta ƙarfe biyu ta dawo zinder lokacin kuma tuni an tafi rufe Momah.A tsakar gida ta zauna dirshen tana kallon yadda ahali suka cika gidan,tana nan tana sharɓar kuka Daddy ya shigo ya miƙa mata dara(zanen gado) wacce aka rufe gawar Momah

da ita.Haka ta ƙanƙame zanen tana wani kuka mai tsuma rai, Safeenatu kuwa duk wanda ya ganta sai ya tausaya mata hatta Murjanatu ta ci kuka sosai.

Jikin Habibah ta zo ta faɗa tana cewa “ wai da gaske Momah ta mutu ba zan sake ganin ta ba?” ba ta ce mata komai ba sai rungume ta da ta yi suka ci gaba da kukan.Daddy na shigo wa Safeenatu ta yunƙura ta je shi ma ta riƙe shi gam tana ce masa “ Daddy ka kai can wurin Momahna ni zan zauna da ita,don mi za a rufe ta babu wanda ya tsaya a can.Daddy ina son ta ba zan iya rayuwa babu Momah ba,gidan duk babu daɗi Daddy don Allah ka taimaka ka maido ta”

Kamar ba soja ba haka shi ma Daddy ya soma hawaye tare da jan ta zuwa can ciki,ɗakinsa ya kai ta kamar wata mai wasu shekarun hankali ya dinga yi mata nasiha daga ƙarshe ya bata maganin bacci ya fito.

Yin mutuwa ba ya hana a ci abinci,haka aka soma raba abinci kamar wani gidan biki mutane suna ci suna hira kai kace ba gidan makoki ba.Hajara ita ce gaba wurin yin komai don in aka fidda Daddy a yanzu babu wanda zai fi ta sanin sirrin gidan,Habibah dai sam matar nan ba ta kwanta mata ba haka take jin tsanarta.Shi yasa ko girkin ba ta ci ba,fura ta dama da madara ta saka Safeenatu gaba bayan ta tashi doli ta sha kafin ta lafe jikinta tana hawaye.Sallah kawai ke tada Habibah daga wurin da ta zauna har dare yayi aka watse,gidan yayi saura sai dangin Momah na kusa da kuma na Daddy.

Tun zuwan Hajara gidan yau ce kawai ranar farko da Safeenatu ta raba shimfiɗa da Murjanatu ta je jikin Habibah ta kwanta.Zanen nan dai da aka luluɓe gawa Habibah ta rufa musu suka soma bacci,sai dai sam baccin tamkar wacce ake yi wa wahayi haka ya kasance wurin Habibah .

A cikin maƙabarta ta tsinci kanta a gaban wani kabari inda aka rubuta sunan Momah kafin daga bisani kabarin ya buɗe yana fitar da wani hasken annuri.Momah ta tashi zaune tana mai cewa “ Habibah na kirawo ki nan ne domin isar da amanar da na bari tun kafin barin duniyarku,ki kula min da Safeenatu ki sani ni ce na haife ta amma ke ce uwarta wacce za ta zauna da ita.Sannan don Allah ina son ki yi min wani ƙoƙari ki duba can bayan ɗakina Hajara ta haƙa rame ta rufe wata baƙar tukunya mai ɗauke da duk wasu abubuwa da suka kasance mallakina.Kar ki bari ta cutar da Safeenatu na san yanzu ita ce abin harin ta na gaba don ganin ta mallaki yayanki”

Tana gama bata labarin sai kuma ta farka ba tare da ita Habibar ta faɗi ko da harafi guda ba,ta dafe gefen zuciyarta tana jin wani ƙishi.Da sauri ta tashi ta fita zuwa can falo inda mutane duk suke kwance suna bacci,ɗakin da aka ce na Hajara ne ta gani da hasken wuta.Sai da ta je kitchen ta sha ruwa sannan ta nufi ɗakin Hajarar ba tare da neman izini ba kawai ta murɗa handle,tana buɗe wa ta yi tozali da Hajara zaune daram kan jan ƙyalle a gabanta kuma wata tukunyar laka ce sai hayaƙi ke tashi.Kallo guda ta yi wa fuskar Hajara ta fahimci tabbas ruhinta yayi tafiyar dogon zango da sauri ta nufi ɗakin Yayanta ta tado shi daga baccin da dama ba wani ne ba.

“Mine ne wai Habibah ?”

“ Ka zo dai ka gani da idonka,don in ni na faɗa ba za ku yarda ba” ta faɗa tare da jansa ɗakin Hajara sai dai suna shiga ta yi turus ganin Hajara kan tapis sanyen da zumbulelen hijabi ta ɗaga hannu sama sai addu'a take tana roƙon Allah ya yi wa Momah gafara.

Daddy ya ja wata ajiyar zuciya yana jin daɗi har ƙasan ransa,ya fi kowa sanin yadda addu'a ke da matuƙar tsada da kuma tasiri wurin mamaci sai kawai ya fita yana jin Hajara na samun wata irin daraja ta musamman a zuciyarsa.Ita kuwa tana jin ya fita ta juyo suna facing juna ita da Habibah wacce har yanzu mamaki bai bar fuskarta ba,Hajara ta sakar mata murmushi ta ce “ kar ki yi mamaki na bar allon sanarwa ne a nan,da zarar wani shigo fadata zan fahimta ko da kuwa esprit nan ba ya nan, wannan yasa na zaburo na dawo.Da zuwana sai na fahimci wani ɗan baiwa ne ya keto hijabin sirrin da na saka don fallasa sirrin da na ɓoye.To amma ya kika ga wasar? Ai tun ranar farko na ji ba ki min ba kamar yadda na san ke ma haka take

wurin ki.Sai dai ki sani babu wani mahaluki da ya isa ya dakatar da ni daga ƙudirina,doli na cika burina ”

Habibah ta ce “ mi anty ta yi miki kika kashe ta?”

“Lokacinta ne yayi,na ga za ta kawo min cikas ne shi yasa na aikata can”

“Ta Allah ba taki ba kuma muddin ina numfashi sai na zame miki ƙarfen ƙafa”

“Hahaha! To mu zuba mu gani ni da ke shege ka fasa” Hajara ta faɗa cike da yaƙini saboda a wannan daren ta je can ɓoyayyar duniya an ƙara mata power sannan tana da tabbaci a kan shugabansu.

Washegari

Tun da safe Habibah ta je can bayan ɗakuna tana dube-dube,yadda hayaƙi ke ɓulɓulowa daga ƙasan ƙasa yasa ta gane wurin ne aka binne abin da ta zo nema.Ba ta wani sha wahala ba ta haƙo su,tukunya ce mai ɗauke da waren takalmin Momah,ɗan kunnai,guntun ƙyalen kayanta da kuma gashin kanta.Tana Bismillah ta ƙona su a nan,yadda hayaƙi ke tashi yasa Hajara ta nufo wurin a guje.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____
```

14/10/24

27_28

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

Hajara ta yi tsaye tana cika tana batsewa ganin Habibah ta ƙona komai,sanin babu yadda za ta iya da ita ɗin ne ta tsaya suna hararar juna kafin ta juya ta koma can wurin da ake ta haɗa girkin masu zaman makoki.

Sai da komai ya zama toka sannan Habibah ta kwashe ta zuba wa wurin ruwa ta koma ɗaki,sai wuraren sallar zuhur ta fito shi ma don yin sallah sai ta tarar da wani

yaro kwance a capet sai jiƙasa masa maganin zazzaɓi ake amma ya ƙi sha sai faman juya ido suke.

Habibah ba ta san ya za ta yi amfani da power da take da ba,amma tana iya ganin abubuwan da ke jikin yaron ta fahimci tabbas maita ce wannan yasa ta fara baza ido ko Allah yasa ta ga Hajara amma wayam ko mai kama da ita babu.Hankali tashe ta bazama neman ta duk da uban mutanen da ke tanƙam a gidan,har ta fidda rai da yaron zai rayu can kunnenta ya zuƙo mata wani irin gurnani kamar na mage.Tana juyowa suka yi ido huɗu da Hajara wacce ke rakuɓe jikin wani icce sai motsi take da baki,tana ganin Habibah ta wani zabura ta buɗe bakinta kurwar yaron ta fice ta koma jikinsa.

Habibah ta ƙanƙance ido tana mai matsowa kusa da ita ta ce “ yau gidan nan ko na ubanki ne sai kin barsa,muguwa, munafuka mai fuska biyu” tana gama faɗa ta wuce ta yi tafiyarta.Tuni kuwa ta tarar yaro ya miƙe daram kamar ba shi ne ke kwance ba,alwala ta yi ta shiga ta gabatar da sallah.

Tana fitowa ta tarar da Hajara riƙe da kaskon wuta tana turare duk illahirin gidan sai faɗi take tana ƙari “ gidan makoki na buƙatar turaren jiji, Allah ya jiƙan rai yayi gafara, Allah kai rahama kabari”

Wani irin mugun sanyi ne ya ratsa Habibah wacce tsabar son tona asirin Hajara yasa sallar ma ko cikin natsuwa ba ta yi ta ba.Burinta kawai ta je ta sanar da Daddy sai ga shi ta ci karo da abin da ya girme ta,powerta iya maita kawai take iya fahimta da kuma tunƙaho sai ga shi a yanzu ta fahimci ashe baya ga maita Hajara shahararriyar MATSAFIYA ce.Babban takaici a nan kuma yadda ta Hajiya mahaifiyarta da ita kanta Kakar Safeenatu suna wani yabon Hajara da alamu turaren asirinta yayi aiki.

Tun daga wannan lokaci sai Habibah ta ji gwiwanta sun yi sanyi,don duk yadda take son ganin Hajara ta bar gidan sai abu ya cuttura.A haka aka yi sadakar uku wanda babu fashi kullum sai ta yi turaren nan,faɗar maganin da ta zuba a abincin mutane don rufe bakinsu irin dangi da kuma yɁan unguwa Allah kawai ya san iyaka.ƘarinTakaici kuma shi ne yadda Safeenatu take wani ƙara shige wa Hajara a jiki,ita ma cikin iya tako take nuna damuwarta a kanta.Har aka yi addu'ar arba'in akwai baƙi waɗanda ba su koma ba ciki kuwa har da Habibah wacce al'amarin Hajara ya girmi tunaninta sai dai duk da haka wani sa'in tana tanka mata sannan duk tsiyarta ba za ta aikata laifin maita ba wanda kuma wannan ɗin shi kuma babbar illa ce ga rayuwar Hajara .

Yau tun safe Daddy ya fito ya raba wa baƙi kuɗi kasancewar duk za su tafi,bayan ya gama da su ne ya dawo kan Habibah wacce ke zaune kan kujera tana kallon ikon Allah Hajara ce ke shafar kan Safeenatu tana cewa “ ƙara ci mana yɁata daga wannan shinenan ,yawwa ko ke fa? Dube ki har hancinki ya ƙara kyau” ita kuwa Safeenar sai murmushi take tana ganin eh tabbas duk da ta yi rashin uwa Hajara na ƙaunarta.

Daddy ya dubi saitin inda Habibar ke kallo ya saki murmushi yana jin daɗin yadda Hajara ke kula da sanyin idaniyarsa.

“Habibah ɗazu Idriss yake ce min cikin satin nan a dube su za su kawo lefe” furicin Daddy ya maido da hankalinta wurinsa.Ta ɗan nisa tana kallon yayan nata ta ce “eh haka ne”

“Amma ya ce min kin zo da wani shirme a bari har wata shekara”

Ta jinjina kai ta ce “ Eh Yaya ƊDayyabu sabo...” ya katse ta da “ ban tambaye ki dalili ba,ina son gargaɗinki kar na sake jin wani shashancin ko haka kike so ki zauna babu aure ?”

Idon Habibah suka ciko da ƙwalla ta ce “ Yaya Ɗayyabu ita Safeenatu fa sai na bar ta?”

“Yau na ji wani shashancin,da can ke kike kula da ita ne? Ki fara shiri ma tun yanzu don ya ce bai so bikin ya jima” yana gama faɗa ya fice.Haka Habibah ta ci kuka ta gaji Hajara dai na gefe farin ciki fal zuciyarta don dama ita kawai ce cikas a rayuwarta ta san da zarar kuma ta yi aure shikenan.

Kamar da wasa sai ga shi cikin satin nan an kawo lefen Habibah ,tuni kuma aka fara shirin biki.Abin da ya fi ɗaga hankalinta guda ne jin mijin na cewa za su wuce can inda yake aiki, wannan ya haifar mata da muguwar damuwa wacce a nan Hajara ta ci galaba kanta wurin nasaka rayuwarta.Ko da aka yi bikin Habibah da sati ɗaya currr,sai Daddy ya zaunar da Hajara kamar wata uwarsa ya shiga yi mata godiya haɗi da bata abubuwan arziki a ƙarshe ya ɗora “ na san duk wannan ba zai biya hallacin da kika yi min ba Hajo,wallahi banda bakin godiya”

Hajara ta murmursa ta ce “ Alhaji mi zai hana ka aure ni kawai sai na zauna da Safeenar ai zai fi,ni dai ko ba ka shigo ɗakina ba kawai dai igiyar auren ce nake so ta hau kaina”

Duk da maganar ta daki Daddy amma sai ya ce zai yi tunani a kai ya bar ta nan.Ta bi bayan shi da harara tana jin takaicin yadda aka yi asirinta bai aiki a kansa,da dadare bayan sun ci abinci ita da su Murjanatu suka yi kallo na wani ɗan lokaci kafin ta matsawa Safeena ta je ta yi lesson.

Tsakar dare Hajara ta yi alwala ta hau tapis de niyyar Allah yasa Daddy ya yarda ya aure ta,tun da dai ta gwada yin asiri ba ta yi nasara ba shine ta koma ga Allah.

Washegari tun safe ta shiga kitchen ta haɗa girki kala biyu , Daddy ya fito tsaf yau a cikin kakin sojoji kana gani ka san yau yɗan aikin sun motsa.A ladabce Hajara ta gaishe shi tana mai cewa “ na zata yau ba za ka fita ba fa,ka ga girki na yi wa Hajiya tuwon tuƙe ne da ɗanyar miya na ga ta fi sonsa fiye da shinkafa”

Daddy yayi tsaye yana kallonta,wato hatta yadda take magana a yau irin cikin salon Momah ne.Ya saki murmushi ya ce “ ki shirya sai mu tafi tare mu kai mata” ta wani sunne kai kai kace mutumniyar kirki kafin ta koma can ɗaki ta ƙara yin wani wankan ta canza kaya ta fesa turare na musamman don sace zuciyar Hajiya sannan ta fito.

A table ɗin cin abinci ta tarar da su suna cin abinci su duka ukun,kamar wata Hajiya haka ta canza tafiya tana murmushi tace “ yau ko jira na ba za a yi ba? ”

“ Abincin yau ya fi na kullum Daddy Gwaggo ” Safeenatu ta faɗa cike da tsantsar farin ciki,Hajara ta ja hancinta ta ce “ dama jiya ba na faɗa miki zan girka miki abincin mai shegen daɗi? Kin ga har wanda za ki ci fa a makaranta na fidda miki yana kitchen ”

Safeenatu ta yi wani ihun murna ta ce “ ina yinki Gwaggona”

Hajara ta zauna tana murmushi ta zuba nata abincin tana ci, sarai ta san da Daddy na kallonta amma sai share ta ci gaba da jan yara da jira har da labarin fina-finai suke da kuma serie ɗin da suke kallo a tare wanda kuma wannan ɗin duk yana cikin plan ɗinta.

Bayan sun gama cin abinci,sabon direba ne ya kai Safeenatu makaranta boko yayin da Murjanatu ta wuce ta islamiyya sai aka rufe gidan Daddy ya ɗauki Hajara a mota zuwa gidan Hajiya .

Karon farko da suka samu kusanci da juna sosai irin haka,don a gaba ta zauna ta rungume basket ɗin abinci tana kallon hanya.Kasancewar gidan babu wani nisa sai suka kai da wuri,a tare suka fito daga motar suka shiga ciki da sallama.

Cike da ladabi Hajara ta gaishe da Hajiya tare da bata abincin da ta kawo,bayan sun gaisa sosai ne Daddy ke cewa “ Hajiya na kawo miki ita ne don ki zama shaida na zaɓowa da Safeenatu uwa ta gari mai kula da ita,in kin amince in sha Allah zuwa jibi za a ɗaura min aure da ita”

Ba Hajiya ba hatta Hajara da take faman jiran hakan sai da zuciyarta ta buga,a tare suka kalli juna kafin hajiyar ta ce “ Allah sa alkhairi ”

Suka amsa da “ amen”

Akan hanyar su ta dawowa sosai Daddy ya ƙara fayyace wa Hajara aurenta da zai yi kawai saboda goben Safeenatu ne amma in ba don haka ba shi mace ba ta gabansa.Duk da ta ji ɗacin furicin amma ta basar,ta nuna masa ra'ayinsu ɗaya.A ranar ya kai ta asibiti aka yi masu gwajin jini sannan ya kai ta wani Mall ta zaɓi wasu kayan sakawa ya maido ta gida.

Ita ɗaya ta shiga tiƙar rawa tana kwaikwayon tafiyar Momah da kuma yadda take yi wa Daddyn,sai ta taɓe baki tana jin tsanar ta.Ɗakinta ta je cikin ƙwarewa da

surkulle duk ta tsafe gidan musamman ɗakin Safeenatu da kuma kayan jikinta.Sai bayan ta gama ne ta ɗora musu girkin rana, Murjanatu ce ta soma dawowa tun ƙarfe sha ɗayan rana ita kuwa Safeena sai ana kiran sallar zuhur,tana shigowa gidan gabanta ya faɗi ga wani irin tsoro da take ji.

Ɗakinta ta wuce tana mamakin yadda babu kowa falon,ta yi wanka sannan ta fito ta shiga kitchen ta zuba abinci ta ci ta ƙoshi sannan ta yi sallah.Sai a lokacin Murjanatu ta shigo wacce take jin saura ƙiris su zama daidai da Safeenatu,a yau hatta yanayin hirarsu sai da ta canza amma ita Feenat sam ba ta san dalili ba.

Falo suka je suna kallo suna hira da dariya har lokacin islamiyya yayi suka je suka dawo sai a lokacin Safeenatu ta haɗa ido da Hajara .Wani irin tsoronta da shakarta ne suka dirar mata lokaci guda,duk sai ta daburce ita kuwa wani makirin murmushi ta saki tana cewa “ ku je ku yi wanka ku canza kaya”

Da dare bayan sallar isha'i Daddy ya cewa da Hajara yana son zuwa ganin magabatan ta,ba ta wani damu ba don ta shirya komai sai ta basa lambar wani mazaunin ƙauyen zinder da ke washa.Washegari Daddy ya je da aminansa biyu ,ba a ɓata lokaci ba aka ɗaura aurensu.

Wani uban ado Hajara ta caɓa har da zuwa saloon aka yi mata lalle da gyaran gashi,hatta fatarta sai da aka yi mata dilka.Safeenatu dai na kallon yadda yau

Murjanatu ke cikin farin ciki,ba ta tsinke da lamarin ba sai da Hajara ta fito wanda yayi daidai da shigowar Daddy.

Abin da duk babu wanda yayi zato ko tsammani ba shi Hajara ta yi,“ oyoyo Daddyn yara tun ɗazu muke ta zuba ido” ta furta tare da rungume shi, Daddy yayi ƙoƙarin fidda ta daga jikinsa amma ina tamkar cingam haka ta liƙe masa.

A rayuwarsa rungumar Momah a gaban kowa bai taɓa damunsa ba,amma yanzu da Hajara ta yi masa sai ya ji kunyar yarsa wacce ta ƙure su da ido ƙurrr ko ƙyaftawa ba ta yi .“Hajo mene ne haka? Ba ki ganin yara ne?” sai a lokacin ta ɗan ja baya tana mai kamo hannunsa suka ƙarasa can ɗakinsa kamar yadda take ganin Momah na yi masa.Zuciyar Daddy wani irin matsanancin bugawa take saboda turaren da Hajara ta yi amfani da shi irin mai bijiro sha'awa,ga kuma salon dressing ɗinta irin na abar ƙaunarsa ne .Babu kunya ba komai Hajara ta soma rage masa kayan jikinsa tare da yi masa rakiya zuwa toilet,wasu yan magana na cewa namiji a gaban mace tamkar yaro ne to hakan ta faru da Daddy Hajara ta dinga juya shi son ranta da kissa da ƙwalisa har sai da ta nemi shi yayi kwanciya da ita.Sai bayan komai ya lafa ne yayi shiru yana mamakin kansa,ko a mafarki bai taɓa tunanin zai haɗa shimfiɗa da Hajara ba amma sai ga shi yanzu a kwance akan shimfiɗa.Ya sauka daga bed ya shiga ya tsabtace jikinsa,ko da ya fito ya tarar tana sharar bacci wani haushinta ne yake ji amma ya daure bai tashe ta ba ya fita zuwa falo sai ya tarar sai Murjanatu a zaune tana kallon tv.

Ɗakin Safeenar ya nufa,a zaune ya tarar da ita tsakiyar gado tana waya tana kuka .Ya fahimci ita da Habibah ne saboda yadda take ambaton sunanta,tana jadada cewa “ aure fa Gwaggo Habibah! Daddy yayi aure shekara da mutuwar Momah ba a yi ba shine ya auro wata,wata ɗin ma yar aikinmu matar da muka taimaka tun tana cikin dattin dauɗa.Ni dai kashe kaina zan yi zuciyata ciwo take”

Daddy ya rumtse ido jin furucinta na ƙarshe wai za ta kashe kanta,a hankali ya je ya zauna bakin gadon sai a lokacin ma ta fahimci ya shigo ta zabura za ta sauka yayi saurin riƙo ta ya ce “ zo nan Feenat ɗina,ban son ganin kukan nan ki bari.Ban auri Hajara don komai ba sai domin ke ta dinga kula da ke, kuma ai na ga ke ma kina sonta ” da sauri ta girgiza masa kai bakinta na rawa ta ce “ a'a Daddy ban so,kar ta ƙara shiga ɗakinka ban so in kuma ta yi haka kashe kaina zan y….” yayi saurin toshe mata baki ya ce “ ya isa haka Feenat! Na ji! Na yarda zan haramta mata shiga ɗakina amma kar na sake jin furucin za ki kashe kan ki,ban so .Je ki wanke fuskarki

ki zo mu ci abinci” duk maganar da suke Habibah na saurare don ba ta kashe kiran ba.Sai da ta ji shiru sannan ta kashe,ita ma ji take kamar ta kama da wuta da ace tana da kuɗin jirgin da za ta baro Burkina faso da tabbas yau ba za ta kwana a ciki.

Safeenatu kuwa tamkar wata yarinyar goye haka ta koma wa Daddy yau,abincin ma ƙin ci ta yi ya ɗauke ta a mota suka je restaurant nan ɗin ma ba ta sauya zane ba sai dawowa gida suka yi a lokacin tuni gimbiya Hajara ta fito daga turaka har ta canza kalar wanka ta saka wasu kayan Momah.Tsoronta shi ya hana Safeenatu cewa komai sai kallon Daddy da ta yi,tuni kuma ya fahimci abin da take nufi.Yayi gyaran murya ya ce “ Hajo je ki sauya kayan nan ki saka waɗanda na saya miki,sannan ki ban makullin ɗakin marigaya na hannunki”

Hajara ta ƙanƙance ido tana kallon Safeenatu tana son tantance ko asirin ne ya watse sai dai ko ɗaya kawai ƙarfin hali ne,sai ta saki fuskarta tana cewa “ to Daddyn yara bari na cire” sai ta koma ɗakin ta cire ta fito ta mayar ɗakin Momah ɗin ta kuma bada key sai ya miƙawa Safeenatu ita kuma ta karɓa tana kallon Hajara a tsorace ta wuce ɗakinta.A bayyane ta ja ajiyar zuciya kafin ta ɗauki wayarta wacce lambar Daddy sai ta Habibah kawai ke ciki ,kiran nata ta sake yi ta shaida mata yadda suka yi Habibah ta tsara mata komai da kuma bata shawarar ta cire tsoron Hajara .

Daddy kuwa bai yi nauyin bakin gindiya wa Hajara shiga ɗakinsa ba,da wannan ƙululun baƙin cikin ta kwana ɗaki guda ita da Murjanatu.

Washegari kuma sai ta tashi da wani salon munafurcin shi ne yi wa Safeenatu cake ta rubuta sunanta ,duk wani abu da ta san zai faranta ran nata sai da ta yi shi ta ɗora kan Dining.Da murmushi kan fuskarta ta shiga ɗakin,a zaune ta tarar da ita kan bed ta yi wanka towel ne kawai a jikinta.Ganin surar Safeenatu ya kusan saka

Hajara manta ainahin abin da ya shigo da ita,dakyar ta iya kawar da maitarta ta ce “ Feenar Daddy zo ki gani” sai ta kamo hannunta tana janta zuwa waje,cike da mamaki Safeenar ke bin bayanta har suka isa falo.Abun ka ga ƙwaila sai ta washe baki tana murna,can ƙasan zuciyarta tana cewa ‘ anya ba gasken-gaske Gwaggo Hajara ke sona ba ? ’

“Je ki saka kaya sai ki zo ki yanka mu gani” Hajara ta katse mata tunaninta,da sauri ta koma can ɗaki ta saka doguwar riga ta fito Hajara ta bata wuƙa ta yanka “ yawwa sa min a bakina” cewar Hajara tana dariya, Safeenatu kuwa ta kai bakinta Murjanatu na yin video daga ɓoye ba tare da sun sani ba.Amma wani abun mamaki a cikin Camera wayar a lokacin da Safeenatu ke yankawar jini ne Murjanatu take ganin yana tsiyaya yayin da kuma cake ɗin ya zama jan nama.

Hannun Murjanatu ne ya soma yin rawa , lokacin da idonta suka yi tozali da fuskar Hajara ta zama irin ta Zombie tana cin ɗanyen nama jini na mata zuba a baki.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

15/10/24
```

Ihun Murjanatu ta ƙwala tare da faɗuwar ƙasa a sume,hakan ne kuma ya jawo hankalinsu.Da sauri Safeenatu ta ajiye wuƙar hannunta suka rugo tare da ita da Hajara suna faman girgiza ta ,“ ɗauko ruwa masu sanyi a frigine ” cewar Hajara a ruɗe, Safeenatu ta je ta ɗauko ta zuba wa Murjanatu su amma ko yatsa ba ta motsa ba.

Daddy ya fito yana da sauri jin muryar Hajara ta cika ko ina na gidan sai ihu take tana faman faɗin ta shiga uku ta lalace.Bai tsaya tambayar ba'asi ba ya fita waje ya ba direba umarnin tada mota,har bakin ƙofa kuwa ya kawo motar Daddy ya ciɓo Murjanatu ya saka mota.Dukkansu suka dugunzuma asibiti ,da isarsu aka karɓe ta tare da soma bata taimakon gaggawa.

“ Wai mine ne ya sumar da ita ?” Daddy ya tambaya.

Safeenatu ta ce “ muna yanka cake kawai muka ji ta fasa ihu,ko da muka juyo kuma a yashe a ƙasa muka gan ta”

“To Allah kyauta ya kuma ba ta lafiya” Safeenatu ce ta amsa don Hajara banda kuka babu abin da take yi.Tsawon lokaci kafin a turo Murjanatu bisa gadon maras lafiya hancinta an saka mata oxygen, idonta tuni sun faɗa .Wani ɗaki aka kwantar da ita ,sai a lokacin Hajara ta daina kuka ta wani je ta zauna kusa da kanta tare da kamo hannunta ta jimƙe.

Ko da Murjanatu ta farka sai kuma duk abin da ya faru ya goge mata a kwanya,ƙarin ruwan na idawa kuma aka sallamo su gida.Cake ɗin da suka bari kan Dining duk ya

ruɓe yana fitar da wari ,cikin abin da ba zai wuce awa biyar ba amma ya lalace.Cike da baƙin ciki Hajara ta kwashe shi ta zubar,tun daga wannan lokacin ba ta ƙara yunƙurin cutar da Safeenatu ba sakamakon laulayin ciki da ta soma mai mugun azabtar da ita ,sosai Daddy yayi murna ko ba komai jininsa ne.Shekara ɗaya har da wata ɗaya kafin Hajara ta haifo yaɗan biyu mace da namiji,irin soyayyar da Safeenatu ta ɗora musu shi ya ƙara kawar da mugun nufin Hajara kanta ba su ƙara samun saɓani ba .

Bayan shekara shidda da haihuwar yaɗan biyu Daddy ne ya shigo shi da wani matashin saurayi dukkansu sanye suke cikin kakin sojoji.Cike da girmamawa yaɗan matan biyu Murjanatu da kuma Safeenatu suka fito suka yi wa Daddy sannu da zuwa tare da gaishe da saurayin.

Daddy ya ce “ Bashir ka ga yaɗayaɗana”

“Ma sha Allah kyawawa da su yalaɓai” ya furta yana murmushi,Hajara wacce fitowarta kenan sai cewa ta yi “ ko dai za ka zama surikin gidan nan ne?” ita ma da murmushi a kan fuskarta,Bashir yayi yaɗar dariya ya ce “ i ina so mana Mama in dai za a bani”

Cikin son shigar da yaɗarta ta ce “ Murjanatu maza ki bai wa angon naki ruwa mana” ita ma cikin iya yi ta je ta ɗauki kofi tana murmushi yayin da shi kuma Bashir ya kafe Safeenatu da ido,ta ce “ ka zauna mana” ya ce “ na gode kyakkyawa” sai kuma ya ci gaba da yi mata wani kallo saboda tuni Daddy ya wuce ɗakinsa Hajara kuma ta take masa baya.

Murjanatu ta basa ruwa ya sha yayi mata godiya ,hira ya soma yi jan su da ita nan ya fahimci Safeenatu ce kawai ke jin French ita kuma Murjanatu da alamu ba ta yi makaranta ba wannan ya ƙara sa hankalinsa kwanciya akan FEENAT shi ɗin mutumen jama'a ne yana da abokai turawa suna zuwa kawo masa ziyara sai yaya kenan in matarsa ba ta iya turanci ba.

Yadda ya mayar da dukkan hankalinsa gaba ɗaya ga Safeenatu shi ya sa Murjanatu ta kwaɓe fuska babban takaicinta kuma shine da suke yin hirar da French ba da Hausa ba.

Hajara ta fito tare da Daddy sai a lokacin ne kuma suka zuba abinci gaba ɗaya aka soma ci,Bashir dai na ta satar kallon Safeenatu duk sai ta ji ta takura ta miƙe ta ce ta ƙoshi tare da shigewa ɗaki.Kwanciya ta yi kan bed tare da kiran Habibah suka fara yin hira nan take bata labarin cewa “ wani baƙo ne muka yi mai shegen kallo ,surutu kuwa ko kuturu albarka.Tun jiya Daddy ya shaida mana zuwansa wai duk cikin yaransa ya fi ji da shi ni na yi tunanin in ga wani babban mutum sai na ga ɗan yaro ko 30 years ba zai wuce ba”

Habibah ta yi murmushi ta ce “ yaushe za ki zo hutu ?”

“Daddy ba zai bar ni ba,ban san mi yasa ba”

“Hum! Ki bar shi dai tun jiya na yi masa magana amma ya ƙi saurara ta,gidan nan ya ishe ni tun da na dawo damagaram ɗin nan babu zaman lafiya matansa sai gori suke min ina ga dai na kusa barin gidan”

Zuwa yanzu Safeenatu ta girma ta zama cikakkiyar budurwa wannan yasa Habibah ta ɗauke ta tamkar wata ƙawarta,“ don Allah ki yi haƙuri,am ... Ina zuwa sai an jima zan sake kiran ki” cewar Feenat tana mai kashe kiran saboda shigowar Murjanatu.Bayanta ta bi har zuwa falo,Bashir ya saki murmushi ya ce mata “ni zan tafi Feenat sai in kuma na sake dawowa” ta ɗan yi murmushi ta ce “ to Allah tsare hanya” tare da Daddy suka fice bayan yayi musu kyautar kuɗi,da wani mugun kallo mai game da tuhuma Hajara ta dubi Safeenar ta ce “ murmushin mene wannan?”

“Komai” ta bata amsa tana jin duk babu daɗi,tun daga wannan rana Hajara ta canza mata ta ɗauki tsanar duniya ta ɗora mata saboda Bashir ya ce ita ce zaɓinsa kuma ya turo magabatansa har aka aura masa Safeenatu.

Daddy ya ja wata doguwar ajiyar zuciya tuna rayuwarsa ta baya,daidai ƙofar gidan Hajiya yayi parking tare da shiga ciki tana ganinsa ta ce “ lafiya dai ko?” bai ce komai ba kamar wani yaron goye ya zo ya zube kusa da ƙafafunta ya ce “ na saki Hajara ! ”

Hajiya ta ja wata sanyayyar ajiyar zuciya kafin ta ce “ alhamdullah! ”

Idonsa ya ciko tab da hawaye,sai yanzu yake jin ina ma ace bai haɗa zuri'a da ita ba? Murya na ɗan rawa ya ce “ Hajiya wallahi Hajara ta cutar da ni,ashe duk tsawon shekarun nan da muka ɗauka da ita mayya ce? Yanzu kuma ta ɗauki ƙanƙararar Maitar ta bai wa yarta ta cikinta Munira.Ina duniya za ta da mu ? Hajiya maita fa” sai kuma ya rushe da kuka sai kace wani ƙaramin yaro,Hajiya ta soma shafar sumar kansa tare da yi masa nasiha “ita da ma rayuwa cike take da ƙalubale ,dayawan waɗanda muka ɗauka masoya to sune maƙiyanmu, Allah ya gani ni dai tun farko matarka ban sonta ban san dalilin da yasa na kasa hana ka aurenta ba amma don cuta ta cutar da mu”

A can gida kuwa Habibah ta saki murmushi ganin Hajara cikin lukutar masifa hankalinta duk a tashe take haɗa kayanta yayin da kuma Munira ke gefe ta rakuɓe duk yanayin fuskarta ya canza.Hajara ta fito jaye da trolly ta kalli Murjanatu wacce ƙiri-ƙiri take nuna tsoron mahaifiyarta,“ idonki sun tabbatar min zaɓinki sai dai ki sani nan ba gidan ubanki ba ne ballantana na bar ki cikinsa dole ki bi mu”

“A'a wallahi Mama ba zan je ba” cewar Murjanatu tana komawa bayan Habibah wacce take ta zuba murmushi.

“Ku taso mu je” ta cewa Munira da Munir wanda yayi saurin yin baya yana cewa “ zan zauna gun anty Murja”

Habibah ta yi wata dariya kafin ta ce “ Hajara ke ɗaya za ki fita don ba zan bari ki tafi da Munira ba zan kai ta gun Sarkin Mayu a cire mata masifar da kika liƙa mata”

Cikin tsiwa Munira ta ce “ zan bi uwata babu ruwanki da ni”

Habibah ta ce “ ke rufe min baki ,da bazawar uwarki nake wacce komai ya ƙare ma” tana maganar ne tana kallon tsakiyar idon Hajara masu cike da tsantsar baƙin ciki da burin ɗaukar fansa.

Hajara ba ta ce komai ba ta ja hannun Munira suka fice, Safeenatu ta ja wata ajiyar zuciya tana jin ƙarshen damuwarta ya zo.Yaranta ta ɗauka tana kallo tana mai yi musu addu'o'in tsari tare da tofe su,Basheer idonsa biyu sai Baseerat ce kawai ke bacci .

Khaleed ya shigo ya zauna kusa da ita ya ce “ Mama kaina ciwo yake”

Ta juyo ta dube shi tare da kama masa kan tana masa addu'a kenan sai ga Habibah “ mene ne kuma ke damunsa?”

“Ce mini yayi kansa ke ciwo,ina Murjanatun?”

“Na ce ta wuce ɗakinta ta zauna kar ta wani damu,kai kuma zo nan na gani kar a ce muguwar can ce kafin ta tafi ta jefe ka da MAITAR IDO (MRS SADAUKI ga mai son book ɗin complet 800 ne) .Jikinta Khaleed ya kwanta duk ya wani shagwaɓe fuska ita kuma tana kallonsa cikin ido kafin can ta ce “ Safeena miƙo min Baseerat ” da to ta amsa kafin ta ɗora mata ita kan cinya,hannun mai safa ta cire tare da ɗora shi bisa kan Khaleed amma bai bado haske ba ta ja ajiyar zuciya tace “ bari na baka magani normal ciwon kai ne”

“A'a ban son magani” ya faɗa kamar zai yi kuka,amma ba ta saurare shi ba ta je ta ɗauko ludayi ta zuba ruwa a ciki sai da ya jiƙa sosai ta danne shi tare da yi masa ɗuren maganin babu jimawa kuma ya amayar da shi doli ta haƙura da basa maganin.

Wasa-wasa jikin Khaleed yayi zafi duk sai Habibah ta ruɗe kamar wata yarinya haka ta saka shi gaba tana shirin masa kuka.

Safeenatu ce ma ta kawo shawarar a kai shi asibiti,jiki na rawa Habibah ta kimtsa tare da saɓar shi a kafaɗa ta fita can bakin titi ta samu ɗan sahu ya kai ta wata private asibiti.Babu wani jira ta ga Dr ta yi masa bayanin komai,jininsa aka fara ɗiba kafin a kawo result ya rubuta duk alluran da za a yi masa Habibah ta sayo.Ana fara haɗa ruwan allurar ya soma kuka,ita kanta jikinta rawa ya ɗauka da Dr ya ce “ sai fa kin riƙe shi Madam ”

“To...to a ina za a yi masa allurar?”

“Ga cinya” ya bata amsa.

“Khaleed ɗina yi shiru mana babu zafi yanzu a gama” ta faɗa cikin rarrashi tana jan wandonsa can sama ta fiddo cinyarsa,ido ta rumtse lokacin da ta ga duk gudan tsiken allurar nan ya shige a cinyar yaronta.Kukansa kuwa har ƙasan zuciyarta yake suka,“to an gama sai kuma gobe in sha Allah ” Dr ya faɗa yana murmushi Habibah ta yi masa godiya ta fito .Sai da ta tsaya a hanya ta saya masa ayaba da wasu kayan marmarin kafin su wuce gida,tun bisa hanya Khaleed ya shaida mata bai son allura amma zai sha magani.

A ɓangaren Hajara kuwa tafe dai take tana jaye da hannun Munira a hannunta na dama, ɗayan kuma riƙe da trollyn kayansu.Zuciyarta tamkar garwashin wuta haka take jin ta, taƙamaimai ba ta san inda za ta kai su ba kawai dai tafiya take can za ta tsallaka titi ta ji murya daga sama “ kamar Hajara nake gani”

“Ita ce mana”

Da sauri ta juya inda muryoyin suka fito sai ta yi tozali da ƙawarta da kuma ƙawar babarta.Ta waro ido ta ce “Rahamu? Laaa har da Ladidi ” sai kuma ta washe baki tana mai isa wurinsu.

“Sai ina haka jaye da ƙaton akwati? Ita wannan ɗin fa wace ce? Oh dama Hajara kina nan a raye tun bayan wannan mugun al'amari da ya faru” cewar Rahamu tana riƙe haɓa.

Hajara ta ɗan yi ƙyaci ta ce “ ke dai bari,sai ina?”

“Asibiti muka je idon Ladidi ne babu lafiya,ke kuma fa?”

“Da dai za ku bani masauki da labarin zai fi daɗin bayarwa”

Mamuh ta ce “ mu je mana can gidan ɗana ki zauna ai ita ma Rahamun yanzu can take” mai ɗan sahu suka samu ya kai su can gidan Abbas .....

□□□GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA□□□

□□*BACK TO VIRGIN KIT* *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin ku♀♀ga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame ☹

□□Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤

□□Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba

□□Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko

□□Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

```MRS SADAUKI□✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

16/10/24

30

Sai da suka sha ruwa masu sanyi suka ɗan huta kafin Hajara ta soma basu labarin gidan mijinta da ta baro.
```

Rahamu ta ce “ mi zai hana ki koma ƙauye ki ƙara samo wasu ɗamarun yaƙi tun da yanzu hatta shi kansa mai gari maye ne? Yanzu fa a ƙauyenmu Mayu sun samu rigar yƴanci ko ɗanki kika haifa kika cinye babu wanda zai zunɗe ki ballantana kuma a kai ki gidan mai gari.Kina ji ko Hajara yanzu abin da ya dace kawai ki bi anty Ladidi ku koma can ƙauye,ta yadda za ki bai wa shegiyar Habibar nan mamaki da ta hana ki rawar gaban hantsi”

Hajara ta ɓata rai don a yanzu ba ta ji za ta iya yin rayuwa a ƙauye ba,sannan yanzu da suka zo gidan Abbas sai ta ga babu laifi yana da kyau duk da ko rabin na Daddy bai kamo ba amma dai ai za ta yi rayuwa cikin hasken ƙwan fitila ga kuma cima mai kyau.“ A'a gaskiya ba zan koma can ba,ki dai sake bani wata shawarar amma wannan ba ta yi ba”

Rahamu ta saki baki tana kallon ta kafin ta ce “ to halan kina da wani gidan a nan Zinder da kike gudun ƙauye ? Hajara kar fa ki manta zaman ZAWARCI ne za ki yi mai cike da ƙalubale don haka doli kin ga ungulu ta koma gidanta na tsamiya”

“Wai don Allah Rahamu ba ki ƙyale ta ne uhum? Ina ce da jibi zan bar garin nan na koma ƙauye wanda hakan na nufin ke ma za ki koma can gidanki,to ƙila tare take so ku je don haka bari na yi shiru” Mamuh ta faɗa tana hararen Hajara da sauri ita kuma ta ce “ ba haka ba ne Mamuh,kin ga Munira tana makaranta in mun koma can ƙauye ya makomar karatunta kenan?”

“Sai ta zauna a nan wurin matar Abbasi mana kin ga ko ba komai mun samu wacce za ta dinga ɗauko mana rahoto” Mamuh ta bata amsa kai tsaye tana wani irin murmushi ita ma Hajara ta mayar mata da martani nan suka shiga yin hira kafin Rahamu ta ɗora musu girki bayan sun ci sun ƙoshi ne Mamuh cike da duniyanci ta ɗauki waya ta kira lambar Abbasi bugu uku ya ɗauka,suna gama gaisawa ta ce “ ka shaidawa gimbiyarka jibi zan koma ƙauye sai ta dawo ta zauna ita ɗaya,sannan akwai wata jikar ƙawata da za ta zauna a nan ta yi karatu yarinyar ba za ta wuce shekara takwas ba” tana gama faɗa ta kashe ba tare da ta jira cewar shi ba.

A can ɓangaren Sakeenatu kuwa a gabanta Abbas ya ɗauki wayar,tana tsaka da basa labarin abin da ya faru jiya.

Yadda ta tsure shi da ido yasa shi jan ajiyar zuciya ya ce “ kika ce me?”

“A jiya da muna kwance sai na ji kamar ana kallonmu ne,irin ana ankare da mu”

Ya shafi gefen wuyanta ya ce “ tunaninki ne kawai amma babu wani wanda ke kallonmu”

Ta ce “ wai ka yarda da zancen fatalwa kuwa?”

“Mi kuma ya kawo wannan maganar?” Abbas ya tambaye ta kafin ta basa amsa suka jiyo ihun Ma'idah da ke can tsakar gida tana wasa.A tare suka fita sai suka gan ta yashe a ƙasa tana kuka a tsorace,“ mine ne babyta ?” Sakeena ta tambaya tana mai jawo ta a jiki.Saitin inda ruwa ke zuba ta nuna mata ta ce “ ƙadangare na gani kore ”

“Babu ƙadangare kore Ma'idah sai in dai hawainiya ce kika gani” cewar Abbas yana mai baza ido amma bai ga komai ba,haka suka dawo cikin ɗaki dakyar suka samu ta yi shiru tana wasa da yar tsanar robarta.

“Zan fita na dawo ki kula sosai kar ki ƙara barin ta fita ko ina” Abbas ya faɗa tare da ɗaukar wasu takardu ya fice.Sai a lokacin Sakeenatu ta ɗauki waya ta kira Feenat ta bata haƙuri tare da sanar da ita uzurinta ta shagala sosai a waya Ma'idah wacce ke zaune wani ɗan ƙaramin malam buɗa takarda ya ɗauki hankalinta sai bado haske yake yana yi yana tashi sama tare da sauka wani wurin .

Da murmushinta ta kuwa miƙe ta je sai ta yi kamar za ta damƙe shi sai yayi firrr ya tashi sama ya dira wani wuri,a haka har suka fito tsakar gida .Wasa ta mayar da abin hakan yasa ba ta san lokacin da ta zo har wurin ɗazu da aka bata tsoro ba,sai a lokacin kuma malam buɗa takardar ya tsaya ta kama shi ido cikin ido suke kallon juna da shi.Wannan shine karon farko na Munira da ta canza siffa a bisa shawara,horo da kuma umarnin iyayen gidanta a wurin maita.Yarinya ce ita ƙarama amma Mamuh ta cusa mata soyayyar jinsi wato lesbian wannan yasa a yanzu take jin wani mugun son Ma'idah .Kamar yadda suka tsara bayan Mamuh ta kira Abbas a waya shi ne za su kawo ma su Sakeenatu ziyara su duka huɗun,Munira ita ce remote ta janye dukkan hankalin Ma'idah ta yadda su duka ukun za su yi ajiya a jikin yarinyar don ruguza farin cikin uwarta wannan kuma faɗan Mamuh ne su ɗin kawai kama mata ne za su yi.

Sosai Munira ta ci nasarar ɗauke hankalin Ma'idah,har suka samu damar zagaye ta Mamuh da Rahamu siffar maciji ce suka zo da ita yayin da Hajara ta ɗauki ta ƙadangare babu tsoron Allah haka suka zagaye ƙaramar yarinya suka aiwatar da mugun nufinsu.Tamkar hayaƙi haka suka zuba ƙwayar cutarsu inda ruhinsu zai samun matsuguni, Ma'idah ta rumtse ido jin tamkar an tsikare ta da allura sai kuma ta yi saurin buɗe su sakamakon Munira da ta yi tsalle ta koma kan hancinta.

Yawunta ta zuba wa Ma'ida a hanci kafin ta tashi sama ita kuma ta ɗaga kai tana kallon ta ,“ mi kike kallo zo nan daga ina waya shine kika fito” Sakeenatu ta faɗa tare da jan hannunta suka koma ciki.

Ta zaunar da ita kan kujera sannan ta kunna musu tv,“ Mama yunwa nake ji” Ma'ida ta faɗa tana wani lumshe ido, Sakeena ta miƙe ta kawo mata abinci sai dai ko minti uku ba a yi ba ta cinye ta ce “ ban ƙoshi ba” sam ba ta kawo komai a ranta ba sai ta ƙara mata tana gama ci ta ɓingire daga bacci inda aka yi ta tsoratar da ita. Ba ita ta farka ba sai da Abbas ya shigo da ledar nama ƙamshinsa ya daki hancinta ta miƙe kuwa tana mirzar ido,duk dariya suka yi mata jin tana tambaya “ Daddy nama ne?”

Babban plate Sakeena ta ɗauko ta juye sannan suka fara ci ,abun mamaki har Ma'ida ta fi su ci.Suna hira ne Abbas ya ce “ Keenat Mamuh za ta koma jibi,gobe in sha Allah sai ku bi motar ƙarfe tara ku koma don ban son a bar gida babu kowa sannan za ki je kasuwa ki yi mata siyaya”

Ji ta yi kamar ya buga mata guduma a kai amma ta daure ,in tana tuna hallacin Abbas gare ta sai ta ga komai Mamuh ta yi mata bai kamata ta yi fushi ba wannan yasa ta danne ɗacin zuciyarta ta ce “ to Allah kai mu goben lafiya”

“Amen!” ya amsa sai kuma shiru ya biyo baya,sarai Abbas ya fahimci ba ta so haka ba amma yana kimanta yin adalci da bai wa kowa matsayin da ya rataya a wuyansa.Yana mugun son Sakeenatu,ya sani kawai ita ɗin ƙaddararsa ce a yadda yake ƙin zina da kuma in ya ji an ce wane mazinaci ne shikenan sai ya ji ya tsane shi amma kuma a hakan Allah ya jarabce shi da auren wacce ta taɓa yin cikin shege.

Ya bi bayanta da kallo ganin ta tashi ta shige bedroom,kai kawai ya girgiza suka ci gaba da yin kallo shi da Ma'idah har dare yayi sosai .“ Baby je ki yi fitsari ki kwanta”

“Ban jin bacci Dad...” ba ta ida ba sai kuma ta ji wani dunƙulalen abu ya zo ya daki kwanyarta a nan take ta soma hamma alamun bacci,Abbas yayi murmushi ya ya cire duk wata wayar lantarki ya kai Ma'ida toilet da niyyar yin fitsari amma a shagwaɓe ta ce “ Daddy ka min wanka”

“Baby kina ganin fa idonki har lumshewa suke saboda bacci amma a haka zan yi miki wanka?” kuka ta saka masa wannan yasa ya cire mata kayan jikinta tare da fara yi mata wankan.Ma'idah wacce Mamuh ta yi aron gangar jikinta tun tuni ta wani kamo hannun Abbas ta ɗora a ƙirjinta tare da yin nasarar shagaltar da shi wurin cuɗa ƙafafunta.

“Mine ne haka Abbasss?” Sakeenatu ta faɗa wacce ta shigo da wani bala'in sauri tana janye hannun Abbas da idonta suka gane mata kamar yana shafar yarta ne .

Ba tare da ya kawo komai a kansa ba ya ce “ wankan nake mata ”

“Shi ne kake wani shafar ƙirjinta? ” wani irin shock ne ya ratsa Abbas jin wani zance marar kan gado,muryarsa har wani shaƙewa take wurin magana “ shafar ƙirji kuma?”

“ Eh! Ko ka zata ban gan ka ba ne? ”

“Haba Keenat wace irin magana ce wannan,Ma'idah ce fa yarmu”

Ta ja hannun yarta tana mai cewa “ ka fita ni zan yi mata wankan”

“A'a Mama ban so na Daddy ya fi daɗi” Ma'idar ta faɗa har yanzu kuma idonta a lumshe suke,Abbas ya fice zuciyarsa na tafasa yayin da Sakeenatu ta soma wanke wa Ma'idah jiki amma caraf ta kamo hannunta tana mai ƙara ɗora shi a ƙirjinta ta ce “ ka wanke nan ɗin da kyau kamar yadda kake cewa kullum yana da kyau a dinga wanke shi da kyau da kuma nan”

Jikin Sakeenatu ne ya soma yin rawa zuwa yanzu ba zargi take ba ,kawai ta yarda Abbas ɗan iska ne wasa yake da yarta.Da wani mugun sauri ta cika bokiti ta zuba wa Ma'idah tare da jan ta zuwa ɗaki,tana kuka tana ƙari ta kwantar da ita kan bed har da wani kunna fitilar wayar ta haska domin duba yarta.

Abbas da ke gefe sarai ya gane mi take nufi hakan yasa a zuciye ya zo ya finciko ta tare da tsinka mata mari abin da bai taɓa yi ba tun zamansu da ita.Sam ya kasa yin magana sai huci da yake yi,ita kuma Sakeenatu ta soma zaginsa “ munafuki ,maciyi amana wanda bai san kunya ba wato don Ma'idah ba yarka ba ce shine kake wasa da gangar jikinta.Ba zan taɓa yafe maka wannan zunubin ba kuma wallahi na gama aurenka ba zan zauna da kai ba,doli ka sake ni ”.....

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki

mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

17/10/24
```

Ganin kamar network ɗinta ya sauka ne sai Abbas ya rarrashi zuciyarsa shi ya sauke nasa zafin kan da na zuciyar ya fita falo ya bar ta nan.Ita kuwa Sakeenatu cike da takaici ta samu wuri ta kwanta bayan ta yi wa Ma'idah shimfiɗa,tunani ne ta soma yi barkatai duk yadda sheɗan ke rura mata wutar zargi amma akwai wani sashen zuciyarta da ya ƙi yarda kan cewa Abbas zai aikata hakan ga ma wata mace ballantana yarta wacce ya riƙa kamar shine uban cikin.Wannan yasa sai duk ta ji ta tsargu kuma ba ta kyauta masa duba da hallacin da yayi mata,kamar wacce ƙwai ya fashewa a ciki haka ta miƙe cikin sanɗa ta ɗaga labule kaɗan.A zaune ta hango shi tsakiyar falo yayi tagumi fuskarsa cike da damuwa,ta ja wata ajiyar zuciya tana mai yi wa kanta faɗa ‘ Sakeena wai mine ne ya shiga kwanyarki ne har kike zargin mutumin da ya suturta ki a lokacin da duniya ta yi miki sintiri? Hakan da kika yi daidai ne Abbas ya cancanci haka? ’ a hankali ta fito tare da isa wurinsa,ta zauna gefensa tare da cire masa tagumin ta ce “ka yi haƙuri wallahi na kasa riƙe fushina ne”

Abbas ya ja ajiyar zuciya ya ce “ wallahi Keenat tun da nake ko yatsan wata mace ban taɓa riƙe wa ba ballantana a kai ga zancen zina,kin san ni kin fi kowa sani ta ya zan aikata wani abu ga Ma'idah? In ba ki yarda ba sai na yi alwala na dafa Alkur'ani” “Ya isa haka komai ya wuce” ta katse shi ,Abbas ya buɗa baki da niyyar yin magana ta yi saurin kai nata kan nasa.Wannan ce hanyar da take jin za ta iya bi don nuna masa ta janye zargin,cikin wani salo take aika masa da saƙonni iri-iri shi ma yana mayar mata da martani.Cikin ƙanƙanen lokaci suka fice hayyacinsu, wannan karon Sakeenatu ce ke gudanar da mu'amalar tasu hakan kuma ba ƙaramin fizgar ruhin Abbas yayi ba har ya kasa jure azababen shauƙin da yake ji ya soma yi mata suratai.Mamuh wacce ke jikin Ma'idah tun fitar Sakeenatu take jiran ci gaban masifar amma ta ji shiru,duk da ta so ta miƙe don ganin wainar da ake toyawa amma ta yi haƙuri sai yanzu da kunnuwanta suka jiyo mata suratan ɗanta wanda take bala'in kishi yana yi wa mace shagwaɓa da abubuwan da baki bai isa ya isa ya fayyace su ba.

Ta yi saurin rairafowa ta leƙo ta jikin labule tana kallon Sakeenatu wacce ke kan Abbas ,wani maƙoƙon baƙin ciki ne ya rufe ta sai ta soma jin hawan jininta zai motsa.

A ɓangaren Sakeenatu kuwa duk da tana cikin wata duniyar amma hakan bai hana ta jin wannan yanayin ba kamar ana ankare da ita .Amma ta share ta ci gaba da faranta ran mijinta,Abbas ya jawo ta tare birkitata ya ɗauki wani salon wanda tsabar baƙin ciki ya saka Mamuh ƙwarewa a jikin Ma'idah ta soma yin wani tari jini na yi mata zuba a baki.

Duk da sun ji tarin ba su tsaya ba sai da suka samu natsuwa,suka mayar da kayansu sannan a tare suka shiga ciki.Yanayin da suka ga Ma'idah yayi matuƙar tayar musu da hankali,jiki na rawa Abbas ya saɓe ta yayi waje Sakeenatu kuwa dogon hijabinta kawai ta saka ta take musu baya.A motarsa suka wuce wata private asibiti,yanayinta kawai likitocin suka duba suka shiga yi mata gwaje-gwaje da kuma yi mata magani.

“ Hawan jini kuma likita? Ka duba kuwa da kyau?” Abbas ya faɗa lokacin da ya samu keɓewa da Dr a ofis ɗinsa yana mai shaida masa abubuwan da suke damun Ma'idah.

“Sosai kuwa shi ne abin da muka gani,ni kaina na yi mamaki sosai musamman da na ga kamar tana matakin ƙarshe ne” Dr ya faɗa .

Abbas ya girgiza kai ya ce “ a'a sam wannan ba zai yiyu ba,shekarun Ma'idah sun yi ƙarancin da ba za ta iya kamuwa da wannan cuta ba”

Shiru likitan ya ɗan yi kafin ya ce “ ya fi sau uku muna gwajin nan,ni ma abin da na ce kenan sai dai in hawan jinin Aljanu ne”

“A'a yʼata ba ta da iskokai sai dai tuntunɓen aiki amma lafiyarta lau ” Abbas ya faɗa yana mai ficewa daga ofis ɗin ya koma ɗakin da aka kwantar da Ma'idah,gefenta Sakeenatu ce a zaune tana ta faman kallonta.

“Mi Dr ya ce? Mike damun ta?” ta tambaye shi,ya bata amsa da “ kar ki wani damu haɓo ne ta yi ”

Shiru ta yi ba don ta yarda ba,ƙarin ruwan na idawa ya ɗauki Ma'idah zuwa mota yayin da ita kuma ta take masa baya suka koma gida.Sam yau kasa bacci suka yi musamman Abbas da ya san amsar da likita ya basa, Sakeena na ankare da shi sarai ta fahimci yana ɓoye mata wani abu ne amma ta ƙyale shi.Washegari tun safe Ma'idah ta farka cike da walwala hakan yasa duk suka ji daɗi,gidan shiga mota ya kai su wacce za ta kai su Zinder.Kuɗi sosai ya bata tare da yi mata bayanin yadda za ta yi da su,sai da ya raka ta har cikin mota ta zauna ya sumbaci goshinta da na Ma'idah kafin ya fita.

Tun da suka kama hanyar Zinder ɗin zuciyarta ke wani bugawa da sauri har suka sauka.Tun a can gidan Bus ta kira Abbas ta shaida masa sun sauka lafiya kafin ta sama musu taxi zuwa gida,tun a bakin get ta ga duk gidan ya canza yayi datti tamkar wanda aka ci kasuwa a ciki.

Da Munira ta fara cin karo wacce ta leƙo tana kallon Ma'idah,duk da kasancewar ba wani zuwa take gidan su Safeenatu ba amma sai ta ga kamar ta san fuskar sai dai ta manta.

“Barka da dawowa anty” cewar Munira tana zuwa da ɗan gudunta ta karɓi jakar hannunta,“ yawwa wace ce ke?”

“Sunana Munira ”ta bata amsa shiru ta yi ba ce komai ba har suka shiga falo,babu kowa sai Rahamu tana kallo.

A ladabce Sakeenatu ta gaishe ta tare da cewa “ ina su Mamuh?”

“Ta yi tafiyarta,ni ma yanzu nan zan tafi tun da kin dawo ga dai yaɗar amana nan ” ta bata amsa tana zunɗen Munira.

“Amma ai cewa ta yi sai gobe ko? Kuma wannan ɗin yaɗar wace?”

“Ki kira mai gidan ki sanar da shi ni kin ga tafiya ta ma” tana gama faɗa kuwa ta fice, Sakeenatu ta bi bayanta da kallo kafin ta wuce ta buɗe ƙofar bedroom ta shiga ta zauna sannan ta kira shi Abbas ɗin nan ne fa yayi mata bayani dalla-dalla,a

zuciye ta kashe kiran kafin ta fito falo sai ta tarar Ma'idah sai dariya take tana walwala suna wasa da Munira.Ta ja yar ajiyar zuciya kafin ta ce “ zan fita na dawo ku zauna nan kar ku saki ku gusa ” dukkansu da to suka amsa kafin ta fita ta je gidansu FA'IZA ba su wani jima ba suka dawo tare .

Gidan FA'IZA ta shiga sharewa yayin da ita kuma Sakeena ta shiga kitchen ta ɗora girki.Buhun da Mamuh ta zo da shi na wake ta buɗe tana mai cewa “ waken ƙaddara shine ta tafi ta bar min shi a nan” daga bayanta ta ji Munira na cewa “ anty ni na ce ina so ta bar min”

Da mamaki wayo irin na Munirar ta juyo tana kallon ta kafin ta ce “ je ki koma falo ” kai ta gyɗa kafin ta tafi.

A ɓangaren Mamuh kuwa tun cikin wannan daren ta soma shirin tafiya don ta ci alwashi yadda Sakeenatu ta maƙalewa Abbas sai ta raba su tare da ingiza ta a inuwar ZAWARCI.Muddin tana numfashi ba za ta taɓa barin ana cutar da yaronta da sunan soyayya ba,Hajara ma wacce ba son komawa ƙauyen take ba ita ma da nata burin suka bar gidan tun kukan zakara na farin.

Suna isa bakin ƙofar da za ta sada su da cikin ƙauyen Hajara ta yi tsaye tana kallon ko ina yayin da kuma daɗaɗen tarihin can baya ya dawo mata a kai.Ta saki murmushi ta ce “Mamuh kin ga wasu yara can suna ɗibar mangoro”

Mamuh ta dubi wurin da ƙatuwar bishiyar take kafin ta ce “mangoron mutuwa kenan! Mallakin mai gari ne,maye kawai zai iya shan magoron can ya wanye lafiya,tsaya ki ga dukkansu mutuwa za su yi daga ƙarshe”

Hajara ta waro ido ta ce “amma ya aka yi idona suka kasa gane min itaciyar mugunta ce?”

Mamuh ta ce “duk tsiyar mutum ba zai taɓa fahimtar wannan ɓoyayyen sirrin ba,ni ma abin da yasa na sani mai garin ne da kansa ya shaida min”

Hajara ta yi wani makirin murmushi ta ce “yanzu kina nufin zan iya samun irin shukarsa?”

“Eh sosai muddin dai za ki sadaukar da jinin ɗaya daga cikin yaƴanki tsaf mai gari zai baki da kuma shuka miki ita duk inda kike so”

Shiru ta yi tana ɗan tunani kafin ta ce “mu je gidan mai garin” suna shiga ciki direct can gidan mai garin suka wuce,Mamuh ce ta gabatar masa da ita ai kuwa ya shaida ta ya soma washe baki yana tambayar Hajara abin da take buƙata ta kuwa shaida masa shi kuma ya ce “babu matsala ai an riga da an gama”

Daga nan suka wuce gidan Mamuh wanda yake na laka,ɗakin nan nata cike yake da komatsai barkatai na tsafi.Da dare can irin gari yayi tsit suka fita yawon dare wanda iya ruhi ne gangar jikin na can a gida,sun tsorata masu zaman majalisa kafin su yi tsinke can birnin zinder.Mamuh ce ta yi wa Hajara rakiya zuwa gidan Daddy, murmushi kan fuskarta ta ce “kin ga tuni Aljanu sun dasa bishiyar mangoro a gidan ”

Hajara ta ce “ Habibah yadda kika tarwatsa farin cikina ke ma sai na tarwatsa naki,da sannu zan fesar da kuɗirina game da mangorona” a haka suka bar wurin.

#GIDAN DADDY

Washegari tun da safe Habibah ta fito tsakar gida ta ɗora tukunyar ruwan zafin jego kafin ta koma ciki.Sam ba ta lura da bishiyar mangoron da ta tsiro dare ɗaya ba sai da ta ga Munir na shansa,cike da mamaki ta ce “ a ina ka samu mangoro da sanyi safiyar nan?”

“Na nan gidan ne mana Gwoggo ” ya bata amsa tare da nuna mata shi,ta yi shiru tana ɗan tunani don dai ita a saninta nan gidan babu bishiyar mangoro.Ɗaki ta koma tana tambayar Safeenatu da Murjanatu su ma duk suka sanar kan cewa a'a babu,sai kuma suka fito a tare duk suna kallon ikon Allah ganin ga bishiyar nan ta fitar da yaya masu kyau sai iska ke faman kaɗa su.A nan take duk suka ji kuma sha'awar ci hatta ita kanta Habibar,“lafiya duk kuke kallon sama kamar masu son ganin sabon wata?” Daddy ya tambaya wanda fitowarsa kenan.

Safeenatu ta basa amsa da “ Daddy mangoro ne dubi” ai kuwa yana ƙyallara ido ya ji yawunsa sun tsinke,tun bayan da ya saki Hajara yake cikin ƙunci abinci ma bai ci ibadar tasa ma ta yi ba wannan yasa ya ji ya fi kowa sha'awar son ci.Kamar wanda ake turawa haka ya je ya ciro ɗaya ko wanke shi bai yi ba ya kai bakinsa yana sha,a take wani garɗin daɗi ya ziyarci kwanyarsa wanda yayi daidai da murɗawar cikin Munir ya fasa ihu.....

□□□GHT B-CLEAR,FEMALE CARE AND GANODERMA□□□

□□*BACK TO VIRGIN KIT* *(SABON BUDURCI)*

Assalam alaikum Mata albishirin kuƤƤga abin da kuka Dade Kuna mafarkin samu ya samu□□

□□Abin nema ya samu ,Kowacce mace aduniya tana mafarkin sake kasancewa virgin

□□Ina manyan Mata da suka hayayyafa😁

□□ina zawarawa masu shirin aure😍

□□Ina budurwa da iftila'i ya fadawa a yayin tsallaka rame 😢

□□Ina Mai jego da keso ta dinke ta game tsaf ciki da waje❤

□□Duk ku marmatso kusa ga GHT back to virgin set na kawo muku ,magunguna ne namu na gargajiya bana bature ba

□□Kuma Sha akeyi ,insha Allahu muddin kikayi amfani da wannan Kayan Zaki dawo da martabar ki ta farko

□□Sai kin gwada za ki tabbatar da hakan.

Sisters no 08142506271 mmn Khadeejah sai najiku

ZAWARCI

BOOK2

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI□✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

Shimfiɗa : A kowacce irin rayuwa ta ƙunci Allah yana kawo sassauci,haka duk yadda shugaba yake azzalumi sai an samu mai taka masa burki wanda bai tsoronsa.Hakan ta kasance a cikin wani ahali inda mayya ce ke mulkarsu take baza mulkinta na tsawon shekaru goma sha uku a duniya,wanda hakan ya faru ne a bisa yarjejeniya ruhin bangon gidan da ta ci nasarar damƙewa.A ƙoƙarin ganin ya samu lafiya ahalin gidan suka haɗe igiyar ZAWARCIn da sune da kansu suka tsinke igiyar auren mayyar matar har ta fita gidan,sai kuma ta dawo a karo na biyu a rayuwarsu inda ta ɗauki azabar duniya ta ɗora musu sai dai kash a lokacin da ba ta yi zato ko tsammani ba tauraron gidan ya haska tare da haske dukkan wani tsoho da sabon tuggunta.....

 1_2

Tun tasowa ta duniya ban san mi kalmar farinciki take nufi ba,zubar hawaye ,damuwa,ƙunci, ɓacin rai su ne suka yi wa rayuwarmu ƙawanya Ni da mahaifiyata sai kuma ɗan uwan tawaicina wanda na kasa banbance cikin wane jinsi zan saka shi .‘ Mutum ko aljan? ’Ita ce tambayar da nake yi wa kaina a kullum in na ci karo da zubin halittarsa wacce ke kama da ta mutum wani sashen yayin da kuma wani zubin sai ya rikiɗe ya zama tamkar dodo.

Sunana Baseerat,yʏa ga wata raunataciyar bazawara wacce tun bayan rasuwar mahaifina take ZAWARCI kamar yadda nake ji a gun Gwaggo Habibah ko sau ɗaya babu wanda ya taɓa nuna ra'ayinsa a kanta ballantana a kai zancen wani

auren.Fara ce ni sol marar ƙiba,idona blue ne kamar na mage ina da dogon gashi wanda da zarar yayi tsayi Gwaggo Hajara ke saka almakashi ta datse shi.A shekaruna na goma sha uku a duniya ban san mice ce rayuwar islamiyya ba sai boko wacce tsabar ilimina da ƙwazona yasa ake min ƙetaren aji ana kai ni na gaba.

Kamar yadda Gwoggo Hajara ta sunnanta wa duk a halin gidan ,kiran sallar farin duk muka fito kowa ya soma aikin da ta raba masa.Shara shi ne aikina,hakan yasa na ɗauki tsintsiya don somawa amma raunataciyar muryar mahaifiyata ta katse min hanzari “ SEERAT je ki ɗauki kallabi ki saka sannan don Allah ki kawar da idonki kan bishiyar mangoron can ban son ganin kina wannan kallon nata kamar tv ”

Na sakar mata murmushi kafin na je na ɗauko kallabin na ɗaura a kaina,sharar na soma tun daga ɗaukuna har na zo tsakar gida na soma.Sai dai an ce mai hali bai fasa halinsa,ina zuwa kan itaciyar da suke kira da ta mangoro na yi tsaye ina kallon ta.Eh zahiri ta mangoro ce,amma tun ranar da na yi birthday na 13years ta sauya min nake ganin wasu abubuwa daban, na ban tsoro da kuma ban sha'awa.Ban san mi zan fassara abin tsoron da nake gani ba,amma a can ƙasan zuciyata sai nake jin ana kimsa min cewa ‘ wannan shi ne ruhi’ tambayar da nake yi wa kaina a duk lokacin da tunanin nan ya zo min sai na ce ‘ to ruhikan su wane ne?’ banda amsa hakan yasa na ci gaba da kallo.A cikin jerin ruhikan da suke a ɗaure akwai ƙwaya ɗaya da nake ganin kamar ya fi su shan wahala sai dai tunanin in cece su ma bai taɓa zuwar min a kwanya ba.Da sauri na gaggauta na ida share gidan kafin na je Toilet na soma wanka,fiye da awa ɗaya ina tsaye gaban shower ruwa na dukana amma ko kaɗan ban gamsu cewa jikina ya fita ba .Bandejin da aka naɗe min hannuna na hagu na duba kamar kullum yau ɗin ma bai jiƙe ba,ina mamakin dalilin da yasa ruwa basa jiƙa shi tun da na taso na gansa a haka kuma har yanzu Mama ta ƙi min bayani akai.

“Seerat ki fito haka ko kin manta za ki kai niƙa ne?” Mama ta faɗa daga can bakin ƙofa,da sauri na jawo towel na fito.Ta ja dogon numfashi lokacin da idonta suka sauka kan hannuna na hagu,“ ki yi sauri ki shirya ki fito za a ci abinci” ta faɗa tare da fita,kai kawai na jinjina kafin na je na buɗe drower kayana na zaɓo riga da wando ina gama sakawa na fito.Da mugun sauri na rumtse idona ganin yadda Gwaggo Hajara ke sa ƙafa tana taka cikin ɗan uwana BASHEER,“ za ka sake hawa kan kujerata? ” cikin wuya ya ce “ a'a ba zan sake ba Hajiya ki yi haƙuri don Allah ” ƙafa ta sa habre masa baki kafin ta je ta zauna.

Duk wannan muguntar da take yi kan kowa na falon a ƙasa yake hatta Daddy wanda a yanzu ya koma ƙarƙashinta.Muna haɗa ido ta saki murmushi tana mai cewa “ ƙaraso mana” a kaf cikin gidan ni ce take ɗan rage ma shi ma na wani lokaci ban san dalilinta na yin haka ba amma daidai da ƙwayar zarra ban taɓa jin ɗigon ƙaunarta ba.

Dakyar na ja ƙafafuwana na isa gun Basheer wanda ya kasance mai rauni,tuni bacci ya ɗauke shi daga wannan dukan da ta yi masa.Na zube a ƙasa tare da tallabo kansa na ɗora a cinyata kamar mai koyon magana na ce “ Basheer?” idonsa ya buɗe farare tasss babu ɗigon baƙi amma sam ban ji tsoro ba,na ce “ tashi ka ci abinci ” ai kuwa ya tashi zaune.Da sauri na je na ɗauko plate ɗin da Anty Murjanatu ta zuba masa abinci,wanda haka tsarin yake ita ce mai zuba abinci ga kowa.Tamkar wani yaro haka na soma basa abinci a baki sai da ya cinye tasss ya ce “ ban ƙoshi ba” sanin sau ɗaya tak mutum ke da alhakin cin abinci yasa na miƙe na ɗauko nawa na soma basa shi ma ya cinye ya ce “ SEERAT ban ƙoshi ba” na haɗiye wasu yawu kafin na shafi gefen fuskarsa da hannuna na hagun sai kuma na yi saurin janye shi sakamakon wani azababen zafi da na ji tsakiyar tafin hannun na yi min.

“Ina son ki ƙanwata” ya furta yana min murmushi sai na ga yayi min kyau,“ ka kula da kanka zan je wurin niƙa na dawo” na faɗa tare da tashi na fita can waje na ɗauki ƙaton bokitin da aka zuba masara.

Babu nisa na isa na ajiye nawa kan layi kafin na samu wuri na zauna,sai dai ban wani jima da zaman ba na lura yadda tururuwa ke wani faman zagaye ni ta ko ina.Ido na ƙanƙance ina kallonsu,irin abin nan da na yi wa laƙabi da ruhi nake gani a tattare da kowacce turuwa.Kamar wacce ta je gidan kallo haka suka dinga yin wani abu kamar masu son bani nishaɗi,ban san lokacin da na soma murmushi ba musamman da na ga jikinsu na fitar da wani haske.

Na shagala sosai cikin shauƙin nan na ji muryarsa kamar daga sama,“ mi kike yi a nan?” da wani irin razani na ɗago don a duk duniyar nan in akwai wanda nake tsoro to bayansa yake.Murya na ɗan rawa na ce “ niƙa na kawo” ya dubi inda ake niƙan ya ce “ kuma kika zauna a nan alhalin har ya kashe injinsa?” yana min tambayar ne yana kallona da shegun idonsa masu kama da na masu jin bacci.

Murya na ɗan rawa na ce “ Yaya Khaleed ban san an gama ba” ya wani kawar da kai gefe ya ce “ tashi ki ɗauko ki wuce gida” jikina har rawa yake wurin tashi tsaye ina kuma mai kallon ƙasa sai na ga dukkan tururuwar ta ɓace.Sai da na je zan ɗauko ne na tuna ban karɓo kuɗin ba ashe,ina fitowa kuwa mai niƙan ya wani taso yana tambaya ta.Khaleed da ke tsaye shi ne wanda ya bayar sannan ya tiso ƙeyata muka kamo hanyar gidan,“ wannan kayan ban son ganinki da su,a yi mutum kamar

yʻar arna kullum da riga da wando? Wai wa yake saya miki su?” kai tsaye na basa amsa da “ Hajiya ” yayi wani ƙyaci kafin ya ce “ in kin shiga ki gaishe mini da Mama” na juyo da sauri ina dubansa,bayan tsoronsa da nake akwai wata muguwar ƙaunarsa da sonsa da nake ji a tsakiyar raina.

Ya kawar da kai ƙila don ya ga idona taf da ƙwalla,“ ki shiga mana ai jibi weekend za ki je can gun Ammy ” sai kuma ya kamo hannuna ya saka min kuɗi a ciki ya juya yayi tafiyarsa sai da ya ɓacewa ganina sannan na shiga gida.

Wanki na tarar Mama na yi wannan yasa bayan na kai garin kitchen na fito nan tsakar gida na kama mata ,kamar wasu kurame haka muke wankin.Can na katse shirun da cewa “ Mama don Allah ki bani labari mana,mi bishiyar mangoron can ke yi a tsakar gidanmu tun da ba shan yʻayʻanta ake yi ba?” wani irin kallo ta yi min ba tare da ta ce komai ba.Na tsaya da wankin na ce “ please Mama ki sanar da ni mana,na yi miki alƙawari babu wanda zan sanar ma ”

“Je ki cikin gida” ta faɗa ranta a ɓace,sai kuma na ji babu daɗi na ce “ ki yi haƙuri”

“Tashi ki bani wuri” ta yi min tsawa hawaye na zubo wa kan kumatunta,maimakon na yi yadda ta ce kawai sai na faɗa jikinta na fashe da kuka.

“Iyeee! A cikin gidan nawa ake koke-koke kamar an yi mutuwa?” Gwaggo Hajara ta faɗa wacce ta fito cikin wani rantsatsen less,da sauri na janye daga jikin Mama ita kuma baiwar Allah ta wanke fuska tare da soma bata haƙuri.Cike da tsanar Hajara na miƙe zan wuce sai kuma ta tsayar da ni “ fita za mu yi da ke,yau baƙi zan yi” na juyo na dube ta kawai kafin na bar ta nan tsaye shaye da mamaki.Haka na shige ɗaki na ci kuka kafin na shiga toilet na sakarwa kaina shower,yin haka ba ƙaramin daɗi yayi min.Tsawon wuni ina toilet ina wasa da ruwa yanzu ma muryar Mama ce ta fiddo ni waje sai dai wannan karon ba ita ɗaya ba ce har da wata mata wacce ita ma kallo ɗaya za ka yi mata ka fahimci damuwa ta aure ta.

“ Zo ki gaishe da Tantinki Sakeenatu,tun kina ƙarama ta bar Zinder suka koma Maraɗi sai yau kuma da ta zo” cewar Mama,gaishe ta ɗin na yi ta amsa tana kallon hannuna tare da tambayar Mama “ har sai yaushe ne za ki kwance mata ƙyallen nan ?” Mama ta kalle ni da sauri ta ce “ Baseerat fita waje” hakan da ta yi ne yasa na fahimci tabbas akwai wani ɓoyyyen sirri a tattare da naɗe min hannu da aka yi da ƙyalle.

Fita na yi zuwa falo na ci karo da wasu yan mata biyu,ɗaya a takure ɗayar kuma cike da walwala sai cin abinci take.Muna haɗa ido ta jefo min harara tare da ƙwala kira “ Mamaa???” sai ga Hajara ta fito daga kitchen tana tambayar ta lafiya.

“Ita wannan ba ta iya gaisuwa ba ne sai kallo? Dubi sai ka ce ba rainonki ba ya na ga haka ?”

“Ke da kin san komai ai kullum kina ganin yadda muke ta fama da ita,sai dai nan gaba ƙila a dace”

“Ko a bani ita?”

“Ke da kike da Ma'idah? Hum ! Bari dai zan nuna miki wani abu ma ”

Yanayin yadda suke magana sam bai nuna alamar yau ne suka ga juna ba kamar ma kullum suna tare,sam irin wannan zumuɗi ko yanayi bai nuna ita budurwar baƙuwa ce ba.Kawai shiru na yi ina nazarinsu da kuma saka ido a kansu,haka kawai nake jin lokaci yayi da zan ƙwatar mana yanci sai dai ban san ta yaya ba.

“ Baseerat kin ga autana Munira ko? Yau suka zo ita da uwar riƙonta” Gwaggo Hajara ta faɗa ƙila don ta ga ina kallonsu, murmushi kawai na yi ina jin hanjin cikina na yin ƙugin yunwa.Sai bayan ita da Munirar sun bar falon ne na zauna tare da ce ma ɗayar “ ya aka yi ke ba ki ci abinci ba?”

“Ai mun ci yanzu” ta bani amsa,da mamaki nake kallon ta don dai ni ban ga ta ci ba.“ Munira ta ci mana” ta ƙara jefa ni cikin cakwakwalin cakwakiya,ƙaton plate ɗin da Munira ta ci abinci na duba sai na ga duk ta cinye tulin abincin nan.Ina da abin faɗa amma na yi shiru tare da nuna kamar ban gane ba,na zauna na zuba abincin a plate yawuna har tsinkewa suke ina ƙoƙarin saka hannu abincin da ke cikin plate ɗin ya rikiɗe min zuwa wani abu daban.A tsanake nake kallon yadda shinkafa da naman da ke ciki suke motsi kamar masu rai, na dubi ɓangaren da take zaune sai na ga ita ma ni take kallo na ƙirƙiro murmushin ƙarya na ce “ ko kin ci?” kai ta girgiza min ,sai na miƙe tare da ɗaukar plate ɗin na ce “ ok bari na koma daga waje na ci in na gama zan zo mu yi hira” ba ta ce komai ba na fice ban zarce ko ina ba sai bakin bishiyar mangoro.Rame na haƙa na zuba abinci ,ko kafin na kai ga mayar da ƙasar abincin ya ɓace wayam sai wani sautin tauna abu da nake ji kunnuwana na zuƙo min.A nan take tsoro ya kama ni,da mugun sauri na rufe ramen na koma ciki hatta yunwar da nake ji ta ɓata.Kasancewar ban sha ko da ruwa ba ne yasa kawai na miƙe da azumi,ko da aka kira sallah Mama ta tanada min abin da zan ci a tare da Basheer muka yi buɗa bakin kafin mu yi sallah.

Da dare aka yi tuwon tuƙe ne aka yi,haka aka zuba ma kowa a plate duk muka soma ci.A tare suka yi wani ihu Munira da Gwaggo Hajara,kafin kuma duk su dafe ciki .Kallon kowa ya koma kansu,Hajara ta yi ƙarfin halin tashi ta shiga kitchen tsawon lokaci kafin ta fito da ragowar garin tuwon ta jefo min tambaya “ uban waye ya biya kuɗin niƙan nan?”

Hantar cikina ce ta kaɗa sanin waye ya biya,wanda a duniyar nan Gwaggo Hajara babu wanda ta tsana irin Khaleed.Muka kalli juna ni da Mama wacce da dukkan alamu tana tune da ba ta bani kuɗi ba kafin na fita,“ ke don ubanki ba ki ji ina tambayar ki ba?” ta sake jefo min tambaya,murya na ɗan rawa na ce “ Khaleed ne” ban rufe baki ba Gwaggo Hajara ta yo kaina ta soma jibgata kamar wacce Allah ya aiko.Da wani mugun gudu na fita a guje ina kuka,ƙafata ko takalmi babu na isa gidan Hajiya kakar Mamana inda a can ne kuma Gwaggo Habibah da Khaleed suke zaune.

Kamar wacce aka jefo haka na faɗa falon,duk suka wani miƙe suna tambaya ta lafiya ban ba su amsa ba sai jikin Khaleed da na je na faɗa .Ina jin lokacin da ya saki littafin hannunsa bai shirya ba tare da ƙoƙarin cire ni daga jikinsa,“Allah kyauta ya kawo mana ƙarshen masifar nan” cewar Hajiya tana mai barin wurin, Gwaggo Habibah ta amsa da “ Amen ” ita ma ta bar falon,sai a lokacin na ji muryar Khaleed ƙasa-ƙasa “ SEERAT cika ni don Allah sai ki faɗa min abin da ke faruwa” dakyar na sassauta riƙon kafin cikin kuka na labarta masa komai,a ƙarshe na ce “ Yaya don Allah kai ka san maƙasudin wannan lukutar masifar da muke ciki? A yi mace kamar rainon fir'auna sam babu imani a ƙirjinta? Kuma wallahi ina ma zargin kamar bokan...” da sauri ya kai hannu ya toshe min baki tare da jawo ni izuwa waje ya ce “ zo na baki labarin abubuwan da suka faru shekaru goma sha uku da suka wuce,a lokacin kina ƙarama ni kuma ina ɗan shekara goma sha haka,an yi abin a gaban idona a tunaninsu ba zan iya riƙe lamarin ba”.....

Littafin kuɗi ne,na ɗaya da na biyu dukkansu 500 kawai za ki biya Hajiya .In kin shirya biyan kuɗin karatunki ki tuntuɓe ni a lambata ta WhatsApp +22795045822

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

ZAWARCI

BOOK2

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

Last 3_4

Zama na gyara ina kallon Ya Khaleed da yanayin fuskarsa ta canza ta cika da ƙunci,cikin wata irin murya ya soma yin magana “ a wani yammaci ne gidanmu ya shiga wani rikitacen yanayi mai wuyar fassara,ga abun almara da ya faruwa.Ba a taɓa shuka mangoro ba,kawai wayar gari muka yi muka ga ƙatuwar bishiyar a tsakar gidanmu.Abin da zai baki mamaki a cikin lamarin nan shine duk wanda yayi tozali da bishiyar sai ya ji sha'awar shan yayanta,Munir shi ne gawar farin wanda ko awa ɗaya ba a yi ba da ya sha mangoron ya baƙunci lahira.Na biyu kuma DADDY ne,ya sha shi kenan ya yanke jiki ya faɗi abu goma da gomiya tara duk suka caɓe mana.A taƙaitaccen lokaci aka kai Munir gidan gaskiya,yayin da Daddy aka wuce da shi asibiti.Tun gwajin farko likitoci suka tabbatar da lafiyarsa lau,wannan ya saka Ammy Habibah cewa a dawo gida .Hum! Abu na farko da ta yi shi ne kiran Sarkin Mayu ,da ya zo ya soma yin abubuwansa maimakon su yi aiki ga Daddy jaririn anty Murjanatu ne ya soma kuka yana magana abin da hankali ba zai ɗauka ba kenan ta ya jariri da ko sunansa ba a yi ba zai yi magana? Ita ce tambayar da duk muka yi,babban rashin sa'ar da aka yi shine a ranar nan mijin Murjanatu ya dira gidan duk abin da ya faru a gaba yana zaune aka yi su.Ciki kuwa har da mutuwar jaririn wanda ba kowa ya ci galabar kashe shi ba sai Munira,a wannan ranar Anty Murjanatu ta yanki ticketin ZAWARCI a nan take ba a wani ɓata lokaci ba mijinta ya sake ta” sai kuma yayi ɗan shiru yana kallona,na ja ajiyar zuciya na ce “ shi ne mafarin ZAWARCInta ashe,to shi kuma Daddyn ya Kuka yi da shi?”

“Sarkin Mayu ya tabbatar mana cewa ba iya kurwarsa ba ne kawai aka damƙe a'a ana gaɓar da aka soma cinakin ruhinsa,muddin ba a nemi wacce ta yi sanadiyar haka ba to zai mutu,mutuwa kuma ba irin wannan normal ba a'a za a tura shi can ɓoyayyar duniya ne.Ammy Habibah ita ce ta fi kowa fahimtar abin da yake nufi ,shi yasa hankalinta ya fi na kowa tashi.Bayan an sallami Sarkin Mayu abu na biyu da aka gwada yi shi ne ɗora hannunki bisa kan Daddy….” na yi saurin katse shi da cewa “ hannuna kuma?” ya jinjina kai ya ce “ eh! An haife ki da alamar M a tafin hannunki wanda kuma babbar baiwa ce a duniyar Ruhaniya ”

“Mine ne Ruhaniya?” na jefo masa tambaya.

Ya ce “duk abin da ya shafi ɓoyayyar duniya mana,tsafi,asiri, Siddabaru da duk wani abu da kika san ya ta'allaƙa ne da Aljanu ko Fatalwa ”

Wani tsoro ne na ji ya kama ni,murya na ɗan rawa na ce “ kenan ni ma ina cikinsu? ”

“Ke ban son shirme fa,kin ga wannan hannun naki da aka naɗe da bandeji to shi ne ke ɗauke da kalmar M.Amfanin shi ne sarrafa abin da ya shige wa wasu duhu,sai dai a ranar sam ba ta yi aiki ba kin san dalili?” kai na girgiza masa,ya wani taɓe baki ya ce “ a ranar dai na ji Ammy Habibah na cewa aljanun da aka yi amfani da su wurin gina bishiyar mangoron nan da kuma na jikinki to kamar maƙiyan juna ne da aka yi yarjejeniyar kar wanda ya ƙara shiga sabgar wani.Fahimtar haka ya sa Ammy ta yarda ta zubar da makaman yaƙinta,kin san tana son Daddy sosai wannan yasa ta bazama neman Gwaggo Hajara”

“To ya aka yi ta san ita ce?”

“An kawo masu magani da yawa fa,kuma amsarsu guda ce wata bazawara ce ummul aba'isar cutar dole ita ce ke da maganin warakar.Sama da wata uku Daddy yayi cikin wannan yanayi,gangar jikinsa ba ta aiki in kika cire idonsa babu abin da yake iya sarrafawa.Hajiya kuwa kullum cikin kuka take,a ranar da ta yanke shawarar soma nema wa ɗanta magani ita malami ta kira yayi masa ruƙiya sai lamarin ya ƙara ƙamari bayan shanyewar jiki sai ƙuraje suka fesowa Daddy ko ta ina har bisa idonsa a doli ya zama makahon doli.Ganin haka sai Hajiya ta dakatar da ruƙiya wanda a lokacin baya na ɗauka shine daidai sai yanzu na fahimci babban kuskure ne,da ace sun dage aka kuma jure da zai samu sauƙi a hankali- a hankali” shiru ya sake yi,na dubi hannuna wanda aka naɗe ɗin da nake jin ya soma yi min ƙaiƙayi na ce “ ni kam sai yaushe za a cire min wannan abun ?”

Bai bani amsar tambayar ba,sai ci gaba da yayi da bani labari“ har ahalin sun fidda rai daga cimma nasara kwatsam sai ga Hajara ta zo gidan ,« in kuna so ya warke ku je ƙauyenmu» shi ne abin da ta faɗa ta juya bayan ta shaida mana sunan ƙauyen,a bisa sharaɗinta dukkanmu dole mu je can .Haka kuwa aka yi,a washegari aka samo doguwar mota bayan an saka Daddy duk muka shiga zuwa ƙauye.Tun a bakin ƙofar shiga gari aka tarbe mu har zuwa gidan mai gari,a can aka yi mana masauki.Tamkar wata sarauniya haka Hajara ta yi mana wuyar gani,sai da ta bari yamma lis sannan ta zo.Ido cikin ido suka kalli juna ita da Ammy Habibah kafin ta ce « sharaɗina na farko shine za a naɗe hannun aljanar jaririyar can na har abada,na biyu kuma doli ki bar gidan Ɗayyabu,na uku za a mayar da aurenmu,na huɗu daga lokacin da Baseerat ta isa yaye ni ce nan ke da alhakin kula da ita da duk lamarinta,in kun yarda da wannan sharuɗan yanzu nan zan warkar da shi» babu wanda ke da wani zaɓi haka aka amince,abu na farko da aka yi wani boka ne ya zo ya naɗa miki wannan bandejin a hannu sannan ita Hajara ta bai wa Daddy wasu

ruwa ta kuma zuba masa su a jiki a nan take ya tashi zaune tare da soma kelaya aman wannan mangoro da ya ci.A kuma wannan lokaci aka ɗaura aurensu a karo na biyu,yunwar duk da muke ji yasa muka ci abincin da aka bamu ashe nan ɗin ma wani salon yaudara ne don ta damƙe zuciyoyinmu ne shi yasa kika ga har yanzu duk tsoron ta suke”

“Kai ba ka tsoron ta?” na tambaye shi ina ƙure shi da ido ,ya saki murmushi ya ce “ abincin da na ci ko minti biyar bai yi ba a cikina na amayar da shi,a wannan rana ne kuma Hajara ta ƙara yarda ni ne dodonta na yi mata nisa ita da makircinta.Kin ji mafarin ƙiyayyar da take yi min,ko da muka dawo nan Zinder Ammy Habibah ta haɗa kayanmu muka dawo nan gidan Hajiya ”

Furicin Hajara na tsoronsa yasa na ji sonsa ya ƙara huda zuciyata har na kasa riƙe kaina na ce “ zan so na aure ka Ya k...” ban kai ƙarshe ba yayi min wata irin tsawa wacce ta dawo da ni cikin hayyacina,ta tuna min cewa kurmuci Khaleed ne a gabana wanda nake mugun tsoro da shakka.

“Tashi ki je gida sakarya kawai” ya faɗa tare da tashi tsaye,jiki na ɗan rawa ni ma na miƙe na kama hanyar fita ina jin ya ja tsuki yana mai cewa “ don kina mahaukaciya haka kika fito babu takalmi a ƙafarki zo ki saka ko na Ammy ne”

Ina shafar ƙwalla na dawo na saka tare da ficewa,sai da na kawo har ƙofar gidanmu ne na lura ashe ya biyo bayana.Ciki na shige ina addu'ar Allah sa babu kowa falo,ai kuwa hakan ne da sauri na nufi ɗakinmu na buɗe ƙofa kenan zan wuce na yi wani uban burki saboda saƙar gizo-gizo da na gani mai faɗi .Hannuna mai bandeji na saka na cire sannan na shiga na maida ƙofa,idona ya sauka cikin na Mama.“Daga ina kike?” ta jefo min tambaya,“ gidan Hajiya ” na bata amsa ba ta ƙara cewa komai ba ta yi shiru.

“Ina Basheer ?” na tambaye ta ganin ban gansa a shimfiɗarsa ba,banza ta yi min wannan yasa na fahimci yana can wurin Gwaggo Hajara wato duk lokacin da na yi

mata laifi shi take hukunta wa saboda na ji zafi da raɗaɗi.Na kama handle kenan na ji muryar Mama na cewa “zo ki kwanta kar na ga kin fita”

Idona ya ciko da ƙwalla na ce “ Basheer fa?”

Ta kawar da kai gefe ta ce “ ai duk tsiyarta dai ba za ta kashe shi ba za ta barsa da ransa”

“Zan je...”

“Ki je ki kwanta na ce” ta faɗa cikin ƙaraji hakan yasa babu shiri na je na kwanta,duk labarin da Yaya Khaleed ya bani ya dinga dawo min a kai,yanar gizo-gizo kuma da na gani ta tsaya min a zuciya ban san lokacin da bacci ya ɗauke ni ba.Baccin da ya zamana shine farkon sanin wace ce ni,mace ce na gani da fararen kaya irin na Fulani tana murmushi tamkar yadda Madam ke yi wa ɗalibai karatu haka ta soma koyar da ni wani ilimin da ban san mine ne haɗina da shi ba.

```Wanzuwar mutum a cikin kansa shi ne abu na farko daga cikin sirri, asirin da ke bayan halitta yana da yawa har ma da kimiyya.A duniya ta Ruhaniya akwai mai kyau da mara kyau. A cikin wannan madaidaicin mahallin, idan ba ku yi imani da wanzuwar ruhaniya ba, zai yi muku wuya ku fahimci abin da muke magana a kai amma . Mu tafi kai tsaye gizo-gizo webs abubuwa ne da ake amfani da su a cikin Ruhaniya ,a cikin ingantacciyar hanya ko kuma marar kyau saboda yanar gizo-gizo ana aiki da ita a matsayin hanyoyin sauka ga masu sihiri,matsafa da dai sauransu. In matsafi ko Maye yana son leƙen asirin wani,ko kuma yana son cutar da wani ta hanyar yanar gizo-gizo zai iya ganin komai tamkar yadda Camera ke ɗaukar rahoto.

A duk lokacin da kuka ga wani abu wanda hankali ba zai ɗauka ba,ko kuma dai wani lamari mai naci da maimaici a rayuwarku.To a nan kamata yayi ku yi aiki da hankali,lamarin nan ba na lafiya ba ne ko dai ana son isar ma da wani saƙo ne ko kuma kai tsaye ana nuna maka rayuwarka na cikin haɗari.

Misali, gizo-gizo suna aiki ne kamar ɗan aike, waɗanda ke aiko da saƙonni daga nazarin bayanai ta abin da ba a gani, don nuna mana inda za mu inganta da kuma irin darussan da za mu iya koya.

Na koyi cewa ta hanyar gizo-gizo a cikin gidanku matsafa sun san duk abin da ke faruwa a cikin  jikinku da muhallinku ,a lokacin da mutum kuma ya ji idan yana tafiya yana jin tamkar yana ɗauke ko kuma ya ji kamar ya ratsa ta cikin yanar  gizo-gizo a fuskarka alama ce ta masu sihiri ko matsafa na haƙarka ko kuma ma tuni ka faɗa tarkonsu.Irin haka ne za ka tsinci kanka cikin matsoli da kuma rufewar duk
```

wasu al'amurranka.Abu na gaba kuma shi ne ku dinga cire yanar gidajenku don barin ta tamkar ka buɗewa maƙiyinka ƙofa ne da kanka.```

Sai bayan ta yi shiru ne na lura a wurin da na tsinci kaina ba ni ɗaya ba ce,har da wasu irin mutane masu kamar inuwa.Tuna ban yi sallar isha'i ba na farka daga baccin hankali tashe,toilet na shiga na yi alwala na zo na gabatar.Sai a lokacin idona ya sauka ga Basheer yana kwance a takure duk jikinsa yayi ja alamun dukansa ta yi,wani baƙin ciki ne ya turnuƙe ni zuciyata ta cunkushe sai na soma jin tamkar babu iskar shaƙa a ɗakin da sauri na miƙe na fita can tsakar gida.Itaciyar mangoron nan ce ta ɗauki wani mugun haske hakan ya bani damar ganin yadda take girgiza,kamar wacce ake tunkuɗa wa haka na soma tafiya har na isa gare ta.Ban yi wani tunani ba na laƙanƙame bishiyar tare da soma haurawa sama,kiɗa ne na soma ji yana tashi haɗi da muryoyin mutane a cikinsu na iya zaƙulo muryar Gwoggo Hajara da kuma ta Munira.A haka dai na isa can saman bishiyar,ashe abun mamaki na sama tamkar wata jaha guda haka can saman bishiyar yake lunguna ne kashi-kashi sai na rasa wacce hanya zan bi .Sautin kiɗan na soma bi har na isa ga dandamalin shaƙatawar ta mugaye,na laɓe ina kallon yadda suke sabgogi kamar wata sallah wasu sai rawa suke yayin da kuma na hangi Munira cike da baƙin ciki,gefenta kuma Gwaggo Hajara ce ke cewa “ mine ne don ki bayar da Ma'idah? Ina ce dai akwai sauran yʻan mata a duniya sai ki ƙara zaɓar wata ni da kaina ma zan nemo miki”

Munira ta ce “ Mama haka kullum kike faɗa ,kin ce a daren yau za ki bani Baseerat amma har yanzu ban ga kin samu ko da bayaninta ƙwaya ɗaya ne ba”

Hajara ta ɗan ɓata fuska kafin ta ce “ ban san mike faruwa ba amma tabbas na ɗora fa Camera a ɗakinsu”

Da ta ce Camera a nan take karatun da Bafulatana ta koya min ya dawo min,wato yanar gizo-gizo da na gani a ƙofar ɗakinmu aikin Gwaggo Hajara ce so take ta bayar ni ga yʻarta lesbian.Tunanina ne ya yanke sa'ilin da na ga an ɗauko Ma'idah an miƙawa wani dattijo ita inda ya soma magana “ kyautar Munira ta iso,ina sanar da ku cewa za a yi shagalin cinye abun sacrifice a can ƙauyenmu a bisa bishiyar magorona ” faɗar haka yasa na fahimci cewa shine mai garin da Yaya Khaleed ya bani labari,da wani mugun sauri na ja baya sakamakon ido huɗu da muka yi da wata tsohuwa da sauri na ruga a guje ganin ta nufo inda nake.Ina kawowa daidai inda zan bi na sauko kawai sai na yi tsalle don na dire saboda muddin na ce a hankali zan sauko tabbas sai ta cabke ni,ina ta jiran na ji na faɗa ƙasa sai kuma na ji wani sabon al'amari gani a tsaye cak cikin iska tamkar wata tsuntsuwa.A hankali kuwa na ji ƙafafuna sun sauka a ƙasa,abin da ya yi matuƙar bani mamaki kenan

amma na watsar saboda tunanin cinye Ma'idah da na ji suna yi.Ko da na koma ɗaki kasa bacci na yi sakamakon goshina da na ji yana ta zugi,ga wani ƙaton ƙurji da ya fito min tsakiyar goshin.A wahalce na miƙe na je na ɗauko madubi don ganin wace sarautar Allah ce ta fito min lokaci guda,cike da razani na saki madubin ya tarwatse sakamakon abin da idona yayi tozali da shi a bayana hakan kuma yayi daidai da ɗaukewar wutar lantarkin gidanmu.Na dafe gefen zuciyata ina jin tamkar za ta faɗo ƙasa,haka na ci gaba da zama cikin duhu har goshin asubah.Sai bayan na yi sallah ne ma na samu bacci ya ɗauke ni,“ innalillahi wa'inna ileyhi raji'un !” na ji muryar Mama a kaina a tsorace na miƙe ina zarar ido sai na ga ta yi baya da sauri,murya na rawa ta soma nuna waje “ wace ce ke sharar tsakar gida? Alhalin ga kuma ki nan kwance kina bacci?” sai kuma ta fita a guje ni ma na take mata baya,ina fita tsakar gida daidai lokacin wata iri na sak tana mai ɓacewa a gaban idona.Mama ta ja ajiyar zuciya ta ce “ sai ki tsora ta ni mana,ashe yanzu kika kwanta” sai ta wuce abunta ta bar ni da tunanin shin wace ce to wannan mai kama da ni.Ɗakinmu na koma na shiga toilet ina wanka,wani irin yanayi ne na ji a jikina tamkar iska ta kaɗa.Babu shiri na ɗaura towel na fito,ina tsaka da saka kaya Mama ta shigo a yanayinta zan iya fahimtar ba lau ba ta ce “ ki fito falo Gwaggo Hajara na son ganin ki” da to kawai na amsa.Bayan na saka kaya na fito,yadda na ga kaf alhalin gidan har da Daddy kawai sai na ji gabana ya faɗi,ban ida ɗimaucewa ba sai da muka haɗa ido da tsohuwar jiya wacce na gani a duniyar matsafa ina tsaka da tunanin mi ya kawo ta nan gidan sai na ji muryar Gwaggo Hajara na cewa “ Mamuh ga duka ahalin gidan”

Wacce aka kira da Mamuh ta wani tsuke baki tare da haɗe rai tana mai ci gaba da kallona,a yadda ta kafe ni ɗin yasa duk kowa ya maido dubansa gare ni a daidai wannan lokacin na fahimci tabbas abin da ya kawo ta gidan.Sai dai kafin ta kai ga yin magana goshina ya soma yin haske wanda kuma na yi imanin cewa normal mutum yayi kaɗan ya gansa sai iya su kaɗai mugayen kawai.Mamuh, Gwaggo Hajara da kuma Munira a tare a lokaci guda duk suka miƙe tsaye yayin da Ma'idah ta faɗi ƙasa ta soma kuka mahaifiyarta Sakeenatu ta nufe ta.Wani murmushin mugunta na yi daidai lokacin da wani matashin mutum ya shigo yana cewa “ Mamuh na gaji da jira a ƙofar gida shine na shigo”

Sakeenatu ta ce “ Abbas na shiga uku zo ka ga halin da Ma'idah take ciki bakinta na fitar da kumfa” a rikice shi ma ya nufi Ma'idar a nan take kuma na fahimci wato ɗan Mamuh ne ko kafin ya kai ga taɓar Ma'idah na yi amfani da hasken da ke fitar min a tsakiyar goshi na shaƙe wuyan Mamuh sai ga muryar Mamuhn raɗam a bakin Ma'idah ta soma yin magana.....

Littafina na kuɗi ne na baku BONUS na page ɗin book 2 yanzu kuma duk mai buƙatar ci gaba sai ya biya 500 ta wannan account 6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank sai ki turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822 in kin san ba ki shirya ba kar ki min magana.

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI□✍```
```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK2

5_6

Dukkan mutanen falon suka mayar da dubansu ga Ma'idah in ka cire ni da na kafe Mamuh da ido ina juya masarrafar furucinta.Tuni Ma'idah ta soma yin magana tana bayar da tarihin rayuwarsu tun tana yar ƙaramarta,amma kuma muryar Mamuh ce raɗam ke fitowa kai tsaye za a ce Mamuhn ce ke tonawa kanta asiri da kanta ta wani salo.

“Tun lokacin da Abbasi ya kawo min Sakeenatu matsayin matar da zai aura Allah ya ɗora min muguwar sha'awarta,na yi ƙoƙarin hana shi aurenta gudun kar mu haɗa mata da shi mu zo muna kishi.Da ace bai aure ta ba iya ni ɗaya kawai zan ci moriyar gangar jikinta,duk wata hanyar da na ɓullowa Abbasi amma sai da ya auro ta.Bayan auren sosai na yi ƙoƙarin kusantar ta amma abu ya cuttura doli na bi ta wani salon,ina bata waken da na tsafe sai na ce ta dafa mini shi ta wannan hanyar ce nake morar ta.Duk wannan bai ishe ni ba sai da na kwaɗaitu da yarta ba ma ni kaɗai ba har da Munira da kuma Hajara kai har da ma ƙanwata Rahamu duk muka shigar da ruhinmu cikin gangar jikin Ma'idah muna cutar da ita.Duk rashin lafiyar da take yi mune sila saboda ta wannan hanyar ce kawai Sakeenatu za ta dinga kashe kuɗin albashinta wurin saya wa yarta magani,ni ce kuma na hana Abbasi tallafa mata na juyar da kwanyarsa ya bar kula da su.Hatta canjin wurin aikinsa ni ce na tsara komai saboda nan Zinder na fahimci Sakeenatu nada alaƙa da wani tsabtataccen ruhi mai warware duk aikin da na yi a jikinta...” shiru Ma'idah ta yi ta

ƙi magana sai Mamuh da ke wani dantse haƙora,duk don kar ta sake faɗar wani sirri ne ni kuma na fi damuwa ma da shi sirrin wanda ba ta son faɗar.Cike da mugunta na ci gaba da matse mata maƙoshi wanda ya kai ta da kama wuyanta tana wani gurnani,“ kar ki kai ni bango! Mine ne haɗina da ke? Ina ce Hajara ce ta illata ahalinku to ki je can ki ji da ita ki bar ni haka zan tafi da ahalina ni ma” Ma'idah ta sake faɗa tare da soma yin kuka,a daidai wannan lokaci ne kuma Hajiya,Ammy Habibah da kuma Khaleed suka shigo falon da dukkan alamu Mama Safeenatu ce ta kira su .

Mamuh ta zube gwiwanta ƙasa kafin kuma muryarta ta ci gaba da fitowa a bakin Ma'idah “ Hajara ce ta sayar da mahaifar Habibah a gun matsafa shi yasa ba ta haihuwa,kuma hatta rashin auren Safeenatu ita ce sila ta yi amfani da mugun sihiri wanda ba Safeenatu ba hatta ɗiyan-ɗiyanta kai duk wani da ya fito ta tsatsonta asirin zai dinga biyayarsu ko sun yi aure sai ya mutu kaf zuri'ar Safeenatu cikin ZAWARCI za su ƙare...” tun da ta soma bankaɗo sirrin Gwaggo Hajara sai ta wani je za ta kama Ma'idah ban san ta yaya ba kawai dai na juya fuskata ɓangarenta sai kawai hasken goshina ya dabaibaye ƙafafunta ta faɗi timmm amma don ƙarfin hali irin na maye haka Hajara ta ja ciki ta rufe bakin Ma'idah.Na saki murmushin mugunta na saka Ma'idar ta gantsara mata cizo a hannu wanda sai da fatar hannun ta zaɓace,tsokar naman hannun Hajara sai ga ta kuma a bakin Mamuh tana tauna ta hatta jinin bakinta ya ɓata ba na Ma'idah ba.

Bayan ta cinye naman ne sai kuma Ma'idah ta ci gaba da yin magana yayin da Mamuh ke nuna ƙaton cikin Sakeenatu,“ hatta cikin da ke jikinki ni ce nan na hana shi zuwa duniya,in kun je asibiti kuwa ni ce ke ɓata abin scanning ɗin likitoci su nuna lafiyarki lau.Ki sani Sakeenatu na tsane ki! Ban ƙaunarki ,har abada ba zan bari ki haihu da Abbasina ba in kin ga kin haife cikin nan to tabbas cikin biyun nan ɗaya ya faru ko dai na mutu ko kuma kin yarda kin rabu da ɗana Abbasiiii” ta ƙarashe maganar cikin wani sauti wanda ya saka labulayen ɗakin tashi sama yayin da hotunan da ke manne a bango duk suka faɗo.

Mamuh ta wani miƙe a tsiyace tana juya ido ta ɗauki siffarta ta mugunta,fuskarta ta yi wani irin baƙi,gashinta ya koma fari ƙal ta buɗe baki ta soma yin wasu ɗalasiman tsafi tare da soma yin magana bibiyu da bakinta da kuma na Ma'idah duk furicin ke fitowa a kuma daidai Lokaci guda.

“Tun da kika yi silar tona min asiri zan kashe yaɗarki ke ma ki ji da baƙin cikin nan” ta yi furicin tare da fesar da wata wuta daga bakinta ta zuba jikin Ma'idah,amma abun mamaki Munira ce ta ƙwala wani uban ihu tare da faɗuwa ƙasa tana fizge-fizge.Gwaggo Hajara ma ta ɗauki siffarta suka soma yin dambe sai dai kash duk yadda ta ƙware wurin sarrafa tsafi Mamuh uwarta ce wurin mugunta a gaban idon kowa Munira ta mutu bakinta na fita da wata baƙar kumfa wanda ba komai ba ce illa ga powerta.

Da sauri na yi baya zan faɗi amma Ammy Habibah ta riƙo ni tana ce min “ sannu” kamar wata yarinyar goye na ƙanƙame ta ina cewa “ kaina ke ciwo ,kuma idona ban gani sosai”

“ Za su dawo normal” ta faɗa tana mai ƙara rungume ni tsam a ƙirjinta,tsawon kamar minti goma kafin na buɗe idona.Duk kusan kowa na wurin kuka yake, Sakeenatu ta kira ƙanwarta Nafisa wacce tuni ta yi aure har da yaranta.Babu ɓata lokaci ta zo gidan namu wanda ya zama kamar na makoki,ko da yake hakan ce ma duk da mutuwar ta Munira iya Gwaggo Hajara kawai ta damu da haka .

Nafisa na shigo wa Sakeenatu ta wani tashi da ƙaton cikinta ta je ta rungume ta tare da soma bata labarin komai.Ita kuwa inda Mamuh ta ɓingire tana bacci ta duba kafin ta mayar da duban ga Abbas wanda yayi zaman yaɗan bori yana zubar hawaye.

“Ba za a jira sai ta mutu ba,kawai Abbas ɗin ya sake ki wannan shine ya dace ” cewar Nafisa.

Abbas da firgici a fuskarsa ya ce “ wallahi ba zan iya sakin Keenat ba”

“Ya zama doli ka sake ni Abbas ,na gaji da jingilar cikin nan sama da shekara biyar ina ɗauke da shi ko dai CIKIN ALJAN (MRS SADAUKI) ne ai na isa haife shi”

Ammy Habibah ta dube ni ta ce “ SEERAT ya kike ganin wannan lamarin?”

Kai tsaye na ce “ ai zai sake ta ne yanzu nan kuwa,wa'adin auren nasu saura minti biyar kacal ” duk suka maido dubansu a kaina,cikin ɓacin rai Abbas ya nuna ni da yatsa ya ce “ ke ƙaramar matsafiya ba ki isa ki yanke min hukunci...” bai ƙarasa maganar shi ba Sakeenatu ta saki wani uban ihu tare da zubewa ƙasa.Kamar mai taɓin hankali haka ta cire rigar jikinta ta yi saura sai bra kawai,Abbas ya nufe ta da niyyar mayar mata da rigar amma yadda cikin Sakeenatu yayi wani shuuu ya ƙara girma da tsayi ya katse masa hanzari.Tamkar randar ruwa haka cikin ya koma sai zugurniya yake yana sama da ƙasa sai kace wanda aka sa ma kiɗa,ita kuwa sai ihu take tana “Abbas ka cece ni”

“Wallahi muddin yar uwata ta mutu kotu ce za ta raba mu,ka sake mana don jaraba ka ce ba za ka iya ba.Ni na fi kowa sanin Mamuh tun da a gaban idona ta zama macijiya ”

Lokacin da na ƙa'ide yana cika Abbas ya ce “ na sake ki saki ɗaya” rufewar bakinsa ta yi daidai da zubewar cikin Sakeenatu wanda ba komai ba ne a ciki sai zallar ruwa da jini.Haka suka dinga gangara suna kewaye Mamuh har cikin nata ya koma normal yayin da ita kuma Mamuh ta buɗe ido taram waɗanda suke sak na macijiya.

Cikin azaba take magana,“ kaicona ni Ladidi ga shi zan bar duniya ban shirya ba,Abbas mi yasa ka sake ta? Ina duk soyayyar da kake yi mata? Sanin cewa kana mugun sonta yasa muka yi yarjejeniya da baƙaƙen Aljanu sai ga shi abin ya zo ta baibayi.” a gaban kowa Mamuh ta soma rikiɗa daga mutum zuwa macijiya mai cike da rauni,da bala'in gudu ta fice ta bar falon ta haye bishiyar mangoro.Ko minti biyu ba a yi ba aka kira wayar Abbas ana shaida masa mutuwar Mamuh daga can ƙauye,ya fita kamar wani zararre.

Sai a lokacin kuma duk muka tsurawa Hajara ido,a kunyace ta sunne kai.Cike da iya sarrafa tunani na yi amfani da muryar Daddy ya ce “ Hajara na yi miki saki ɗaiɗaya har uku na tsinke duk igiyoyin uku na sake ki ɗaya,na sake ki biyu,na sake ki uku” a razane ta ɗago ta dube shi kafin ta ja gawar Munira ƙiiiii ta fice,ita ma ta bishiyar magoron ta bi wanda kuma a nan take ya ɓace ya bar tsakar gidan.

Tamkar yadda in an kashe wutar murhu biɗiɗin suraci ke tashi haka gidanmu ya ɗauki wani yanayi duk wata iskar guba ta soma ficewa.Khaleed ya tako zuwa inda Daddy ya zube ya soma yi masa karatun Alkur'ani,daga ƙarshe kuma ya samu kofi da ruwa yayi masa ya sha.Ya ja wata doguwar ajiyar zuciya ya ce “ ita waccan har yanzu tana kwance ba ku duba ta” yana nufin Ma'ida ,kallonta kawai na yi ta tashi zaune suka rungume juna ita da mahaifiyarta .Da za su tafi ne na ce “ ya kamata a kai ta asibiti a duba ta,gangar jikinta duk a gajiye take” Sakeenatu ta yi godiya har sun kai bakin ƙofa na ce “ keee!” Ma'idah ta yi wani irin juyo wa,na gyara tsayuwa na ce “ ke mi kike jira da ba za ki fitar da ƙazamin rubinki a jikin ɣar mutane ba”

“Dama yanzu zan tafi” ƙanwar Mamuh ta faɗa wacce ita ɗaya ta yi saura,babu shiri kuma ta fice daga jikin Ma'idah.Na sakar mata murmushi kafin su tafi,muna haɗa ido da Khaleed na ga yana min wani kallon mai saman ruwa.Sai na ji duk babu daɗi,na sunne kai kawai har suka bar gidan bai min kallo mai kyau ba ballantana magana mai daɗi.

Bayan sallar magarib ne na ɗauko jakata ta makaranta na soma duba tsofin littattafaina,saura kwana uku mu koma makaranta ban san mi yasa ba wannan karon sai na ji ban zumuɗin zuwa ƙila kuma don na faɗa soyayya ne.Ina tsaka da gyaran Mama ta shigo ta zauna kusa da ni ta yi shiru can kuma ta yi gyaran murya ta ce “ SEERAT mun yi magana da Ammy Habibah ta ce ya kamata a kai ki can ƙauye wurin dangin mahaifinki”

Na ɗago na dube ta na ce “ amma ba a nan dangin suke ba? Kaka ce kawai fa ke ƙauye ”

“Eh wurin ta za ki je dama,gobe tun da safe Khaleed zai zo sai ku tafi tare tun da shi ya san gidan”

Na ja wata ajiyar zuciya jin tare za mu je da shi,ta shafi gashina ta ce “ da buƙatar ki je can ɗin tun da an ɗauki lokaci ba ki je ba,kuma abin da ya faru yau kwanyarki na buƙatar sarari”

“To Mama mi yasa ba za mu je da Basheer ba?”

“A'a shi ba yanzu ba ƙila dai bayan jarabawarku”

“To Allah kai mu”

“Amen” shiru ce ta ratsa kafin ta je ta ɗauki wata jaka ta saka min kayana,ko da muka ci abinci muka yi sallah sai na ɓingire da bacci.Washegari tun bayan sallar asubah na yi wanka na shirya tsaf cikin riga da wando jeans baƙi da riga fara.Ƙarfe bakwai na safe sai ga Khaleed kuwa ya zo,Anty Murjanatu ce ta zuba mana abinci muka ci kafin Mama ta yi mana rakiya har bakin ƙofa inda mai adaidaita ke jiranmu.Har da kuɗi ta bani sannan muka shiga dukkanmu a baya,ina lura yadda Khaleed ke yi min wani kallon ƙasa-ƙasa fuskar nan tasa a murtuƙe na san duk hakan bai rasa nasaba da yanayin shiga ta.A haka dai mai ɗan sahun ya kai mu tashar mota,bayan Khaleed ya shaida ƙauyen da za mu je aka nuna mana motar da za mu shiga.Yadda abin yake babu tsari maza da mata ya saka shi jan tsuki ya fi shuren masaki,kujera ta kusan window ya umarce ni da na zauna shi kuma ya zauna gefena.Muna nan zaune har motar ta cika aka soma tafiya ,karen direba ya soma karɓar kuɗin mutane har ya zo gare mu yana kallona ya ce “ yʻar baturiya a kawo kuɗin mota” cike da masifa Khaleed ya soma magana kafin ya biya kuɗinmu,ya juyo yana hararena ni dai ban ce komai ba sai jakata da na ƙanƙame.Ana ta kwasar gudu da mu tun ina kallon hanya har na gaji na soma jin bacci,ban san ya aka yi har na faɗa jikin Yaya Khaleed ba sai da na farka na ga yadda duk na kwanta a jikinsa.Tuni kuma an kawo mutane na ta sauka,jakar hannuna ya karɓa yana cewa “ tashi mu fita” sai da na miƙe ya saka ni gaba kamar wata yʻarsa sannan muka fito ɗin.Daga nan tafiyar ƙasa muka yi har zuwa gidan Kaka mahaifiyar mahaifina,shi yayi sallama ta yi saurin ajiye moɗar hannunta wacce take shan ruwa ta amsa murmushi kan fuskarta.

Tabarma ta shimfiɗa mana a inuwae kurna,haka kawai na ji kaina na ciwo ba tare da na san dalili ba.Bayan an yi yʻan gaishe-gaishe ne ta bayar da umarni a kamo kaji an yanka mana amma kafin nan sai aka kawo mana fura har da ƙanƙara.Khaleed ya ce “ Kaka wai mi yasa kika fi son ƙauyen nan fiye da can cikin gari”

“Gidanku ! Nan ɗin ne ƙauye? Ga wuta ga pampo to mi muka rasa da zan yi ta zama can nesa ga dangina? ”

Yayi murmushi kafin ya ce “ har yanzu gargajiya na burge ki dai”

Daga nan ban sake sanin abin da suka tattauna ba sakamakon wani bacci mai nauyi da ya ɗauke ni mai cike da abubuwan ban al'ajabi.Ko da na farka ban ga Khaleed ba sai Kaka,ta sakar min murmushi ta ce “ kin sha bacci har zanen tabarma ya fito miki gefen fuska”

Na dafe kaina da na ji ya ɗan rage ciwo na ce “ yunwa fa nake ji har yanzu ba a gama dafa kaj…” sauran maganar ce ta maƙale min a maƙoshi sakamakon ganin Yaya Khaleed ya fito daga banɗaki daga shi sai gajeren wando,fafaɗen ƙirjinsa mai yalwar gargasa sai wani sheƙi take ,sajensa da maidaidaicin gemunsa na ɗigar da ruwa.A yadda yake a haka ɗin nan za ka rantse ya kai shekara talatin ,mugun kallon da ya watso min yasa na yi saurin ɗauke idona a kansa.

Kaka ta ce “ ke ma da wankan kika yi jikinki ya wartsake ki fitar da gajiya” da “ to zan yi” na amsa ina mai wasa da yatsun hannuna sai da na tabbatar ya bar farfajiyar gidan sannan na ɗago kai nan kuma na yi arba da wata yar matashiyar budurwa ta shigo hannunta riƙe da allo da dukkan alamu daga makaranta take.

“Samira zo ga yar uwarki ta zo daga zinder,yar gidan marigayi Bashir ce” Kaka ke faɗar haka,ta waro ido ta ce “ wai yan biyu?” sai kuma ta nufo ta zube kan tabarmar tare da rungumo ni.Mun gaisa sosai kafin na shiga wanka bayan na ɗauki zanen Kaka,ko da na gama wankan na yi ɗaurin ƙirji na fito.Yaya Khaleed na gani a zaune yana sharɓar romon kaji,muna haɗa ido ya kawar da kai.Ɗakin Kaka na shiga,Samira ta miƙo min wasu riga da siket nata na atamfa na saka ba su wani ɗame ni ba tun da ta fi ni yar ƙiba.Bayan na fesa turare muka fito,a tare muka ci abincin kafin Khaleed ya ɗauko wata hira da ta ja hankalina.

“Kaka wai ya zancen rijiyar nan har yanzu ba a samu jarumin da ya ƙara ɗebo ruwan cikinta ba?”

Kaka ta ja baki ta ce “ to wa zai tarar aradu? Duk fa ƙauyen nan an yi itifaƙin cewa rijiyar Mayu ce, wannan ya saka duk wacce ma aka gani kusa da rijiyar yɗan gari ke gudunta a cewarsu mayya ce.Kwanan baya ma wasu yɗan buɗa ido sun zo,duk da an yi musu bayani fa haka suka je can bayan gari inda rijiyar take,maganar da nake yi ma bayan Camera babu abin da aka tsinta.A washegarin da abin ya faru kaf illahirin ƙauyen nan ya turniƙe da ƙamshin nama,wanda babu shakka Mayu ne ke shagalin yɗan buɗa idon nan”

Khaleed ya shiga yin dariya ya ce “ wannan fa da Film aka yi da tabbas sai an samu kuɗi,kai mutanen ƙauye akwai canfi sosai”

“Au wai ba ka yarda ba? Hum ! ” a nan duk suka bar hirar yayin da ni kuma ta tsaya min a rai,da yamma bayan Samira ta ja ni mu je makaranta ana tashe mu na ce “ Ni kam Samira wai duk abin da Kaka ta faɗa gaskiya ne?”

“Eh sosai ma ai ƙauyen nan muna ganin abin al'ajabi ”

“Ni kam ina son ganin rijiyar nan” na faɗa .

Ta ci wani uban burki ta dafe ƙirji ta ce “ rufa mana asiri”

Na yi yɗar dariya na ce “ kawai ganinta nake son yi ko daga nesa ne” sai ta ja ajiyar zuciya ta ce “mu je na nuna miki” haka muka nufi bayan gari har muka zo wani wuri inda aka kewaye shi da ƙaya,sai na ga ta ja ta tsaya tare da cewa “ daga nan kawai aka yarje a tsaya in kika ƙanƙance ido za ki hango wani dogon bututu to gefensa rijiyar take”

A hankali na ƙanƙance ido har na yi tozali da rijiyar mai ɗauke da baƙin murfi,na ce “ yanzu nan an hana shiga?” ba ta bani amsa ba sai ja na gefe da ta yi muka yo baya.

Muna isa gida Kaka ta tambayi ina muka tsaya amma Samira ta ƙirƙiro ƙarya ya faɗa mata.

Sam abincin daren da aka aiko mana iri-iri daga yɗan uwa da abokan arziki bai gabana,wani irin abu nake ji ya danne min zuciya.A haka duk aka shiga bacci,ni

kuwa ganin haka yasa na sulale na fito kamar wata aljana hanyar tsit take babu kowa amma na doshi wurin rijiyar nan har na isa ,yar siririyar hanyar da za ta sada ni da ita kai tsaye na bi har na zo daf da rijiyar.Hannuna na hagu na saka na buɗe murfin,wani turniƙin hayaƙi ya daki fuskata yayin da kuma mugun iskan da ya fito yayi cilli da ni na faɗa can gefe amma don ƙarfin hali haka na yunƙura na sake komawa.Dariya na soma ji ,sautinta na fitowa daga can ƙasan ƙolin rijiyar ga kuma wata murya cikin raɗa tana kiran sunana haɗi da fuzgo ruhina na ɗauki ƙafata kenan zan shiga ciki na ji an wani fuzgo ni daga baya.....

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK2

7

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉
```

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

Kan ƙirjinsa ya wani manna ni muryarsa cike da masifa ya ce “ mi za ki yi a nan ɗin? Wato duk yadda ake gudun wurin ke da kika iya tarar aradu shine kika zo ki ga abin da ke wakana ko?” duk da dare ne amma hasken wata ya haska sosai ta yadda ina iya ganin ƙwayar idonsa.Ko kafin na kai ga yin magana wata irin dariya ta sa duk muka maida hankalinmu ga rijiyar,tamkar yadda in ruwa sun tafasa suke tashi sama haka rijiyar ta soma ɓulɓulo da ruwa suna tashi sama yayin da muryoyin suka ruɓanya sai dariya ake.

Yaya Khaleed ya ja ni domin barin wurin amma na tirje ina mai cewa “ don Allah ka bar ni na gani kiran sunana fa ake” wani gigitacen mari ya ɗauke ni da shi tare da saɓa ta a kafaɗa muka fice.Har kan shimfiɗata ya dire ni kafin na ga ya ɗauki kujera ya zauna can kusan ƙofar fita,wato gadina zai yi don kar na koma.

Ni kuwa luf na yi ina tunanin abin da na gani a madarkina,eh tabbas duk abin da ya faru yanzu na gansa sai ga shi kuma ya faru a gaske .Daga inda nake a kwance na ji tsayuwar mutum kusan kaina,ban ɗago ba na dai kai dubana a wurin sai na ga ƙafafuwan mace sun sha jan lalle ga kuma zanenta fari ƙal.A hankali na soma ɗaga kaina har na sauke idona kan kyakkyawar fuskarta ta Fulani ta sha ado irin yadda suke zane da kwalli,tufafinta ma irin na Fulani ne.Kan gwiwanta ta zube tare da buɗe bakina,gyanɗamar hannunta ta buɗe ta soma shayar da ni nonon shanu haɗi da shafar gashina a haka bacci ya ɗauke ni mai daɗi.Muryar Kaka ce ta tashe ni da asubah na miƙe na yi sallah,bayan mun gama na zata bacci za a koma a'a sai na ga Samira ta ɗauko allonta na jiya ta miƙawa Kaka ta riƙe yayin da ita kuma ta soma koro hadda abin da ke rubuce.Cike da burge wa nake kallonsu yadda da zarar ta faɗi ba daidai ba ko ta cije sai Kaka ta gyara mata,na shagala sosai a kallonsu na ji muryarsa kamar daga sama .“Irin haka nake son gani kin zama,ki yi ta aman ayoyin Alkur'ani ba wai shigar maza ba” na ɗago kai na dube shi,sai ya zabga min harara da sauri na sunne kai ina tunanin zuci ‘ wato so yake na zama mahardaciyar Alkur'ani? Tabbb yo ina zan iya wannan….’ tunanina ya yanke sakamakon gidanmu

da aka shiga bubugawa ana jijiga ƙofar tamkar za a karya ta a shigo,sai muryoyin mutane ke tashi tsabar yawansu ba a ma jin abin da suke cewa.

Jikin Kaka na rawa ta tashi tsaye tana kallonmu ni da Khaleed kafin ta ce “ fatan dai cikin ku babu wanda ya je wurin rijiyar Mayu ?” a tare muka kalli juna,na yi tunanin zai rufa mana asiri amma kai tsaye ya ce “ eh jiya ne da dare...” ko kafin ya ida Kaka ta yi zaman yan bori tashin hankali ƙiri-ƙiri a fuskarta,Samira kuwa dafe ƙirji ta yi ta ce “ mun shiga uku”

Kaka ta miƙe da sauri tana cewa “ ko da an tambaye ku kun je kuce a'a ban son rigima da tashin hankali ” sai kuma ta nufi ƙofar ta buɗe tana mai aro jarumta da kawar da tsoron da ke ranta .Tana buɗewa duk suka kutso kai cikin gidan,abin mamaki yawancinsu duk tsoffi ne babu matashi ko ɗaya haka kuma jinsi biyu ne maza da mata.

“Ina ce dai lafiya duk kuka yi ayari gidana?” Kaka ta tambaya cikin ɗaga murya,wacce ta fi su kauɗin baki ce ta amsa da cewa “ yaushe kika yi baƙi ? Ba ma dai wannan ba sammaci muka kawo miki don haka mu haɗe gidan mai gari sai ki tawo da tawagarki” tana maganar ne tana kallon mu.

“To babu damuwa ku je muna zuwa” Kaka ta faɗa ,bayan sun gama yan dube-dubensu suka fice,Khaleed ya ce “ to wai laifin mine ne don mun je? ”

“Ku shirya mu je gidan mai gari,ko an tambaye ku kuce ba ku je ba kun dai ji na faɗa muku” Kaka ta faɗa ranta a ɓace.Haka muka shirya muka nufi gidan mai garin,duk fadar tasa ta cika maƙil da mutane.Duk hankalinsu ya dawo kanmu musamman ma ni da hatta mai garin kafe ni yayi da ido kamar mai son tantance wani abu,Kaka ce kawai ta gaishe shi tare da zubewa ƙasa yayi gyaran murya ya ce “ ashe baƙi muka yi a garin?”

“Eh wallahi jikokina ne jiya suka zo” cewar Kaka.

Shi kuma ya ci gaba da cewa “ to madallah Allah ƙara tsarewa,amma ki ja musu kunne a nan ƙauyen ba ko ina ba ne mutum yake sa ƙafa ba in ka je wani wuri ka fito wani wurin gawarka ce za ta fito,kai wani wajen ma ko ƙasusuwanka ba za a samu ba.Kuna iya tafiya amma a kula sosai” mai garin ya ida faɗa yana kallona tsakiyar ido,sai na fahimci duk saƙon nan ni ce yake son isar wa da shi.Na saki murmushi na ce “ ya mai girma mai gari in babu damuwa ina son zagaya garin nan saƙo da lungu don ganin ɓoyayyen sirrikansa da kuma....” mitsikar da Yaya Khaleed yayi min ce a gefen ciki ya saka ni yin shiru.

Mai gari ya ce “ babu damuwa in kin shirya ko yanzu sai a haɗa ki da dogari ”

Kaka ta ce “ a'a wasa take fa,ita da jibi ma za ta koma a dai yi haƙuri mun gode a huta lafiya” sai kuma ta miƙe ta wani kama hannuna muka baro wurin,a kan hanya ita da Khaleed kamar za su cinye ni tsabar yadda suke yi min masifa shi don mugunta har kaina yake dungure wa.

Muna isa gida muka tarar Samira ta ci kuka har ta gaji,amma da ganinmu sai ta taso a guje ta rungume ni cike da murna tana tambayar abin da ya faru bayan mun je can.

Kaka ta faɗa mata a ƙarshe tana mai cewa “ Khaleed ku haɗa kayanku gobe tun carar zakara ta farko zan kai ku tashar mota”

Ya harare ni kafin ya ce “ to Kaka” sai kuma ya nufi ɗakin da aka sauke shi.

Wunin ranar haka na yi shi sukuku musamman yadda duk suka canza min,ƙarin takaicina kuma guda yadda na ga hankalin Khaleed duk ya koma kan Samira duk in ta miƙe idonsa na kanta,tsabar iya yi har da koya mata karatu yayi.Tun kiran sallar magrib na rakuɓe can jikin bishiyar kurna da ke tsakar gidan,duk tsohon

ƙuncina,tuƙuƙi baƙin cikin da ya zamar min abokin hira a ko yaushe su suka taru suka yi min jagora na isa zuwa ɓoyyyen sirrina ko nace ɓoyayyar siffata wacce mahaifiyata da Gwaggo Hajara da Ammy Habibah suka yi ƙoƙarin binne wa don wanzuwar zaman lafiyar al'ummar gidanmu.Kururuwa haɗi da hargagin dabbobi ta sa na miƙe a zabure na nufi hanyar fita daga gidan,malam buɗa takarda ya ja ragamar ruhina na nushi dajin da aka yi ma laƙabi da kogon mutuwa,tafiya ƙasa tasa tafukan ƙafata fashewa amma ko kaɗan ban ji wata aba ba wai gajiya haka na ci gaba da kutsawa ciki har na isa ga wani kogo mai ɗauke da wasu ƙwarin ɗajin.Tamkar yadda in ɗa ya ga uwarsa yake zuwa yayi mata oyoyo haka duk suka yaɓe ni suna min kukansu na ƙwari,kafin daga bisani su kama bandejin hannuna su soma jansa suna warware shi.Sama da minti talatin ana warware dogon bandejin wanda a ido za ka ɗauke ɗan guntu ne amma a baɗini zai iya yi wa yaro riga da wando.Cire bandejin yayi daidai da ƙara tsananta bugun zuciyata wanda ba komai ya haifar da haka ba sai wankin ido da aka yi min nake ganin duk abubuwan da hankali ba zai ɗauka ba.

Abubuwan da na nema a wurin mai gari sai ga su ɓoyayyar siffata na kawo min su daki-daki,duk wani lungun muguntar ƙauyen taram nake ganinsa.Kamar tsuntsuwa haka na tashi na tashi sama, ban dira ko ina ba sai rijiyar Mayu wacce nan ne cibiyar muguntarsu.A inda nake tsaye ina hango duk abin da ke ƙarƙashin rijiyar,ba komai ba ne ciki illa tarin al'umma birjit suna cin baƙar azaba.Tafin hannuna na hagu na haska duk sai mutnen suka yo sama suka fara fitowa daga ciki suna guduwa tare da nusar cikin gari a haka har kowa ya fito sai a lokacin kuma rijiyar ta kama da wuta duk wata powers su ta ƙone.

“Laha'ilah! Ashe kun ganta fa nan zaune tana bacci” muryar Kaka ta tashe ni ko kuma ta fitar da ni daga halin da ban san taƙamaimai mine ne ba.

“Wato duk ihun neman ki da muke kina ji?” cewar Khaleed tare da finciko ni,na saki ƙara ina cewa “ ƙafafuna” Kaka ta haska fitilar hannunta a tare duk suka ɗauki salati kafin Khaleed ya saɓe ni zuwa ɗaki.

Yadda Kaka ta rakuɓe wuri guda sai ta baka tausayi,idona na zubar da ƙwalla Yaya Khaleed ke cire min ƙayoyi a tafukan ƙafafuna da suka yi wata irin dauɗa.Samira ta kawo ruwan zafi,haka ya dinga tsoma towel a ruwan yana gasa min ƙafa,sai kuka nake ina faman kiran sunansa haɗi da riƙe shi.

“Wai duk wannan mine ne Kaka? Na ga lokacin da muka neme ta muka rasa kin fita hayyacinki sosai tare da wasu lafuza da ban gane ba” Khaleed ya faɗa .

Ita kuwa ni ta duba tsakiyar ido ta ce “ ina kuka je Baseerat ? Wane wuri suka kai ki?” shiru na yi ban bata amsa ba ina tunanin duk abin da ya faru kafin na ɗago hannuna na hagu wanda tun da aka haife ni yau ce ranar farko da na yi tozali da shi a haka babu bandeji.

“Wa ya cire miki?” Khaleed ya tambaya yana kamo hannun,wani girrrr duk muka ji yayin da shi kuma yayi saurin dafe zuciyarsa yana mai kallona tsakiyar ido.

Yadda gari ya ɗauki harama ne yasa duk suka fice tsakar gida,ina jin Samira na cewa “ wuta ce ta tashi dubi yadda take fitowa daga bayan gari,ai wallahi sai na je na gani”

An ɗauki lokaci kafin su shigo,Samira wacce ta je ganin ƙwam da ta dawo take cewa “ Kaka duk yaran garin nan da suka ɓata sune suka dawo,hatta yɗan buɗa ido ma suma ga su can duk sun dawo har da Kulu mai waina ma ta dawo,sai dai fa mai gari ya mutu haka ma Talle,da Saude da kande….” nan ta soma zanen mutanen ƙauyen waɗanda dukkansu Mayu ne babu na kirki a ciki.

A gabana Kaka ta ce Khaleed ya kira mata Ammy Habibah ,abu na farko da ta ce shi ne “ alhamdullah!” kafin kuma ta fita waje ban san mi suka tattauna ba.

Abinci Yaya Khaleed ya ɗauko ya soma bani a baki yana kallona har sai da na ƙoshi ya bani ruwa na sha,sai ya fice.Ni kuwa salloli nake son yi amma ban iya tashi,a nan na ɓingire na soma bacci.Bai yi wani nisa ba,na ga Bafulatanar nan kusan ƙafafuna tana shafa min magani haɗi da yi min murmushi, washegari ko da na tashi ƙafar duk sun dawo normal na yi wanka da alwala na yi salloli muna gama cin abinci muka nufi tashar mota bayan Kaka ta bamu tsaraba mai yawa.Muna tsaka da gudu a hanya direba ya tsaya ya ɗauki wani dattijo,tun shigowarsa na ji tafin hannuna na yi min ƙaiƙayi.Gefen da yake na duba,sai na ga kusa da wata mace ce mai goyo yaronta na ta yin kuka sai ya fiddo ruwa gora ya ce “basa ya sha ” ta karɓa tana godiya sai dai yaron ya ƙi sha,tana murmushi tace “dama tun ɗazu nake jin ƙishi” sai ta shiga sha shi kuma yana kallonta yana murmushi.Zama na gyara ina son ganin gudun ruwansa,ko minti ɗaya ba a yi ba matar ta cewa direba ya tsaya za ta yi fitsari.Bakin titi ya samu ya parker ta fita zane a hannu kamar fitsarin na son kubce mata,sama da minti goma ana jiranta har direba ya kai ga cewa “wai ina matar nan ne wata ta fita ta kirawo ta” na so miƙewa amma Khaleed ya zaunar da ni,wata ce ta fita sai ga ta kuma ta dawo hankali tashe tana cewa “matar nan fa tun da ta fita fitsari ne kawai ke shatata ya ƙi tsayawa,kuma ...kuma ina ganin ruwan wannan mutumen ne da ta sha” sai ta harare shi,tsoho yayi dariya ya ce “eh sosai kin yi gaskiya,muddin tana so ya tsaya doli sai ta zo ta saka hannunta ga al'aurata ” .....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK2
```

8

Dukkan mutanen da ke cikin motar suka cika da mamaki jin wai fitsarin ba zai tsaya ba sai in har matar ta yarda ta taɓa al'aurarsa.Tuni wasu sun fara zagin tsohon,wanda ya fi zaƙewa shi ne direban motar cike da masifa yake cewa “yau na ɗauko wa kaina masifa,kai daga taimako shine za ka jawo mana bala'i don ka cika tsohon ɗan iska wanda bai tsoron Allah to wallahi haɗuwa za mu yi mu maka shegen duka” ko bakinsa bai rufe ba tsohon ya ƙyalƙyace da dariya tare da tofa yawunsa kan fuskar direban,sai ga direba ya koma mimi-mimi da baki amma muryarsa ba ta fita,ganin haka yasa duk mutane suka sha jinin jikinsu.Raina ne ya ƙara ɓacewa,na yunƙura a karo na biyu amma Khaleed ya riƙe ni can ƙasan maƙoshi ya ce “wai uwar mi za ki yi? So kike ki saka mu a matsala ne uhum?” uffan ban ce masa ba sai kallon matar da na yi wacce har zuwa yanzu fitsarin sai zuba yake mata duk zanenta ya jiƙe sharkaf,yayin da idonta ke ta tsiyayar da hawaye tana gwanjin kuka yƴarta na kama mata.Zuwa wannan lokacin duk mun sauka daga motar,mun yi cirko-cirko kamar kaji.Da rairafe matar ta zo har gaban tsohon,a wannan karon cikin ɗaga murya na ce “Yaya Khaleed kana ganin fa matar nan taɓa wa za ta yi kamar yadda ya buƙata,ba zan bari hakan ta faru ba”

Duk sai kallo ya dawo kaina,sai kubce-kubce nake amma Ya Khaleed ya riƙe ni gam a ƙirjinsa,ina ji ina gani a gaban kowa tsohon nan ya since azargagin wandonsa matar ta kai hannunta za ta saka kenan na ture Yaya Khaleed ina mai furta “dakata!” haɗi da yin alama da hannuna na hagu wanda tuni kalmar Ɱ ɗin ciki ta fito raɗau tana fitar da haske.Wannnan abin da na yi shi ya fitar da al'aurar tsohon ta dawo tsakiyar goshinsa,duk mutane suka ja baya suna “wayyyo! Tashin hankali!” yayin da shi kuma tsohon ya shiga mummunan tashin hankali.A nan take kuma fitsarin matar ya ɗauke ɗif,hatta zanenta da ya jiƙe sai ga shi ya koma ƙamas babu lema.

“Mi kike yi haka SEERAT? Mi yasa za ki shiga abin da bai shafe ki ba? Kin san yin haka mi zai jawo miki ne? Ɱutane za su soma zargin ki ne” Yaya Khaleed ya faɗa yana mai ƙara finciko ni,na saki murmushi na ce “kowa ya shiga mota” kamar masu jiran umarnina kuwa duk suka shiga suna waige na,matar kuma har da yi min godiya yayin da Baba tsoho ya zube a gabana yana bani haƙuri bayan ya cire rigarsa ya ɗaura a kai.

“Jikata ki yi min rai,ki tausaya min ashe sara na yi da mutum sama.Da ace na san kina cikin motar nan ko kusa da ita ba zan je ba,ki gafarta min don Allah ” tsohon ke faɗa yana kuka wiwi,na kalli Yaya Khaleed kafin na janye jikina daga nasa na shige mota shi ma ya take min baya ya zo ya zauna kusa da ni,haka shi ma Baba tsoho ya shigo motar yana kuka,don bai san kunya ba sai ya soma yi wa mutane magiya “ku taimaka ku saka baki ta mayar min abina wurin da yake,don Allah ku tausaya ki taimaki dattijo wanda ke kan gargadar mutuwa to kwana nawa ne ma ya rage min a duniyar”

Lafuzansa sun fi komai baƙanta min a rai wannan yasa na ƙara tunzura na ce “ka san shekarunka sun ja shi ne kake mugunta? Wato kai ga matsafi za ka yi amfani da siddabarunka wurin sa mata su dinga biya ma buƙata? Faɗa min ma dai mine ne yasa ba ka yi aure ba in buƙatar mace kake? Wannan halinka ne da dukkan alamu ba yau ka saba yinsa ba don haka ka girbi abin da ka shuka” na faɗa tare da mayar da dubana kan windown mota,can na ɗan ɗaga murya na ce “ direba don Allah tuƙa mu sauri muke da akwai abin da za mu yi” motar ya soma ja,har zuwa yanzu an kasa samun mai jarumtar yin magana tsit kake ji kamar an yi ruwa an ɗauke in ka fidda Baba tsoho da ke ta rantse-rantse haɗi da alkawarin ya daina ba zai sake yi ba.Kanzil ban sake ce masa ba har muka isa tashar motar Zinder inda a nan kowa zai sauka,na ɗan yi gyaran murya na ce “ direba gidan sarki za ka kai mu, ke ma ki tsaya kar ki fita za a yi mana shari'a ne”

Bayan kowa ya fice direba ya kai mu gidan sarki,zuwa wannan lokacin sai da tsoho yayi zawo a wando.Kowa ya san yadda Sarkin garin ke da tsatsauran hukunci akan azzalumai musamman ga Mayu ko kuma masu muguntar ire-iren haka.Khaleed ƙin fita yayi sai mu uku kawai muka je,matar ce ta yi wa wani dogari bayani kafin ya yi mana iso har can fadar sarki.Nan ɗin ma sake jaddada ma sarki duk abin da ya faru ta yi cikin kuka,abu na farko da sarki ya ce “ mayar masa da maganarsa” ƙiri-ƙiri babu kunya tsoho ya ce “ to” sai ya tofa wa direba yawu a fuska raɗam muryarsa ta dawo ya soma yi wa sarki godiya.Sai a lokacin kuma sarki ya maido dubansa gare ni ,na yi saurin sunne kaina amma tambayar da ya jefo min ta saka na ɗago a razane muna kallon juna ido cikin ido .

“Ke mayya ce?” Sarkin ya sake tambaya ta yana turniƙe fuska,zuciyata na ji tana tafasa sosai dakyar na buɗe baki na ce “ in ita ce mi za ka yi min?” daga bayana na ji saukar dorinar dogari har sau biyu ya tsala min ita yana cewa “ ki gyara kalamanki in ma giyar maye kika sha ki dawo hayyacinki nan fadar sarki kike”

Ido kawai na rumtse ina jin raɗaɗin bulalar na ƙara ratsa ni,can ƙasan zuciya na ce ‘ tabbas Yaya Khaleed ka yi gaskiya ga shi kuwa an soma zargin nawa ’

“Ku ɗauke su ku kai can ku kulle in ta shirya magana sai a fiddo ta domin amsar tambayoyi” sarki ya faɗa yana mai tashi tsaye yana tattare alkyabarsa,dogarai suka soma yi masa kirari haɗi da take masa baya yayin da wasu su biyu suka tisa ƙeyata ni da Baba tsoho zuwa gidan yarin masarauta.Ɓangaren maza aka kaisa ni kuma na mata,dogari ya ɗunguza ni cikin raga yana cewa “ ƙaramar yarinya da maita ki je can ki ƙarata rayuwarki a nan shegiya muguwa ” raina a ɓace na ce “ ba ka ma san muguwa ba ce ni sai nan gaba ,wanda ya kashe ɗan uwansa don ya gaji muƙamin zama kusa da sarki” ya wani dawo da sauri tare cakumo wuyana yana zarar ido “ uban waye ya sanar da ke?” ban ce komai ba sai fuskata da na soma matsewa ta yadda goshina zai tsuke tam ,ina gama yi na yi cilli da shi can gefe ya bugu ga katanga .Na sakar masa wani murmushi ina mai mayar da tabon goshina ciki,sannan na ƙarasa can ciki na zauna ina tunani.

“Laifin mi kika yi aka kawo ki nan?” muryar wata mata ta katse ni,na ɗago na dube ta sai kuma ta ci gaba da cewa “ ina nufin wa kika sanƙame wa kurwar?”

“Ni ba mayya ba ce” na bata amsa kai tsaye,ta ƙyalƙyace da dariya ta ce “ to raina min hankali,dama ai maye ba zai taɓa faɗar aikinsa ba.Amma wanda ya baki kambun nan ba ƙaramin taimakon ki yayi ba,matsalar da ke ɗin ce kin kasance marar sa'a ga shi za ki mutu tun wuri”

Wani kallo na yi mata irin na ba kida hankali,sai ta kuwa zauna da ni ta ce “kina ji yɗata? Kusan mu ashirin da uku ne a cikin ragar nan amma ɗaya bayan ɗaya duk an kashe su saboda doka ce mai zaman kanta ”

“To ai ni ba mayya ba ce ballantana a kashe ni,wani ne na kama da wani laifin na hukunta shi maimakon na bari doka ta yi aikinta.Amma na tambaye ki ke mayya ce?”

Shiru ta yi ba ta bani amsa ba,na ce “ kin ga in kina son fita daga nan ki bani labarinki ni nan zan fitar da ke”

Ta kalle ni ta yi dariya ta ce “ ke ɗin ce za ki fitar da ni ?”

“Kar ƙaranta shekaruna su sa ki yin babban kuskure don na zarce yadda kike tunani” na faɗa ina wasa da tafin hannuna wanda bayan fitar da hasken wuta babu abin da yake.

“Mine ne wannan? Tsafi?”

“Baiwa ce” na bata amsa kai tsaye,ta ɗan gyara zama kafin ta ce “ ban taɓa maita ba na dai karɓi kambunta ne wurin wata ƙawata saboda ina son ganin bayan ƙanwar mijina”

“Laifin mi ta yi miki?”

“Yɗata ta lalata,muna zaune ne ni da surukata a gida guda kasancewar mijina bai da hali to ƙanwarsa aurenta ya mutu kin san dayawan mata ba su iya jurar rayuwar ZAWARCI maimakon su kame kansu,a'a sai su faɗa biyar maza tun da dama dai ce babu wani budurci ballantana su ji tsoro.To ita wannan muguwar bazawar ƙanwar mijin nawa akan yɗata duk ta zube damuwarta tana amfani da ita...” sai kuma ta fashe da kuka,na ɗan yi shiru na ce “ ko dai ita mayya ce? Kwana biyu da suka wuce an samu wasu case masu shigen haka.Tabbas akwai lauje cikin naɗi,yin lesbian na ƙara ƙarfin power maita kenan?”

“Haka ƙawata ta ce shine dalilin da yasa ta ban ƙanƙarar maitar,sosai nake azabtar da ƙanwar mijina da farko hanjinta na riƙe sam ba ta iya cin abinci sai hakan ya haifar mata da muguwar rama sai ƙaton kai,daga nan kuma na riƙe ƙafafunta ta bar tafiya,yatsun hannunta kuwa duk an guntule su”

“Saboda me?"

“Saboda da su ta yi amfani ta cutar da yʻata” ta bani amsa kai tsaye.

“To mi ya kawo ki gidan sarki?”

“Su suka kawo ni nan a bisa zargina da suke,mijina da mahaifiyarsa saboda ƙanwarsa in banda sunana babu abin da take faɗa in dare yayi.Da aka kawo ni nan na ƙi amsa laifina ,mafarin aka shigo da ni nan da zumar ranar da na shirya yin magana sai a fidda ni.Amma kin ga na kai wajen wata ɗaya da wasu kwanaki,na yi zama da Mayu a ɗakin nan sun bani labari sosai ”

“ Tabbas an cutar da ke,don haka zan taimake ki na cire miki wannan abin da ta saka miki dubi ke ma sun fara cutar da ke” na yi maganar ina nuna saitin zuciyarta tare da bata umarnin ta kwanta ta rufe idonta.

A tsorace ta yi yadda na ce,na buɗe bakinta yayin da Bafulatanar nan da ta zama tamkar inuwata ta zuba mata wasu ruwa a bakinta nan wani baƙin abu ya fita daga bakin nata kafin ta miƙe ta soma yin tari kamar ranta zai fita.Na saki murmushi kawai,na ce “ yanzu ya za a yi ki shaida kin shirya magana?”

“Sai in an zo kawo mana abinci ” ta bani amsa.

A can waje kuwa direba ne ya yi wa Khaleed bayanin abin da ya faru, hankalin tashe ya shigo ciki sai dai babu wanda zai tunkara da maganar.Zuciyarsa kamar za ta fashe don baƙin ciki da takaicin SEERAT,duk gudun matsala irin wannan yasa yayi ta ƙoƙarin hana ta amma da yake kunnen ƙashi ne da ita ba ta saurare shi ba.Jakar kayansa da tata ya ɗauka tare da neman mai ɗan sahu ya kai shi can gida,da shigarsa yayi yarɓi da su ya soma masifa wacce kusan ma kamar a jininsa take.A jawaban da yake yi ne Ammy Habibah da ke zaune tana tsintar wake ta fahimci abin da ke faruwa amma ko kaɗan ma bai ga alamun hankalinta ya tashi ba.

Ya ɗan yi ƙasa da murya ya ce “Ammy SEERAT fa na can gidan sarki amma shine kike ta yin aikinki”

Ta ɗago ta dube shi tare da cewa “to me zan yi? Ƙaddararta ce wanzar da adalci a wurin da aka tauye wani,dama ai ni na san da hakan ka kwantar da hankalinka gobe za ta dawo”

Khaleed ya saki baki yana kallon ta kafin ya ce “ na kasa tantance ke da SEERAT mutane ne ko jinsin jinnu, wannan ɗin ma kin yi mafarkin nasa?”

Ta jinjina masa kai tana murmushi.....

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK2

9

Khaleed ya wuce ɗakinsa,ya rage kayan jikinsa sannan ya je yayi wanka .Ammy Habibah ta kawo masa abinci tana mai cewa “ ka ci sai mu wuce”

“Zuwa ina?”

“Gidan sarki mana ” ta basa amsa.

Ransa ya ƙara ɓaci ya ce “ Ni fa Ammy ba zan ƙara shiga sabgar SEERAT ba,wato ita abin da na lura taurin kan tsiya ne da ita.Abin da kowa ke gudu ita sonsa take,sannan ke ma har da laifinki ke ce kike ɗaure mata gindi take yin abin da ta ga dama.Ki duba fa zuwan mu ƙauye ke ce kika tsara shi,kafin nan kin bani labarin rijiyar Mayu kika kwaɗaita min shi sosai ta yadda muna zuwa na tambayi Kaka,a daren kuma ban san mi ya shige ni ba haka na bi bayan SEERAT izuwa can .Kin san mi na haɗu da shi a hanya Ammy?” ba ta ce komai ba sai kallonsa da take,shi kuma ya ci gaba da cewa “ ina tsaka da tafiya na ga akwatin gawa a gabana,sanin dama ƙauyen akwai miyagu yasa ban wani tsorata ba na ci gaba da addu'o'i har na isa
```

gun da SEERAT ta shiga.Nan ɗin ma sai da aka so firgita ni da wata ƙatuwar mujiya ta fi jimina girma amma duk na share na isa ga SEERAT ɗin wacce saura ƙiris ta faɗa tarkon Mayun nan don wallahi da cikin rijiyar za ta shiga”

Murmushi ɗauke kan fuskar Ammy Habibah ta kai hannuwanta ta tallabo haɓar Khaleed ta ce “ wannan dalilin yasa na ce ku tafi tare a madadina,yarona ina son ka san cewa alƙalamin ƙaddararku da SEERAT a haɗe yake wuri guda.Allah ne kawai yasa dalilin da yasa ya haɗa ku wuri guda,amma tabbas ina jin hakan alkhairi ne.Yi maza ka ci abinci ina jiran ka a falo ” tana gama faɗa ta fice,shi kuwa tsaye kawai yayi yana kallonta cike da mamaki.Bai wani ci abincin sosai ba ya fito cikin doguwar riga fara ƙal,sumar kansa ya wanke ta tass sai ta kwanta luf gwanin sha'awa.Ammy Habibah ta tsure shi da ido a zuci tana cewa ‘ anya Khaleed ba cikin jinsin baƙaƙen Larabawa ya fito ba?’

“Ammyyy!” ya faɗa a shagwaɓe cikin salon sangartatun yara,ta saki murmushi tare da miƙewa tsaye suka fito ta rufe ɗakin sai a lokacin ya ce “ ina Hajiya ?”

“Ta fita” sai suka fito har ƙofar gidan sai da ta ƙargame sannan suka wuce gidan sarki,cike da girmamawa ta yi wa dogarin bayanin tana son ganin sarki ne akwai magana mai muhimmancin da za su yi.Wuri ya nuna musu suka zauna,sai da aka ɗauki lokaci kafin ya dawo ya ce “ sarki yana hutawa ba zai samu damar ganawa da kowa ba,sai dai ku sake zuwa wani lokacin”

“Don Allah ka taimaka na faɗa ma maganar na da muhimmancin sosai,muddin na ƙara lokaci da matsala”

Cike da masifa dogarin ya ce “ ba ki ji abin da na ce ba? Nan fa gidan sarki ne gidan yɗan wasar kwaikwayo ba” Khaleed ya zabura zai miƙe amma ta yi saurin dakatar da shi tana mai cewa “ bar shi! Bar shi kawai,wato duk yadda nake son nuna musu hanya ba su son gani tashi mu je gobe da kansu za su zo har gida neman mu” ta kama hannun Khaleed suka fice,shi kuwa dogarin ya ci gaba da yin masifa yana zagin Ammy Habibah .

#SEERAT

Bayan na gama wargaza duk wani sharri da ke jikin matar sai na samu wuri na rakuɓe a jikin gini ina tunanin Khaleed .Tsawon lokaci ina a haka kafin kuma na soma jin dodon kunnena na zuƙo min sautin Ammyn Habibah ,na lumshe ido na mai ci gaba da sauraren duk jawabinta da kuma abin da shi dogarin ya ce mata.Tafin hannuna kawai nake murzawa ina jin raina na ɓaci," ga dogari ne ya kawo mana abinci na sanar da shi ina son yin magana " matar ta faɗa tana murmushi,na juyo na dube ta sai ta ci gaba da cewa " na matsu na ga ahalina,duk da na san kuma yanzu in na fita rayuwar ZAWARCI zan faɗa " sai ta goge ƙwallar da ta ciko a idonta,na ɗan ja ajiyar zuciya na ce " Mama ai da wani auren gwara ZAWARCI,mata da yawa suna ganin rayuwar ƙasƙanci a gidajen aurensu amma suka yarda suka rungumi ƙunci don gudun ZAWARCI,yanzu faɗa min mine ne amfanin auren da za a tauye wa mace haƙi a illata rayuwar yarta wacce ita ɗin ta kasance amana ce a gare ki? Ba kukan shiga ZAWARCI ne ya fi muhimmanci ba a yanzu,a'a goben yarki ne ya kamata ki nuna damuwa saboda ke kin yi taki rayuwar "

Ta yi wani murmushi ta ce " yata har yanzu ke yarinya ce ba ki san mine ne ZAWARCI ko aure ba,ki sani duk wuyar gidan miji gwara ita da rashin auren .In yanzu ya sake ni gidanmu zan koma tsofe-tsofe da ni uwar wasu kakar wasu? In na koma gida zan ƙarawa mahaifana nauyi ,ga shi ba wani aiki nake yi ba ballantana na ce zan dogara da kaina,saɓanin gidan aurena duk mijina ne zai yi min komai "

"Eh ni yarinya ce tabbas,amma dai zan baki shawara tun da kin ji kin gani gidan auren kika zaɓa kan rayuwar yarki.Amma don Allah ki nisanta yar daga gidan ko kuma shi mijin naki ya kama miki haya" muna tsaka da yin hira dogarai biyu suka shigo," ku fito dukkan ku" duk muka miƙe muka bi bayansu .

Muna shiga fada sarki ya ƙure ni da ido kafin ya dubi wani da ke kusa da shi ya ce " ga ta nan"

Na maida dubana ga mutumin muna yar kallon-kallon kafin ya ce "tabbas aikinta ne,ya mai girma ita wannan yarinyar yar baiwa ce kawai amma ba ta da niyyar cutar da kowa.Muddin ka ga ta yi hakan to hanyarta aka shiga,amma Allah ƙarawa mai martaba lafiya ina ga abin da ya fi shine mu nemi sulhu dogarai na cikin wani hali"

Kai kawai sarki ya jinjina kafin ya bada umarni a shigo da dogarai uku waɗanda suke jin jiki,ɗaya wanda ya tsala min bulala ne duk jikinsa yayi ja sai soshe-soshe yake,na biyun kuma wanda ya cilla ni cikin raga ne a wulaƙance kansa yayi girma ya cika da iska ,sai na ukun wanda ya zagi Ammy Habibah ne ya faɗa mata baƙaƙen manganganu halshensa ya zazzalo sai yawu ke yi masa zuba.

Tsayuwa na gyara lokacin da muryar sarki ta daki kunnena,“ ki yi haƙuri ki bar su haka,sun aika miki ba daidai ba a bisa kuskure”

Cike da wata gadara na ce “ sai sun taɓa ƙafafuna sun nemi yafiya ” na zata Sarkin zai ji haushi ne amma sai na ga ya saki murmushi,haka dogaran suka zube a gabana suna magiya.Da hannuna kawai na yi amfani wurin taɓa kawunansu sai ga shi sun koma ƙalau, wannan lamari ya sa sarki tashi tsaye yana ƙara kallona da mamaki sai kuma yasa aka shigo da baba tsoho.Sai da aka kai ruwa rana sannan na yarda na mayar masa da al'aurarsa inda take bayan kuma nan duk na ɓata wasu laƙaninsa na Siddabaru.

Da kaina na yi wa sarki bayani akan lamarin matar ,sai ya sa aka nemo mijinta da kuma ƙanwarsa domin yi musu shari'a.“Ku wuce da ita can cikin gida kafin a je a ɗauko min iyayenta,ku tabbatar ta yi muku bayani mai kyau yadda za ku fahimta” cewar sarki ,matar wacce na ji yana kira da jakadiya ta kama hannuna muka fito duk yadda na so jin yadda shari'ar za ta kaya amma ban ji ba.Can ɓangaren matar gidan aka kai ni bayan na yi wa dogarai bayani tiryan-tiryan akan unguwarmu da gidanmu.

“Wannan fa?” cewar matar sarkin wacce take hakimce kan kujera bayu na yi mata fifita,jakadiya ta zube kan gwiwanta ta ce “ sarki ne ya ce a shigo da ita ciki” wani

kallon wulaƙanci na ga tana yi min tun daga ƙasa har sama,ni ma sai na dubi kaina ɗin.Kayan Samira ne a jikina waɗanda ta bani,atamfar sabuwa ce ba ta tsufa ba ballantana na ce ƙila shi yasa take min kallon kamar wacce ta ga kashi.

“Sai kuma ki rasa wacce za ki kawo wa ita sai ni ko? ” ta sake jefo tambayar,jakadiya na shirin yin magana ta wani daka mata tsawa “ ki ja ta ku ɓace min da gani” sai da na rumtse ido tsabar takaici,jikinta na rawa ta kama hannuna tare da fara ja na.Sai da muka kai bakin ƙofa na juyo na dube ta,kallo ɗaya na yi wa ƙwayar idonta na fahimci kaf tarihin rayuwarta da kuma abin da ta fi so a yanzu sai na sakar mata murmushi.

“Ki yi haƙuri don Allah!” jakadiya ta faɗa lokacin da muka fito,ban ce mata komai ba har muka iso wani sashen shi ma ya haɗu sosai sai dai wancan da na baro ya fi kyau.

Sallamar da jakadiya ta yi kamalaliyar matar ta amsa fuskarta ɗauke da murmushi kafin ta ce ,“yau kuma ke ce nake gani ko idona ne?”

Jakadiya ta yi murmushi ta ce “ eh wallahi dama sarki ne ya ce na kawo wannan kafin ya shigo yayi miki bayani,ki gaishe ta” cewar jakadiyar tana mai zungura ta ,da sauri na ce “ ina wuni?”

“Lafiya lau alhamdullah yʻan mata ya sunanki?”

“Baseerat” na bata amsa kai tsaye,nan jakadiya ta fita ni kuma na samu wuri a ƙasan lallausan capet na yi zaune a bisa umarnin gimbiyar.

Kan kujera ta zauna tana sakin murmushi wanda na lura tabi'arta ce,idona na saka cikin nata ba tare da tsoro ko shakka ba,sannan ba kuma don niyyar cutar da ita ba a'a sai don ina son ƙwamushe kudin sirrin rayuwarta.Ita ce ta yi saurin kawar da kanta gefe kafin ta ƙwala kiran sunan “Hawa?” aka amsa daga can cikin wani ɗaki kafin wata kyakkyawar budurwa ta fito,“ga ni Mama”

“Ki kawowa baƙuwa abin motsa baki” kai ta jinjina cike da ladabi tare da nufar wani wurin da nake zaton kitchen ce,ba a ɗau lokaci ba kuwa ta fito ɗauke da tray ta ajiye shi a gabana tana mai ce min “ sannu da zuwa”

“Yawwa na gode” na faɗa tare da ɗaukar apple na soma ci ina tunanin abubuwan da ke ƙumshe a cikin wannan masarauta,na yi nisa sosai a tunanin nan kafin muryarta ta katse min shi “ faɗa min wace ce ke?”

Da sauri na ɗago muka haɗa ido da ita,tabbas sai yanzu na fahimci ma tana da wata baiwar ita ma kusan dai kamar ta Ammy Habibah sai dai powerta nada rauni sosai.

Na saki murmushi na ce “ Baseerat ce ni ”

“Kar ki raina min hankali kin san sarai abin da nake nufi,ban tambaye ki sunanki ba” gimbiyar ta faɗa wannan karon ranta a ɗan ɓace kuma yanayin fuskarta ya canza.

“A yi haƙuri Mama,kin fi kyau in kina murmushi.Seerat ba ta zo nan don cutar da ke ba, hasalima zuwana a masarauta tamkar zuwan ƙarshen damuwarki ce ya ke uwar yaɗammata” na faɗa cike da ladabi ina kallon ta ,ta ja wata ajiyar zuciya ta ce “ amma mine ne asalin abin da ya shigo da ke nan?” ban ɓoye mata ba na bata labarin har abin da ba ta tambaye ni ba,wato zancen rijiyar Mayu da kuma yadda na kawo ƙarshensu a ƙarshe kuma na ɗora da cewa “ ina da yaƙinin kawo ƙarshen duk wani ko wata da suka laƙanci maita,da masu tsibo ” murmushi kan fuskarta ta zo ta zauna kusa da ni a tare muka ci abin da Hawa ta kawo muna ta yin hira kamar wasu sa'inin juna.

Sarki ne ya shigo tare da ahalin gidanmu,da sauri na je na rungume Mama sannan Ammy Habibah ina jin wani sanyi na ratsa ni.

“Ina Yaya Khaleed?” na tambaya,“yana gida shi da Yaya Ɗayyabu suna duba wasu takardu” Ammy Habibah ta bani amsa ,murya ƙasa-ƙasa na ce “ita ma tana da baiwa”

“Eh na gani”

Sarki ya ce “ku zauna don Allah ina zuwa” sai ya fita,“Mama ki zauna” na faɗa ganin ta yi tsaye kamar haure sai kallon gimbiya da take yi,zaman ta yi amma ta kasa haƙuri ta ce “ni kam kamar na san ki” Mama Safeenatu ta faɗa ,gimbiya ta murmusa ta ce “to ƙila” Mama Safeenatu ta yi shiru na wani lokaci kafin ta miƙe tsaye ta ce “eh tabbas ke ce Salmu ba ƙawar Gwaggo Hajara?”

A tare muka haɗin baki ni da Ammy Habibah wurin cewa “Kawar Hajara ?”.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK2

10

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉
```

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Gimbiya ta yi saurin cewa,“ don Allah duk ku kwantar da hankalinku,duk da tana ƙawata amma halinmu ya sha banban da na juna.Tabbas na san Hajara ta ci amanar mahaifiyarki tun da ta aure Ɗayyabu,ni ma tun lokacin na yanke alaƙa ta da ita musamman da na gano cewa ita ce ta yi silar mutuwar uwar ɗakinta.”

“Kenan ita ta kashe Granny?” na furta ina mai fiddo ido waje ,Mama Safeenatu ta soma yin kuka wiwi tana jin tamkar a yanzu ne Momah ta rasu.Ita kuwa gimbiya haƙuri kawai take bayarwa haɗi da zagin Hajara ,cikin takaicin ƙin kashe Hajara da ban yi ba tun ranar nan na ce “ kin san ƙauyensu?”

“Eh na sani sosai ma ai ba ta ɓoye min komai musamman da ta fahimci ina da baiwa kuma ta ga ban taɓa yunƙurin hana ta yin duk abin da take so ba,ni kuma rashin sanin yadda zan hana ta ɗin ne ban sani ba”

Ammy Habibah ta ce “ duk in kina neman muguwa wacce babu ɗigon imani a zuciyarta to bayan Hajara take,ban taɓa ganin mai kalar muguntarta ba.Ki kashe matar gida ki auri mijinta sannan ki koma ga yaɗarta ,tsabar mugunta fa ranar da aka haifi Basheer ta so cinye shi Allah yayi sa'a Baseerat nada baiwa ta tarwatsa plan ɗinta”

Gimbiya ta yi murmushin da ya fi kuka ciwo ta ce “ Hajara fa tun tana jinjira ta ci gadon maita gun mahaifiyarta,kuma kusan duk ƴan gidansu Mayu ne .Maitar tsafi ce suke mai wuyar karyawa,suna da power sosai ta yadda ko kama su aka yi zai yi wuya su miƙa wuya ko sun nuna sun yi nadama to ta munafurci ce.Yanzu duk ba wannan ba ina ita Hajarar take?”

Ammy Habibah ce ta bata dukkan labarin abin da ya faru,sannan ta ɗora “ yanzu ba mu san inda za mu same ta ba…” na yi saurin katse da “ to me za ta yi mana Ammy?”

“Da akwai abubuwan da dole ita ce za ta warware su” ta bani amsa kai tsaye.

“Kamar me fa?” da ido kawai ta yi min magana kan bata son surutu da yawan tambayoyi,kawai sai na ja bakina na yi shiru.

Sarki mai martaba ne ya shigo hannunsa riƙe da wani ɗan ƙaramin akwati,duk muka gaishe shi tare da ƙara nutsuwa muna sauraren abin da zai ce.

“Na gode sosai matuƙa da wannan karamci naku,ga kyauta zan bayar ga Princess” sai ya miƙo min ɗan ƙaramin akwatin yana murmushi,na duƙa na karɓa cike da girmamawa tare da yi masa godiya ina jin daɗi har ƙasan raina duk da ban buɗa na ga ko mine ne a ciki ba.

“Zan sa a mayar da ku gida,sannan don Allah in shi Ɗayyabun ya dawo ku shaida masa ina son ganinsa a fada in kuma bai iya zuwa ni zan je na same shi ga lambar wayata duk yadda ake ciki sai a sanar da ni” ya miƙawa Ammy Habibah wani kwalli mai ɗauke da lambarsa.

“Mu ke da godiya mai girma mai martaba,in sha Allah kuma da kaina zan yi masa bayani” cewar Ammy Habibah kafin duk mu miƙe,Gimbiya ta dube ni tana murmushi ta ce “ fatan dai Baseerat za ta dinga kawo min hira?” na gyaɗa mata kai ina mai mayar mata da martanin murmushin,har bakin mota ta yi mana rakiya .

A nan gidanmu aka sauke mu,muna shiga na dubi Khaleed da ke tsaye yana ɗurawa wata tsuntsuwa abinci a baki.Da sauri na isa gare shi ina mai cewa “ dubi kyautar

da sarki ya bani ” kanzil bai ce min ba in banda dubana da yayi da ido.Jikina ne duk yayi sanyi na ce “ ka yi haƙuri”

“Matsa ki ban waje don Allah kin tare min iska” ya furta a zafafe,a shagwaɓe na ce “ please Yaya Khaleed ” wata uwar tsawa yayi min wacce ta rikiɗar da shi ya dawo min Khaleed ɗin da na sani wanda nake mugun tsoro,babu shiri na bar wurin idona na zubar da ƙwalla.Ina shiga ɗaki toilet na shiga na soma yin wanka bayan na fito na buɗe akwatin,wata ɣar ƙaramar sarƙa ce ta gwal an yi mata zanen kifi a tsakiya cike da jin daɗi na saka ta a wuyana kafin na je na tsaya gaban madubi sai dai fa sam ya ƙi nuna min ko da akaifata ce ballantana fuskata.Haka kawai na je na cire sarƙar na ƙara zuwa na yi tsaye gaban madubin, wannan karon ras na fito abina.Na saki murmushi ina tuna mafarkin da na yi akan Bafulatana mai kawo min ziyara don tuni ta yi min bayani akan sarƙar wuyan.Ɗauko ta na yi na mayar,don shirme na tsaya a gaban madubi duk da ina da yaƙinin ba zai taɓa nuna ni ɗin ba.“ Na zama katangar ƙarfe ,inuwa gun maƙiya,ciwon idon mugaye ” na soma yi wa kaina kirari ina jin wata power na ratsa ni.Tsakar gida na fito ina kallon Khaleed wanda har yanzu sai faman ciyar da tsuntsuwar nan yake,na ɗan yi murmushi tare da nufarsa “ mi sunanka?” na tambayi tsuntsuwar,Khaleed ya harare ni ya ce “ wa ya faɗa miki Aku ne ballantana yayi magana”

“Yana magana mana,daga wace masarauta kake? Wane saƙo ka zo isar wa ?” na yi tambayoyin ina shafar kan tsuntsuwar wacce ban sani ba ko Khaleed ya lura har da wani tambari a wuyanta.

Furrrr ya cilla tsuntsuwar sama ta kuwa tashi da gudunta ta soma shawagi a sararin samaniyar gidanmu kafin ta ɓace wa ganinmu.Na ja ajiyar zuciya na ce “ Yaya Khaleed ko ka san wannan tsuntsuwar ba normal ce? Ga shi dai shi ba namiji ba ,shi ba mace ba kuma yana jin magana fa da alamu aiko shi aka yi”

Tsaye yayi yana kallona kamar ya ga mahaukaciya,“ ya dai?” na faɗa .

“To Allah kyauta da dukkan alamu ke taki baiwar da taɓin hankali ta zo”

Dariya na soma yi har da riɓe ciki,kawai sai Yaya Khaleed ya soma yi min karatu kamar wata mai jinnu har da riɓe kaina.Shatun yatsunsa ne na ji sun ɗauki zafi kamar wuta suna ƙona ni,na yi ƙoƙarin janye hannun amma ya ƙi bari kawai sai na zube kan gwiwaina ina hawaye .Shi kuwa ya ƙara ƙaimi wurin karatun,a haka Daddy

ya zo ya tarar da mu da ya tambayi ba'asi Khaleed ya ce “ iskokanta ne suka motsa”

“To taimaka mata ta je can ciki” kamar wata yarsa haka ya ɗauke ni ya kai ni tsakiyar falo ya kwantar.Duk nan suka shiga tambayar lafiya shi kuma yana basu amsa kan jinnu ne suka motsa min,daga inda nake kwance na ga an buɗa labule hasken rana ya shigo amma babu kowa.Tsudum na ganta a tsaye a gabana fuskarta kicin-kicin,“ kar na sake ganinki da yaron can! Ki yi nesa da shi,taurarinki da nasa sam ba su zamo ɗaya ba” Bafulatana ta faɗa tana mai nuna min Khaleed wanda ke zaune can gefe suna hira amma duk rabin hankalinsa na kaina.Da farko na yi tunanin ko shi ma yana ganin Bafulatanar amma ganin sam bai kallon inda take sai na fahimci iya ni ɗaya kawai ke ganinta.Tana barin wurin ya zo yana tambaya ta “ kin tashi?”

Kai kawai na jinjina masa bai ƙara cewa komai ba sai wani tsure ni da yayi da ido yana kallo,hakan kuma ba ƙaramin ƙara gudun bugun zuciyata yayi ba ina son Yaya Khaleed sosai.Na lumshe ido kawai ina jin marata na murɗa min ,tun tana yi a hankali har abin ya ƙara ƙaimi ban san lokacin da hawaye suka zubo min ba.Hannunsa na ji kan kumcina yana goge su haɗi da tambaya ta mi nake ji,ban iya yin magana da hannu na masa nuni da cikina sai ya miƙe tsam ya je ya ɗauko kofi da ruwa yayi addu'o'i sosai kafin cikin bayar da umarni ya ce ” tashi ki sha”

“Ban iyawa wallahi” na basa amsa,kusa da kaina ya zo ya tallabo ni ya soma bani ruwan na sha.Kamar minti biyu na ji abun ya lafa sai kuma wani sabon al'amari da nake ji da sauri na miƙe tsaye nan idona yayi tozali da jinin da ya ɓata kujerar da na kwanta,hankalin kowa sai ya dawo kaina da na yi ihu yayin da shi kuma Khaleed yayi saurin ficewa.Ammy Habibah ce ta kai ni Toilet ta kimtsa ni tare da yi min bayani dalla-dalla kan alamomin girma ne suka zo min,ko da na fito kuma hatta kujerar an gyara.Wata azababiyar yunwa ce nake ji ban jinkirta shiga kitchen ba wurin anty Murjanatu ta zuba min na ci na ƙoshi na sha ruwa,ina fitowa na ga Yaya Khaleed sai wata irin kunyarsa ta kama ni.Na sunkuyar da kai ƙasa,ina jin lokacin da ya saki murmushi mai sauti kafin yayi wani furuci da yasa na yi saurin ɗago kai.

“Ammy kika ce sai in ta girma za a bani aurenta” shi ne abin da ya faɗa ko kunya bai ji,na dube ta ina jiran amsar da za ta basa “ Khaleed dukkan ku fa karatu kuke ko ka manta? Ita SEERAT ka ga ajinta na ƙarshe take za ta zana jarabawa,kai kuma da saura sosai kafin ka gama naka karatun”

“ Ammy ɗazu takardun da kika ga ina gyara ba na komai ba ne sai na shiga aikin soja,kin ga maganar aiki na magance ta ita kuma SEERAT sai ta ci gaba da karatunta ba wata matsala ba ce”

“Hum! Wa zai bari ka tafi aikin soja ? Ni? Allah tsare ni”

“Don Allah Ammy kar mu yi haka da ke,a kodayaushe kece kike faɗa min farin cikinki shi ne nawa kuma duk abin da nake so kina sonsa”

“To na ji ka bari har Yaya Ɗayyabu ya zo sai na ji yadda za a yi”

“Har da maganar auren?” Khaleed yayi saurin tambaya,Ammy ta ɗan haɗe rai ta ce “ shekarunka nawa wai kake ta sauri haka? Ashirin da biyu ne fa” ya shagwaɓe fuska ya ce “ to ai auren wuri ya fi kan sai mutum ya tsufa”

Da sauri na yi ƙasa na ɓuya bayan kujera ganin yana satar kallona,saitin zuciyata na dafe ina jin tana buga min fat!fat! Ba komai nake tunawa ba sai rayuwar cikin auren don ƙarancin shekaruna ba su hana ni sanin komai ba.Duk hirar da suke yi ina jin su,har mamaki Khaleed ke bani ta yadda bai jin kunyar mahaifiyarsa.

Ina nan zaune Basheer ya shigo gidan,tun zuwana dama ban gansa ba.Kusa da ni ya zo ya zauna yana nuna min wani abin harbi da yayi,na saki murmushi na amsa tare da jan kaushu ɗin na ce “ ashe za mu ci tsuntsaye,ai dai ka iya harbin ko?”

Ya jinjina kai alamun eh don ba kullum yake magana ba,wanka ma sai Mama ta yi da gaske yake tamkar wani ruwa biyu haka yake yin shirme.Wannan wunin biye masa na yi wurin taya shi shirmen sai na ga hakan ya wanzar masa da farin ciki,kiran sallah yasa duk kowa ya watse ya bar ni hatta Basheer sai da ya tafi shi da Khaleed ina zaune ina tunani na hango wani ƙaton gidan gizo-gizo a tsakiyarsa wani ƙaton ido ne fari ƙal da shi kamar na macen kifin ruwa.Da sauri na tashi ina shirin kai hannu na ɓata saƙar Khaleed caraf da shi ,na kalle shi sai ya min wata muguwar harara ya ce “ hannunki za ki saka a maimakon ki ɗauko icce ko tsintsiya”

Na ja numfashi ina duba saƙar sam idon da na hango ya ɓata,sai na ɗauko tsintsiya na cire shi.Bayan nan kallo muka sa a TV muna kallon wani shirin indiya hausa,da an zo inda suke kissing sai Khaleed ya ɗauki remote yayi tariya ni kuwa haushin haka nake ji har na kasa haƙuri na ce “ Yaya Khaleed mu dai don Allah ka bar...” saurar maganar ce ta laƙe min a maƙoshi sakamakon shegen kallon nan da yayi min,da sauri na tashi na koma can uwar ɗaka ina jin haushi.Baccina na sha ban san lokacin da suka tafi gidansu ba,bayan na tashi na yi wanka na canza ƙunzuguna sanan na fito na ci wani abinci tare da kama musu aikin gida.

Bayan sallar magarib muna zaune aka kira Mama wai Yaya Khaleed babu lafiya suna asibiti.Sai da Daddy ya zo sannan muka wuce can inda aka kwantar da shi,muna shiga idonsa ƙurrr a kaina har sai da na tsargu.Duk kowa yayi masa ya jiki banda ni da na sunne kai,ina jin Ammy Habibah na yi wa Daddy bayanin cewa wai ciwon cikinsa ne ya motsa shi kuma Daddyn ya soma yi masa nasiha mai kamar faɗa ban fahimci komai ba abin da na riƙe kawai an ce ya daina tunanin duk abin da zai motsa ciwon.

Likita ya shigo yana mai cewa “ zan yi ma allura a cinya tun da ƙarin ruwan ya ida” nan fa na ga ikon Allah,kamar wani ƙaramin yaro haka Yaya Khaleed suka fara kokowa sai da Daddy ya riƙe shi aka yi masa allurar.Mi zan yi in banda dariya,ai kuwa na shiga ƙyalƙyatawa ina kallonsa,yau dai duk harar da yayi min ban ji wani tsoronsa ba mun ɗan jima kafin mu koma gida .A daren sam kasa baccin kirki na yi ina ta tunanin abin da ke damunsa ga kuma tunanin makaranta da za mu koma gobe.

Washegari tun safe Mama ta ɗumama min ruwa tare da cewa na yi wanka da su,bayan na gama ne na fito ta miƙo min pad Always da wasu sabbin pant da kuma uniform ɗin makaranta.Cike da kunya na shirya a gabanta,ita kuma ta soma yi min nasiha irin wacce iyaye kan yi wa yaɗansu in sun fara jinin al'ada.

Abinci na ci na karɓi kuɗin da zan sayi wani abu kafin na fita zuwa makaranta,babu wani nisa nan bayan gidanmu ne a ƙafa na je.Cak na yi tsaye ina kallon yadda ɗalibai suka yi dandazo a wurin wata mai sayar da dambu,da wani bala'in sauri na je na fizge ledar dambun hannun Ubaidah ina mai cewa “ kar ki ci don Allah” ta waro ido tare da rungume ni tana cewa “ Baseerat Bashir tun ɗazu nake baza ido ko Allah yasa na gan ki amma shiru yau na rige ki zuwa,kin ga yunwa nake ji wallahi” ta ƙarashe maganar tana mai son karɓar dambun na ce “ a'a ba za ki ci ba”

“To bari na sayi wani ”

Na dakatar da ita na ce “ ke dambun nan fa duk guba ce cikinsa” ta dafe ƙirji ta ce “ guba?” da sauri na ja ta can bayan aji ina rage murya na ce “ ke ba fa poison ba,a'a gubar tsafi kin san wasu yan kasuwa don su samu costumers suna yin abubuwan da ba su dace ba”

Wata irin dariya Ubaidah ta yi kafin ta ce “ yo kowa ma ai yana neman sa'a,ba ki ga ko ɗalibai in za a yi jarabawa ba suna kai bironsu wurin malamai?”

Na girgiza kai don na fahimci ba za ta gane ba,na ce “ zo ki ga na nuna miki wani abu” na ciro sarƙar wuyana tare da ɗora ta kan dambun nan take yayi baƙi ƙirin kamar gawayi.A tsorace Ubaidah ta ja baya na ce “ ke kar fa ki ji tsoro,bari na sayo dambun waccan baiwar Allah wacce babu mai saya sai mutane ƙalilan” na je na sayo na ɗora sarƙar amma bai yi komai ba,Ubaidah don tsiya sai ta ƙara zuwa ta sayo dambun na ƙara ɗora sarƙa ta ga ya koma baƙi ƙirin.Da ni da ita babu wacce ta zargi sarƙar sai dai mai dambun kawai,wanda kuma ni kaina ban san da akwai rufaffen RUHIN ALJAN (MRS SADAUKI mai son complete 500 ne) a cikin wannan sarƙa ba.

Kʻarar rawa aka kaɗa wannan ya saka duk muka nufi aji, Ubaidah banci guda muke zama ni da ita tun ranar farko jininmu ya haɗu da ita.Ba zan kira ta da ƙawata ba kai tsaye amma muna shiri da ita,ba yar asalin zinder ba ce daga ƙauye ta zo karatu.

Cours Madam ɗinmu ke yi mana,da zarar mun haɗa ido da ita sai ta janye nata ni kuma ina ta ƙoƙarin ganin ta tsayar da su wuri guda don fahimtar damuwar da na gani shimfiɗe a ruhinta.Amma tamkar ta fahimci abin da nake so ɗin sai ta bar kallon inda nake,Madam na da kirki sosai sannan ina ɗaya daga cikin ɗalibanta da take so.Tana gama cours ta fita,haka kawai na ji ina son take mata baya wannan yasa na bibiye ta ba tare da ta sani ba har muka shiga ofishin shugaban makarantarmu wanda yake masifaffe.

Kʻofa biyu ce ke da ofis ɗin,falo da kuma can ƙurya inda a can ne yake.Ni a na farkon na tsaya na kara kunne jikin ƙofa ina jin lokacin da take cewa “zan ajiye ma aikinka daga yau don haka ka fitar rayuwata”

“Madam Rakiya mi yasa kike barazana da igiyar aurenki? Ko dai ke ma so kike ki bi layin sauran Madam ɗin da suka yi biyu babu? Ba su ga auren basu ga aikin ?” ina

jin cikin kuka tana basa haƙuri tare da cewa “ amma ai dai ka san ba mu riga mun aikata masha'ar ba ko? ”

“Ke ce kika san wannan amma shi mijinki kina tunanin zai yarda ne muddin na tura masa hotunan da kika turo min?”

“Don Allah ka rufa min asiri ,na ji na yarda amma ka yi min alƙawari sau ɗaya tak za mu yi abin nan”

“Yawwa ko ke fa,ai ni dama sau ɗaya nake neman mace” na ji muryar shugaban yana mai matso ƙofa ya murɗa key.Na dafe saitin zuciya ina mai cewa “ kutumelesi wato a haka ne da yawan mata ke faɗa wa zawarci,su je su yi iskanci da aurensu in miji ya gano ya sake su” gigitacen marin da na ji ya kifa mata ne ya dawo da ni da soki burutsun da nake,yayin da furucinta kuma yasa na yi amfani da tafin hannuna na buɗe ƙofar da aka sa wa key.A tare duk suka juyo suna kallona cike da tsoro da razani, shugaban makaranta ya wani wurgo bindinsa na kifi da niyyar cutar da ni sai dai me zan gani? Sarƙar wuyana ce ta ɓalle ta rikiɗa izuwa ƙaton kifin da hankali ba zai ɗauka ba ta haɗiye shi sarai.Madam ta saki ihu ta rakuɓe a jikin bango,yayin da ni kuma na duƙa na ɗauki sarƙarta wacce tuni ta dawo normal ina nufar Madam kawai ta faɗi a sume.....

Chères sœurs de la population D'Agadaz, CHAFA'ATU MAKE UP

Vous présente une formation en maquillage et différents attaches foulard,pose faux cils .Les frais de la formation est de 20.0000F pour une durée de 2 semaines .Pour plus d'informations contactez nous au 88584336.

```MRS SADAUKI✍```

BONUS

My book is only 500 via
```

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne

_____

BOOK2 27/10/24

11

Assalamu alaikum,mata da yan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

Tamkar ƙyaftawar ido Bafulatanar matar nan wacce na saba gani a bacci ta bayyana cikin ɗakin,da ido kawai ta kalle ni na fahimci abin da take nufi kawai sai na fito daga ofishin shugaban makaranta wanda zuwa yanzu yana tare da ni a cikin sarƙar wuyana.Na ɗan saki murmushi ina mai kai hannu kan tsakiyar sarƙar daidai zanen kifin,wani irin motsi na ji tamkar ana dambe a ciki.Na ɗage dukkan kafaɗuna irin ko ohon nan,sannan na wuce aji Ubaidah na ganina ta ce “daga ina kike? Tun ɗazu nake neman ki”

“Ina toilet cikina ne ya ɗan murɗa” na bata amsa.

“Hum! Duk kin koma wata iri daga zuwa hutun makaranta amma tamkar an canza ki,ke ce yau kika shiga banɗakin makaranta alhalin kullum cikin zagin masu shiga kike?” shiru na yi ban bata amsa ba sai ma tunani da na soma na abin da ya shuɗe can baya,ɗaya daga cikin abin da yasa na ce na tsani banɗakunan shine kusan masu iskokai duk a nan suka same su,da zarar an soma ruƙiya aljani zai ce ɗalibar da ta shiga toilet ya ga ta yi masa ya shige ta,abu na biyu kuma da idona na taɓa ganin baƙar mage mai idon mutane kan katangar banɗakunan tana yawo kai kace sojan da ke bakin iyaka.

“Keeee?” Ubaidah ta katse min tunanin,na dube ta na ce “ ya aka yi?” da ido ta yi min nuni da malaminmu wanda ke koya mana French sai murmushi take,na ɗan haɗe rai ina hararar ta saboda na san tun da farkon shekara ta kamu da sonsa.

Cours ɗinsa yayi ya gama,Ubaidah uwar iya yi ta tashi ta ɗauki jakarsa don kai masa aji na gaba da zai bayar da karatu.Ina nan zaune ta same ni,yadda bakinta ya ƙi rufuwa yasa na ce “ halan ya yarda da soyayyarki?” kamar ƙaramar yarinya ta wani gyaɗa min kai kafin ta rungume ni, murmushi na saki da na tuna Yaya Khaleed “ ni ma na fara soyayya” na faɗa kamar suɓutar baki,“ da gaske? Nan makarantar yake?”

“A'a Yayana ne” shigowar teacher ya hana hirar tamu yin tsayi ita ma tana gama nata cours ɗin ta fice, dama yau darussa uku ne gare mu kawai sai ajin ya soma watsewa amma sam ban ga Ubaidah na da niyyar tashi ba.

“Ke ba za ki je gida ba?” na tambaye ta ina saɓar jakata.

“Zan je mana,ina jiran Awwal ne ” ta bani amsa,Awwal wani ɗan ƙauyensu ne ba tare da na damu ba kuwa na fice na bar ta nan.

Kafin na isa gida sai da na tsaya na saya wa Basheer biscuits da wasu abubuwan don tamkar ƙaramin ƙanena haka na ɗauke shi, musamman in yana yi min shirme sam ban ɗaukarsa matsayin ɗan uwan tawaicina.Ina shiga ciki kuwa da shi na soma cin karo,jikinsa duk yayi fututu amma haka ya zo ya rungume ni yana ce min “ da ba ki nan Daddy ya kawo mana sabuwar Granny ” na yi dariya tare da ciro abin da na sayo na basa na ce “ Yau ba ka je makarantar islamiyya ba kenan?”

“Na tafi” ya bani amsa yana ƙoƙarin cire ledar biscuit na karɓa na buɗe masa sannan na ce “shine kuma ka yi duk wannan uban dattin?”

“Yanzu zan yi wanka,wasa muka gama yi”

“Kai da wa?” na tambaye shi.

Ya juya yana nuna min wani sashe sai dai ni ban ga kowa ba,“ ga su nan”

“Babu kowa Basheer” na faɗa ina ƙara ware ido don ko Allah yasa zan ga wani abu da zai ban tabbacin ba shi ɗaya ba ne.

“To abokai sai an jiman ku na gode” Basheer ya faɗa yana ɗaga hannu sai washe baki yake,na yi tsaye sororo ina kallon ikon Allah tare da zancen zuci ‘ wato shi Aljanu ma yake gani?’ muryarsa ce ta katse ni inda yake cewa “ SEERAT sai kace wani ƙaramin yaro kin wani sayo min biscuits,a maimakon ki taimaka min wurin roƙon Mama ta bari na koma makaranta a'a sai dai ki sayo min tsaraba ”

“Yi haƙuri za ka koma” na faɗa ina mai yin gaba ,tare da mamakin halayyarsa da ke canzawa lokaci zuwa lokaci.A falo na tarar da anty Murjanatu tana zaune ta rabka uban tagumi,ban damu ba don kusan dama kullum a haka take cikin damuwa wani sa'in ma har da kuka musamman in sun keɓe ita da Mama suna hirar mazajensu.Na gaishe ta tare da wucewa can ɗakinmu,wanka na yi na canza kaya sannan na fito ina tambayarta “ ina Mama ta tafi?”

“Tana asibiti wai Ammy Habibah ce babu lafiya ita ma,ina ga ciwon Khaleed yayi tsanani shine ita ma ta kwanta” anty Murjanatu ta bani amsa.

Babu shiri na je na ɗauko hijabin Mama na saka tare da ficewa,banda kuɗi hannuna hakan yasa na shaida wa mai adaidaita sai in mun je can zan karɓo na basa .Yana ajiye ni ƙofar asibitin na fita a guje duk hankalina a tashe yake sai kuma na yi turus sakamakon hango Mama da na yi zaune ita ɗaya sai murmushi take,fuskar nan wacce kullum cike take da ƙunci yau dai ga shi na ganta cikin walwala tana murmushi har gefen kumatunta suna lotsawa.Horne ɗin da mai ɗan sahu yayi ce ta maido ni hayyacina na yi saurin isa gare ta ina cewa “ Mama bani dala talatin” miƙo min ta yi na je da sauri na kai masa,da na dawo na soma tambayar ta masu jiki “ ki shiga suna ciki duk da sauƙi” na wuce ina kallon ta a zuci na ce ‘ alhamdullah Allah da ka nuna min ranar da Mama ke cikin tsantsar farin ciki ’ na tura ƙofa na shiga idonmu ya sarƙe cikin na juna kawai sai na yi tsaye ina ƙare masa kallo.Sanye yake da farar singlet duk ƙirarsa ta bayyana,fuskarsa ta faɗa sai hakan ya fiddo manyan idonsa irin na masu jin bacci .Kyawu na ga yayi min fiye da kullum,sai na sakar masa da murmushi kafin na isa gare shi,bakin gadon na zauna ina mai cewa “ ya jikin?”

Ya dubi can gefe,ni ma na kai dubana sai na ga Hajiya ce a kishingiɗe sai bacci take yi kusa da Ammy Habibah wacce ita ma baccin take ga ƙarin ruwa an saka mata.

“Nan nake jin yana tsira min SEERAT ” muryarsa ta dawo da hankalina kansa,na dubi daidai inda ya ɗora hannunsa can ƙasan cikinsa sai kuma na ɗago muka haɗa ido da shi.Hawaye tab idonsa ya ce “ ji nake kamar ba ni ne ba SEERAT ” ƙiiiii na ji an buɗe ƙofar shigowa na waiga sai na ga Bafulatana ce,daga can jikin ƙofa ta soma yi min bayani “ ɗaya daga cikin likitocin da suka kula da shi yau,wani ya so sace semen/semence ɗinsa amma bai yi nasara ba to shine dalilin da yasa yake jin zafi a wurin”

“Dama ana iya sace masarrafar ƙwayaƙwayin haihuwa?” na tambaye ta,kai kawai ta jinjina min,“ to mi zai yi da su? Ta yaya za a ce ana satar ƙwan haihuwa?”

“Seerat a duniyarmu babu abin da matsafa ba su yi ke dai kawai a gode ma Allah tun da dai shi ɗin dodon mugaye nr”(Ga masu son sanin jin yadda ake sace semen da kuma abin da ake yi da shi za su iya neman book ɗina na MAITAR IDO)

“Mi kike kallo haka?” ya tambaye ni,sai na yi saurin maido dubana gare shi ina mai cewa “ zai daina ai”

“Allah sa ”

“Amen!” sai kuma muka yi shiru,ina jin idonsa a gare ni sai wani numfashi yake saukewa.Na ɗago na dube shi ,murya na ɗan rawa na ce “ Wai Yaya Khaleed mike damun ka?”

“Ke ce SEERAT ” ya ban amsa cikin taushin murya,ido na tsura masa don jin ƙarin bayani sai ya ci gaba da cewa “ da zarar an yi aurenmu shikenan ”

Na ja wani dogon numfashi ina jin ƙaunarsa na tsarga mini duk wani ɓargo.Tsawon lokaci muna aikin kallon juna kafin Mama ta shigo,“ har yanzu ba ta tashi ba? ”

“Eh tun da na shigo bacci suke”

“Ya karatun?” Mama ta tambaye ni,sai yanzu ma na tuna da Madam Rakiya a zuci na ce ‘ ko ya Bafulatana ta yi da ita?’

“Ba ki jin ana tambayar ki ya karatu?” muryasa ta katse ni,sai a lokacin na amsa da “ alhamdullah Mama ” sai kuma muka hau hira.Daddy ne ya kawo mana abincin da muka ci,wuraren ƙarfe shidda na maraice Mama ta ce “ SEERAT tashi ki kama mana layi yanzu likitan zuciya zai hau aiki na ga ma tuni mutane sun fara zuwa”

Da “toh” na amsa tare da karɓar takarda mai ɗauke da sunan Ammy Habibah da dukkan alamu hawan jininta ne da ya hau yasa take da buƙatar likitan zuciya ya duba ta .

Nan falon asibitin na fito na samu wuri na kama layi,kamar tururuwa kuwa haka muka taru sosai a wurin.Ina nan zaune sai ga wasu mata su biyu jaye da wata tsohuwa tuguf sai sannu ake yi mata kafin su zaunar da ita.Luf tsohuwar ta yi jikin kujerar ta soma bacci,har zan ɗauke idona a kanta amma wani abu ya ja hankalina.Daga bakinta take fitar da wani abu baƙi mai kamar inuwa shi ma sak yanayin gangar jikin mutum,shiru kawai na yi ina kallo har lokacin da inuwar ta yi tsaye kan ƙafafunta nan na fahimci tsohuwar nan baƙin ruhinta ne ta fitar cike da son ganin ƙul uwar daka na gyara zama.A gaban idona ruhin tsohuwar ya je kusan wata mata wacce ke rungume da ɗanta da bai zai wuce shekara ɗaya da wasu watanni ba,wandon yaron ta zumbule ta soma nuna masa jikinta tana son yin lalata da shi dab da za ta cin nasara na buɗa baki a hassale na ce “ keee mine ne za ki yi?” a firgice ruhin tsohuwar ya juyo ya dube ni kafin ta fara ƙoƙarin komawa a gangar jikinta sai dai yadda sarƙar wuyana ta yi wani zillo ta cabko ruhin ta haɗiye ya ƙi bata damar haka.

Na kai hannuna na shafi sarƙar lokacin da waɗanda suka kawo ta suka soma jan “ Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un! ” wannan karon ma motsi nake ji daga ciki,wanda ban san na mine ne ba.Mama da Ammy Habibah ne suka fito,sai kuma suka tsaya ban magana suna yi musu ta'aziya ,duk mutanen wurin babu wanda lamarin bai tsorata shi ba amma ni ko oho .

Yadda Ammy ke yi min wani kallo na fahimci tamkar tana son gano wani abu ne amma na kawar da kaina gefe,tare da tashi na bata kujerar ta zauna babu jimawa

kuma likitan ya zo.Ɗakin da Yaya Khaleed yake na koma,can na rakuɓe na shiga tunanin taƙamaimai abin da ya faru yau ,ga shugaban makaranta da kuma na wannan tsohuwar.A can ƙasan zuciyata na tambayi kaina ‘ to mi yasa sarki ya bani sarƙar nan? ’ sai dai banda amsar doli na yi shiru.Har lokacin da su Mama suka dawo Ammy Habibah na ci gaba da yi min wannan kallon amma na basar,da dadare sai ga anty Murjanatu ita da Basheer Daddy ya kawo su.Abincin da suka kawo aka umarce ni da na zubawa Ammy da alamu special aka yi mata don an hana ta cin magi,plate ɗin da na zuba abincin na miƙa mata .Murya can ƙasa take cewa “ ki dinga kula da kyau yayin aikinki,ban son jinkiri don in kin tsaya sanyin jiki maƙiyi zai iya yin nasara akan abin hari” murmushi kawai na saki mai sauti,wato tsayawa da na yi kallon abin da tsohuwar ke da niyyar yi kuskure ne , Ammy na son nuna min inda tun da ta fitar da ruhin na damƙe shege.

Kusa da Khaleed na je na zauna kamar an ce in duba screen ɗin wayarsa nan na hango Ubaidah kwance cikin mawuyacin hali ƙofofin hancinta sai zubar da jini suke.Hannu'a har rawa yake wurin karɓe wayar ina karanta rubutun da aka yi a ƙasan hoton ```an tsinci wata ɗalibar makaranta a cikin ajinsu a mawuyacin hali,bayan an yi mata fyaɗe kuma an yi ƙoƙarin kashe ta,su waye suka yi mata wannan aikin? Har yanzu yan sanda na kan bincike``` banda tafasa babu abin da zuciyata ke yi, musamman yadda na ga rigar ta duk ta ɓace da jini fuskarta a kumbure,babban abin baƙin ciki kuma shi ne an yi mata fyaɗe.

“Kin san ta ne?” Yaya Khaleed ya tambaye ni,kai na gyaɗa masa kafin na ce “ ko wace asibiti ce aka kai ta?” “ga shi a rubuce babbar asibitin gwamnati ”

Tsam na miƙe na fita,ɗan sahu na samu ya kai ni can yana tsayawa na dire ban biya ba kuma bai tambaye ni ba.Asibitin mutane na ta shiga don lokacin ziyara ne ban sha wahala ba ,sai da na nufi inda nake tsammanin can ne ɓangaren da aka kwantar da Ubaidah duba da yadda yan jarida ke tsaye.

Wani likita na gani a tsaye yana cewa “ kar ku bari kowa ya shiga in ba dai ma'aikacin jinya ba,yarinyar tana cikin choc har yanzu ba za ta iya yin magana ba,an ce ku bari har gobe amma kun ƙi” da sauri na yi baya ina jan tsuki daga

bayana na ji ana saka min riga ko da na duba sai na ga Bafulatana ce,kayan likitoci ne ta bani har da abun sauraron bugun numfashi da abin maƙalawa a hanci.Ba ta taɓa burge ni ba irin na yanzu har da godiya na yi mata kafin na saka komai kan tsari na nufi ɗakin da aka kwantar da ita,masu tsaron ƙofar yɗan sanda ne wannan yasa suka wani dakatar da ni “ wannan yɗar yarinyar ce likita?” cikin French na mayar masa da cewa “ ai ba shekaru ke aiki ba” sai ya ban hanya na wuce,cak na tsaya a bakin ƙofa ina kallon yadda aka saka mata na'urori a jiki.Na taka a hankali na isa gare ta,ina shirin ɗora hannuna jikinta daga bayana na ji an ce “ wace ce ke?” ba sai na juyo ba,ko cikin dubu ai ɗalibi zai iya shaida muryar malaminsa.Ido kawai na rumtse ina jin baƙin cikin na ƙara hauhawa a zuciyata,mutumin da yau saboda ya amsa mata tayin soyayya ta shiga tsantsar baƙin ciki wato shine silar komai. Biris na yi da shi duk da kuwa ina jin yana ƙoƙarin bayyana ɓoyayyar siffarsa wacce ba a da ita yake yawo ba,“kar ka ɓata wa kanka lokaci don ƙaramin tsafinka ba zai aiki a kaina ba ” na furta tare da danna saitin zuciyar Ubaidah nan take ta wani zabura tana jan numfashi yayin da kuma danjojin da aka saka mata suka fara kuka.

“Mi kike haka kar ki maido ta duniyar nan” Malaminmu ya furta yana mai zuwa shi ma da niyyar mayar da ruhin Ubaidah can duniyarsu ta ɓoye amma kifin jikin sarƙata ya kai masa wata irin cabka wacce ta wanzar masa da zubar jini,powersa kuma ta fita sarai daga jikinsa ta shige jikin sarƙar kafin komai ya koma normal.Ya faɗi a sume ,yayin da likitoci suka shigo da yɗan sanda na san kuwa ba komai ya jawo hankalinsu ba sai ihun malam da kuma kukan na'ura.

“Mike faruwa a nan?” wani ɗan sanda ya tambaye ni yana kallon malam da hannunsa ke ta zubar da jini,kai tsaye na basa amsa kan cewa “ yayi ƙoƙarin kashe ta ne shine ni kuma na yi amfani da wancan dutsen zafin na hana shi”

Likitoci kuwa cike da mamaki suke kallona gani na a cikin kayan aiki alhalin kuma ni ba nurse ce ba,ga shi kuma na maido patient ɗinsu cikin hayyacinta.

Tuni aka fitar da malam zuwa wani ɗakin don basa taimako,yayin da kuma ɗaya daga cikin yɗan sandar ke cewa “ ita ma doli mu riɓe ta wurin mu ”

“Eh dama sai haka” babban likitan ya faɗa ,nan aka tisa ƙeyata zuwa waje aka kai ni cikin mota babu ɓata lokaci kuma aka nufi da ni police station wanda kuma zuciyata take da yaƙinin tabbas ba banza aka kawo ni ba nan ɗin ma akwai aikin da zan yi.Ai kuwa tun a falon ofishin yanayin jikina ya bani da matsala,ina baza ido sai na ga ashe mugaye sun kawo wa ofishin caffa.

Cikin raga aka ingiza ƙeya ta,na shiga tare da kallon wata matashiyar budurwa wacce idonta ƙurrr kaina kamar ma ta san da zuwana.“ Ina jin ki ? Mine ne matsalar?” ta ja wani dogon numfashi kafin ta ce “ gaske ke ce wacce za ki fitar da ni a nan?”

Can jikin bango na je na zauna na ce “ in ba za ki faɗa ba ki riƙe labarinki,zuwa gobe dai zan bar wurin nan don haka shawara ta rage ga mai shiga rijiya”

“Yi haƙuri na gan ki yɗar ƙanƙanuwa ne”

Na ɗago na yi mata wani mugun kallo kafin na ce “ to sannu uwar mata” sai ta saki murmushi tare da zuwa kusa da ni ta zauna,shiru kamar ba za ta yi magana ba kafin ta ce “ Ni karuwa ce”

“Na sani Malama ki je kai tsaye ga kanun labarai in kuma kika jinkirta kin ga yɗan sandar can wajen huɗu? Duk an shiga tunaninsu mugun duka za su yi miki har sai kin mutu kuma sun kashe banza”

“Bayan mutuwar aurena na shiga ƙuncin rayuwa na talauci da tsangwama a wurin mahaifiyata,abinci ma ba ta bani sai in ta ga dama.Kullum cikin gorin na kashe aurena na dawo mata a gida ina takura ta take yi min,ko sau ɗaya bata taɓa tambayata dalilin mutuwar auren ba.Rayuwar ZAWARCI mai cike da ƙunci,damuwa da kuma da na sani su suka ingiza ni izuwa bazama neman malamai da bokaye.Burina kawai shine in ga na yi aure,an ci kuɗina sosai amma ban dace da samun mijin ba sai farin jinin zawarawa maza da ke zuwa wurina da farko kamar gaske a ƙarshe kuma sai su nuna kawai lalata ce ta kawo su” tana kawowa nan sai ta yi shiru tare da ɗagowa ta kalle ni tsakiyar ido,“ hum! Tun kina bijirewa har ta kai kawai kika fara yarda da su kuna ban manda na baka gishiri ko?” kai ta jinjina min kafin ta ce “ cikin rashin sa'a kuma wani malami ya ban laƙanin tatsar alijihun maza,ashe ban sani ba cuta ya bani duk namijin da ya kusance ni cikin ya ɗau lokaci to kwana uku zai mutu”.....

Littafina na kuɗi ne Hajiya ,ki cire maƙo ki biya kuɗin karatunki 500 ne kacal duk wacce ta shirya ta yi min magana ta WhatsApp +22795045822

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI□✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim
```

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK2

12

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

A tare muka sauke ajiyar zuciya,kafin ta ci gaba da bani labarin “ to da farko na damu a ƙarshe kuma sai na ga tamkar ma jihadi ne nake yi,ko ba komai an rage mugayen maza masu cin amanar matansu a waje.Sati biyun da suka wuce na zo zinder,nan ne fa muka haɗu da wani matashin yana da mata,a nan unguwar da na sauka suke har da ma mahaifansa.Soyayyar kwana uku kawai muka yi kafin ya gayyace ni gidansa tare da shaida min matarsa ta tafi wurin biki,da farko ya nuna kawai yana so na ga tsarin gidan ne amma da na je sai ya fake da yin lalata da ni ban ja masa aji ba na bada kai bori ya hau.Muna tsaka da holewa matarsa ta rutsa mu,a kunyace na mayar da kayana na bar gidan .Kwana biyu da yin haka ya mutu shine suka kawo min sammaci a cewarsu da asiri na kashe musu ɗan uwa ”

“Yadda kike biyar malamai to shi a danginsa matsafa ne,su kansu suna da bokaye masu kawo musu rahoto.Ni yanzu ban ma san dalilin da yasa ake so na cece ki ba alhalin muguwa ce ke” na yi furicin tare da miƙe wa na je can jikin raga na yi tsaye tare da kama ƙarafanta.

“Ki taimaka mini don Allah,na yi miki alƙawari daga yanzu ba zan sake sanadiyar mutuwar wani ba .Zan tuba na koma ga Allah har ya kawo min mijin da zan aura”

“Hum! Shi kuma tsafin da kika sa aka yi miki? Za ki koma wurin malamin ya karya shi ko ya?” na tambaye ta ina mai juyowa muna facing juna.Shiru ta yi na ɗan wani lokaci kafin ta ce “zan koma na yi miki alƙawari,kuma ma fa duk tsafin da aka yi ni ce da hannuna na binne su in na tone su na ƙona hakan ya yi? Ya isa ba sai na je wurinsa ba?”

“Eh!” na bata amsa tare da soma yin motsi da hannuna na hagu,daga inda nake tsaye nake jujuya duk abin da na ga dama har na binciko takardar shiga ƙarar da aka yi mata,na canza fasalin rubutun.

“Mi kike haka?” ta tambaye ni,amma ban bata amsa ba har sai da na tabbatar na ida da duk wata matsala sannan na ce “ zan buɗe miki ƙofar nan za ki fice,ki tabbatar zuwa gobe kin bar garin nan kin koma naku”

“Na gode sosai ” ta furta cike da murna,ƙofar na buɗe ta fita jikinta har rawa yake kafin na mayar da ita yadda take.Tunani ne barkatai suka dinga zaga kwanyata,wanda na fi jin daɗinsa shine na Yaya Khaleed ko da wasa ban taɓa sanin yana dakon sona ba sai jiya zuwa yau sam ya kasa controling kansa har yake furta min za mu yi aure.

“Ke fito” ɗan sandar ya faɗa yana mai buɗe min ƙofa,na fito ina murmushi kafin kuma na haɗe rai ina kallonsu ɗaya bayan ɗaya.

“Lafiya za a tara min yan jarida cikin daren nan?”

Ɗan sanda ya katsa min tsawa ya ce “ ke ki shiga hankalinki za su yi miki tambayoyi biyu ne kawai don cika umarnin gwamnan jiha ”

“Ya aka yi kika fitar da ita daga cikin coma alhalin likitoci sun yi iya bakin ƙoƙarinsu sun kasa?” tambayar farko da wani ɗan jarida ya jefo min kenan,a ɗan dake na basa amsa “ba ni ce na fitar da ita ba,Allah ne ya nufa ta farfaɗo a daidai lokacin da na shiga cikin ɗakin”

“Mi ya kai ki ɗakin alhalin an hana kowa shiga ? Ina kuma kika samu rigar likitoci ?”

“Ta wata nurse ce na saka,na shiga ɗakin ne saboda a duniya ita ɗaya ce zan nuna a matsayin ƙawata” ina gama faɗa na nufi hanyar komawa amma suka tsayar da,“ kuka ce tambaya biyu ? To ai na yi” na faɗa ina kallo su tsaf don na san duk ƙarya suke ba wannan ce tambayar da suke son yi min ba.

“Mi yasa kuke wani bin ta a hankali? Ke faɗa mana gaskiya ko kuma mu yi miki shegen dukan tsiya,malamin da kika jima ciwo a hannu wane magani za a saka masa don ya warke?” ɗan sanda ya faɗa ,na lura duk cikinsu ya fi su zafin rai .Amma na basar na ce “ to yalaɓai ta ya za a yi ni na sani alhalin ni ba likita ba ce? ”

Duk suka kalli juna kafin wani kuma ya sassauta murya ya ce “ kina ji yar baiwa don Allah taimako za ki yi, dukkaninmu nan mun san ke ce za ki iya faɗar maganin da za a basa saboda a can asibiti da zarar an yi masa allura hannun ne ke ƙara kumbura,abu guda kawai likitoci suka yi nasara yi shine farfaɗo da shi daga suma.In taƙaice miki magana dai hannunsa ya soma ruɓewa,shine da bakinsa ya sanar da mu cewa ke ce silar komai” wani ya karɓe da ci gaba da cewa “ yanzu muna saurarenki ki taimaka komai kike so za mu baki”

Shiru na ɗan yi kafin na ce “ to ku kai ni na gansa” da murna kuwa aka ja ni zuwa mota wannan karon a can gaba na zauna har muka isa asibiti.Ɗakin da yake kwance na shiga,yan sanda biyu suka take min baya muna haɗa ido da shi ya soma kuka yana roƙona.

“Maganin da zai warkar da kai yana gare ka,zaɓi yana gare ka.Da zarar ka fito ka shaidawa duniya abin da ka yi wa ɗalibarka Ubaidah,da kuma dalilin yin haka to tabbas garas za ka warke in kuma ka ƙi sannu a hankali gangar jikinka za ta ruɓe gaba ɗaya”

Malam da yake kuka cak ya tsaya yana kallona,babu babban tozarci a wurin masu tsafi tamkar su tozarta kansu da kansu.” In ka shirya faɗa a samu ɗan jarida guda yayi maka video wacce za a watsa a duniya kowa ya gani,in kuma ka zaɓi mutuwar tozarci wannan kuma ruwanka” na faɗa tare da ficewa abun mamaki ko kaɗan yan sandar ba su yi yunƙurin tsayar da ni ba.Haka na yi tafiyar ƙasa har gida, toilet na shiga na yi wanka na canza pad tare da shirin bacci.

Washegari tun da safe Mama ta tashe ni,na yi shirin makaranta tsaf na fito ko abinci ban tsaya ci ba na karɓi kuɗi na wuce.Daidai ƙofar shiga makaranta na tsaya ina kallon matar jiya mai sayar da dambu sai wani surutu take tana kallon wani ɗan akwatinta na kuɗi.Na saki murmushi tare da nufar ta “ ina kwana Mama?”

“Lafiya lau yʻata dambun nawa za a baki?” ta amsa fuskarta cike da fara'a,cikin kuɗin da Mama ta bani na ɗauki 100f na miƙa mata amma abun mamaki sai ta ƙi karɓa sai kallona da tsaya yi.

“Ko ba za a sayar min ba?” na faɗa ina kallon tsakiyar idonta,tuni kuma akwatinta na katako ya soma yin motsi kamar zai tsage.Jikinta ne ya ɗauki rawa lokacin da ta ga na yi amfani da hannuna na hagu na nuna akwatin tare da furta “ shuuut!” halittar da ke ciki ta bar motsi,“ ki karɓa ki bani” na ƙara faɗa ina yi mata murmushin mugunta.

Hawaye suka zubo mata shaaa a kumatu kafin ta ce “ yʻata ki sani wani sa'in doli ce ke sa mu yi wasu abubuwa ba tare da muna so ba,ki ɗauka ni ɗin mahaifiyarki ce za ki ji daɗi ki ga ƙawayenki na zuwa makaranta alhalin ke kuma kina yawo a unguwa saboda mahaifiyarki ba tada kuɗin da za ta kula da ke? Ni bazawara ce mai yʻayʻa,a cikinsu ma har da ɗan tsintuwa.Nauyin kula da su duk yana wuyana,sana'ar in ka yi ba a siya shine dalilin da yasa ki ga na yi haka”

Duk da kalamanta sun dake ni amma na mayar da tausayin gefe na ce “ duk wannan bai isa su saka ki dinga cutar bayin Allah ba,ko kin san da cewa sa'ar kasuwa da malaman tsibo ke bayar wa tare take da ruhin aljani? Ita wannan halittar da kike ɓoyo ki sani cutarwa ce gare ki ga kuma al'umma.Kin ɓoye ta a nan ciki tana jawo hankalin mutane izuwa gare ki ko da kuwa ba su da niyyar cin dambun a ranar”

“Na sani amma ki duba halin da nake ciki na ƙuncin rayuwa”

“Allah ne ya ɗora miki sai ki yi haƙuri da juriya wata rana sai labari”

“To zan yi in sha Allah kuma na daina aiki da zoben” ta faɗa tare da buɗe akwatin,a idonta zobe ne amma ni a nawa jaririn kunkuru ne da sauri na karɓe zoben na yi gaba sai da na samu wani lungu sannan da kaina na baiwa sarƙar wuyana shi ta haɗiye.

Ina shiga can cikin makaranta na soma jin labarin ɓatan shugaban makaranta wasu ma sun ce tun jiya yʻan sanda ke bincike a kai,gafe guda kuma hirar Ubaidah ce kan cewa an yi mata fyaɗe.Waɗanda basu da ta ido ma har ni suka tunkara da zancen amma na share,haka muka shiga aji muka yi cours muka gama ina fitowa na ji an kira sunana.Na waigo da sauri sai na ga Madam Rakiya ce,cike da ladabi na gaishe ta tare da cewa “ ya jikin?”

“Alhamdullah,don Allah in babu damuwa ina son neman wata alfarma ki zo mu je gidana” na saki murmushi na ce “ to Madam ” inda take ajiye motarta muka nufa a gidan gaba na shiga har muka isa wani danƙareren gida.Sai na yi ta mamakin ‘ to wacce ke cikin wannan gidan ce har za ta yarda ta bada kanta saboda kawai ta yi aiki?’ sai amma kuma wani sashen na zuciyata ya ce min ‘ duk abin da mutum zai yi tabbas akwai hujjar yin haka’ ashe kuwa zan samu duk amsoshina nan kusa.

Muka fito ta yi min iso har falo,yʻar aikinta ta kawo min ruwa da abinci na kuwa ci na ƙoshi.Sai bayan na nutsu ne Madam ta soma yin magana “ na gode sosai a bisa taimakona da kika yi,ni yʻar Sarkin garin nan ce ,mijina kuma abokin shugaban makarantarku ne.Mijina nada mugun kishi wannan yasa ya hana ni aiki,ni kuma babu abin da nake so sama da na ga ina koyawa wannan yasa na bi ta hanyar tsohon banzan can don sosai mijina ke ɗaukar shawarsa.Hum! Da ya ce min ai na san kowane tasiri yana da farashi ban yi tunanin jikina yake so ba sai bayan na soma koyawa”

Da ido na tsure ta sai yanzu na ga kamaninta da gimbiya Salmu,“ in babu damuwa ina son don Allah ki yi min wani aiki don daga jiya zuwa yau na gano ke yar baiwa ce”

“Bayan kin suma mi ya faru daga nan?” na jefo mata tambayar saboda abin da nake son sani kenan,ta bani amsa da “ tashi na yi na tsince ni a gadon asibiti ”

“ Ok to babu damuwa wane aiki ne kike so na yi miki?”

“Ina so ki dinga ziyartar masarauta,zan koma da can da zama na tsawon wata ɗaya ina so ki dinga zuwa kamar a matsayin ɗalibata ta yadda babu wanda zai zargi wani abu”

Na jinjina mata kai alamun na yarda,cike da murna ta je ta ɗauko min wata leda ta bani da kuma kuɗin taxi na yi godiya na baro gidan.Bakin titi na zo na yi tsaye ina jiran adaidaita,kamar an ce na juya ai kuwa sai na hangi motar Daddy a parker a wani ƙofar gida ya buɗe ƙofar wurin zaman direba yayin da kuma wata mata ke tsaye suna hira .Kallonta na yi ta yi kamar ina son tuna inuwarta amma na kasa tunawa kawai na basar na yi gaba abina.

#SAKEENATU

Bayan duk abin da ya faru sosai ta shiga ɗimuwa,a ranar suna isa gidansu Nafisa ta sanar da Mama komai wacce zuwa yanzu tsufa ya tunkaro ta.Babu abin da take yi na sana'a sai dai rufin asirin Allah,cikin haka suke rayuwa ita da Sakeenatu da kuma

yꞌarta Ma'idah.Tunani da damuwa duk sun ruguzar gangar jiki da ruhin Sakeena,dakyar ta iya jarumtar gyara takardunta ta soma neman aiki amma shiru kake ji babu aikin.

Yanzu ma daga wata sabuwar asibiti take wacce aka buƈa ta je ta kai takardunta,ko kuƈin da za ta shiga adaidaita ba tada haka ta soma tafiyar ƙasa tana yi tana hutawa.Wuri ta samu cikin inuwa ta tsuguna,tana tsaka da tunanin yadda za a yi ta isa gidansu cikin uwar ranar nan kawai sai gani ta yi mota ta tsaya a gabanta.

“Keenat?” ya furta bayan ya zuge madubin motarsa,tsabar tashin hankali ba ta san lokacin da ta yi daɓas ga ƙasa ba tana fiddo ido waje.Ya buƈe murfin motar ya fito,sanye yake cikin costume baƙaƙe haka ma takalminsa sumar gashinsa ya gyara ta sosai ta yi kyau gwanin sha'awa.

“Keenat dama zan sake ganin ki?” ya furta,sai a lokacin ta miƙe ganin yana shirin taɓa ta.

“Agali ban son iskanci ” ta furta tare da nuna shi da yatsa sai kuma ta soma tafiya kamar za ta tashi sama,duk yadda ya so ta tsaya ƙiyawa ta yi haka ya dinga biyar ta cikin mota har suka isa gidansu .

“Keenat don Allah ki tsaya ki saurare ni ” ya furta amma tuni ta shige cikin gidan,shi ma ya take mata baya yana faman kiran sunanta.Cak ya tsaya numfashinsa na barazanar tsinkewa ganin Ma'idah ta fito daga banƈaki,ita ma sai ta yi ƙuri tana kallonsa ganin hoton fuskarta a tattare da tasa.....

Assalamu alaikum,mata da yꞌan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ƈaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuƈin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta

wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK2

13

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍
```

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Ma'idah na kallon Agali ta raɓa ta shige kewansu,zaune ta tarar da Sakeenatu na sharɓar kuka yayin da Mama ke faman tambayar ta lafiya.“ Wani ne ga shi can waje shine ...” sai kuma Ma'idar ta yi shiru,kafin Mama ta ce wani abu ta jiyo Agali daga can waje yana sallama,ta amsa tare da basa izinin shigowa.

Suna haɗa ido da Mama ya sunne kai yana mai gaishe ta,ba ta amsa ba sai ido da ta zuba masa.Tun da take ba ta taɓa ganin Agali ba,amma ko mahaukaci ya gansa zai gane shine mahaifin Ma'idah.Haƙuri ya shiga badawa don kuwa ya lura hatta Mamar ranta ya ɓace daga ganinsa,“ a yi haƙuri Mama duk bawa bai wuce ƙaddara ba,ku ɗauka haka Allah ya ƙaddara mana za mu samu yɗarmu ta farko ta wannan hanyar.Amma in sha Allah yanzu na dawo zan gyara kuskurena na baya,na yi alƙawari zan kula da Keenat da kuma yɗarmu...” cike da masifa ta ce “ kar ka sake danganta yɗata da kai,Ma'idah tawa ce ni ɗaya ba ta san ka ba kuma ka sa a ranka wannan zuwan da ka yi bai isa yasa na yafe maka ba na tsane ka fita! Fita! Fita ka bamu gida” Sakeenatu ta faɗa kamar wata mahaukaciya tana nuna masa ƙofa shi kuwa Agali ido kawai ya zuba mata yana mamakin yaushe ta zama masifafiya.

Ganin bai da niyyar tashi ta zo ta cakumo shi da ƙarfin tsiya tana tura shi waje,gam ya riƙe hannunta yana mai kiran sunanta “ Keenat Please ki saurare ni mana wallahi ban zo nan da na cutar da ke ba”

Cikin takaici ta canza harshe daga Hausa zuwa French ta yadda Mama ba za ta ji abin da za ta ce ba,sai dai ta manta Ma'idah na wurin kuma ta yi boko.

“Waccar ranar ma haka ka faɗa min kalamanka na yaudara, Keenat ban yi haka don cutar da ke ba.Agali na tsane ka,duk wannan soyayyar da na yi ma a baya ka sani mummunan zunubin da ka aika ya goge ta,ka ɗauke ni ka kai ni ƙasar waje don

cutar da ni na yi tunanin taimakona ne ka yi ashe da wata manufa. Shekaru biyu ka kwashe kana nuna min soyayyar ƙarya ta yaudara,a shekarar ƙarshe wacce nake tunanin za ta zame min ta farin ciki saboda kammala karatuna a wannan shekarar ce ka fiddo min ɓoyayyar fuskarka ka shiga jirgi ka biyo ni ka cuce ni ,ka yi min ciki ka tafi ka bar ni da ɗawainiya shine yanzu ka dawo ka ƙara ruguza ni ko?”

“Keenat wallahi ban taɓa tunanin tarayyarmu da ke sau ɗaya tak za ki samu ciki ba,kuma da kika gano kina da ciki mi yasa ba ki neme ni ba?”

“Saboda na san ko na neme ka amsa guda za ka ban na zubar da cikin,ni kuma har abada ba zan aikata zunubi biyu ba.Yanzu dai fita ban ma san mi yasa nake ɓata lokacina ba ina sauraren ka”

“Zan tafi amma ki yi min alƙawarin in na sake dawowa za ki saurare ni”

“Ban yi ba,fita!”

Agali ya dubi Ma'idah wacce ke faman zubar da hawaye,tun da take ba ta taɓa sanin cewa ita shegiya ba ce sai yanzu.Tana ganin ya nufo inda take ta yi saurin shigewa ɗaki Sakeena ta take mata baya,ya ciro kuɗi masu yawa ya ajiye saman kujera kafin ya fice .

Juyin duniya Ma'idah ta ƙi barin kuka,rarrashinta suke amma ta ƙi har Nafisa aka kira ta zo ta yi mata nasiha amma ta ƙi haƙura.Zazzaɓi tuni ya rufe ta ga kuma amai babu tsayawa,kuɗin da Agali ya bari suka yi amfani da su aka kai ta asibiti sai da saka mata ƙarin ruwa kawai bacci ya ɗauke ta.

Suna nan zaune jungum Nafisa ta katse shirun da cewa “ anty Sakeena ya fa zama doli ki ture dokin zuciyar nan ki tsaya ki saurari Agali,kin ga dai halin da kuke ciki a gida abincin da za a ci ma wuya yake.Aikin ma shiru kin ƙi samu, maimakon wannan fushin da kike da tunanin gobenki kika tsaya kika yi da zai fi.Allah ne da kansa ya ce a cikin tsanani akwai sauƙi,ta yiyu zuwan Agali alkhairi ne a gare ki da ma mu kam .Amma shawara ce kawai in kin ga ta yi miki ki ɗauka,in kuma jiran Abbas ɗin za ki yi ai shinenan ” Nafisa na zuwa nan da zancenta sai ta juyar da kai ganin Sakeenatu ta soma shiriritar kuka kamar wata ƙaramar yarinya.

“Amma ai dai kin san irin yadda ya cutar da rayuwata ko?”

“Ko ma dai mine ne ai ke ma da laifinki,a tare kuka aikata kuskuren nan kenan sai a taru a rufawa juna asiri ita kanta Ma'idar hankalinta zai fi kwanciya in tana zaune gidan mahaifinta”

Sakeenatu ba ta ce komai ba ta ja bakinta ta yi shiru,ƙarin ruwan da ya ida aka cire.Haka suka jira sai da ta farka sannan suka dawo gida,ayaba kawai Ma'idah ke iya ci sai lemu exotic.Sai bayan sallar magarib Nafisa ta koma gidanta,ana sallar isha'i kuwa samari suka fara shigowa da kayan abinci .Can kuma sai ga wani mutum ya shigo kana ganinsa ka san ya haɗa iri da Agali saboda kamar da suke,bayan an basa izini ya zauna ya gaishe da su sannan ya gabatar da kansa “ Ni yayan Agali ne ,ya shaida min duk abin da ya faru a madadinsa ina mai sake baku haƙuri kafin su Abih su zo gobe in sha Allah.A yi ta haƙuri ita ƙaddara musulmi take ci,kuma kowa bai wuce ƙaddara ba sai dai a yi ta addu'a”

Mama ta ce “ haka ne Allah ƙara rufa mana asiri”

“Amen!” da zai tafi ne ya ajiye ma Sakeenatu kwalin waya iPhone kusa da ita amma ta ƙi ɗauka har sai da Mama ta yi mata faɗa sannan ta buɗe kwalin.Wayar sabuwa ce dal har da layi a ciki,tana kunnawa babu jimawa saƙonninsa suka soma shigo mata amma ta basar ba ta karanta su ba sai da ta zo kwanciya.Kaso hamsin na ƙuncinta da kuma haushin Agali da take ji sai da suka ragu haka ta yi bacci cike da tunani iri-iri.

Washegari kuwa bayan sun dawo daga asibiti sai ta tarar da iyayen Agali sun zo maza da mata,gefe guda kuma dangin mahaifinta ne da na Mama waɗanda duk ba ta san lokacin da aka aika musu katin gayyata ba.Ta dai gaishe su kafin ta wuce can uwar ɗaka,yayin kakar Ma'idah wacce tamkar an tsaga kara ita da ita ta janyo ta tare da yi mata tambayoyi tun Ma'idar na ɗari-ɗari har ta saki jikinta.

An ci an sha kafin a watse sai dangin mahaifin Sakeenatu maza biyu da suka tsaya yi mata nasiha,tare kuma da shaida mata sun ɗaura mata aure da Agali tun da babu idda a kanta.Banda kuka babu abin da take yi,haka suka tafi suka bar ta sauƙin abin ma da Nafisa ta zo.

Cikin sati guda Mama ke ta shirya Sakeena,kullum kuma da sabuwar nasihar da take yi mata.Har yanzu ta ƙi ɗaukar kiran Agali sai text kawai shi ma ba kowanne take maidawa ba,in kuma ya zo gaisuwa ce kawai ke shiga tsakaninsu.A sati na biyu ne aka soma shirin tarewar ta,tana zaune ta ɗauki waya ta kira lambar Abbas kafin ya ɗauka zuciyarta sai bugawa take.Sai da ta jera masa kira biyu a na uku ne ya ɗaga,ta gaishe shi ya amsa kafin duk su yi shiru.

“Mi kike so?” ya tambaye ta.

Murya na ɗan rawa ta ce ” dama za mu je can maraɗi a kwaso kaya shi ne...shine muke buƙatar ka bar key ko a wurin makwabta”

“Kin gama aurena kenan Keenat?Tun bayan da na zo nan ko sau ɗaya ba ki taɓa kirana ba.Ko ta'aziyar Mamuh ba ki yi mini ba, shikenan kin bar ƙaunata”

Idonta tab da ƙwalla ta ce “ Abbas na yi aure gobe zan tare”

“Kin yi mi?” ya tambaye ta cike da tashin hankali,Nafisa da ke kusa da ita ta yi saurin ƙwace wayar ta kashe tare da ciro layin ta karya.“Ni fa in ba don Mama ce tace a kwaso kayan ɗakinki ba wallahi da barin su aka yi can tun da dai Agali zai yi miki komai”

“A'a gwara a kwaso ɗin ko siyar da su sai a yi”

“Hum!” haka Nafisa ta fice ta bar Sakeenatu tana hawaye a zuciyarta ta fi son Agali amma ta fi son yin zaman aure da Abbas saboda halarcinsa gare ta amma babu yadda ta iya.

Washegari da misalin ƙarfe takwas na dare aka miƙa Sakeenatu a tanfatsetsen gidanta da aka gina mata a nan garin Zinder.Tun daga kayan kitchen har zuwa katakai da kuma kujeru Agali yayi su, danginta da nasa kowa sai addu'ar zaman lafiya ake yi musu kafin su watse a bar ta ita ɗaya.

Shi kaɗai ya shigo hannunsa riƙe da ledoji,iya sallama kawai ta amsa masa amma duk janta da hira da yayi shiru ta yi.Ganin haka ya umarce ta da ta je ta yi alwala,a tare suka yi sallah sannan suka ci abinci ya fice ya bar ta.Wanka ta yi ta saka kayan bacci ta haye gado ta soma tunanin ranar aurenta na farko tana murmushi,ba ta ji shigowarsa ba sai wawuyar rungumar da yayi mata.Da shegun idonsa yayi nasarar cire mata duk wani rashin mutumcin da take ji kafin su raya daren cike da shauƙi,yayi musu wanka suka dawo suka sha bacci.

Washegari Sakeenatu na fitowa ta tarar tuni an gama yi mata girki an gyara gidan tsaf.Ta je table ta zauna da sauri mai aikin ta zo ta fara buɗe mata abubuwan da ta girka har da cimar Bugaje ,ta zaɓa aka zuba mata a plate tana ci tana tunanin rayuwar baya.

Ma'idah ta shigo da sallama tana turo baki,kafin Sakeenatu ta kai ga tambayar lafiya shi ma Agali ya shigo yana cewa “ preety haƙuri za ki yi fa amma doli ki tafi Kanada,kin ga tare za ku je Momy” ta maƙe kafaɗa tare da zuwa kusa da Sakeenatu ta zauna ta ce “ Mama wai karatu zan je ƙasar waje inda ban san kowa ba”

“To ai haka abu ne mai kyau sai ki yi murna,kin ci abinci ne?” Sakeena ta faɗa .

“Eh tun ɗazu ni da Momy”

“Ina Momyn?”

“tana can ɗaya sashen ita da sauran mutane”

Sai a lokacin Sakeenatu ta dubi Agali wanda ke tsaye tun ɗazu yana kallonsu,ta miƙe da sauri ta ce “ bari na fito sai mu je ki kai ni ” tana shiga ɗaki Agali ya take mata baya,“ ko gaisuwa babu wifer?”

“Ta me ? Ina ce kan bed guda muka kwana ”

“Eh gaskiya kam babu buƙatar tambaya kin san yadda nake” ya faɗa tare da matso ta.

“Don Allah ka bari Ma'idah na falo tana jirana ”

“Ni babu ruwana kawai ki kula da ni ”

“Mi kake haka kamar wani ƙaramin yaro?”

“To ai shi ne,kin ga akwai ma maganar da nake so mu yi”

“Ta me?”

Sai da ya ja numfashi kafin ya ce “ tun ranar da Yaya ya ga Ma'idah ya ce yana son a haɗa su aure da ɗansa Heesham,shine na ce sai mun yi shawara tun da ban sani ba ko tana da wani wanda take so”

“Ma'idah ba ta taɓa yin saurayi ba”

“Shikenan kin ga sai a yi auren su tafi da mijinta can Kanada”

Ba tare da ita Sakeenatu ta san yaya Heesham ɗin yake ba ta ce “ to babu damuwa Allah sa alkhairi ” ya amsa da “ Amen ” kafin ya yi mata rakiya izuwa sashen da su Momy suke.....

Assalamu alaikum,mata da yɗan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yɗan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK2

14_15

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi
```

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

#BASSERAT

Ina samun mai ɗan sahu sai na ce ya kai ni can asibiti,tun bakin ƙofa na hango Mama yau ma murmushin take wanda ban san mi ya wanzar da shi ba.Ina daf da na isa gare ta na ga wani likita ya zo ya miƙa mata kofi shi ma murmushi kan fuskarsa,turus na yi tare da tsaya wa cak ina kallo su da dukkan alamu hirar da yake yi wa Mama tana matuƙar saka ta farin ciki kuma tana jin daɗinta.Sosai ta yi min kyau ,sai na ji ina sha'awar zuwa na rungume ta mu yi farin cikin tare.Kamar wacce aka jefa haka na je na faɗa jikinta “ Mamaaaa!” na furta ina dariya har sai na kusa kayar da ita amma ta riƙe ni gam tana murmushi mai sauti ta ce “ SEERAT har kun taso?” na ɗan janye daga jikinta ina gyaɗa mata kai kafin na kai dubana ga likitan na ce “ ina wuni?”

“Lafiya lau yɨan makaranta ya kike?” ya amsa.

Na ce “ alhamdullah!” kafin kuma na maida dubana ga Mama na ce “ kin ga malamarmu ta bani” na nuna mata ledar.

“Je ki ciki ina zuwa” Mama ta faɗa tana shafar kaina,na sakar mata murmushi tare da nufar ciki har na kai bakin ƙofa na waigo sai na ga likitan ya duƙa yana yi mata magana ita kuma ta watsa masa ruwa a fuska suna ta dariya.

A fili na furta “ wato wannan shine silar farin cikin da Mama ta shiga tun jiya?” sai kuma na yi murmushi na ida shigewa a zuci ina cewa ‘ soyayya daƒi har da su Mama ’

Na buƌe ƙofar na shiga,cak na tsaya ina kallon yadda Yaya Khaleed ke faman rumtse ido don za a yi masa allura.Abin sai ya ban dariya na ce “ ƙato da tsoron allura” ai kuwa ya buƌe idonsa taram a kaina ya watso min shegen kallon nan nasa mai kaƌa hantar cikina.Da sauri na sunne kai ina jin tsoronsa na taso min,“ zo ki zauna” cewar Ammy.Na turo baki tare da isa kusa da ita na zauna “ ya jikin?” na tambaye ta.

“Da sauƙi alhamdullah! ” ta amsa tana mai kallon ledar hannuna,na miƙa mata tare da maƙe murya na soma bata labarin Madam Rakiya da abin da ya faru har zuwa yau hatta batun na ga Daddy a wani ƙofar gida sai da na sanar mata.

“ Na sani matar da zai aura ce,ita kuma wannan ledar ki ajiye ta har zuwa wani lokaci musamman turarukan nan” Ammy Habibah ta faƌa bayan ta duba abubuwan da ke ciki,ban tambaye ta dalili ba kawai dai na amsa mata da “ toh”

Yar ƙarar da Yaya Khaleed ya saki ce yasa na mayar da hankalina gare shi,tamkar wani ƙaramin yaro haka yake gudun allura.Na yi murmushi a zuci ina cewa ‘ in sha Allah karatun likita zan yi ko don na dinga tsikarar ka’

“Mama ki taso za a yi miki wasu gwaje-gwajen” cewar nurse,Ammy ta miƙe ta fita ƌakin sai yayi saura daga ni sai shi.Ganin kallon da yake jifana da shi yasa na jawo ledata na soma duba kayan ina buƌe kwalaban turaren tare da ƌan fesawa don jin ƙamshinsu.

“Keeee!” na ji muryarsa a dake,na ɗago na dube shi zuciyata na bugawa.“ Uban mi kike fesawa?” ya tambaye ni kamar wani makaho,na turo baki na ce “ ruwa ne”

“Zo nan!” ya faɗa cikin bayar da umarni ,na kuwa maƙe kafaɗa tare da soma mayar da komai cikin ledar don guduwa.Har na miƙe zan fita yayi wata dirowa ya damƙo ni,“ don Allah ka yi haƙuri” na furta ina shirin kuka.

Muryarsa na ɗan rawa ya ce “ yaushe kika fara raina ni uhum?” ban basa amsa ba sai ƙwayar idonsa da nake kallo mai ɗauke da abubuwa wasu ina iya fassara su yayin da wasu kuma ban san mi suke nufi ba.Na shagala sosai cikin kallonsa na ji bakinsa kan laɓana,da farko kamar bai son kissing ɗin kafin kuma ya zaƙe yana yi min shi cikin fitar hayyaci.Ina jin ɗumin hawayensa a kan haɓata da kumatuna,jikina banda rawa babu abin da yake yi ko kaɗan kuma ban yi ƙoƙarin hana shi ba.

“Mi nake gani haka?” muryar Ammy Habibah ta daki kunnena,sai a lokacin na soma yunƙurin ƙwatar kaina amma Yaya Khaleed ya riƙe ni gam.Ina jin lokacin da Ammy Habibah ta kai masa dundu a baya tana cewa “ don ubanka ka sake ta” amma ya ƙiya tamkar wanda bai da kunnuwa sai da ta ƙara masa wani dundun kafin ya ture ni yayi baya ya je ya hau gadonsa ya fashe da kuka.

Ni ma kukan na soma ina mai ɓoyewa bayan Ammy wacce fuskarta ta yi kicin-kicin saboda ɓacin rai.Cikin zafin zuciya ta soma balbale shi da masifa “ kai ne farko da ka taɓa shiga zangon samarta? Irin tarbiyyar da na koyar da kai kenan? Ka sha giya ne ko hauka ne ka soma?”

Daga can inda yake kwance cikin kuka ya soma magana “ to Ammy ya kike so na yi? Kin san komai nawa ban ɓoye miki damuwata ba amma sai ki nuna kamar abin ba zai yiyu ba....”

“Ka rufe min baki don Allah! Tun ranar da ka faɗa min ba na ce na ji ba kuma zan yi tunani? Yanzu mi kake ƙoƙarin yi? So kake hawan jinina ya ƙara hawa zuciyata ta buga na mutu ? Daga yau kar na sake ganin haka ko tunanin ƙara kuskuren nan ka yi ban yafe ma ba” ta faɗa tare da nufar gadonta ta zauna ta bar ni nan tsaye.

Rasa abin yi na yi kawai na yi zaman yaɗan bori,ban cikin hayyacina sosai amma na san lokacin da na fasa ihu tare da soma ihuce-ihuce da lokacin da duk suka yo kaina Ammy ta riƙe ni gam yayin da shi kuma ya soma yi min karatu.An ɗan ɗauki lokaci kafin na soma jin abin da yake zagaya kwanyata ya tsaya,ganina a jikin Ammy Habibah sai na ji raina yana ƙara ɓacewa na fizge tare da miƙewa na shiga toilet.Can ɗin ma sai da na yi kuka kafin na fito,Mama na gani zaune tana sauraren jawabin Ammy Habibah inda take cewa “ kawai don na yi wa Khaleed faɗa ne shine iskokan suka tashi”

“Ni ban san ta da su ba,yau ne kawai suka taɓa bayyanar da kansu” cewar Mama tana kallona,na turo baki tare da zuwa na ɗauki jakar makarantana da kuma ledata.Har na kai bakin ƙofa na ji muryarsa “ kar ki fita!” a amon muryarsa kawai na fahimci umarni ne ba shawara ba.

Raina zafi yake,wani irin baƙin Ammy nake gani shi yasa nake son barin asibitin amma kuma ko da wasa ban ji ina iya ƙetare umarninsa ba .Ina gunguni na zagaya can baya ta ɗaya ɓangaren na zauna a gadon da yake kwance na bai wa inda su Mama suke baya.

Murya can ƙasa-ƙasa yake min magana ta yadda iya ni ɗaya zan ji,“ komai iyaye suka yi mana ba a fushi da su,kuma wannan kumburar da kike kina ƙoto kar na sake ganinki a haka ki mayar da fuskarki normal” sai yayi shiru na ɗaga kai na dube shi muna kallon juna cikin ido,ya ja ajiyar zuciya ya ce “ turaren nan nada ƙarfi sosai SEERAT kar ki saka shi,sannan kin ga banda lafiya ki bar yi min irin wannan kallon” na lumshe idona tare kuma da buɗe su na zube su kan nasa.

“ Ki yi min addu'a na samu sauƙi na wuce makarantar horar da ƴan sanda ,ƙila in ba mu kusa komai zai zo min da sauƙi” ya faɗa yana cizon leɓe.

“Mike damunka?” na jefo masa tambayar.

Ya ɗan saki murmushi tare da kallon gefen da su Mama ke zaune sun yi tsit hirar ma sun bar yi.

“Kin ga fa mu suke kallo,ki bari wani lokaci zan yi miki bayani” Yaya Khaleed ya faɗa cikin tausasa murya,na maƙe kafaɗa a shagwaɓe na ce “ ni yanzu nake so” sai da ya rumtse ido ya furzar da numfashi kafin dakyar ya ce “ SEERAT in namiji yana son mace to akwai lokacin da yake buƙatar keɓewa da ita don nuna mata soyayyar gaɓai ba wai ta kalamai ba” shiru na yi ina kallonsa tare da nazarinsa kamar yadda shi ma yake kallona,muryar ya ƙara gyarawa kafin ya ci gaba da cewa “ kin ga abin da muka yi yanzu? To shi ma yana ɗaya daga cikin muradin masoya”

“Hum! To ni ban so”

“Za ki so daga baya,faɗa min ya karatun naki yake tafiya?” ya jefo min tambayar yana mai jawo jakata ya zuge.Na yi ƙasa da kai don kuwa akwai pad ɗina a ciki wacce Mama ta yi min bayanin kan cewa a duk lokacin da nake period muddin zan fita na dinga ɗaukar ƙwaya uku saboda halin canzawa.

“Yanzu kwana nawa da kika soma yi?” ya jefo min tambayar,na turo baki sannan na basa amsa da “ kwana biyu”

“Yawwa ki yi lissafi fa sannan ki riƙe kwanan wata” na jinjina masa kai sai kuma duk muka yi shiru.

Ina jin idonsa a kaina kafin ya kira sunana “ SEERAT?” ba tare da na ɗago ba na ce “ uhum!”

“Ki yi hujen hanci yana burge ni” na ɗago da sauri kafin na ce “ da zafi fa”

“Khaleed?” Ammy ta faɗa wacce ke daf da gadon da alamu ko shi bai san da tsayuwar ta ba,kuma da dukkan alamu ta ji furucina duba da kallon da take yi min.

“Na'am Ammy ” ya amsa.

“Baseerat za ta tafi gida saboda Basheer na can shi ɗaya ba zai ji daɗi ba in bai gan ta ba”

“To Ammy ” ya amsa tare da kallona ya ce “ ki tashi ki tafi gida kuma ki kular min da kan ki kin ji ko?” na gyaɗa masa tare da tashi na fice.

Maimakon na tafi gidan a'a sai na wuce asibitin da Ubaidah take , wannan karon ana barin mutane shiga ɗakin da take har da ma danginta ke jinyarta.Idonta biyu,tan ganina ta saki murmushi na ƙarasa na zauna kusa da ita bayan mun gaisa da kowa .

“Ya jikin naki?”

“Da sauƙi sai dai fa har yanzu ban ji a jikina sun maido min abin da suka cire ba” ta bani amsa a hankali.

Na kamo hannunta na jimƙe cikin nawa tare da tsura ma tsakiyar idonta kallo,abubuwan da suka faru ne na soma gani daki-daki .A ranar da na bar ta nan cikin aji ƙarya ta yi min malam ne take jira ba abokinta ba,abu na farko da yayi mata shine ya bata hannu suka gaisa daga nan kamar wacce ta yi maye sai ta yi luuu ta zube jikin bancin makaranta.Sai kuma malam ya buɗe jakarsa ya shafa mata wata hota a matacinta,daga nan sai wani abu ya fito shi kuma ya ɗauke shi ya naɗe a ƙyalle ya fice.A ƙa'idar aikin ƙaddararwar da yayi a jikinta ya shafa mata hodar tsafi mutum na mutuwa ne ,irin ta ɓoyayyar duniya zai bar duniyar mutane ya koma can ya ci gaba da rayuwa a duniyar fatalwa,matsafa da kuma ruhi sai aka yi rashin sa'a tsafinsa bai yi aiki akan Ubaidah ɗari bisa ɗari ba. Da sauri na sake mata hannu ganin wata mummunar siffa ta bayyana a gare ni da alamu dodon da malaminmu yake yi wa tsafi ne.Murya na ɗan rawa na soma yin magana “ Ubaidah za ki iya faɗa min abin da ya faru bayan barin ki wannan duniyar?” shaf na manta ba mu biyu ba ne a ɗakin sai da na ji sun soma yin salati.Da wani irin sauri kuma na ɗaga tafin hannuna,tamkar an haska fitila haka hasken ya mamaye su yayi mana iyaka da su.“ Ina jin ki yi sauri ki faɗa min”

“ Mi kike haka Baseerat?”

“Ki bani amsa don Allah Malama kin tsaya yi min banzar tambaya” na faɗa cikin ƙaraji.

Ubaidah ta kalli hannuna wanda har yanzu ban sauke shi ƙasa ba kafin ta soma cewa “ tamkar wasu fatake haka na tsinci kaina cikin wasu yan matan muna tafiyar ƙasa har muka isa wani baƙin kogo inda wasu halittu ke jiranmu,ɗaya bayan ɗaya aka soma kiran sunayen mutane duk wacce aka kira sai ta je ta shiga wani jirgi ana daf da kawowa gare ni kawai sai na ganki tsudum a wurin kin ciro ni sama.A gaban idona malam ke ihu yana son kamo ni amma tuni kika kuɓutar da ni,daga nan ne na farka na gan ni a gadon asibiti”

Na miƙe tsaye tare da janye hannuna,mutanen da ke ɗakin sai na ga sun yi kamar ma ba su san abin da ya faru ba duk sun manta.Ɗakin da malam yake na nufa,har yanzu akwai yan sanda masu gadin ƙofar suna ganina suka bani hanya na wuce.Yana kwance cikin azaba,a wahalce yake kallona kafin ya jefo min tambayar “ mi kika zo yi?”

“Ina abin da kuka cire a jikin Ubaidah?”

“Yana wurin oga” ya bani amsa .

“Ka je ka karɓo”

“Ban iya yin amfani da power ɗina duk sun tsayar da komai,sannan sun gargaɗe ni kan cewa muddin na sanar da duniya gaskiyar lamari za su kashe mahaifana,matata da kuma yaya”

“Tun yaushe kake wannan mugun aikin?” bai bani amsa ba,sai na sake jefa masa wata tambayar “ mine ne mafarin shigar ka cikin jerin mugaye?”

Bai bani amsa ba sai wuri guda da ya kafe da ido,ina juyawa don ganin mine ne kawai na ji an kife ni da mari tamkar walƙiya kuma haka na tsinci kaina a wani jeji a maimakon asibiti.

Na lumshe ido kawai ina tunanin hanyar da zan bi na tsira,“ ki bar wahalar da kanki don wannan dajin shi ake kira da jejin mutuwa.Wato duk riƙe mana ɗaya daga cikin members ɗinmu da kika yi bai ishe ki ba,ƙoƙarin tursasa shi ma kike yi ya sanar da ke inda Daularmu take?” wata murya ta daki kunnena wacce tasa na yi saurin buɗe idona,wani gabjejen mutum na gani mai jiki irin na dragon amma kansa na mutum.Duk ɗaƙiƙa ɗaya kuma fatar jikinsa na canzawa kamar wata hawainiya,shiru na yi ina nazari idan ban manta ba Bafulatana ta karanta min littafin MAITAR IDO inda a cikinsa ta sanar da ni masu power dragon sun fi kowa ƙarfin iko a kaf duniyar Ruhaniya.

Ban kai ga ida tunanina ba na ji muryarta ta karaɗe jejin,“ ita ɗin ƙaramar yarinya ce har yanzu ba ta ida sanin dokokin duniyar Ruhaniya ba,ina kira ga mai girma Shakal da ya ji tausayin Queen SEERAT ya mayar da ita duniyar bil'adama ”

Muryar Bafulatana ce amma sam ba ni ganinta,shi kuwa wanda na ji ta kira da Shakal sai ya turnuƙe fuska yana mai cewa “ Zan yi domin ke” daga nan ban sake

sanin abin da ya faru ba sai tashi na yi na gan ni kwance a gidanmu wai har magarib ta yi.

Na dafe gefen kaina da yake min ciwo kafin na shiga toilet na yi wanka na kimtsa kaina.Falo na fito sai na tarar duk suna cin abinci,kusa da Basheer na zauna na soma cin abincin .Muryasa na ji can ƙasa-ƙasa yana cewa “ ki dinga kawar da ido ga duk abin da bai shafe ki ba,aikinki shine kawai kuɓutar da rayuwar yarinyar ba wai karɓo abin da tun can farko ba mallakinta ba ne namu ne”

Cak na tsaya da cin abinci ina kallonsa tare da auna furucinsa ,ya ɗago muna kallon juna ya sakar min wani murmushi tare da tashi ya bar ni nan sake da baki.

Anty Murjanatu ta miƙe ita ma sai wurin ya yi saura daga ni sai Mama ,a hankali cikin taushin murya ta soma yin magana “ Baseerat mi ya kai ki fadamar mutane? In mangoro kike so ai sai ki faɗa a saya miki.In ba don Allah yasa Basheer yana a wurin ba ai dukan da za su yi miki sai ya fi wannan”

“Fadama?” na tambaya cike da mamaki ,ta haɗe rai ta ce “ kar na sake ji dai ki kiyaye” ita ma ta miƙe ta bar ni nan zaune.Tafin hannuna na soma shafawa don yana ina da buƙatar ganin Bafulatana ita kaɗai ce za ta yi min bayanin abin da ke faruwa a nan.Face da ni na ganta tsudum a zaune kan kujera,raina a ɗan ɓace yake hakan yasa na ƙi magana .

“Ina ce dai na rufe babin ƙawarki Ubaidah,sam ban nuna miki a mafarki ba cewa ki je karɓar semen ɗinta ba,ko kin yi mafarkin haka?” ta faɗa kamar wata uwata,na girgiza mata kai ta ci gaba da cewa “ to amma mi yasa kika je? ”

“Mah ita ɗin ƙawata ce” na bata amsa .

“Ba wannan na tambaye ki ba,dalilin zuwan naki ne har ki yi bincike akan abin da bai shafe ki ba nake son ji.A duniyarmu komai yana da tsari,sannan muna girmama

alƙawari kin san mi zai faru da ke a jejin can inda ban je ba? Kin san wane Sarki Shakal? Duk ma ba wannan ba mi yasa ba ki maida hankalinki akan gidan Sarkin zinder ba? Na ga wannan ma sam bai cikin jadawalin abin da kike hari alhalin tun ranar farko na haska miki komai kika gani”

Idona suka ciko da hawaye don na fahimci cewa taimakon Ubaidah sam ba zai yiyu ba,ta miƙe tsaye tare da cewa “ ki shirya gobe ki ziyarci gidan sarki sannan a cikin turarukan da Madam Rakiya ta baki akwai wani na nan mai jan murfi shi za ki yi amfani da shi .Ki aje hankali ki yi komai a tsanake ban son shirmen nan naki,tun da kika fara soyayya duk kin bi kin tarwatsa tunaninki”

Na ɗago kai na dube ta,sai na ga fuskarta yau babu walwala.“ Ya aka yi Basheer yake min magana haka?” na tambaye ta dakyar.

Ta kawar da kai kafin ta ce “ saboda shi ya tsinto ki a fadamar wasu mutane ”

“Amma ai ni ban je can ba,kuma na kasa tuna abin da ya faru da ni”

“Shakal ne ya cilla ki can” ta bani amsa tare da ɓacewa hakan yayi daidai da shigowar ƴan rakiyar amaryar Daddy sai guɗa suke suna cewa “ Rahamu kin yi sa'ar miji irin wannan gida”

Ina kallon su suka nufi sashen Goggo Hajara suka buɗe suka shiga,sai guɗa suke wacce ƙila ita tasa Mama da anty Murjanatu suka fito suka shiga ɗakin.Tamkar wata shuka haka nake a zaune a wurin har waɗanda suka yi wa amarya rakiya suka fice,babu jimawa Daddy ya shigo Mama da anty Murjanatu suka sako sabuwar matarsa tsakiya suka fito falo.

In idona bai yi min gizau ba hararena na ga tana yi,yayin da take kallona tsakiyar ido har na samu damar hango tsagaron ƙiyayyata a cikin idonta kamar wacce ke son ɗaukar fansa.Jawabin Daddy ne ya janye hankalina daga gare ta inda yake gabatar mana da ita da kuma shelar auren anty Murjanatun da wani abokinsa ,a ƙarshe ya ɗora da “ ke kuma Safeenatu sai ki yi wa likitan magana ya zo a tsayar da zance tun da dukkanku ba wasu yara ba ne.Shi aure dama fahimtar juna ce kawai”

Na dubi Mama wacce ta kasa ɓoye farin cikinta ta soma murmushi tare da amsawa da “ to Daddy in sha Allah zan sanar da shi” nan dai duk aka watse.Ina shiga ɗaki na ji Mama na waya tana sanar da bazawarinta saƙon Daddy,can kan bed na haye ina tunani da na ji kaina zai soma ciwo kawai sai na mayar da tunin kan moments ɗinmu da Yaya Khaleed.

Washegari

Tun da safe na tashi har na rige Mama,wata irin yunwa nake ji hakan yasa na nufi kitchen.A firgice ta saki butar ruwan zafin tana kallona,ni kuma ƙatuwar tasa da ta shimfiɗa ɗan kamfai ta zuba Lipton da citta da sauran kayan haɗin tea na duba.

Muƙut ta haɗiye wasu yawu kafin ta ce “ mi kika zo nema?”

“Mi pant yake yi cikin tasar shayi? Ko shi ma yana ƙara ɗanɗano?” na tambaye ta ina tsure ta da ido.A daburce ta ce “ dama-dama wanke shi zan yi saboda cutar infection da ta yi yawa”

Na gyara tsayuwa na ce “ yaushe wannan sabon salon ya fito wanke ɗan kamfai da Lipton da citta?”

“Kin ga banda lokacinki ki yi abin da za ki yi ko ki fita ki bani wuri,ina ce dai nan gidana ne ko? Aure nake ke kuma agola ce ba ke mai gidan ya haifa ba” Rahamu ta faɗa tana son naɗe tabarmar kunya da hauka.Na saki ɗan murmushi na ce “ haba Goggo daga wannan sai ranki ya ɓace? Ki rufa min asiri in Daddy ya ji ai sai ki sa

yayi min faɗa ya ce ina faɗa da ke saboda kishi” a nan take na mayar da abin barkwanci kafin na koma ɗaki da tunanin ‘wacce irin mata ce kuma Daddy ya auro?’

Daga bayana na ji muryar Basheer ya bani amsa kai kace malamin duba ,“ ƙanwar Mamuh Ladidi ce wacce kika kashe mana!” na juyo da bala'in sauri ina kallonsa,sai na ga yau siffarsa ta canza daga irin wacce na sani.....

Assalamu alaikum,mata da yɗan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yɗan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK2
```

16_17

Shiru na yi ina kallonsa,da sauri ya lumshe idonsa kafin ya buɗe su sai na ga ya dawo normal.murya a ɗan dake yace "mine ne ?" "babu komai" na basa amsa tare da ɗaukar jakar makaranta na fice.Har na isa ina tunanin lamarin BASHEER,yau bayan mun gama dukkan darasi yɗan ajinmu suka tsara tafiya ganin Madam,ban san wa ya sanar da su tana gidan sarki ba amma duk can muka yi tsinke.Tarba mai kyau muka samu ,duk muka yi mata ya ji kafin duk kowa ya fice ni kuma na zauna saboda a iya kallon da Madam ke yi min na fahimci so take na zauna.

Sai da ta tabbatar duk kowa ya watse kuma babu wanda zai ji mu sannan ta soma magana"Tsawon shekaru huɗu kenan da Mama ke zawarci duk da kuwa igiya guda tal ce mai martaba ya tsinke amma ya gagara mayar da ita,zaman yɗayɗanta ne take wanda mune muka taru muka yanke hukuncin babu inda mahaifiyarmu za ta je.Kaf yɗayɗan sarki mata ne babu namiji,wannan ya ɗaga hankalinsa yasa shi kauce hanya,kullum masarauta cikin karɓar malamai da bokaye take,abun mamaki kuma kusan amsa ɗaya suke bayarwa magauta sun raunata semen dinsa mai karfin wanda zai iya sa ya samu namiji sai dai akwai ƙwaya ɗaya tal da ke iya wanzar da samun namiji.Wannan dalilin ne yasa sarki ƙaro aure tun da ita Mama haihuwarta ta tsaya cak.Ni dai tun da aka soma al'amarin nan hankalina bai kwanta ba sam ,sai na fara bibiyar amarya tare da sa mata ido har na samu abin zargi.Ƙanen sarki yana yawan shiga sashen amarya,ban sani ba ko ya fahimci ina saka masa ido kawai sai ya yi waya mijina ya zo ya tafi da ni don dama jinya ce ta maido ni gida"madam na zuwa nan sai ta yi shiru,nace "amma ai cikin jikin nata da kike zargi na sarki ne,sai dai bayan haka akwai wani ɓoyayyen sirri a tattare da matar.Kai tsaye za a iya kiranta da matsafiya tunda da shi ta yi amfani wurin dakatar da haihu Mama Salmu,shi kuma ƙanen mahaifinki babu wata alaƙa da ke tsakaninsu in kika fidda ta kasuwancin ruhikan mutane"sai kuma na yi shiru jin duk idea ta tsaya kamar wani network,a take kuma na fahimci kuskurena wato ban shafa turaren da bafulatana ta umarce ni da na shafa ba.

Tamkar Madam Rakiya ta fahimci haka kuwa sai ce min ta yi "ya kamata ki tashi ki tafi zuwa gobe in sha allah zan aika a ɗauko ki" ban musa ba na kuwa miƙe ,bayan

na fito na samu adaidaita ta kai ni gida da zan yi wanka sai na ga jinin ya ɗauke irin yadda mama ta koya min wankan na soma mai hade da alwala amma kuma sai na ji na manta.haka na mayar da kayan na fito na samu anty Murjanatu a kunyace na zauna kusa da ita sai kuma na kasa tambayarta.

Ta dube ni tace "ya dai Baseerat ko yunwa kike ji?" na girgiza kai na fara magana a hankali "dama ranar nan Mama ta koya min yadda ake wanka shine kuma na manta" ta yi murmushi kafin tace "to ya danganta da wane iri ne,da farko za ki ɗauki niyyar yin wankan a zuciya misali ke yanzu sai ki sa a ranki zan yi wankan haila ne,bayan nan sai ki karkata bokiti ki wanke hannunki sau uku da zarar kin yi haka to najasar tafukan hannu ta gushe kina iya tsoma hannun a ruwan,sai ki yi tsarki,ki wanke gashin kanki da kunnuwanki da fuska,daga nan sai ki game gangar jiki bayan nan sai ki kuskure baki sau daya ki shaka ga hanci sau daya shikenan"

Sai da na bari ta ida jawabin kafin nace "amma ba haka ita ma ta fada min"tace "to ai wankan dama ba doli sai wancan ba,na fada miki wannan ne don ya fi sauƙi"na ɗan gyara zama na ce "amma ɗazu na ji kamar kin ce in mutum zai yi wankan ya danganta da wane iri ne wurin ɗaukar niyya to dama bayan na hailar akwai wani?"

Shiru ta yi tana kallona kamar ba za ta bani amsa ba kafin ta ce"wannan sai in kin yi aure kuma"duk da ban gamsu da amsar ba haka na miƙe ba tare da na takura mata kan cewa sai ta yi min bayani ba. Bayan na tsarkake jikina na zaɓo riga da wando na saka na fesa turare tare da zuwa gaban madubi na yi tsaye,can saman ƙarfen labule na hango wani maciji sai naɗe ƙarfen yake da bindinsa yayin da idonsa suke a kaina.Da farko na zata ko irin mafarkin da na saba yi ne da maciji sai da na gansa tsudum yayi tsalle ya diro a gabana.Ko kaɗan ban ji tsoronsa ba sai na ji tamkar ma mun san juna da shi,kamar wacce ke son kama fara haka na ware tafin hannuna a hankali shi kuma ya rage girma ya zo ya shige.Ido na tsura masa ina sauraron jawabin da yake min na shine mai ɗebe min kewa sannan kuma abokin aikina wurin kawar da magauta.

Can falo na jiyo sautin ihun Murjanatu tare da wata murya na cewa "tun da uwarki ta yi silar mutuwar yar uwata wallahi ke ma sai kin mutu"da sauri na nufi falon Rahamu ce tsaye kai ga anty Murjanatu tana zuke kurwata tana ɗura ta cikin wata butar shayi,tuni na makara don kuwa babu abin da zan iya yi wa Murjanatun a halin yanzu amma ba zan ƙyale Rahamu ba wannan ya saka na jefa mata macijin hannuna shi kuma kamar jira yake ya ciro dukkan idonta biyu ta yi kara tare da sakin butar shayin sai dai ba ta kai ƙasa ba sarƙar wuyana ta kara tsayi kifin nan ya hadiye butar .Na nufi Murjanatu ina kiran sunanta amma tuni rai yayi halinsa,daga bayana na ji muryar BASHEER na cewa "ta fa mutu"furicinsa yayi daidai da shigowar Daddy.

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un !” shine abin da DADDY ya ce kafin ya zo yana duba anty Murjanatu,muryar Basheer ce ta sake ɗaukar amo “ amaryarka ce ta kashe ta,ka ganta nan kwance ta suma” nan hankalin Daddy ya ƙara tashi cike da takaici ya ce “ yaushe na auri wannan ɗin?” sai dai ba mu basa amsa ba.Babu jimawa yaransa suka shigo,wasu suka ciciɓi Murjanatu wasu kuma Goggo Rahamu “ ku wuce da ita can gidan sarki tun da mun yi magana da shi yana maganin tsageru irin ta” Daddy na gama faɗar haka ni ma na take musu baya zuwa can gidan sarki.

A bakin ƙofa na ji an kira sunana na waiga sai muka haɗa ido da matashiyar budurwar nan wacce farkon zuwana Mama Salmu ta umarce ta da ta kawo min abin motsa baki.Murmushi ta sakar min kafin ta ce “ tun ɗazu nake ta jiran dawowar ki a nan”

Na dube ta da ɗan mamaki na ce “ kamar ya?”

Ta ce “ eh na san za ki dawo ai”

Jin haka yasa na gyara tsayuwa na ce “ ya aka yi kika sani?”

Ta ce “ saboda na ga hakan ne a tattare da ke ɗazu da kika zo nan”

“Wace ce ke?” na jefo mata tambayar ina saka idona cikin nata sai dai sam na kasa ganin allon sirrinta.

“To ni kaina dai ban sani ba,kawai abin da zan iya cewa shine in na kalli mutum ina gane wasu abubuwa dangane da shi”

Na jinjina kai ina mai ci gaba da kallonta,ita kuma kamar wacce aka tsikara ta soma bani labari.

“Ina da labarai da yawa a duniya, wata rana ina wanke farantin da na ci abinci kusan pampo, sai na ji wata murya da ta yi magana a kunnena tamkar ta wani matashi da na taɓa gani a hanya,muryar umarni ta soma bani kan na je na gidan maƙwabciyar mu da ta haihu na faɗa mata kar ta ci naman da wata za ta kawo wurinsu domin idan ta ci wannan za ta rasa gidan aurenta mijin zai kore ta. Amma sai na ƙi tafiya saboda tsoro kuma ban ɗauka maganar gaskiya ce ba sai washegari da na ji an ce wai mijin ya kore ta”

Na ce “ to don me ba ki je ba?”

“In na je na faɗa mata kamar na cakawa kaina wuƙa ne don ba lallai ta yarda ba,kuma in ta tambaye ni wa ya faɗa min mi zan ce mata?”

“Amma bayan nan bai sake zuwar miki ba? Ina nufin muryar?”

“ Bayan nan ina ganin abubuwa da yawa masu hana ni samun rayuwa ta normal mutane, a duk inda nake ina ji ko tsammanin cewa wani marar ganuwa wanda ido basu iya gani yana kula da ni, kamar dai akwai tashoshi biyu da ke magana da ni a cikin kwanyata haka kawai sai in ji ina karanta tunanin mutane .Hakan sai ya bani sha'awar fara rubuta littafi game da mafarki da duk abin da nake gani”

“Zan iya ganin littafin?” na tambaye ta,sai ta girgiza na ja tsuki na ce “ to uwar mi zan yi miki da kika wani tsaya jira na?”

Murya na ɗan rawa ta ce “ ki yi haƙuri na ga kina kama da matashin saurayin nan ne da muka haɗu a hanya kuma wallahi muryarsa ce ke yi min magana a kullum cikin kunne”

Kallonta kawai na tsaya yi jin wani zance kafin na ce “ siffanta min shi ya yake?” ai kuwa ta soma zayyano sifofin BASHEER,na taɓe baki na ce “ ban san shi ba” sai na yi gaba abina.Ko da na isa fadar sarki tuni Goggo Rahamu an farfaɗo daga suma sai dai babu idanu sai kuka take tana yi wa sarki bayani “ na tuba don Allah kuma ka duba duk jikina babu wata ƙwayar maita,dama fansa na zo ɗauka da suka kashe min ƴar uwa ban taɓa sanin cewa mutuwata ce na zo wurinta ba”

Daga bayanta na ce “ ya aka yi har kika auri Daddy shi nake son sani wannan dalili yasa ma na zo nan ɗin”

“Baseerat zo ki zauna nan” sarki ya furta yana mai nuna min kujera,tsabar iya yi dogarai biyu ɗin nan da na koyawa hankali wancan lokacin har da yi min kirari.Sai yanzu na gaishe shi tare da zaunawa,sarki ya ce “ yau Princess za ta yi shari'a don haka ki yanke mata hukunci”

Na saki murmushi na ce “ a kaita can a rufe har wani lokaci ” ai kuwa suka ja ta ƙiiii kamar wasu kayan wanki.Sarki ya ba kowa umarnin fita,“ ina ta jiran ki amma shiru ba ki dawo ba” ya furta cikin wata murya yana kallona.Na sunne kai ina murmushi,daga bakin ƙofa jakadiya ta soma kirari kafin ta ce “ uwar Magaji na son ganawa da mai martaba”

“Bismillah” shine abin da Sarkin ya ce,na ɗago kai na sauke idona kan gimbiyar nan sai wani shan ƙamshi take tana turo ciki gaba.

“Ina son yin magana da kai ne Daddyn Prince mu biyu kawai” ta furta tana wani yi min malalacin kallo,da sauri na miƙe ba don tsoro ba sai don saboda kar ran sarki

ya ɓace.Bakin ƙofa na tsaya ,tsawon lokaci kafin ta fito tana hurar hanci jakadiya ta take mata baya.Sai da na bari sun yi nisa sosai sannan na ware tafin hannuna na zarge ƙafafunta ta faɗi timmm da ƙasa kuma bisa cikin.Na saki murmushi tare da fita,sai a lokacin kuma na nufi asibiti ganin Yaya Khaleed sai na tarar ma an basu takardar sallama Mama na gangamar kaya.

Tsaye kawai na yi ina kallonsa ina jin sonsa na tsikarar zuciyata,da sauri na sunne kai ganin ya tawo.“ Daga ina kike?”ita ce tambayar da yayi min.

“Gida” na basa amsa,“ na sani! Amma kafin ki zo nan nake nufi ”

Na ɗago na dube shi,ya zabga min harara kafin ya ci gaba da cewa “ wannan kayan ban hana ki saka su ba?”

“To ai banda wasu”

“Zan ɗinka miki,sannan wannan sarƙar ta wuyanki ban son ganinta ki cire ta” shiru na yi kawai,“ ko ba ki ji ba?”

“Na ji zan cire in sha Allah ”

“Ban gane za ki cire ba? Wato ba ma yanzu za ki fitar da ita daga wuyanki ba?” ya faɗa kamar wani ubana.Na turo baki tare da kai hannu na cire ta daga wuyana,ya buɗe tafin hannunsa duk da na fahimci abin da yake nufi amma sai na ƙi ɗora masa sarƙar.

“Mu je kuka yi tsaye kamar sojoji” cewar Ammy Habibah.Yaya Khaleed ya kama hannuna ya murɗe tare da ƙwace sarƙar,idonsa kamar zai faɗo tsabar yadda yake harare na.

Waje muka fita,sai na ga ashe bazawarin Mama ne zai kai mu gida.Yaya Khaleed ya shiga gaba mu kuma a baya ,ko da muka isa har an haƙa rumfa a ƙofar gida “ mike faruwa kuma nan?” Mama ta tambaya.

Kai tsaye na bata amsa da “ anty Murjanatu ce ta rasu”

Duk suka fara salati,muka fita muka shiga ciki nan dai Mama ta yi ta kuka kafin wani lokaci mutane sun fara shigowa gefe guda kuma an ɗora tukunyar abinci.

Ina nan zaune na ga Basheer ya shigo yana harare na,da mamaki na dube shi ina yi wa kaina tambaya ‘ to laifin mi na yi masa?’ sai dai banda mai bani amsa.

A ranar aka sallaci gawar Murjanatu an yi zaman makoki kuma da addu'ar uku du a ranar.Da dare ina kwance ina tunanin da ya aure ni na Yaya Khaleed kawai na ji an yi kutufo da ni har sai da na zabura na tashi da sauri,ido huɗu muka yi da Basheer sai cika yake yana batsewa .Ban kai ga yi masa tambaya ba ya wani finciko ni ya shaƙe min wuya sosai,muryarsa cike da ɓacin rai ya soma magana “ saboda iskanci da baƙin ciki irin naki kin kasa cika min burina,wato da ta zayyano miki siffofina maimakon ki tabbatar mata cewa ni ɗin ɗan uwanki ne amma kika gwasalar da ita”

“Kai sake ta” Muryar Yaya Khaleed ta furta,a hassale ya ce “ ka san laifin da ta yi min ne kake wani cewa na sake ta?”

“Umarni ne ba shawara ba” Yaya Khaleed ya sake faɗa , Basheer ya ture ni da ƙarfi har sai da na faɗi kafin ya fice.“ Ina son sanin sirrin da ke ga wannan sarƙar wuyan naki ” ya faɗa yana kallon wuyana,da sauri na laluba ina mai cewa “ amma ai tana gare...” sauran maganar ce ta maƙale jin sarƙa daram a wuyana.

Yadda ya doso ni gadan-gadan yasa na yi saurin tashi da sauri,yana isowa na faɗa jikinsa na ƙanƙame shi.Duk da ina jin yadda yake kokowa da numfashinsa hakan bai sa na janye jikina daga nasa ba,ban yi hakan da wata manufa ba sai don kar ya dake ni amma sai abun ya haifar masa da matsala.Muryasa na sarƙewa yake cewa “ SEE..R..ATH don Allah ki bari ina jin wani iri”

“A'a za ka dake ni ne kuma ban so” na faɗa ina cusa fuskata a ƙirjinsa har ina jin yadda gargasarsa ke zuzar fuskata.Numfashi ya soma saukewa akai-akai,da dukkan alamu jikinsa yayi sanyi bai da ƙarfin cire ni.Aka turo ƙofa tare da furta “ innalillahi na shiga uku ni Habibah”

Sai a lokacin na sake shi tare da rugawa da sauri na nufe ta ina cewa “ don Allah Ammy ki ce kar ya dake ni” amma ashe gudun Gara na yi na faɗa gidan zanzaro,wani uban dundu ta yi min tana cewa “ in na sake ganin ki da shi sai na karya miki ƙafa” na fita a guje ina kuka,ina fita tsakar gida kamar dama zaman jirana yake sai na ji ya damƙo ni “ don ubanki ko ki koma ku yi magana ke da Hawa'u ko kuma wallahi na yi miki lahanin da ba ki taɓa zato ba”

“Wace Hawa'u kuma?” na tambaya a wahalce.

“Yʼar sarki mana”

“Ina ka san ta?”

“Babu ruwanki ki yi kawai abin da na ce”

“To na ji gobe zan je na kawo ta har nan gidan” cike da murna Basheer ya sake ni ya fice.Na bi bayansa da kallo cike da mamaki ,ina nan tsaye na ji muryar Khaleed “ ki koma ciki”

“Ina za ka je?” na jefo masa tambaya,“ gidan Hajiya ” ban ƙara ce masa komai ba na wuce.Hankalin Ammy Habibah na kaina da zarar mun haɗa ido sai ta harare ni,da na gaji da ganin haka kawai na shige ɗaki na haye gado.

Washegari ta kama ranar alhamis ba muda cours tun safe wannan yasa da na gama sallah na yi kwancina,sama-sama nake jin Ammy na shaida wa Mama yau za ta je sayen trolly da kuma kayan lefen yaya Khaleed.

“Haba don Allah Goggo yanzu don ya ce aure zai yi sai biye masa? Duka-duka nawa yake? ” Mama ke faɗa .

“Wata mai kamawa zai shiga shekara ta ashirin da biyu,gwara dai a yi auren hankalina zai fi kwanciya.Kullum cikin yi min ƙorafi yake ,sau biyu kuma ina ganinsa da Baseerat sun yi kusanci dayawa ”

“To amma ai aikin soja zai shiga”

“A'a na hana,na ce dai yayi ɗan sanda tuni Yaya Ɗayyabu ma ya kai takardunsa”

“Allah ya nuna mana”

“Amen ya Rabb,gobe za a ɗaura aurenki bayan sallar juma'a mijinki kuma ya ce ranar Litinin za ku wuce can Cotonou”

“Ya faɗa min ɗazu,amma ina ta tunanin barin BASHEER a nan ɗin”

“To ni mine ne amfanina ? Wurina zai zauna mana kafin Yaya Ɗayyabu ya auro wata”

“Hum! Allah sa dai ta ukun ba mayya ba ce”

“In ma ita ce za ta koma da sharrinta....” ban sake jin hirar tasu ba saboda bacci,ƙarfe takwas ta gota Mama ta tashe ni na yi wanka na shirya cikin uniform ɗin makaranta.

Ina fitowa falo na ga yaya Khaleed a zaune yana shan tea,muna haɗa ido ya ajiye kofin.A sanyaye na isa wurinsa,“ babu gaisuwa?” ya furta,na ɗan turo baki tare da waigawa baya na ga babu kowa sai na duƙo na ce “ yau Ammy za ta je sayo akwatinan aurenmu”

Ya saki murmushi ya ce “ wa ya faɗa miki?” ban basa amsa ba sai ɗan madaidaicin gemunsa da na ja tare da ficewa a guje.Ina isa makaranta sai na ga yau Ubaidah ta zo,da murna muka rungume juna ina mai cewa “ ya jikin naki?”

“Da sauƙi alhamdullah! Amma tsoro nake ji kar ƴan aji su yi ta min iskanci ”

“Ke manta da su mu je”

“Malam fa ya mutu”

“Yaushe?”

“Jiya da dare,duka gangar jikinsa ta zuganye”

Na yi murmushi kawai,da muka isa can aji haka yan gulma ke kallonmu amma na ce Ubaidah ta share su.Haka muka yi cours har muka tashi,ina fito bakin ƙofa na ci karo da Hawa'u tana jirana.Na ɗan taɓe baki na ce “ wannan ɗin ma kin gansa?”

Kai ta jinjina min ta ce “ eh za mu je gidanku” kanzil ban ƙara ce mata ba har muka isa gida,Basheer na zaune kan kujera a tsakar gida yana ganin mu ya tashi tsaye ita kuma murmushi ta saki.Ban bi ta kansu ba na bar su nan na wuce ciki,na tarar da Mama ta shafa dilka ta gyaran jiki na dubi ƙofar kitchen na ce “ Allah sarki anty Murjanatu Allah ya jiƙan ki” sai kuma na shiga na zuba abinci na ci na ƙoshi sannan na wuce ɗaki na cire uniform na yi wanka.Na haye bed ina tunanin dalilin da yasa sam Bafulatana ba ta kawo min hira ba,bacci ya ɗauke ni nan na ci karo da ita kuwa a mafarkina fuskarta kicin-kicin alamun fushi.Ba ta ce min komai ba har na tashi,na yi wanka na yi sallah.

Dab da magrib Ammy Habibah da wasu ƙawayenta biyu suka shigo gidan da akwatina maƙil da kaya.Sai da Daddy ya zo da Hajiya sannan aka buɗa su,ina daga can gefe ina hange komai masu kyau ne da tsada daidai ƙarfinta.

“Yanzu dai har a gama na goben in hankali ya kwanta sai a je can a kai gidan dangin mahaifinta” cewar Daddy.

Ammy Habibah ta ce “ tun jiya mun yi waya da Kaka duk na shaida mata komai,har da auren Safeenatu ta ci kuka ta kuma yi murna tare da addu'o'in fatan alkhairi ”

Hira sosai aka yi akan kan lefen nan,abun mamaki sam yau Yaya Khaleed bai zo da dadare ba.Washegari tun safe aka soma shirin walimar bikin Mama,dangi duk sun zo ni ma sai na ƙi tafiya makaranta haka na zauna har da yin lalle da wankin gashi .Bayan sallar juma'a aka ɗaura auren Mama da likitanta,sosai aka yi walima mun ci mun sha.

Kamar kuma yadda aka tsara ranar Litinin ya zo da mota aka tafi da Mama sai kuma dangin Momah su biyu waɗanda za su yi mata gyaran ɗaki.Sosai na ci kuka saboda Ammy Habibah ta hana a tafi da ni,a kuma wannan ranar ce aka kai lefena can wajen dangin mahaifina wanda ban taɓa gani ba sai a hoto.Duk yinin ranar na yi shi ne a ɗaki a takure,sai yamma lis yɑn kai lefe suka shigo suna guɗa suna cewa aure ya ɗauru.Hawaye suka zubo min masu game da farin ciki lokacin da wata ke cewa “ an riga an ɗaura an tsayar da biki kuma nan da shekara ɗaya da wata biyu lokacin shi angon ya gama karatun aikin ɗan sandar da zai yi”

“Allah ya kai mu ai kamar gobe ne” wannan karon muryar Ammy Habibah ce,wacce tsantsar farin cikinta har kana jinsa a muryar.

“Amarsu” Basheer ya furta yana murmushi,na dube shi sai kuma na yi saurin cire bargon da na rufe na je na rungume shi na fasa kuka.Dariya ya shiga yi har da ƙyarƙyatawa kafin ya ce “ ke duk kukan nan fa ba zai sa na ji tausayin ki ba gwara ma ki bari”

Na ɗago na dube shi na ce “ Mama fa ta tafi”

“Za mu je daga baya kar ki damu,ni yanzu yunwa nake ji wallahi”

“Bari na samo ma abin da za ka ci”

“A'a kar ki fita akwai mutane sosai,bari na je da kaina” sai kuma ya fice.Haka na zauna ni ɗaya na tsawon lokaci kafin Ammy ta shigo hannunta riƙe da plate,“ tashi ki ci abinci” ban musa ba don har yunwa ina ji.Sai da na ci na ƙoshi na sha ruwa sannan na yi sallah,ina kan sallaya na tsinkayo muryar Yaya Khaleed don zuwa yanzu kowa ya kama gabansa.

Ina shirin miƙewa ya turo ƙofa,idonmu suka sarƙe cikin na juna na yi saurin ƙasa da kai .Ya tako ya iso gare ni kenan Ammy Habibah ta shigo “ mine ne kuma?”

A shagwaɓe ya ce “ Ammy ” ta ƙwafa ta fita,sai ya finciko ni kamar zan faɗi sai da na ɗora tafin hannuna a ƙirjinsa.“ Ke ko gaishe ni ba ki yi ko?”

“Ina yini?” na faɗa a hankali.

“Yau an ce kin yi ta kuka” na jinjina masa kai,“ saboda me?”

“Mama ta tafi” na basa amsa hawaye na zubo min,sai kawai na ji bakinsa kan fuskata yana lasarta kafin ya dire shi kan lips ɗina.Riƙe shi kawai na yi ina jin yadda yake yin komai,can ya sake ni murya can ƙasan maƙoshi ya ce “ ina son kiss sosai” sai na ji kunya,yayi murmushi mai sauti tare da jawo hannuna ya damƙa min waya ya ce “ zan kira ki in an jima mu yi hira” na dubi wayar cike da murna,irin yɗan ƙaramar nan ce sosai wacce ko cikin tafin hannu ka jimƙe ta ba a gani.

Da wannan murnar ya bar ni,na zauna ina ta shiga da fice sallar isha'i kawai da aka kira yasa na ajiye kuma ina gamawa na ɗauke ta.Kiransa ya shigo na ɗauka,na yi tunanin yau ma irin hirar da muka saba yi ce zai yi min amma tamkar wani malami haka ya tsaya yana faɗa min rayuwar aure ,wasu har kunya nake ji tare da tambayar kaina ko duk ina ya san su.

Washegari

Kamar kullum ina zuwa makaranta na sanar da Ubaidah zancen aurena,ta yi min murna tare da cewa “ ni ma fa saura watanni biyu a yi bikina a can ƙauyenmu ai za ki je ko?”

“Eh sosai in sha Allah ” da muka tashi sai na ciro wayata da nake ta jin tana girrrr tun cikin aji,miss call ne na Yaya Khaleed sai kuma saƙon yana waje a ƙofar makaranta yana jirana.Da sauri na fita,can na hango shi ƙarƙashin bishiyar bedi yana zaune kan babur na isa da yɗar murna ta na ce “ Yaya Khaleed tun yaushe ka zo”

“Na kai minti ashirin” ya faɗa yana kallona har sai da na tsargu na sunne kai.“Hau mu je” ya faɗa yana kunna babur ɗin,na dafa kafaɗarsa na hau .Maimakon ya kai ni gida sai na ya nufi gidan Hajiya da ni,ban kawo komai a raina ba har muka isa sai na ga yasa key ya buɗe ƙofa gidan sannan muka shiga daga ciki ita ma ƙofar ɗakin sai da ya buɗe ya shiga ni kuma na tsaya daga waje.“ Ki shigo mana kamar wata baƙuwa”

Murya na ɗan rawa na ce “ Yaya Khaleed ni gida zan je”

Ya fito yayi min wani kallo wanda yasa na ji tsoronsa na shiga ɗakin,sai na ga ya ja murfi ya rufe ƙofar.Hawaye suka zubo min shaaa,“ wai mine ne?” ya tambaye ni,“ tsoro nake ji”

“Na mi?” na girgiza kai kawai,sai ya wuce ɗakinsa.“Ki shigo” ya faɗa cikin ɗaga murya,ina shiga ya jawo ni jikinsa ya soma magana “ babu abin da za mu yi kawai

ina so mu yi wasanni,mu kuma yi wanka tare” bai bani damar yin magana ba ya soma yi min abubuwa marar misaltawa ni dai banda rawar jiki babu abin da nake yi,a ranar ne kuma Yaya Khaleed ya bani amsar da anty Murjanatu ba ta min bayani ba .A tare muka yi wanka tun ina noƙewa har kuma na saki jiki da shi,duk tsoron da nake masa ya gushe.Duk da ba mu yi sex ba amma mun gaji sosai haka muka zube kan katifarsa muna hira a haka bacci ya ɗauke mu,jijigar ƙofar falo kuma ta tashe mu muka farka muna kallon juna.....

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI□✍```
```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK2

18

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

A tsorace nake kallon Yaya Khaleed wanda shi ko kaɗan ban ga alamun damuwa ba,ya tashi ya mayar min da kayana sannan shi kuma ya ɗauko jallabiya ya saka.Na riƙe shi ganin ya nufi ƙofa ina girgiza masa kai,“ don Allah kar ka buɗe” na furta ina jin ƙwalla na cika min ido.Ya jawo ni sosai ya manna a ƙirjinsa,ya haɗe fuskokinmu har hancinmu na zuzar na juna a hankali ya furta “ tsoron me kike ji uhum? Ba gani ba? Ke fa matata ce yanzu ,ni ban shakkar kowa don ma na san za ki yi kuka da tun yau mun yi komai an wuce wurin” yana maganar ne haɗi da yawo da hannunsa ga gangar jikina,har zuwa yanzu jijiga ƙofar ake ana bugawa.Amma da alamu Yaya Khaleed kamar ya manta don tuni ya soma sumbatata.

Daga can aka ɗaga murya aka ce “ wallahi zan ci mutumcinka in ba ka zo ka buɗe min ba” muryar Ammy Habibah ce.A razane na fizge daga jikinsa na yi baya ina yarfa hannu,shi kuwa murmushi yayi ya fice.Daga inda nake zaune ina jin ƙarar buɗe ƙofar da kuma sautin muryar Ammy Habibah tana balbale shi da masifa.Da sauri na cusa kaina cikin cinyoyina ganin ta buɗo labulen ta shigo ɗakinsa,tuni kuma na soma kuka wiwi.

“Haba Ammy dubi yadda kika saka Angel ɗina kuka” yayi fuelrucin tare da zuwa ya rungumo ni tare da janye hannuna da nake ta ƙoƙarin rufe fuskata da shi,suman tsaye Ammy Habibah ta yi tana kallonmu bakin ya mutu murus shi kuwa Khaleed sai wani lalaɓa ni yake yana goge min hawaye waɗanda har yanzu sun ƙi tsayawa.

“Ammy ina zuwa” ya faɗa don so yake ta fita, Ammy ta ce “ ah dama fitar zan yi ” ya sakar mata murmushi mai sauti,tana fita kuwa ya soma shanye hawayena haɗi da kai min sumba ko ta ina tare da sauke min nufashinsa,murya cike da shauƙi da bege yake ce min “ ban son kina kuka,haka tsoron nan ki dinga mayar da shi gefe muddin ina ga wuri ba zan taɓa bari a cutar min da ke ba saboda mugun sonki da ƙaunarki da nake” ya ida furicin yana kamo leɓena na ƙasa ya dantse da haƙoransa

ta yadda ba zan ji zafi ba sai ya ɗan ja shi kafin ya saki yana murmushi.Danshin yawunsa na ji sai na kai bayan hannuna na goge,ya waro ido ya ce “ au ba ki so?”

Da sauri na girgiza masa kai saboda ganin yana shirin rikiɗa zuwa Yaya Khaleed ɗin da nake tsoro ,bai saurare ni ba ya tura ni na yi baya shi kuma yayi min rumfa.Yawunsa ya dinga ɗura min tare da sumba mai tsayawa a rai,har sai da ya ga numfashina na fita da sauri-sauri sannan ya bar ni nan ya shige toilet.Na tashi zaune ina cewa a zuci ‘ wato dayawan masu aure da suke cewa bai da daɗi ƙarya ce suke’ sai na saki murmushi kamar wacce aka tsikara na je na buɗe ƙofar toilet ɗin.

A tsaye na hango shi yana facing ƙofar shigowa,idonsa a lumshe suke yayin da ruwa sai sauka suke a sumar kansa wacce ke da masifar kyau har kwantowa take a gefen fuskarsa.Ya ɗan ware idonsa muna kallon juna,ya miƙo min hannu alamun na tawo,na maƙe masa kafa ina sakar masa murmushi tare da ƙare masa kallo.Sai yasa hannu yana kare jikinsa tare da turo baki,na tuntsire da dariya ina mai ida shiga toilet ɗin na rufe ruf.Ina nufar inda yake babu wani tunani na shige ƙarƙashin shower tuni kuma uniform ɗina ta jiƙe.

Yaya Khaleed ya ɗan rage ma ruwan ƙarfi ta yadda muke iya ware ido muna kallon juna,gashina da ke harɗe a tsakiya ya cire wa shushun ya kuwa baje a kafaɗuna.Kamar wani mai tsoron taɓa ni haka yake shafa fuskata,daga can bakin ƙofa kuma masifar Ammy Habibah ta sake fargar da mu.Na waro ido tare da dafe saitin zuciya ni tuni na manta ma ta dawo.

Da sauri na fice daga toilet ɗin,na yi tsaye ruwa na yi min tsiyaya ina kallonta ina kyarma. Da hannu ta finciko ni ta yi waje da ni,ɗakinta ta kai ni tana min masifa har da cewa in na yi ciki shinenan sai na huta na zauna rainonsa na bar zuwa makaranta.Zane ta bani na cire uniform ɗin na yi ɗaurin ƙirji,haka ta wanke min sumar kaina wacce kullum take a haka don ban yin kitso.

Yau dai kam haka ta zauna bayan ya bushe ta shafa masa mai ta soma kitse min shi,guda huɗu ta ware ta zubo min su ta gaba suna shillo.Ko da aka gama tuni idona sun yi ja tsabar wahala,har yanzu kuma Yaya Khaleed bai fito ba .

“Je ki yi wanka ki saka kaya ki tafi gida” cewar Ammy,har na nufi sashen Khaleed sai kuma ta yi min uwar tsawa dole na tafi ɗakinta,ko da na fito har ta kawo min uniform ɗina da tuni sun bushe na mayar ina cewa “ jakata na can ɗakin yaya”

“Zai kai miki in ya tashi wuce maza ki tafi gida,kuma ban son sakarci kar ki tsaya ni ma ba jimawa zan yi ba zan koma”

Yaya Khaleed ya shigo ɗakin sai baza ɓamshi yake ,“ haba Ammy in ta je can ita ɗaya za ta zauna? ” ya furta yana kallona.

“To sai a fita tun da ka gama kallon ta”

“Kitso na ga an yi mata”

“Eh sai aka yi me?”

“Yayi kyau ne” ya furta yana takowa inda nake,ya kai hannu zai shafa Ammy ta buge hannun tana cewa “ wallahi ka kiyaye ni” ya shagwaɓe fuska ya ce “ ni yanzu Ammy shikenan kin bar sona ”

“Eh tun da na ga kana son nuna min ka girma”

Ya saki murmushi mai sauti haɗi da jan gemunsa ya ce “ Ammyna....” “ ban son ji don Allah,je ka yi aski ka san da sarai tafiyar ku ta matso ”

“Zan yi Ammy,amma yanzu yunwa nake ji ”

“Ka shiga kitchen ka dafa”

“Ban iya ba sai dai SEERAT ta yi min”

“Ta ƙi ta yi ɗin”

“Matata ce fa” bai rufe baki ba Ammy ta kai masa dundu a baya tana dariya,shi ma dariyar yayi tare da ficewa.

Ni kuwa murmushi kawai nake faman yi,yadda Ammy da Khaleed ke yin lamurransu kamar wasu abokai ko kuma Kaka da jika.

A tare muka yi aikin da ta zo yi,sallah kawai ke tsayar da mu da kuma cin abinci wanda ashe ta tawo da shi.Sai daf da magrib Yaya Khaleed ya shigo,yayi aski ya fidda dukkan sumarsa da saje da gemu sai na ga ya rage kyau.Zuciyata na ji tana zafi tun ina ɓoyewa har na kasa na ce “ Yaya Khaleed sam ba ka yi kyau ba da ka cire suma”

“Aikin da zai yi ne SEERAT suka shimfiɗa dokar” Ammy ce ta bani amsa yayin da shi kuma ya zauna yana cin abinci yana kallona.Na turo baki na ce “ to dole sai yayi aikin?”

“In ba shi ba wane zai yi? Kʼasar ce ko ka yi karatu ba aikin za ka samu ba,sannan ga aurenku da aka yi ko mu ne za mu dinga kula da ku in bai yi aikin ba?” na girgiza kai,ta ci gaba da cewa “ SEERAT ba dukkan abin da muke so muke samu ba,sannan ba wai yadda muka tsara rayuwa take tafiyar mana ba.Shi namiji da nema aka san shi,dole ce take sa magidanci barin gidansa da iyalinsa don neman abin da zai rufa wa kansu asiri .Duk yadda masoya ke son junansu in babu cima soyayyar gushewa za ta yi,don ba a iya rayuwa da yunwa ko kuwa ya zauna nan ɗin kin yarda ku dinga shan ruwa ?” nan ɗin ma kai na girgiza idona na cika da ƙwalla don na gane tuni Ammy ta fahimci ban son Yaya Khaleed ya bar ni ne shi yasa take yi min nasiha.Sosai kuma na ji daɗin haka tare kuma da ƙaruwa,sai bayan sallar isha'i Daddy ya zo har nan gida da motarsa ya ɗauke mu da kayan da Ammy ta zuba a trolly.

Muna shiga na ga Hajiya ,da sauri na je jikinta cikin murna na ce “ashe kina nan tun ɗazu”

“Eh ina ta jiran dawowar ki sai Basiru yake ce min ai kina can tare da Khaleed” Hajiya ta bani amsa,na juya na dubi inda BASHEER ke zaune sai faman zane yake da takarda, ‘ wato duk inda na je ya sani?’ na tambayi kaina a zuci amma da mamakina sai na ga ya ɗago kai ya jinjina tare da sakar min murmushi.Na harare shi tare da nufarsa,na yi tsaye ina kallon yadda ya zana Hawa'u yar gidan sarki.“Ita ta ce ka yi ne?” na tambaye shi,ya girgiza kai ya ce “ a'a ni dai na yi niyya,zan kai mata shi ranar birthday ɗinta”

“Yaushe wai ka san ta?”

“Da jimawa fa sosai,ita ce matar da zan aura in na zama saurayi ” Basheer ya faɗa yana kallona,na waro ido na ce “ Hawar?” “ ita fa” ya ban amsa.Na ja kujera na zauna tare da kamo hannunsa don na yi tunanin ko abin nasa ne ya motsa,cikin rarrashi nake cewa “ ita fa ko yanzu sai ta yi aure,kuma ta girme maka”

“Na sani ai,shekarunta goma sha shidda ni kuma sha uku to sai me? Haka aka ce ni zan aure ta kuma na zama sarki saboda mahaifinta bai da Magaji ”

Na ce “ a'a ga shi nan amaryarsa za ta haifa masa shi”

Ya ce “ kin manta kin kayar da ita ta faɗi ɗan cikin nata ya mutu?”

Gabana ya faɗi rasss,kafin na kai ga cewa wani abu sai ga Yaya Khaleed yana cewa “ mi kuke tattaunawa haka?”

“Babu komai Yayanmu” cewar Basheer,tashi na yi na bar su a nan na wuce ɗakinmu wanda yanzu nake jinsa yayi min girma saboda babu Mama.Hawaye suka zubo min ina jin maraicina na dawo wa sabo dal,da ace mahaifina nada rai da yanzu Mama ba ta yi nisa da ni ba sam amma babu yadda na iya sai haƙuri.

#COTONOU

Cikin amincin Allah suka isa ,kasancewar suna zuwa Niamey daga nan jirgi suka shiga .Dangin mahaifiyar Safeenatu sosai suka yi murna ganin gidan da suka kawo ta,wanda ba sai an faɗa maka ba an gama tara dukiya har an gaji.Yadda dangin likita Mu'az suka tarbe su kuwa abun ba magana,cike da karamci da daraja.Ita kanta Safeenatu sai ta ji ta ƙara samun nutsuwa da kuma ƙaunar Mu'az,sun ci sun sha kafin a nuna musu sashen da za ta zauna wanda tuni an zuba masa kaya iri-iri babu wani gyara da yake da buƙata.Wani ɓangare suka kwana yayin da ita kuma Safeenat ta zauna ɗakinta tana jiran shigowar mijinta,tsawon lokaci kafin ya shigo da murmushin nan nasa wanda ke ƙara lula ta cikin duniyar sonsa.Hira sosai ya yi mata a wannan daren har ta yi bacci,tun washegari yan rakiya suka kamo hanyar gida bayan sun samu goma ta arziki.

Safeenatu ta yi wanka ta fito cikin wani rantsatsen less ja sai walwali take,fuskarta ɗauke da murmushi ta fito falon inda surukanta ke zauna da kuma yayansu.Cike da girmamawa ta ƙara gishe su,suka amsa cikin sakin fuska kafin Mamy mahaifiyar Mu'az kenan ta ce “ yawwa amarya a nan gidan muna da wata al'ada,in an kawo amarya muna shirya mata liyafa ,da farko za a yi mata wanka da ruwa masu tsarki floris sai kuma turaren wuta daga nan sai cin abinci fatan Mu'az ya sanar da ke duk wannan?”

Safeenatu ta yi murmushi kawai,yayin da kuma wata daga cikin yan gidan ta zo ta kama hannunta ta miƙar da ita zuwa wani sashe duk suka take mata baya.Zuciyar Safeenatu sai da ta kusa tsinkewa sa'ilin da ta ƙetara wani jan layi ta ji zuuuu duk wata sutura da ke ga jikinta sai da ta fice da kanta,amma abun mamaki ko kaɗan ba ta ji za ta iya yin gardama ba.

Kan wani jan ƙyalle aka kwantar da ita can kusan kanta aka ɗora wani kasko mai ɗauke da wutar kyandir,sai ɗakin yayi duhu sai hasken wutar kawai.Ta lumshe ido sa'ilin da aka soma zuba mata ruwan masu masifar sanyi a gangar jiki,ji take tamkar ana sauya mata halitta ne daga ta yan adam zuwa wata can daban.Waƙe-waƙen da suke yi masu kama da na waƙoƙin coci jinsu take tamkar ana zage ranta ne,tsawon lokaci kafin a yi mata sutura da wani jan ƙyalle aka naɗe ta da shi kamar sahari sai kuma matar nan ta ƙara jawo ta suka fita zuwa wani sashe inda ke da wani ƙaton table mai abinci iri-iri.

Matar ta zaunar da ita face da kujerar Mu'az wanda zuwa yanzu sam fuskarsa babu ɗigon annuri cikinta, Safeenatu ta ɗaga kai ta dubi shi sai ta ga wannan ba wanda

ta aura ba ne .Idonta taf da ƙwalla take kallon tsakiyar nasa idon,da sauri ya kawar da kai gefe ita kuwa tuni ta fahimci rayuwarta na tsikin hatsari.

“Lokacin yanka cake yayi a kawo shi” wannan karon Papy ne ya yi magana,yayin da matar nan wacce ta ja Safeenatu ta je ta ɗauko ƙaton cake ɗin , Mamy ta miƙa wa Safeenatu wuƙa ta ce “ ki yanka” ita kuwa ido ta tsura wa cake ɗin ganin an yi shi ne da hoton fuskokin mutanen da duk duniya ta fi so,sune duniyarta ba hoton kowa ba ne sai na SEERAT da BASHEER.....

Assalamu alaikum,mata da yan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .
```

_____

BOOK2

19_20

Duk da Safeenatu ba matsafiya ba ce,amma ta san sarai wannan alama ce ta duniyar Ruhaniya.Ta yaya ma za a ce hoton yaƴanta ne kan cake? Ta yi imanin cewa Dr Mu'az bai taɓa ganin BASHEER ba sai SEERAT kawai ta dai shaida masa yaƴanta biyu kuma Twins ne.Sai ga shi yanzu ta ci karo da cake mai hoton fuskokinsu,tana tsaka da tunanin wannan wane irin gida ne kuma ta kawo kanta? Sai jin muryar Dr Mu'az ta yi bayanta yana cewa “sweety ki yanka mana”

Idonta taf ƙwalla ta juya tana kallonsa kafin ta ce “ yaƴana ne fa”

“Bai komai fa kawai na yi amfani da hotonsu ne don faranta miki rai na nuni miki ni ma yaƴana ne ,don ina da niyyar kawo su nan ɗin su ci gaba da yin karatu” Mu'az ya faɗa cikin taushin murya yana yi mata murmushi.

Safeenatu ta girgiza kai ta ce “ Ni dai ba zan iya yanka yaƴana ba”

“Kin ga al'adar gidanmu ce wannan,doli ki yanka shi” Mamy ta faɗa tana zuwa ta kama hannun Safeenatu mai riƙe da wuƙa ta nufi cake ɗin duk yadda ta so ƙin yankawa amma sai da ta yi sakamakon wani mugun ruƙo da Mamy ɗin ta yi mata wanda ta yi imanin ba nata ba ne kawai.

Yanka biyu aka yi da wurin fuskar BASHEER da kuma ta SEERAT,dukkan mutanen gidan suka hau ihu annuri cike da fuskokinsu shi kuwa Dr Mu'az wani murmushi yake yana kallon tsakiyar idon Safeenatu wacce banda kyarma babu abin da jikinta ke yi,hannunta ya kama suka nufi sashensu tana waigo ta ga yadda suke cin cake ɗin sai kace mayuwanta ko kuma yau ne suka soma ganinsa.

Har tsakiyar gado ya kwantar da ita ya ja zane ya rufe ta tun daga ƙafafunta har zuwa ƙirjinta ita kuwa banda kallonsa babu abin da take yi.Ya goge hawayen da ke yi mata zuba ya ce “kin fi kyau in kina murmushi Feenat ɗin Mu'az”

Ta buɗe baki da niyyar yin magana amma kuka ya kubce mata,“yi shiru mana na san kina da tarin tambayoyi a gare ni ,amma ki yi haƙuri da sannu za ki fahimci komai” sai y yunƙura zai tashi ta yi saurin kamo hannunsa murya na rawa ta ce “don Allah kar ku cutar min da yarana ina sonsu,su kaɗai gare ni waɗanda suke maye min gurbin mahaifinsu ”

Ya ɗan ɓata rai ya ce “kenan ni ban maye gurbin ba?”

Ta girgiza kai ta ce “Dr Mu'az babu ta yadda za ka maye gurbin mutumin kirki irin Bashir ,halinka da nasa ba iri ɗaya ba ne ko kaɗan ba su yi kamanceceniya ba.Shi ruhinsa tsarkake ne ba irin naka ba,ko kaɗan ban yi tunanin rayuwar ƙunci ka yi min tanadi ba.Duk mene ne wannan? Wanka da ruwa masu tsarki,yin waƙa kamar ta tsafi ga wata wutar kyandir da aka kunna haka ma kayan jikina suka cire kansu”

Bai bata amsa ba sai fuskarsa da ya matsa kusan tata,bai ɗauki wani lokaci ba ya soma sumbatar ta.Duk uban tsimin da Safeenatu ta sha na gyaran jiki ya tashi a banza saboda tsaka mai wuyar da take ciki,ko kaɗan ba ta jin daɗin abin da yake yi mata.Duk yadda ta so katange masa jikinta amma ba ta yi nasara ba sai da ya san ta a ɗiya mace,abu guda ya bata mamaki yadda ya kawo addu'ar kasancewa da iyali tare da wasu dogayen addu'o'i na tsari.Ta hasken da ya rage yake kallon ta,wani irin mugun sonta ne ya ratsa masa zuciya a yanzu da ya gama mu'amala da ita.

“Feenat ....” bai kai ƙarshe ba ta dire daga bed ɗin ta shiga toilet.Tana wanka tana kuka ,sai da ta fito shi ma ya shiga .Kayan atamfa ta saka tare da ɗaukar wayarta hannunta na rawa ta turawa Goggo Habibah text kan cewa “ Goggona na shiga uku

ashe ban auru ba,da matsala gidan matsafa na faɗo” saƙon ko minti ɗaya bai yi ba Habibah ta kira ta,“ ki aje hankalinki ki yi mini bayanin duk abin da ke faruwa”

Sai da Safeenatu ta waiga ta ga eh babu dai kowa sannan ta soma yi wa Goggo Habibah bayanin komai daki-daki a ƙarshe ta ce “ ban taɓa tunanin Dr Mu'az zai yi min haka ba,sai yanzu nake mamakin yadda na aminta da shi cikin sati guda kacal har na aure shi” ga mamakinta sai ta ji ita Habibah na yin wani murmushi kamar wacce aka yi wa bushara da gidan aljanna ta ce “ Safeenatu in ba ki manta ba tun SEERAT na cikin tsumman goye na taɓa shaida miki cewa sai kin yi haƙuri za ki dinga ganin abin da hankali bai ɗauka,to wannan ɗin ma yana ciki sai ki yi haƙuri ki samu nutsuwar zuciya ko kaɗan kar ki nuna musu wankan ƙaddamawar da suka yi miki bai game jikinki ba .Sannan in sha Allah tun yau zan shirya kayan Twins suna nan tafe kamar yadda suka aiko musu katin gayyata,in kin fita ki shaida musu yaranki suna nan tafe” tana gama faɗa ƙittt ta kashe kiran.

Kaso ashirin na fargaba da damuwar Safeenatu sai ta ji sun gushe,ko ba komai ta san Goggonta ba za ta taɓa yi mata ƙarya ba ballantana ta saka rayuwar yaranta da ita kanta cikin matsala.Ta saki wani murmushi tuna yadda SEERAT ta yi wa Mamuh,kamar wacce aka tsikara haka ta miƙe ta je gaban dressing mirror ta shafa hoda da kwalli da man leɓe.Ko da Dr Mu'az ya fito ya tarar da ita tana zaɓar kayan da za ta saka,wata doguwar riga ta ɗauko blue ta saka ta ɗora mayafinta a kai.

Shi ma a gaggauce ya shirya kafin ya zo inda take tsaye ya ce “ kina jin yunwa ne?” kai ta jinjina masa,da kansa ya zaɓo hijabi ya saka mata sannan ya ja hannunta zuwa waje.Ga mamakinta duk ahalin gidan hankalinsu na kan ƙofar fitowa wannan yasa suna ganinsu duk suka miƙe suna kallon Safeenatu.Ita kuma ta dubi Dr Mu'az ,ya ce “ ki faɗa musu” har za ta tambaye shi me? Sai kuma ta tuna da zancen Goggonta sai ta sakar musu murmushi ta ce “ suna zuwa nan da kwana biyu” fuskokinsu ne suka faɗaɗa,Mu'az ya ja ta zuwa waje .

Direba ne ya ja su zuwa wani gidan cin abinci,suna baya zaune Dr Mu'az sai wasu abubuwa yake yi mata don nuna ƙaunar da yake mata.Tamkar wata yarinya haka ya kama hannunta suka shiga ciki,da kansa ya ja mata kujera ta zauna sannan ya zauna face da ita yana saka mata murmushi.

Wanda ke kula da baƙi ya zo ya tambaye su abin da suke so,nan suka faɗa masa babu jimawa aka kawo musu.Hankali kwance suke cin abincin,ita dai Safeenatu can ƙasan zuciyarta sai saƙe-saƙe take bayan sun gama sai ya kaita can wurin Teku Cotonou .Daga inda take tsaye take hango wani haske can tsakiyar ruwan,ta ƙanƙance ido tana kallo sai ta ga wani ƙaton kifi ya fito tare da sake yin nitso ba ta san lokacin da ta ce “ dubi kifi” ta nuna masa da hannu.

Dr Mu'az ya ce “ da gaske kin ga kifi?” ta buɗe baki za ta basa amsa kifin ya sake yin sufa ya fito wannan karon SEERAT ta gani zaune daram kansa kafin ya koma cikin ruwan.

Ta waro ido tana jin zuciyarta na ɗan bugawa,ganin ba za ta basa amsa ba kawai ya ja ta suka koma mota direba ya ja su zuwa gida.Wannan karon babu kowa tsit yake,part ɗinsu suka wuce Dr Mu'az sai hira yake yi mata don gusar mata da damuwarta ita kuma tun tana saurarensa har bacci ya ɗauke ta.

Ko da ta farka ba ta gansa ba,yunwa take ji sosai sai ta fita falo duk da tana tsoron cin abincinsu har yanzu babu kowa gidan tsit yake tamkar ita ɗaya ce ma a ciki.Hanyar da take tunanin kitchen ce ta nufa,komai jere yake ras babu datti daga bayanta ta ji motsi ta juyo da sauri sai ta ga ashe Dr Mu'az ne.Ya sakar mata murmushi tare da miƙo mata ledar hannunsa ta karɓa tare da fitowa tana cewa “ gidan yayi shiru”

“Ai ba za su sake fitowa ba sai kuma wani lokaci”

Da mamaki ta dube shi ta ce “ don me?”

“Hum!" Shine kawai abin da ya ce har suka isa sashensu,ledar ta buɗe kayan maƙulashe ne Cocao ɗin ta soma ci har sai da ta ƙoshi ta hauda madara.

#NIJAR

Da kuka da zubar majina aka ɓanɓare ni daga jikin Yaya Khaleed wanda yake tsaye cikin shirin tafiya Yamai.A gaban idona ya shiga mota yana ɗaga min hannu,shi kansa a fuskarsa ina iya hango rashin jin daɗin rabuwar tamu.Haka muka dawo gida ni da Ammy,tamkar wata laɓuɓuwa haka na koma ina manne a jikinta maraici duk ya dabaibaye ni ta ko ina.Dakyar na iya barin ta shiga kitchen ta yi mana girki,ina nan kwance ina tunani iri-iri sai ji na yi tana cewa “ SEERAT za ku je ke da BASHEER ku yi wa Mamarku sati guda sai ku dawo,zan je makarantarku na shaida musu”

Wani irin daɗi ne na ji ya rufe ni ban san lokacin da na miƙe na je na rungume Ammy ba,a gaban idona ta haɗa kayanmu.Basheer na dawowa daga yawonsa na je da murna na faɗa jikinsa ina cewa “albishirin ka?”

Bai ce komai ba sai murmushi da yayi min yana mai jan tsoron kitsona,na buge hannunsa na ce “kai ai ba ka san abun arziki ba ina cewa albishir shine ka yi wani banza da ni”

Ya kamo tsintsiyar hannuna ya ce “ SEERAT na fi ki zaƙuwa da mu je gun Mama fa”

“Ya aka yi ka san can za mu je?”

“Ke zo ki ga wani abu” ya faɗa tare da jan hannuna zuwa tsakar gida,irin tsuntsuwar nan ce wacce na taɓa ganin Yaya Khaleed na bata abinci.

“Tun ɗazu take zagayen gidan nan ko me take nema oho” cewar BASHEER.

Ni kuwa tambarin da ke kusan wuyanta kawai nake kallo tabbas na san shi amma na manta .“Tsuntsuwa ce fa kawai” na furta zan koma ciki amma Basheer ya riƙe min hannu yana mai cewa “mi ya haɗa ku faɗa da Bafulatanarki?”

“Wace Bafulatana ?” na tambaye shi,yayi min wani kallo kafin ya ce “kar ki raina min hankali mana kin zata ban sani ba?”

“Mi ka sani?” na faɗa don son tabbatar da shin gaske ya sani ɗin,hannuna ya jimƙe sosai har sai da na yi ƙara cike da azaba na basa amsa “ni ma ban sani ba kawai dai ta bar zuwa”

Ya sake min hannu yana dariya tare da yin gaba,na bi shi da kallo ina mamakin yadda Basheer ke da ƙarfi har haka.

Da dare sai da Ammy ta kira mana Mama muka yi yar hira tare da faɗa mata jibi za mu zo ita ma ta nuna murnar ta .Da Daddy ya dawo Ammy ce ta yi masa bayani,da farko har zai hana amma kuma sai ya haƙura.A cikin kwana biyu aka shirya tafiyarmu,gidan mota Daddy y kai mu bayan ya miƙawa Basheer kuɗin da za mu ci abinci a hanya.Daga Zinder motarmu da ta tashi ta Maradi muka fara biyowa,muka tsaya aka ƙara ɗaukar wasu kafin mu cira zuwa Niamey.Ina kusan window yayin da Basheer ke gefena yana bacci,na juyo tare da tsura wa fuskarsa ido tamkar wani Zaki haka nake ganin fuskar na rikiɗa.Cikin magagin bacci yayi kamar zai faɗi amma na yi saurin taro shi na kwantar da kansa a kafaɗata,ya ɗan ware ido kaɗan yana kallona kafin ya ci gaba da baccinsa.Sai da motar ta tsaya wani gari ne sannan na tashe shi,a tare muka fito muka yi tsaye muna kallon wurin.Dukkanmu yau ne muka soma yin balaguro,“ yunwa fa nake ji” cewar Basheer,na dube shi abin da na lura tun da aka ce za mu yi tafiyar nan ya soma cin tsiya kamar mai MACIJIN CIKI (MRS SADAUKI).

“Ni dai fitsari zan yi” na faɗa ina kallon banɗakunan da aka rubuta na mata ne,“ to in kin gama sai kuma cikin mota ni bari na sayo mana abinci” a haka muka rabu na je na ɗauki buta sai da na jira wata ta fito sannan na shiga ina fitowa kuwa na koma cikin mota.

Ina ta jiran BASHEER amma shiru ga mutane sai shigowa suke tuni kuma direba ya zauna mazauninsa yana tambayar in kowa ya shigo,duk suka amsa kowa na kusa da shi ya dawo amma banda ni da tuni na miƙe ina cewa “ ƙanena bai dawo ba don Allah ku tsaya na dubo shi” na faɗa kamar zan yi kuka tare da fita.Duk sai da na bincike gidan motar amma ban ga Basheer ba ina jin direba na min horne amma na yi banza da shi sai raba ido nake.

“Ke ki tawo mu tafi kin wani tsaya kan hanya ki riƙe ƙugu” cewar karen mota yana mai jan hannuna ya nufi motar da ni,“ in ya dawo ba za a rasa motar da za ta kai shi ba can tun da motocinmu na dayawa” ya ƙara faɗa bayan mun shiga motar .

Tsaye na yi ƙiƙam ina ƙarewa mutanen ciki kallo,direba ya ja mota na ce “ ka dakata babu fa inda za mu je sai na ga ƙanena” nan fa mutane suka yi min caaaa har da masu zagina.Sam ba zan lamunci a yi tafiyar nan babu Basheer ba,zancen wata mota za ta kai shi ban yarda ba hakan yasa na yi amfani da hannuna a gaban kowa na tsayar da motar ta hanyar cire key ɗinta ya dawo hannuna.Tsit motar ta yi ana kallona kowa ya sha jinin jikinsa,“da na ce muku sai an jira shi kun ɗauka wasa nake ? To babu inda za a je”

Wani mutum ne ya miƙe,sayen yake da dogayen kaya har da saka casbaha a wuta.“ Yʻata ki yi haƙuri amma ɗan uwanki na can gaba da mu bai cikin garin nan,ƙila in mun tsaya a wani gun zai shigo” a tsakiyar idonsa na hango gaskiya yake faɗa ,kuma na fahimci malamin tsibo ne mai aiki da Aljanu .Na ja ajiyar zuciya tare da mayar da key ɗin motar,direba ya soma jan mu.A haka na samu wuri na zauna ina tunanin Basheer mutum ne ko aljani,sama da awa biyar muna gudu kafin mu tsaya wani garin abun mamaki can na hango Basheer zaune kan kujera sai cin biredi yake yana ganin motarmu ya miƙe tare da nufo ta.Kasa haƙura na yi da sauri na fito tare da faɗawa jikinsa ina kuka,ban taɓa sanin har haka nake sonsa ba sai yau.

“Dallah Malama cika ni,nan duk a gajiye nake kun wani tafi kun bar ni sai a ƙafa na zo” ya faɗa yana janye ni daga jikinsa.Kʻafafunsa na duba duk sun yi datti,leda ya miƙo min kafin ya ja hannuna zuwa ciki.Mutane sai kallonmu suke,bayan mun zauna ya ɗan rage murya ya ce “ ina tsuntsuwar nan da muka gani a gida? To wallahi RUHIN ALJAN ne a jikinta cabbb har garinsu fa na bi ta,kin ga in kina son gani zan nuna miki ”

Ledar da ya bani na buɗe na soma cin gasasar kazar har sai da na ƙoshi,sannan muka hau hira.

Sai kusan sallar asar muka isa Yamai,nan gidan motar muka kwana ina ta jin haushin da banda waya ballantana na kira Yaya Khaleed.Washegari sallar asubah kawai muka yi kafin mu ɗauki hanyar Kotonu,muna shigar garin na buɗe window na soma shaƙar iskar sararin samaniya.Ƙamshin furanni da kuma yanayin damina duk ya haɗe garin,ko da muka sauka Dr Mu'az yana zaune zaman jiranmu na san shi wannan yasa na gane shi.A motarsa muka shiga sai tambayar mu hanya muke ,ni kaɗai ke basa amsa har muka isa aljannar duniya don sai haka za a kira gidan komai tsaf.

Murna sosai muka shiga yi da Mama kamar mun shekare ba mu ga juna ba,duk ta haɗe mu wuri guda ta rungume.Muna tsaka da nishaɗinmu Dr Mu'az ya cewa Mama “ ki zo mana ki yi min rakiya mu karɓo wani saƙo”

Fuskar Mama ta ɗan canza ta ce “ da dai ka aiki direba ,ko kuma ka tafi kai ɗaya”

“No tare za mu je kafin lokacin sun yi wanka sun ci abinci”

Har Mama za ta sake yin magana amma Basheer ya tari numfashinta,“ Mama ku tafi kawai kar ki wani damu” ta jinjina kai tare da bin bayansa suka fice.

Na ɗan ɓata rai na ce “ mene ne wannan ka yi? Muna tsaka da nishaɗinmu,kwana nawa rabon mu da ita?” maimakon BASHEER ya ban amsa sai yayi min nuni da hannu tare da rage murya,“ dubi can cikin ƙwan fitila” ido na ƙanƙance ina kallon wurin a zahiri za ka ɗauka ƙwan fitila ne nan kuwa ƙwarangwal ce.Basheer ya min nuni da ido na kalli ƙasa,ina kai idona capet ɗin da ke shimfiɗe a ƙasa da fatar mutane aka yi shi,“ ki dubi can wurin cin abinci” ya faɗa cikin muryar raɗa.Sakin baki na yi ina kallon yadda fatale ke zaune ras suna cikin abinci,“ duba can” ya sake yi min raɗa.Na kai dubana ga wani ƙaton madubi wanda in mutum ya gansa zai ce na ƙawata ɗaki ne nan kuwa matattarar ruhika ce.

“Kar ki taɓa nuna kin ga waɗannan abubuwan mu yi kamar ba mu san komai ba don ganin gudun ruwansu”

“Su wa?” na tambaye shi .

“Waɗanda suka tura mana katin gayyata mana ” ya ban amsa.Muna nan zaune kuwa sai ga wasu tsofi biyu sun fito da alamu mata da miji ne,macen ce ta soma yin magana “ Barka da zuwa jikokina ku zo nan na ji ɗumin jikin ku”

Haka muka je muka rungume ta,dakyar na iya sheɗawa tsabar yadda take warin gawa.“ Mamy sunana wannan kuma ku kira shi da Papy” ta sake faɗa duk muka sakar mata murmushi.

“Ku taso mu je ku ci abinci in kuka biye ta wannan haka za ta yi ta muku surutu” cewar Papy.Muka yi dariya tare da bin bayansu,wani sashe suka nufa da mu wanda yake da mugun sanyi .Muna shiga BASHEER ya takure wuri guda tare da saurin riƙe hannuna,murya na ɗan rawa ya ce “ SEERAT jiri nake ji,idonaaa ” ya furta da ƙarfi lokacin da muka hau kan wani madubi wanda daga ƙasa kana iya hango ruwa da kuma halittun cikinsu.Na jawo BASHEER na ɓoye fuskarsa a ƙirjina,yayin da kuma na tsura wa mutanen da ke zagaye mu ido kowanne da wuƙa a hannunsa kamar sun ga nama.

Abu guda zuwa biyu ne damuwa ta,na farko yadda BASHEER ke rawar sanyin nan,na biyu kuma yadda sam Bafulatana ba ta nuna min wannan farmakin ba da za a kawo min ballantana ta sanar da ni mafita.Ina cikin tunanin mafita na ji an yanke ni ga damtsena,na rumtse ido saboda yadda azaba ta ratsa ni.Dakyar na ware ido na dubi wacce ta yanke ni ɗin Mamy ce,jinina wanda ke jikin wuƙar take lasa tana jinjinawa ɣan uwanta kai.A tare a lokaci guda sauka yo kanmu na ɗaga hannuna tare da buɗe tafin haske ya fita wanda yayi mana iyaka da su duk suka ja baya,amma kuma ba su zubar da makamai ba na fahimci za su iya kawo min hari na biyu.

“SEERAT ki yi wani abu ban iya yin komai a nan,cikin ɗakin kwalba muke babu iskar duniya duk sun rufe wata iskar shaƙa” BASHEER ya faɗa a wahalce yana rawar sanyi.

Na ɗaga kai sama ta madubin na hango sararin samaniya ta yi baƙi ƙirin,ina jin lokacin da goshina ya soma motsi kafin haske ya fita ya naushi madubin ya ɗan

tsage kaɗan su kuma suka sa ihu,haka na ci gaba da yi har na samu ya fashe tamkar wani hayaƙi haka BASHEER ya suɓuce daga jikina yayi sama ya fice ta hudar madubin.

Mamaki yasa na manta ina tsakiyar magauta sai jin wata sara na yi a bayana an caka min wuƙa har ta fito a cikina.Na saki uban ihu tare da zubewa ƙasa,buguwar tafin hannuna na hagu da madubin ya haifar masa da tarwatsewa na faɗa kwacaaaa cikin ruwan.....

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu....

```MRS SADAUKI□✍```
```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK2

21_22

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

A hankali na soma nitsewa ƙasan ruwa,idona a buɗe suke taram sai dai bana gani sosai.

“Ta galabaita” na ji wata murya na faɗar haka amma sam ban ganin mamalikinta,daidai inda aka caka min wuƙa na soma jin wani tattausan hannu na shafa wa tare da furta “ cutarwa ta koma ga wanda ya haifar da wannan cutar” kamar cirar ƙaya haka duk wani raɗaɗi da zugi ya ɓace min sai dai wata irin gajiya nake ji sosai.

Daidai saitin cikina wani ƙaton kifi ya danna nan na soma fitar da wata baƙar guba a bakina wacce tsabar galabaita sai da na fita hayyacina.

“Seerat?” na ji muryar Mama kaina,dakyar na iya ware ido na dube ta kafin na yi ƙoƙarta na tashi sai na gan ni kwance kan kujera sai da na ƙarewa ko ina na falon kallo,nan duk abin da ya faru ya dawo min wanda na kasa tantance shin mafarki na yi ko gaske?

“Na'am Mama har kun dawo?” na furta ina mai duben ta.

Ta saki murmushi ta ce “eh tun ɗazu muka shigo muka tarar kina bacci”

“Ina BASHEER?”

“Yana tare da Dr Mu'az ” ta bani amsa,na lumshe ido ina zancen zuci ‘ tabbas yau sai ka faɗa min kai wane ne ’

Da taimakon Mama na samu na wuce can bedrom da trolyna,kayan jikina na rage na shiga wanka.Har ƙarshe na kai shower ɗin ruwan suka dinga zuba da ƙarfi,na ɗaga kaina sama ruwa suka yi ta dukar fuskata sai dai abin da na lura sam ban jin alamar nan ta kamar numfashi zai ɗauke haka kuma ban rufe idona kamar yadda ba su shiga ƙofofin hancina ba.

Daga ƙasan tile nake ganin wasu ƙananun kifaye na ɓulɓulowa har suka cika toilet ɗin,cike da murna na rage tsayi ina wasa da su yayin da ruwan pampo ke ta shatata ga ƙasa.

Waƙe-waƙen halittun ruwa da kuma maganarsu da nake ji shi ya shagaltar da ni da hankalkuwa ruwa sun cika toilet ɗin saura ƙiris su taɓa rufinta.

Muryar mijin Mama ce na soma ji cikin kakarin mutuwa yana kiran sunana,yayin da kuma Mama ke tambayar shi lafiya.Da mugun sauri na je na kashe pampon yayin da ruwan kuma suka fara bin duk wata hanya suna shigewa.Na ja ajiyar zuciya tare da saka towel na fito,a gaggauce na shirya na fito abun mamaki ahali guda na gani sun cika falon dukkaninsu fuskokinsu ɗauke da damuwa.Ɗaya bayan ɗaya na kalle su,duk na shaida su kallona na tsayar kan Mamy wacce ke kwance tana fitar da numfashi kamar za ta mutu gefenta kuma mijinta ne sai faman naɗa mata bandeji yake a gefen cikinta.Na saki murmushi don yanzu na samo amsar tambayata ta ɗazu,wato ba mafarki nake ba a gaske ne.

“Lafiya na ga kowa sai kallona yake?” na yi tambayar ina duban ahalin,cikin masifa wata mata ta ce “ iskancin banza muna kwancinmu kika wani gayyato mu shine za ki tsaya kina tambayar lafiya?”

“Ki yi wa mutane shiru don Allah! ” BASHEER ya katsa mata tsawa cikin sautin muryarsa mai fita bibiyu,da tasa da kuma ta wani babban mutum.Da dukkan alamu hatta Mama ta ji haka don na ga ta zabura tana kallonsa,shi kuwa BASHEER a sannu a hankali na ga fatar jikinsa na fitar da wasu abu tamkar sayu suna rufe jikinsa tare da fitar da zane,muryarsa a wannan ta ɓace sai ta babban mutumin “ SEERAT ki yi wa mijin Mamarki tambaya ya faɗa mana dalilin da ya tura mana katin gayyata”

Na tsure shi da ido ina son tantance ƙwayar idon nasa,tabbas wannan kallon irin na tsohon da na gani ne a can dokar daji wato sarki Shakal.

“Dr Mu'az mi yasa ka auri Mama? Na fi matse da wannan tambayar don ɗayar ina da satar amsa” na tambaye shi ina mai dubansa.

Ya kalli Mama wacce ta ƙure shi da ido da dukkan alamu ita ma tana buƙatar amsar,jikinsa ya soma yin rawa lokacin da BASHEER ya shaƙe masa wuya,ba wai yayi amfani da hannu ba ne a'a iska wannan mai kaɗawa ce ta zagaye wuyan Dr Mu'az tana matse shi sosai.

“Ka bar ni zan yi magaba” ya furta da ya ji uwar bari, Basheer ya saki murmushi.Cike da kunya ya sunne kai ya ce “ da farko dai na auro ta domin naman jikinta kawai,zan baiwa ahalina ita matsayin sacrifice.Ban taɓa son Safeenatu ba sai ranar farko da muka kasance,ki yarda da ni Feenat wallahi ina sonki yanzu” ya ida furicin cikin kuka yana shirin taɓa ta amma Basheer ya hura iskan bakinsa ya ture Dr Mu'az da shi har sai da ya faɗi.

Yanayin fuskokin mutanen wurin ne ya ƙara munana na rashin jin daɗi da tsoro.

“Ka faɗa mana ɓoyayyen sirrin ka” Basheer ya faɗa yana kunna sigari tare da soma sha,ban san a ina ya same ta ba amma kuma ban yi mamaki ganin ta a hannunsa ba.

Sai da Dr Mu'az ya zube kan gwiwansa sannan ya soma bamu labari“ a shekaru goma sha biyu da suka wuce na gama karatuna Mamy da Papy da kuma duk sun halarci taron karrama ni,bayan an gama ni ne da kaina na ɗauke su cikin sabuwar motata domin isa gida.A nan muka yi hatsari motar ta juye da mu,dukkansu suka mutu alhalin ni ko targaɗe ban yi ba.Hankalina ya tashi sosai nan na soma ihun neman agaji sai dai babu kowa kasancewar mun shigo daji wanda daga shi sai garinmu.Ina cikin wannan halin ne wata murya ta daki kunnena tana yi min albishir kan cewa za ta iya maido su da rai muddin na yarda na aure ta.Amsa mata kawai na yi na yarda,sai a lokacin wata farar Bafulatana ta bayyana a gabana tana da kyau sosai ba ƙarya amma ta fi min kama da jinsin jinnu.A gaban idona ta buɗe ƙwaryar da ke kanta ta dinga watsawa Mamy da Papy wasu ruwa abun mamaki rasss suka miƙe hatta motata ma ta dawo daram.Murmushi kan fuskarta ta shaida min sunanta Naylah kafin ta doshi can cikin ciyayi ta ɓacewa ganina.Har muka iso gida ina tunaninta,kwana biyu sun shuɗe na dawo daga wurin aiki na tarar da Naylah ta zo gidanmu suna ta yin hira da iyayena,abin da ya fi ɗaure min kai yadda suka jingina ta a matsayin matata sannan da dukkan alamu ma sun saba da ita sosai.Hankalina bai ida tashi ba sai da na ga a ranar ana kwashe kayanmu wai za mu koma sabon gida,duk yadda nake son yin tunani kuma na kasa a doli na biye musu muka dawo nan gidan” yana kawowa nan sai yayi shiru yana kallon matar da ta yi min tsawa ɗazu,ya nuna ta da yatsa ya ce “ Ga Naylar nan,tun bayan zuwanmu nan gidan take tunzura ni auren zawarawa,auren kuma duk yayi tsayi bai wuce wata uku sai matar ta mutu kun ga duk mutanen nan da kuke tunanin ahalin gidanmu ne? To duk ni nan na aure su dukkansu zawarawa ne babu wacce ta taɓa haihuwa,sannan mazajensu mutuwa suka yi ba wai saki ne ya shiga tsakaninsu ba.Da na fahimci Naylah muguwa ce na so fasa aure-auren nan ne fa ta shaida min da cewa ba zan sake ganin iyayena ba muddin na daina,ina sonsu sosai shi yasa na ci alwashin zan yi komai muddin dai zan dinga ganinsu”

Cikin ƙaraji Naylah ta ce “ yadda na ci alwashi dole na cika burina,ba zan taɓa barin wata bazawara a doron duniya ba tana kukan mutuwar mijinta.Dole ne ta shigo duniyarmu don haka Safeenatu ke ma sai kin mutuuuu ” ta yi furicin tare da yin wani tsalle ta dira gaban Mama ta ɗaga wuƙa za ta caka mata , Bafulatanata ta bayyana ta riƙe wuƙar tare da ɗauke ta da wani gigitacen mari har sai da ta zube ƙasa “ Naylah don mijinki ya mutu kin shiga baƙin ciki da damuwa,kika kasa haƙuri kika kashe kan ki kin yi tunanin dukkan mutanen duniya haka suke ? To duk wannan iskancin naki zai tsaya a yau za ki koma makwancinki ke da duk waɗannan fatalen

da kika cika a gida sannan Dr Mu'az zai fita ya koma rayuwa cikin mutane” Bafulatanata ta faɗa ,daga ni sai BASHEER kawai ke iya ganinta sai kuma fatalen Mama da Dr Mu'az kuwa iya muryarta kawai suke ji.

“Ba zan koma cikin kabari ba,ko na shiga sai na fito” Naylah ta faɗa cikin ƙaraji.Bafulatana ta yi murmushi tare da kiran sunana “ SEERAT āvashā” shiru na yi ina tunanin ‘ mi ma kalmar ĀVASHĀ ke nufi? ’ can na samo tana nufin ɗalasiman esprit ɗin cikin ruwa,na same su ne lokacin da na nitse a ruwa.Bakina har rawa yake wurin soma karanto su,nan ruwa suka soma ɓulɓulowa ta ƙasa Bafulatana ta ce “ Basheer gare ka” ko baki ba ta rufe ba ya buɗe bakinsa yana hura iska duk wani rufin ɗakin da kuma bangunan suka soma rushewa suna nitsewa cikin ruwa kafin ƙyaftawar ido komai ya shafe kamar ba a taɓa ƙawata gidan ba.Kabaruruka ne suka fito ta ko ina,Mamy da Papy da sauran duk fatalen wurin masu siffar mutane duk suka koma makwancinsu sai Naylah uwar taurin kai saboda ita tana da power sosai.Bafulatana ta dube ni,na sakar mata murmushi tare da ciro sarƙar wuyana na cilla jikin Naylah,kifin nan ya haɗiye Naylah na duƙa na ɗauki sarƙata na mayar.

Bafulatana ta ɓace, Basheer ya dawo normal,Mama da Dr Mu'az suka fara yʻar kallon-kallon kafin Mama ta yi luuu ta za ta faɗi yayi saurin taro ta.

“Mi muke tsakiyar maƙabarta?” Basheer ya tambaya yana wani ƙarya wuya,ban basa amsa ba sai wurin Mama na nufa ina kiran sunanta.

Basheer ya matso ya ci gaba da tambayata “Wai mine ne ke faruwa? Ni na kasa tuna komai,wai ba ....” cike da masifa na katse shi “ don Allah ka rufewa mutane baki kana yin wani abu tamkar ba ka san kai ɗin wane ne ba,da wannan banzan surutun da amfani ka yi da powerka ka hura mu can cikin gari nan dai ai ka ga a dokar daji muke”

Murmushi yayi ya ce “ wato yanzu kin fahimta” na buge masa hannun da yake jan hancina.Ina shirin sake yin magana Basheer ya hura mu kamar ƙyaftawar ido sai ga mu a cikin wata harabar asibiti,Dr Mu'az ya saɓi Mama da sauri ya shiga ciki ni kuma dube-dube na soma ta inda BASHEER zai ɓullo.Kamar minti biyu sai ga shi ya tawo ƙafafunsa duk sun yi datti,na dube shi na taɓe baki kafin na wuce gaba ta take min baya.Tuni an karɓi Mama an soma yi mata aikin,kan kujeru muka zauna

Basheer ya rage sautin muryarsa ya ce “ SEERAT dubi wata budurwa can wallahi duk ciko ne ta yi ba hips ɗinta ba ne ko na nuna miki ki gani?”

Na girgiza kai ina murmushi ba tare da na basa amsa ba,ai kuwa ya hura mata iska rigarta ta yi sama ta saki ihu tana tattare rigar ta mayar daidai.Basheer ya ƙyalƙyace da dariya ya ce “ kin gani ko?” na jinjina masa kai,“ to kar dai ki yi koyi da ita babu kyau,maza ba su so a cuce su sai an yi aure suka ba haka ba a ta yi wa matan wulaƙanci.Amma ko da yake ke duk Yaya Khaleed ya gama gane miki jiki”

Na haɗe rai na ce “ wai Basheer mine ne haka? Duk ya ake yi kake sanin haka? Kenan bibiyata kake?” kai ya girgiza ya matso kusa da ni sannan ya ce “ yar Bafulatanarki dai ce matar Alhajin cikin kwanyata kin ga duk abin da kuka yi zan sani,ke ma nan fa in na yi wani abun sai kin sani”

Shiru na yi ina nazari,amma ya ƙi bani damar yin tunanin ya ce “ ke wasa fa nake,babu abin da za mu sani kawai dai saboda Bafulatanata na mitar cewa kullum Khaleed na manne da ke ba ta samun damar zuwa wurin ki haushi yake bata shi yasa ni ma na sani.Kullum ai suna yin hira da mijinta,kin san mi yasa take fushi da ke?” na girgiza kai,ya ci gaba da cewa “ kin bar bin umarninta in ta saka ki abu wanda kika ga dama kike yi,ko matar sarki da kika kayar ɗan cikinta ya mutu ta ce ba da yawunta kika yi ba kuma ba haka ta tsara ba”

Dr Mu'az ya fito ya kira mu sai muka bar zancen tare da nufar shi,ɗakin da Mama take tana bacci ne ya kai mu.Na koma gefe ɗaya na zauna shi ma Basheer haka sai muka saka ta tsakiya kowanen mu kuma ya riƙe hannunta.

“Don Allah ko za ku yi min fashin baƙi dangane da abin da ya faru?” Dr Mu'az ya faɗa , Basheer ya ce “ wane bayani kuma za a yi ma bayan a gaban idonka komai ya faru? Ka fara tunanin rubuta takardar sakin Mamarmu shi ya fi kan wannan banzar tambayar”

“Iyayenka sun daɗe da rasuwa tun shekaru goma sha biyu, waɗanda kake tare da su MUTUM NE DA RIGAR ALJAN (MRS SADAUKI) su ɗin fatale ne jinin da kake basu na matan da ka aura tamkar ban ruwa ne kake yi musu,yanzu kuma sun koma makwancinsu sai ka yi haƙuri” na furta cikin taushin murya ina kallon Basheer da ke harare na.“ Sai wani lalaɓa shi kike kamar ubanki,ke ko irin ɗan kishin nan uwarki ta auri wani namiji ba ki ji? To wallahi sai ya sake ta” shiru na yi masa ban ce komai ba haka ma Dr Mu'az sai kuka yake kamar wani ƙaramin yaro.

Sai da Mama ta kwashe wajen awa ɗaya kafin ta buɗe ido,da mu ta soma yin tozali ta jawo mu ta rungume tana hamdala ga Ubangiji.Hawayen da suke yi mata zuba muka shiga goge mata kafin mu tayar da ita zaune,Dr Mu'az da ke can gefe ya taso ya ce “ Safeena ya jikin naki?”

Ta kawar da kai gefe ba tare da ta amsa ba,a ƙarshe ma toilet ta shiga bayan ta fito ne ta bamu umarnin mu tashi mu tafi.

Duk muka fito waje ina mai tambayar “ yanzu ina za mu je Mama?”

“Wace irin tambaya ce wannan? Gida za mu je mana can Nijar ” cewar Basheer.

“Kafin ku tafi don Allah ku yi min alfarma ku zo mu je can gidana” Dr Mu'az ya furta.

Cike da iya shege Basheer ya ce “ gidan fatale?”

“A'a gidana dai”

Duk yadda suka so ƙiyawa amma sai da na ci galaba kansu muka bi Dr Mu'az,wani gidan ne daban ya kai mu shi ma babu laifi yana da kyau.Kuɗi masu yawa ya fiddo ya ce “ ga wannan ku tafi da su don ba za su yi min amfanin komai ba”

“Ka bani takardar sakina to” cewar Mama.

“Na daɗe da rabuwa da ke Safeenat Allah ya baki miji na gari”

“A'a ka rubuta dai don Allah ” cewar Basheer,haka Dr Mu'az ɗin ya rubuta mata takardar sakin kafin mu fito.

Gidan mota muka nufa bayan mun sayi abubuwan da za mu ci , Basheer sai murna yake.“Wai yanzu daƒi kake ji don auren Mama ya mutu?”

“Seerat wai mi yasa kwanyar kifi ce da ke? Kina tunanin Dr Mu'az haka zai zauna daram da hankalinsa alhalin ya kwashe shekaru masu yawa yana rayuwa da matattu? To wallahi mahaukaci zai zama shi yasa na ce sai ya saki Mama,ko so kike ya dinga dukanta?” ban ƙara ce masa komai ba.

Nan muka zauna har dare don sai gobe da asubah motarmu za ta tashi tuni kuma mun sayi ticket ɗinmu.Kafin motarmu ta tashi mutanen da Basheer ya tsokana Allah kawai ya san iyakar su ,daga waɗanda yake ɗagewa hijabi ko zane sai waɗanda yake cilla abin da suka sayo sama haka mutum zai ta gudu don kamo abinsa shi kuma yana gefe yana dariya.

A cikin mota kujera mai zaman mutum uku muka ɗauka,ni kusan window, Mama a tsakiya shi kuma Basheer daga farko. Sosai balaguron ya bada citta musamman yadda Basheer ke nishaɗantar da mu yana saka Mama dariya,kwana biyu muka yi a hanya kafin mu iso gida .Kayan jikinmu ashe sun rige mu zuwa hatta na Mama sai da muka taras,na rage murya na cewa Basheer “ wannan dai aikin aljanunka ne” ya tuntsire da dariya ya ce “ aljanunmu dai”

Ammy Habibah ta ce “ za ku zo ku ci abinci ko kuwa shirmen za ku yi?” da sauri muka ƙarasa muka zauna ta zuba mana shinkafa tare da miyar kifi, Basheer ya soma ci ni kuwa na kasa sai kifin nake kallo.

“Mine ne kuma?” Ammy Habibah ta tambaya ,sarƙar wuyana na nuna mata mai hoton kifi.Ta saki murmushi ta ce “ ai kuwa akwai tuwon tuƙe da na yi Safeenatu bari na zubo miki ” haka ta zuba min tuwo da miyar kuɓewa ɗanya na ci na ƙoshi.

Na miƙe zan shiga ɗaki na ga yanar gizo-gizo ta ko ina,na yi tsaye ina cewa “ Ammy tun yaushe gidan nan ya koma haka?”

Daga can ta ce “ ya ya koma? Ni ma yau fa na zo tun jiya na tafi can ƙauye wurin Kaka lefen Samira aka kawo”

“Da matsala fa! Ina Daddy yake?” na furta da ƙarfi ina juyowa muka haɗa ido da Ammy wacce fuskarta ta bayyana da tsoro.Basheer ya miƙe tsaye ya tako izuwa inda nake ya dubi yanar gizo-gizon sannan ya ce “ wannan faɗana ne ba naku ba,Goggo Hajara ta ziyarci gidan nan a karo na biyu kuma ta ƙara damƙe ruhin Daddy tana can cikin jeji a tunaninta mafaka ce ta samu ba tare da sanin mutuwarta ce ta kaita har daulata ba” .....

```MRS SADAUKI✍```

BONUS

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK2

23

Assalamu alaikum,mata da yan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .
```

“SEERAT samo min ruwa a kwano ki biyo da cokali” cewar BASHEER,ban tambaye shi mi zai yi da su na je na kawo masa ya karɓa yana cewa “ saura madubi” ni da Ammy Habibah muka je muka ciciɓo na ɗakinmu.Shi ya nuna mana daidai inda za mu tsaya da kuma yadda za yi,madubin ya haska yanar gizo-gizo ta fito ɓaro-ɓaro a ciki.Basheer ya tofa yawunsa a kwanon ruwan kafin ya ɗebo ɗaya da cokalin ya watsawa yanar gizo-gizon a nan take Goggo Hajara ta bayyana cikin madubin da muke riƙe da shi mu biyu.

Hankalinta a tashe take kallonmu tana son yin magana amma ta kasa,a hankali BASHEER ya soma rikiɗa yana zama tamkar mai siffa biyu kafin ya matso ya shiga madubin shuuut ya wuce kamar wanda ya shiga ɗaki tsabar firgici ya saka na saki madubin tuni kuma ya yi wa Goggo Habibah girman da ba za ta iya riƙe shi ita ɗaya ba sai ya suɓuce mata ya faɗi ƙasa tare da tarwatsewa. Hakan yayi daidai da shigowar Daddy dafe da saitin zuciya ya zube kan kujera yana wani haƙi kamar mai cutar huka,muka kalli juna ni da Ammy.

“Mine ne na ji ya fashe?” Mama ta tambaya wacce fitowarta kenan,da sauri ta nufi Daddy tana kiran sunansa.Mu ma muka je muna jijiga shi saboda idonsa da suka fara kafewa,muna cikin wannan tashin hankalin ne madubin da ya tarwatse a ƙasa ya soma yin motsi ji kake “ kacauuu! Kacauuu” duk suna motsa kansu tamkar ana yaƙi.

“SEERAT ki yi amfani da powerki ki haɗa madubin nan” na ji muryar BASHEER ta fito a cikin tattakar madubi.Jikina na rawa na soma juya hannuna na hagu ,a hankali suka soma haɗewa har ana jin ƙarar gamewar tsaf madubin ya koma daidai tamkar bai taɓa fashewa ba.Na yi baya kamar zan faɗi saboda Basheer da ya cillo Goggo Hajara daga cikin madubin,ya haye kan ruwan cikinta ya shaƙe mata wuya idonta suka fito luhu-luhu.“Tun ina jariri kika yi ƙoƙarin kashe ni amma ba ki ci nasara ba,to yau ni nan zan aika ki lahira kafin nan....” sai kuma ya ɗago ya dube ni,da sauri na ƙaraso na ɗora hannuna kan goshinta ta saki razananen ihu har sai da ƙwan lantarki ya tarwatse.Ta bakin Goggo Hajara wani abu ya soma fita yana dosar hancin Daddy,kamar tsawon minti biyu kafin Daddy yayi atishawa tare da kelaya amai.

Basheer ya fizgo sarƙar wuyana ya ɗora wa Goggo Habibah,kifin ya kuwa haɗiye ta.Yayi baya a wahalce ya zauna yayin da ni kuma na ɗauki sarƙata na mayar.

“Alhamdullah! Burina ya cika,sai ki je can ki ƙarasa rayuwarki a ɓoyayyar duniya” cewar Ammy Habibah tana zuwa ta rungume ni da BASHEER.Kafin kuma mu je mu yi wa Daddy sannu,daga nan muka gyara gidanmu yayi fesss ƙyallin rahama ya shigo a yanzu babu wata fargaba duk maƙiyanmu mun kawar da su.

#GIDAN SAKEENATU

A sannu a hankali ta soma koyawa kanta rayuwa a tare da Agali,kulawa ta musamman yake bata sannan ya buɗe mata wata yar ƙaramar asibiti inda take kula da majiyanta.Ɓangare guda sai shirye-shiryen auren Ma'idah ake da mijin da ita kanta ba ta san shi ba,ko kaɗan ba za ta ce tana farin ciki da auren ba haka ma ba ta baƙin ciki.Abu guda ta sani za ta auri cousin ɗinta ne,yadda kuma Daddynta ke kula da ita yana yi mata duk abin da take so kawai sai ta yi amanna ba zai taɓa cutar da ita ba.A haka har aka yi bikin auren,an yi mata kitso da lalle tuni kuma an gama gyaran takardunta.

Idonta tab da hawaye take kallon mahaifiyarta wacce a kullum suna tare duk tsanani duk wuya sai dai ga shi yau za su rabu.Sakeenatu ta shafi gefen kumatunta ta ce “za mu dinga yin waya ai,sannan Daddynki zai dinga kai miki ziyara akai-akai.” Ma'idah ta faɗa jikinta ta fashe da kuka ta ce “zan yi kewar ki Mama” ita ma ta rungume ta,tsawon lokaci suna a haka kafin Agali ya ja hannun Ma'idar yayi mata

rakiya har cikin jirgi,da kansa ya ɗaura mata belt yayi kissing nata a goshi tare da yi mata sallama.

Tun da jirgin ya lula da su sama ta soma tunani iri-iri ,a haka bacci ya ɗauke ta.Sanarwar jirgi zai sauka ne ya tashe ta,a sannu duk mutane suka soma fita ita ma ta bi ayari tana saɓe da jakarta a kafaɗa sai waige-waige take can ta hango wani farin mutum riƙe da wata balon ɗin leda an rubuta sunanta.Da sauri ta ƙarasa tana ce masa “barka” kai ya jinjina mata tare da yin gaba ta kuwa take masa baya,gidan gaba ya buɗe mata ta shiga ta zauna sannan ya je ya nemo kayanta ya saka a Booth .Da ya dawo kawai tuƙi ya fara ba tare da ya ce mata komai ba ,a haka har suka isa wani tanfatsetsen gida wanda tsabar haɗuwarsa sai da Ma'idah ta saki baki tana kallon ko ina. Har ciki yayi mata iso,ɗakin da ya buɗe ya jera mata trollynta sai ta fahimci nan ne masaukin da ya bata kenan.Toilet ta shiga ta yi wanka,ko da ta fito ta tarar ya kawo mata abinci sai da ta ci ta ƙoshi sannan ta shirya cikin doguwar riga marar nauyi ta yi sallolin da suka hau kanta.Bed ta haye don hutawa kawai sai ta ga an turo ƙofa,shi dai ne ya shigo idonsa ƙyam a kanta.Ita ma sai ta zuba masa na mujiyar tana ƙare masa kallo,fari ne sosai ƙal za ta iya cewa ma Albino ne yana da kyau kamarsu ɗaya da mahaifinsa.Bai da ƙiba sai uban tsayi,yana da gemu da kuma saje haka ma jikinsa irin mai gashi ne sosai.

Ya tako zuwa bed ɗin ya zauna,zanen da ta rufe jikinta da shi ya yaye tare da nufo ta ya yi mata rumfa.Tsoro ne ya kama Ma'idah,ita da ta yi tunanin ba zai kula ta ba sai sun saba sai ta ga abun mamaki.Sumba ya soma aika mata ta ko ina ,jikinta da nasa duk rawa suke abu guda ta lura da shi shine ya cimma burinsa na tarayya da ita .Kuka ta soma ta ce “ don Allah ka bari ban so na gaji” kanzil bai ce mata ba ya raba ta da kayan jikinta shi ma ya cire nasa,tsoronta ne ya ɗan ragu ganin ƙanƙantar halittarsa sai dai yɑn magana na ce ba a rena allura ita ma ƙarfe ce .Razananen ihu ta ƙurma ta soma kuka kenan ya mirgina gefe yayi baya,ta yi tunanin ko tausayinta ne ya ji ya bar ta sai da aka ɗauki sama da minti talatin kuma ya sake lalubo ta wannan karon ma ko minti biyu ba a yi ba ya samu gamsuwa ya fice ya bar ta nan.Sai da ta gaji da kuka sannan ta miƙe ta shiga toilet ta yi ,ta cika baho da ruwan ɗumi ta shige.....

ZAWARCI

BOOK 3

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

1_2

Tamkar wata sabuwar halitta haka nake jin kaina,mutanen da ke bi suna wuce wa nake kallo ina duban abubuwan ban al'ajabin da ke tattare da dayawan su.Wata mace na gani tana tafe yayin da wata baƙar inuwa ke take mata baya,wanda kuma na yi imanin cewa ita kanta ba ta san da akwai wani abun cutarwar da ke bibiyar rayuwarta ba.Na shagala sosai da kallonta na ji muryar wani ɗan yaro na cewa “ a'a ban ka yi tafiyar ka ,ni ban son kuɗin aljani” yaron duka-duka ba zai wuce shekara uku zuwa huɗu ba,inda yake kallo na duba sai na ga irin inuwar nan dai ce ta matar nan.Daga nan ne na fahimci wato aljani ya fitowa yaron ne ɓaro-ɓaro suna ganin juna alhanin ni kuma inuwarsa ko kuma nace sawunsa kawai zan iya gani a matsayina na babba.

“ SEERAT wai mene ne duk wannan kin tsaya cak wuri guda,dubi yadda mutane ke kallonmu” na ji muryar Yaya Khaleed ta daki kunnena,ni tuni na manta ma a tare muke.Na ja ajiyar zuciya kafin na je na hau babur,sai da muka ɗan yi nisa sannan na ce “ ɗazu lokacin da na faɗi kamar na ji muryar Basheer”

“Eh shi ne,yayi tafiyarsa ne tun da ya ga kin miƙe” Yaya Khaleed ya bani amsa.Ban ƙara cewa komai ba na soma tunanin sabon al'amarin da ya riske ni yau,kwatsam kamar an ce in duba na kai kallona a madubin da ke manne ga babur.Ban san lokacin da na fasa ihu ba tare da ƙanƙame shi ina kyarma,saura ƙiris ya juye da mu amma Allah ya gyara Yaya Khaleed ya ci nasarar cin burki sai dai tuni madubin babur ɗin ya tarwatse da kansa.

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un ! Wai SEERAT don Allah meke damun ki ne?”

“Yaya tsoro nake ji” na furta kamar wata doluwa.

“Yaushe SEERAT ta soma jin tsoro? Ke ɗin ce ke jin tsoro? ”

“To ai ni ma mutum ce” na basa amsa .

“Mai neman abin da ya fi ƙarfinta ba,ina ce nan har rijiyar Mayu kika taɓa zuwa tsakar dare” Yaya Khaleed ya waigo yana kallona,ƙirjina ya buga saboda muninsa da na hango,da kuma wani abu mai kamar ƙiyayya.

“Hum!” yayi tare da ci gaba da tuƙa mu,muna daf da shiga makaranta ya ce “ mine ne kika gani cikin madubin?”

Ban basa amsa ba har ya tsaya na sauka daga babur,tsintsiyar hannuna ya riƙe ya ce “ ina sauraren ki”

“Ni ban ga komai ba” na faɗa ina jin tsoronsa ganin ya canza fuska alamun halinsa na rashin mutumci ya hau kansa.

“Ke kar ki raina min hankali faɗa min abin da kika gani” ya faɗa cikin tsawa.

“Allah Yaya Khaleed ban ga komai ba ka yarda da ni ” na faɗa don haka kawai nake son ɓoye masa.

“Shi kuma madubin uwar mece ta saka shi tarwatsewa? SEERAT ki sani duk duniyar nan babu wanda zai fi ni sanin ki ciki da baya,bari ganin kanku haɗe ke da Ammy to naku wasa ne ni na fi kusa da ke fiye da ita.Duk wani abu da zai faru da ke ina ji a jikina,kai kuma da kake bayanta in ma a tunaninka za ka iya raba hanta da jini to ka makaro aurena da SEERAT mutu ka raba ne takalmin kaza ” yana gama faɗar haka ya wani ɗingiza ni na yi baya shi kuma ya buga babu ya tafi ya bar ni sake da baki.

Har waigawa na yi a bayana don ganin ko akwai da wanda Yaya Khaleed ke magana amma wayam,ciki na shige ina tafe ina kallon ƙasa har na isa aji.

Yau haka-haka nake ji na,duk lissafina ya dame.Ƙawata Maryam ta zo ta zauna kusa da ni ta ce “ yɁan mata” na ɗago na dube ta sai kuma na ɗan zabura ina kallon inuwar da ta yi tsaye ƙiƙam kusa da ita.

“Na ji daɗi sosai da muka haɗu yau wajen sati ɗaya kenan ba mu ga juna ba,ga shi ke kuma ba ki da waya ballantana na kira ki.Shikenan kuma yanzu da mun yi awa ɗaya sai mu rabu zuwa asibiti,na yi kewarki sosai” Maryam ta faɗa ,wacce ta kasance abokiyar karatuna ce kullum muna tare yanzu ne da muka tafi aikin gwaji a asibitoci aka raba mu.

“Wai mi kike kallo?” ta tambaye ni tana mai waigawa,na girgiza kai na ce “ babu komai fa,ya aikin ?”

“Alhamdullah ! Akwai gajiya kam,jiya sai dab da magrib na koma gida Habibi na ta masifa kamar zai cinye ni ”

Na taɓe baki don in da sabo na saba da ƙorafin Maryam akan mijinta,sam bai son karatun da take.Muna nan zaune a sannu duk ɗalibai suka cika ajin,nan na ƙara fahimtar wani abu sannan na samo amsar tambayata ‘ wannan inuwar mece ce?’ ba komai ba ne face jinnu waɗanda ba su samu damar shiga gangar jikin mutum ba sai dai dama kaɗan suke jira suke shige.

Malamin da zai koyar da mu dabarun kula da majiyancin da ke ɗauke da wata cuta wacce mutane ke ƙama,amma kasantuwarmu malaman jinya bai kamata mu ma mu nuna ƙyama ba sai dai tausayi da kuma taka tsantsan.Har ya gama jawabinsa ban fahimci komai ba saboda duniyar tunani da na lula,bayan mun fito ne nake cewa Maryam “ wai don Allah mine ne ke yawan gama ku faɗa da Habibinki?”

“Karatuna mana,sannan na faɗa miki ban ɓoye miki ba ni sam-sam banda wani desir shi kuma hakan na ɓata masa rai” Maryam ta bani amsa,na ce “ yanzu dai sai an in mun sake haɗuwa zan yi miki bayanin yadda za ki kawo ƙarshen matsalarki ” ta wani rungume ni tana godiya kafin mu rabu kowa ya kama gabansa.

Asibitin da aka kai ni na tafi,ɗakin da ake ajiye kaya na shiga na ajiye jakata na kuma ɗora farar rigar likitoci sannan na nufi sashen maras lafiya.Da ni da sauran ɗaliban da suka zo koyo duk muka dinga duba maras lafiya,in kuma abin ya fi ƙarfinmu sai manyanmu su duba.

“ To yau za mu shiga ɓangaren masu fama da ciwon asuma wato huka,da farko za ku yi musu tambayoyin abin da suke ji kafin ku fara basu magani” cewar likitar da ke koyar da mu,duk muka jinjina kai kafin mu take mata baya.Da na shiga ɗakin sai da na ji tsikar jikina ta yi wani tsammm,cak na yi tsaye ina ƙarewa majinyatan kallo,dayawa daga cikinsu babu wata cutar asuma da suke fama da ita face jinnu ne ke haifar musu da ɗaukewar numfashi tare da danne musu ƙirji.A haka dai muka duduba su muka fito,yanzu damuwata guda ta ya zan taimaki mutane ban sani ba.

Sai da muka yi aiki tuƙuru kafin mu tsaya mu ci abinci,yau ɗin ma ƙarfe biyu muka tashi.Na fito kenan ina neman abin hawa sai na tsinkayi Yaya Khaleed,fuskar nan tasa kicin-kicin tamkar bai taɓa dariya.Mugun tsoronsa da shakkarsa ce na ji suna yi wa zuciyata ɗaurin goro,a sanyayye na ƙarasa kusa da shi sallama ɗauke da bakina.Ya amsa ciki-ciki,sai kawai na soma wasa da yatsun hannuna.

“Sai na ce ki hau sannan za ki hawa ko?” ya tambaye ni yana min wani kallon mai saman ruwa,da sauri na je zan hawa jiki na yi min rawa amma ya daka wata uwar tsawar da ta kusa sa na faɗi don tsoro.

“Kar ka saki ka hau min babur ni sa'an ka ne?” Yaya Khaleed ya faɗa yana hararena,wani shuuu ! Na ji kamar fitar iska ya gusa daga jikina har sai da na ja ajiyar zuciya.

Babur ɗin na hau ,ya daidaita sabbin madubin babur ɗin da ya canza yana kallona ta ciki.Kamar wacce aka shuka haka ni ma na tsayar da ƙwayar idona cikin nasa muna kallon juna,wani irin azababen so nake hangowa cikin idon Yaya Khaleed da zurfafiyar ƙauna.

“Hummm!” na ja wani dogon numfashi ba tare da na shirya ba ina mai kai dukkan hannuwana na zagaye cikinsa,a hankali na kwanta a gadon bayansa ina mai lumshe ido.

Na saki wani guntun murmushi jin Yaya Khaleed ma ya sauke ajiyar zuciya,a hankali ya soma tuƙa mu kamar bai son gudu.Mun yi nisa sosai kafin na tsinci muryarsa “ ina son ki SEERAT ”

“SEERAT na son Yayanta” na basa amsa ina mai fitar da zallar yarintata.Wani murmushin na kuma saki lokacin da na ji hannunsa kan nawa da ke manne ga cikinsa,“ zan kula da ke,zan kuma nuna miki ƙauna sannan duk rintsi ba zan bari a raba mu ba”

“Na gode Yayana” na furta ina jin wata irin nutsuwa,a hanya ya tsaya ya saya min kayan marmari muna isa gida ya miƙa min ledar.Wanka na soma yi kafin na wanke su na yayanka,a tare duka yan gidanmu muka ci Yaya Khaleed sai kallona yake kamar yadda na lura kuma yau hakan na yi wa Ammy Habibah daƈi .

Bayan nan Mama ta miƙo min jiƙe-jiƙen da ta yi na kuwa shanye su tasss,bayan sallar la'asar kuwa wata dunƙulalar kaza ta bani na ci na ƙoshi hatta romon sai da na sha.

Da dare kuwa ina zaune a ƈaki ina duba littattafaina Ammy Habibah ta shigo ta zauna gefena.Na rufe littafin ina mai kallon ta,na saki murmushi na ce “ Ammy yau kamar kina cikin damuwa”

“A'a ko ƈaya,kawai ina tunanin wani sati mai zuwa kina can Yamai a ƈakinki” ta faƈa tana wani murmushi wanda na fahimci ƙirƙirar shi ne ta yi amma ba daga ƙasan zuciyarta ya fito ba.

Na ɗan rufe fuskata da tafin hannu ina yɼar dariya,ta ce “ ja'ira! Buɗe fuskar faɗa min abubuwan da suka faru da ke a yau”

‘ Dama na san akwai abin da ya kawo ki ’ na faɗa a zuci kafin na ɗan yamutsa fuska na ce “ babu komai kawai aiki ne kamar kullum”

Hannuna ta kamo ta ce “ kina ji na SEERAT kar ki ɓoye min komai,ki sanar da ni kar ki ji tsoro ko shakka .Ammynki na tare da ke a kowane irin yanayi,ɗazu yayanki ya sanar da ni kin ga wani abu har madubi ya fashe , please ina son ki siffanta min abin da kika gani ɗin”

Jikina ne ya ɗan soma rawa kafin na soma bata labari,“ wasu halittu ne biyu ɗaya baƙi ƙirin,ɗayan kuma fari tasss ”

“Wane ya fi girma daga cikinsu?” ta yi saurin jefo min tambayar kamar da alamu ta san da zaman halittun.

“Baƙin ya fi girma” na bata amsa,sai ta ɓata rai tana cewa “ da saura dai har yanzu”

“Mi?” na tambaya.

“Babu komai yi karatunki” tana gama faɗa ta fice,na bi bayanta da kallo kawai ina jin a zuciyata tabbas akwai abin da take ɓoye mini.

#KʼASAR KANADA

A nutse Ma'idah ke shirya wa cikin riga da wando jeans,bayan ta gama ta ɗora After dress baƙa .Tana tsaka da naɗa kallabin a kanta Heesham ya shigo yana yi mata kallon nan da ya saba yi mata tun lokacin da aka kawo ta.Wani takaici ne ya rufe ta ganin ya nufo ta,don tuni ta san sauran ba ta da ikon yin kwalliya ta yi tsaf sai ya neme ta kuma kayan takaici ba gamsar da ita zai yi ba.

Ta rumtse ido hawaye na silalo mata sa'ilin da ta ji yana cire duk uban kayan da ta yi ado da su.Heesham bai magana,ya zama kurma ne na ƙarfi da ya ji ko kuma ma za a iya cewa ya mayar da kansa kurma ta sanadin shaye-shayen kayan maye.Wannan ya saka babu wata fahimtar juna tsakaninsa da matarsa Ma'idah,ba su yin hira kawai dai yana sauke buƙatarsa ne a kanta.

Ko kaɗan ba ta ƙi basa haƙinsa ba,sai dai shi yayi kiɗinsa da rawarsa.Ko cikakken minti uku ba a yi ba ya koma gefe yana mayar da numfashi,ita kuma cike da takaici ta tashi ta shiga Toilet ta tsarkake jikinta.A gaggauce wannan karon ta shirya cikin doguwar riga fara sol mai mayafi,jiƙaƙen gashin kanta ta gyara kafin ta ɗauki jakar makarantarta ta fice .

Direbanta na ganinta ya taso da sauri ya buɗe mata mota,har aka kai ta makarantar tana tunanin mafita sai dai ta rasa wa za ta tunkara da maganar.Sosai take jin kunyar Mamarta Sakeenatu, dama-dama anty Nafisa kuma ba lallai in ta shaida mata za ta bata shawarar rabuwa da Heesham ba duba da ɗan uwanta ne na ji.Sannan rabuwar aurensu tamkar saka igiyar auren mahaifiyarta ne a haɗari,don ta lura an aura mata Heesham ne don ya zame mata ƙarfen ƙafa.Har suka gama duk darasinsu na yau takaicin mijinta bai gushe mata ba,ko da ta fito tuni direba ya zo ɗaukarta.Kalle-kalle ta soma yi tana yaba kyawun garin,har za ta ɗauke idonta daga window sai kuma suka sauka kan wani allon sanarwar kan hanya.“Ɗan dakata!” ta cewa direba ya kuwa taka burki ta ce “ yi baya kaɗan ” sai yayi yadda ta ce ɗin rubutun da ke kan allon sanarwar ta karanta,kafin ta ciro wayarta a jaka ta ɗauki wani abu.“ Mu tafi” ta faɗa tana sakin murmushi,direba na sauke ta direct ciki ta shige a falo ta tarar da shi yana aiki da system.Ta taɓe baki ta ce “ kamar da gaske” ya ɗago ya dube ta kawai,ita kuma ta ɗauke kai kafin ta shige bedroom ɗinta.Wanka ta soma sannan ta zo ta haye gado,Mamarta ta kira suka gaisa kafin ta ɗauko abin nan da ta gani kan allon sanarwa ta shiga facebook.Searching/recherche ta yi babu jimawa kuwa sai ga group ɗin ya bayyana babu wani tunani ta shiga,a

hankali ta soma bibiyar duk abubuwan da aka taɓa posting da kuma comments ɗin mutane.Posting na ƙarshe ne ya ɗauki hankalinta sai ta ga ma tamkar tana son shiga,zance ne akan mutum ya tura hotonsa za a faɗa masa duk matsalolin da ke jikinsa da kuma maganinsu.Kamar wacce aka tsikara haka ta miƙe ta je ta ɗauko hoton Heesham ta tura a group ɗin da yau ne kawai ta shige shi ba ta san komai a kansa ba.Bayan Ma'idah akwai waɗanda suka turo nasu hotunan,kamar ƙyaftawar ido haka kuma kowa ya samu amsashoshin duban da aka yi masa.Ma'idah ta wani yi zumbur ta tashi zaune tana waro ido ganin an bata tarihin Heesham tun daga ranar da larurar ta same shi har aurensu da shi,da kuma matsalar da yake fuskanta.Gabanta na faɗuwa ta danna wani jan layi inda aka rubuta in mutum na son kawo ƙarshen ɗamuwarsa ya danna nan,ta kuwa danna babu jimawa aka aiko mata da amsar da ta girgiza tunaninta. Dukkannin illahirin jikinta rawa yake,“ wannan ai tsafi ne ” ta furta tare da son yi left daga group ɗin sai dai abu ya cuttura don da zarar ta goge sai ta ƙara ganinta ciki,da ta matsa kuwa sai ga kira ya shigo wayar mai ɗauke da sunan group ɗin Ruhaniya.....

ZAWARCI

BOOK 3

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

3_4

Wayar hannunta ce ta suɓuce mata jin wata muryar marar daƈin amo na ce mata “ Barka da shigowa duniyar Ruhaniya,gidan wanke zuciya da biyan buƙata.Hajiya Ma'idah haƙiƙa kin yi jajirtacen aiki na ceta mijinki da kika,zai samu lafiyar dukkan matsalolinsa mun taya ki murna aikinki yayi kyau mun cika miki muradinkk saura ke ma ki ji namu,ohhhh sai mun sake zuwar miki a karo na biyu” tsit muryar ta tsaya.

Ita kuwa Ma'idah ƙuri ta yi wa wayar tana kallo cike da tsoro,tana cikin wannan yanayin sai ga Heesham ya shigo da sallama ƈauke da bakinsa ,fuskarsa kuwa cike da annuri.

“Maaa...'idaaah!” ya kira sunanta kamar mai koyon magana kafin ya ƙaraso ya rungume ta,“ kin ga na soma magana ,bakina ya buƈe” ya sake furta cike da tsantsar farin ciki.

“Mine ne? Ya na ga ba ki murna? Kuka kuma? Kukan mene ne?” ya furta yana ƈora ta kan cinyarsa ya soma share mata hawayen.Cike da tattali ya soma rarrashinta tare da furta mata kalmar so,“ tun ranar da na fara ganin ki na soma son ki ,na san ke ma kina sona ko?” ba ta ce masa komai ba ta zare jikinta daga cikin nasa ta shige toilet.Ƙarƙashin shower ta shige ta buƈe shi har ƙarshe ruwan suka soma jiƙata,kuka take sosai tana da na sani marar amfani a halin yanzu ta fahimci rayuwarta na cikin haƈari.

Ta yi saurin lumshe ido jin Heesham a bayanta ya rungume ,tamkar a Film ƈin India haka ya soma yi mata wanka in romantic ya wani juyo da ita suna facing juna ya kafe ta da idonsa kuma ya ƙi bata damar janye su.Sai da ta ji laɓansa kan nata ne sannan ta ƙara lumshe idon a karo na biyu,kissing ƈin da yake yi mata ya sha banban da na sauran lokuta ya na musamman ne har ita sai da ta ji a

jikinta.Ma'idah ba ta ida ruɗewa ba sai da ya raba su da kayan jikinsu,ko kaɗan bai kashe pampo ɗin ba ya dai rage gudun ruwan a cikin kunnenta take jin yana karanto addu'a.Ta yi saurin ƙanƙame shi cike da shauƙi,yau ta ji abin da ko a duniyar mafarki ba ta taɓa jinsa ba.Sai da Heesham ya shayar da su duniyar zuma sannan yayi musu wanka ya ɗaura musu towel ya kama hannunta don su fita amma ta yi tsaye tana kallonsa,ya sakar mata murmushi tare da sa dukkan hannuwansa ya saɓe ta zuwa waje.

Kan bed ya kwantar da ita,yayi mata rumfa da ƙirjinsa suna kallon juna.“ Mine ne ke damun ki?” ya tambaye ta,kai kawai ta girgiza masa .Ya ce “ kar ki yi min ƙarya Ma'idah sanar da ni ko ma mene ne”

“Babu komai” ta furta dakyar tana mai yunƙurawa za ta tashi amma ya mayar da ita.“ Sai kin faɗa min gaskiya”

“Allah babu komai” Ma'idah ta furta.

Ya girgiza mata kai ya ce “ wallahi ƙarya kike akwai abin da ke damunki,kawai ki sanar da ni zai fi miki ”

“Na ce maka babu ko ƙarya kake so na yi?” ta furta a ɗan hassale tare da tashi ta nufin dressing mirror.Lotion ta buɗe ta soma shafe jikinta da shi ta ƙi yarda su haɗa ido ita da Heesham ko ta cikin madubin,ta ɗauki turare ta fesa sannan ta gusa zuwa drower ta zaɓi kaya ta saka duk a gabansa.Tana gamawa ta fice falo,tv ta kunna ta koma gefe ta soma kallo duk don mugun tunanin Ruhaniya ya fita kwanyarta amma kayan takaici tana tsaka da kallo aka soma wani shiri mai laƙabi da MAFIYA (Sunan littafina na gaba kenan in sha Allah) alamomin yadda za a gane mutum ɗan mafiya da kuma dalilan da ke sa mutane su shiga,da farko ta soma jin haushin shirin amma daga ƙarshe sai ta buge da kallo har da tashi ta ɗauko madara a cikin frigine.Tana kallo tana auna dukkan abubuwan da aka faɗa ,“ kallo kike?” Heesham ya tambaye ta kai ta gyaɗa masa.Ya zauna gefenta tare da karɓar robar madarar ya soma sha suna kallon juna,“ ka kira su uncle ne?” ta samu kanta da tambayarsa.

“A'a sai na samu kanki tukuna,maimakon ki taya ni murna sama da shekara biyar ina cikin wannan halin amma sai kika tsiro da wani game fuska”

Ma'idah ta ja dogon numfashi kafin ta ce “ ka yi haƙuri,akwai wani ɗan abu ne da ke damuna”

“Mene ne shi?”

“Kai ne!” ta basa amsa tana mai sakin murmushi mai sauti haɗi da jan haɓarsa, Heesham ya saki murmushi mai sauti ya ce “ Allah sa ba laifi na yi ba? Kin san ban so ranki ya ɓace ki yi fushi da ni”

Ma'idah ta cusa kanta a ƙirjinsa tare da lafewa ta yi shiru, Heesham ya aje robar madarar kan table center sannan ya tallabo ta.“ Faɗa min na ji mene ne?” yayi mata tambayar cike da kulawa,ta girgiza kai ta ce “ tsoro nake ji”

“Tsoron me kuma alhalin gani tare da ke?” shiru ta kuma yi masa,ya ƙara jawo ta jikinsa ya ce “ ko mu fita shan ice cream hakan yayi miki?” kai ta jinjina masa,a tare suka miƙe suka je suka canza kaya.Wannan karon da kansa ya tuƙa su zuwa wani haɗaɗen wurin shaƙatawa,kula ta musamman Heesham yake bai wa Ma'idah wacce ta saka ta jin zuciyarta fayau babu ƙunci .Sai da ya nuna mata gari sosai sannan yayi musu shopping kafin su dawo gida , tamkar yadda sabbin masoya ke ɗaukin juna to su ma hakan ce ta kasance da su.Wanka suka yi tare,bayan sun fito shi ya wuce masjid ita kuma ta yi sallah a gida.Suna idawa ya dawo,gefenta ya zauna tare da soma cin fruits ɗin da ta yanka.Ta ɗan saki murmushi ta ce “ Heesham bani labarinka mana”

Ya dube ta kafin ya ce “ wane iri kenan?”

“Irin yɗan matan da ka yi soyayya da su”

“Gaskiya ba su da wani yawa,biyu ne zuwa uku kuma duk cikinsu ɗaya ce ta wahalar da ni ta jefa ni cikin ƙuncin da kika same ni ciki na rashin magana” sai kuma yayi shiru yana jin ciwo,Ma'idah ta ce “ tana ina yanzu? Ko ta yi aure ne ta bar ka?”

“Dama matar auren ce ! Yaudara ta kawai ta yi sai da ta bari na kamu da tsananin sonta ta sanar da ni a ƙuraren lokaci don tana tsaka da shaida min mijin nata ya zo ya fincike ta tun daga kuma wannan ranar ko a hanya ban sake ganinta ba”

Wani haushi ya rufe Ma'idah don a yadda take kallon fuskar Heesham yanayinsa ya nuna har yanzu yana sonta.Amma ta daure ta ce “ amma kana da hotonta har yanzu?” kai ya jinjina mata kafin ya miƙe ya shiga ɗakinsa babu jimawa kuwa ya dawo hannunsa riƙe da hoto.

Ma'idah ta karɓa tana kallon kyakkyawar baturiya,a cikin kwanyarta take jin ana yi mata bayanin budurwar jikin hoton.“ Wannan Surabiyya ce yar sarkin aljanun ruwa ita ɗin ta kasance macen kifi rabinta ne kawai na mutum,kamar yadda tarihi ya nuna Siren suna shigowa duniyar bil'adama har su ja ra'ayin jinsin to hakan ne ya faru da Heesham kuma tana nan kusa da shi saura ƙiris ta zo gare shi ta.....”

“Ya dai?” Heesham ya faɗa yana dafa kafaɗar Ma'idah,ta wani zabura a tsorace tana mai sakin hoton tare da dafe kanta ga dukkan hannuwanta ta fasa ihu saboda har yanzu muryar da ke yi mata magana cikin kwanya ba ta daina ba.

Hankalin Heesham yayi mugun tashi yana shirin taɓa Ma'idah sai ya ga hoton da ke yashe ga ƙasa ya miƙe tsaye tare da ƙara girma.Bai ida firgita ba sai da ya ga budurwar cikin hoton ta fito tana taka tile ɗin ɗakin,muryarsa na rawa ya ce “ Surabiyya?” ambaton sunanta ya saka Ma'idah buɗe idonta da ta rumtse gam nan ta yi tozali da farar mace mai gashi baƙi ƙirin mai kuma tsayi.

“Sai yau kawai ka tuna da ni ? Na daɗe ina jiran wannan lokacin sama da shekara uku nake shawagi a duniyarku amma ban gan ka ba” ta yi furicin tare da kama hannun Heesham ta miƙar da shi tsaye,Ma'idah ma tashi ta yi tsaye tana kallon ikon Allah.Ba ta firgita ba sai da Surabiyya ta juyo ta ga zallar kyawunta,ta rausayar da kai ta ce “ na gode sosai!” sai kuma ta ja hannun Heesham ta bi ta window da shi suka wuce shuuuu.

Zuwa wannan lokacin kwanyar Ma'idah kasa jura ta yi kawai sai ta zube a sume.Sai a washegari gari ne direbanta ya shigo ya same ta a yashe,shine ya kaita asibiti kwananta biyu kafin a samu ta daina suratai.Lambar Sakeenatu ta bayar aka kira gidansu aka sanar,a washegari kuwa Daddynta ya isa ƙasar KANADA.

Ma'idah na ganinsa ta je ta faɗa jikinsa tare da soma basa labarin abin da ya faru,amma sai ta lura tamkar ma bai yarda da ita ba don Agali likita ya soma tambaya “ an duba ta sosai kuwa? Mike damunta? Ya take magana irin haka?”

Dr ya ce “ abin da na lura jinnu ne a tare da ita,don mun yi scanning ɗin ƙwaƙwalwarta komai normal”

“Daddy lafiyata lau, wallahi gaskiya nake faɗa maka Heesham ya bi aljanar ruwa sun tafi sun bar ni ” Ma'idah ta faɗa cikin kuka.Wata asibitin Agali ya canza mata amma nan ɗin ma amsa guda ce lafiyarta lau,gefe guda kuma sai kiran layin Heesham yake amma bai ɗauka kuma direba da mai gadi sun shaida Heesham bai fita ba tun bayan sallar magarib.

Ma'idah kuwa jikinta sai ƙamari yake babu damar allurar bacci ta sake ta,da zarar ta farka sai ta dinga faɗin Heesham na can tare da aljanar ruwa.

Ganin zaman bai yi musu suka tattaro suka dawo gida Nijar inda duk family ke zaman jiransa da cikakken bayani,suna isa tuni kowa ya haɗu .Ma'idah jikin Sakeenatu ta je ta zauna ta rungume ta gam ta fashe da kuka ,a gaban kowa ta yi musu bayanin yadda aka yi amma babu wanda ya yarda da ita sai ma malamin ruƙiya da aka kawo ya soma yi mata karatu nan kuwa aljani ya bayyana ya kuma shaida suna da yawa don sun kai su saba'in a kanta.

Tsawon lokaci kafin a bar karatun , Ma'idah ta zube sai baccin gajiya.Sakeenatu ta rabka uban tagumi tana kallon yarta ɗaya tilo,sai a lokacin ne ƙawarta Safeenatu ta faɗo mata a rai wacce rabon ta da ita tun wancan lokacin.Ta ja ajiyar zuciya tare da ɗauko wayarta ta shiga duba lambobi sai dai aka yi rashin sa'a ba ta ga lambar Safeenatu ba,sai kawai ta kira Nafisa ta shaida mata abin da ke faruwa.

#GIDAN DADDY

Wata irin kulawa ta musamman ake mini,tuni na yi ɓulɓul da ni na yi kyau abina.An yi mini kitso da lalle sai ƙamshi nake bazawa,dangin Mama da na mahaifina duk sun zo.Gobe ake taron walimar,da zarar an yi kuma washegari za mu wuce Yamai ni da mijina kuma Yayana.

Ina kwance na yi lamo kan gado ina sauraren hirar Samira da kuma ƙawata Ubaidah labarin daren farko suke mai cike da ɗumbin tarihi.

Ubaidah ke cewa “ ko tsabar azabar da mutum ya ji a ba zai sa ya manta ba ballantana kuma a ranar kuka cika burinku na zama ɗaya”

Samira ta karɓe da cewa “ ke ni fa don wautata na ɗauka ba a komai sai da na ga mutum kawai ya soma yi min iskanci,kai amma da wuya wannan lamari har tausayin SEERAT nake fa”

Ubaidah ta ɗan yi min dundu a baya ta ce “ munafuka kin yi wani shiru kamar gaske tsoron kike ji”

Na dube ta na ce “ ni fa kaina ke ciwo , wannan kitson da aka yi min da zan samu wacce za ta kwance min shi da na huta da azaba”

“Ai kuwa yayi miki kyau ki bar abinki,ko ba ki so Yaya Khaleed ya shafa?” cewar Ubaidah.

Samira ta ce “ don Allah bar ta in kina lalaɓa ta sai ta aza mana tsiya tace sai ta kwance shi” duk suka shiga dariya sai kuma suka koma hirar yadda banda tsoro.

Basheer yayi sallama ya shigo yana yi min wani kallon mai saman ruwa,na tashi zaune ina mai cewa “ ya dai lafiya?”

Ya haɗe rai ya ce “ mi kuke nufi ke da Yaya Khaleed? Nufinku ku yi aure ku tafi haka nan ba tare da kun sallame ni ba? In na bari ya tafi da ke Allah tsinan! Sai an bani kuɗin da na yanka masa ko kuma a yi min akwati ni ma” yana gama faɗa ya juya zai fita na ce “ don Allah ka yi haƙuri ka ga duk yayi hidimar biki kuɗinsa sun ida...” yadda ya juyo da sauri yasa na yi shiru, BASHEER ya tsira mana masifa yana ɗaga murya har ya jawo hankalin mutane suka shigo.

Dangin mahaifinmu ne fa suka fanshi Yaya Khaleed inda aka shiga haɗa masa kuɗi kamar yadda ya buƙata,ita kuwa Mama har da basa babur ɗina nan kawai na samu ya sake min mara.Babu kunya kuwa ya karɓe kuɗin ya fita yana dariya har da su cewa in muna so za mu iya tafiya tun yau.Ni dai ban kula shi ba na shiga toilet,kayana na cire tare da lumshe ido na sakarwa kaina shower.Ɗigar ruwan farko na soma jin wani abu na sauko min kamar saukar wahayi,ƙasan ruwa ne nake gani tare da abubuwan da ke ciki.Wata masarauta ce mai ɗauke da jinsi biyu,wasu rabi mutum rabi kifi,wasu kuma gangar jikin maciji da ta mutum.Ina shirin buɗe idon na ga giftawar bil'adama a cikin ruwan,da kuma rufe su ɗin sai ban ga komai ba.Na ja ajiyar zuciya tare da kama sarƙar wuyana da ta soma kaɗa kanta tana motsi,towel na jawo na ɗaura tare da kashe pampon.Ina fitowa na shirya cikin kaya marar nauyi,ɗakin babu kowa suna can suna kallon lefena ga waɗanda ba su gansa ba tun farko.

“mi Bil'adama ke yi ƙasan ruwa?” na tambayi kaina sai dai babu mai bani amsa,haka na kwana da tunaninsa.

Washegari kuwa tun safe aka ta hidima wasu sai lokacin suka samu damar zuwa,ciki kuwa har da ɣan makarantarmu.Shagalin biki kawai ake ina son ganin Yaya Khaleed amma ya ƙi shigowa sai da rana ,hotuna aka yi mana da shi sai jifana yake da mayen kallo.

Tsakiyar kaina ne na ji yana min motsi ,tunanin bil'adamar nan ya ƙara dawo min.Sai na yi kasaƙe ina sauraren abin da ke wakana,ban ma san lokacin da yaya Khaleed ya fita ba.Sallamar Mama ce ta katse min tunani,ta kamo hannuna tare da jana muka fita zuwa wani sashen.Muna haɗa ido da Ma'idah duk abubuwan da suka

faru da ita shige min kwanya,“ ƙawata ce Sakeenatu kin tuna ta?” Mama ta tambaye ni,na jinjina kai ina mai ci gaba da kallon Ma'idah sai kuma ɗakin yayi tsit.

“Mi ta ce miki lokacin da za ta tafi da shi?” na jefo mata tambayar, Ma'idah ta dubi mahaifiyarta kafin ta bani amsa.Na saki ɗan murmushi na ce “ki nemi takardar saki a wurin iyayensa ko kuma wurin alƙali don kuwa ya shiga ƙasan ruwa kenan ba zai fito ba”

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un ! Kenan abin da take faɗa gaskiya ne? Na shiga uku ni Sakeena”

“A'a ba ki shiga uku ba,ya cancanci zama a ƙasan ruwan ne shi yasa” na faɗa tare da ficewa,na ji muryar Ma'idah bayana na tsaya cak.Ta iso gare ni,idonta shaɓe-shaɓe da hawaye ta ce “ SEERAT ki taimaka min magana ake yi min cikin kwanya,kuma....kuma kafin abin nan ya faru sai da aka sanar da ni”

“Wa ya sanar da ke?” na jefo mata tambayar,ta bani amsa da “ ni ma ban sani ba” na jawo ta tare da kai bakina saitin kunnenta na ce “ da hannunki kika buɗewa kan ki hanyar shiga duniyar Ruhaniya ba komai ne da aka gani kan media ko kuma allon sanarwa ba ake saurin aiki da shi sai ki kula”

Ina gama faɗa na yi gaba,dab da zan shiga ɗaki na ji kururuwa a can waje da sauri na nufi ƙofar fita wacce za ta sada ni a tsakar gida.Kaina kawai na ɗaga ina kallon tsuntsuwar wacce ke riƙe da soyayen nama ,muna haɗa ido ta buga fukafukinta ta yi sama.....

ZAWARCI

BOOK 3

LoVe aNd HoRrOr StOrY☠

Mallakar: Chamsiya Laouali Rabo

(MRS SADAUKI✍)

Lambar waya: +22795045822

FIRST CLASS WRITER ASSOCIATIONS☀

Home Of Qualities And Trusted Writer's Of The Nation.

Sadaukar wa: Rahama Sabo Usman

_____

Last free page

5_6

A gabana duk illahirin mutanen wurin ke ihu wasu kuma suna son jefa tsuntsuwar amma ina tuni ta yi gaba ɗauke da soyayen nama.Tambarin wuyanta har yanzu na kasa tuna inda na san shi,ɗaki na koma sai na tarar da ƙawata Maryam ta zo ashe .Barka ta yi min tare da bani kyaututtuka masu yawa,murya a raunace ta ce min “ har yanzu dai kin ƙi sanar da ni matsalar da ta haifar min da rashin ni'ima,kin ga ko jiya Habibi sai da yayi ta yi mini masifa tare da cewa ya gaji da sayen lubrifiant shi aure zai ƙara kuma bai da halin riƙon mata biyu na zaɓi biyu ko ZAWARCI ko kuma na dinga ciyar da kaina tun da dai ga shi saura ƙiris na kammala karatu”

Na ɗan sakar mata murmushi na ce “ ki bani labarinki mana”

“Wane irin labari kuma? Duk waɗanda na baki ba su gamsar da ke ba? To ni kam sai na shimfiɗar aurena kawai suka rage”

“Kafin aurenku nake nufi wane irin ƙalubale kika fuskanta?”

“Ko ɗaya ”

“Ki dai sake tunani,ba ki mafarkin da kike jin kin tsane shi?” na tambaye ta cike da kulawa,shiru ta yi yanayin fuskarta na canzawa kafin ta ce “ ina yi! Ina yawan mafarkin wani namiji na amfani da ni,babu dare babu rana haka yake zuwar min a duk lokacin da zai ziyarce ni wani mugun ciwon kai yake saukar min daga nan sai bacci shi kuma sai ya fake da haka ya kusance ni”

“Amma in kin tashi ya kike ganin yanayin jikinki? Ƙamas ko da ni'ima?” dundu ta kai min da na yi mata tambayar tana cewa “ amma dai Baseerat ba kida ta ido ni kike yi wa wannan tambayar? Ni kin sa ma na ji kunya” sai kuma ta zo daf da kunnena ta faɗa min “ ba zan ɓoye miki ba na fi gamsuwa a mafarki fiye da zahiri in ina tare da Habibi ,kuma na ɓoye miki ne har yanzu fa ina mafarkin jefi-jefi shi yasa ma nake ganin kamar shi Habibin ne bai iya gamsar da ni ba” sai kuma ta janye bakinta tana kallona,na ɗan ja ajiyar zuciya kafin na ce “ to aljani ne a jikinki! Kuma shi ne ke ɗauke ni'imarki,don haka dole ki tashi tsaye.Ki nemi Musk tahara,da jan Musk ,da kuma musk A'isha sai ki haɗe su da man habbatu sauda ki yi musu karatu a ciki na ayatul ƙursiyu,da amanar rasulu ke da duk wani abu da kika sani a cikin Alkur'ani tunda dukkansa waraka ne .In kin gama sai ki dinga dangwala auduga ciki kina shafawa a ƙasanki”

“Na gode sosai amma ya aka yi kika san da wannan?”

Shiru na yi don ni kaina ban sani ba kawai dai na samu bakina da furta hakan,na basar na ce “ ke dai magani kika ja kuma ga shi nan na baki” ta ce “ in sha Allah kuwa zan neme su” daga nan ta dinga bani shawarwari da kuma wayar mini da kai dangane da daren farko na kuwa ci ɗamara in sha Allah zan cire tsoron na bai wa Yaya Khaleed haɗin kai mu yi komai cikin soyayya.

Abinci aka shigo da shi na kuwa zauna na ci don Allah na gani duk wata fargaba da nake ji ta gushe.A haka aka gudanar da walima har kowa ya watse,da ruwan ɗumi na yi wanka na kwanta tun da wuri saboda gobe motarmu za ta cira zuwa Yamai.

Ƙarfe biyu na dare aka tashe ni na ƙara yin wani wankan na kimtsa,dukkan kayana dama tuni an tafi da su.A falo na fito na samu mata biyun da za su yi min rakiya,ɗaya daga dangin Mama ɗayar kuma ta wurin mahaifi.Cikin motar Daddy muka isa gida gidan Bus ɗin,sai kuka nake wanda tun a gida na soma shi.Har muka shiga ciki ban daina ba,sai a lokacin na ga Yaya Khaleed bai ce mini komai ba har motar ta soma gudu da mu.Babu jimawa kuwa bacci ya ɗauke ni,ban farka ba sai da muka iso Maradi a nan duk muka yi sallar asubah kafin mu cira kuma.

Duk garin da aka tsaya sai Yaya Khaleed ya saya mana wani abu,a haka har muka isa .Wani abokinsa ne ya zo ya ɗauke mu da mota,gidan da ya kama mana haya mu uku ne a ciki kowacce da lungunta an kewaye shi da katanga an saka murfi kuma.

Ɗakin muka shiga ciki ɗaya ne da falo sai toilet,na ɓata rai ina mai cewa “ wannan ɗan ƙaramin ɗakin” Yaya Khaleed yayi min wani kallon ƙasa-ƙasa kafin ya fice,duk wanka muka yi muka canza kaya kafin mu ci abinci da ya samo mana.Daga nan kuma suka hau gyaran ɗakina wanda dama tun kafin mu iso motar katakaina da kujeru ta rige mu isa.

Har cikin dare ba su ida haɗa komai ba,an dai saka kujeru da kuma gado inda abokan yaya Khaleed biyu suke taimaka musu.A gajiye duk muka yi bacci,sam bai kwana gidan ba tun da safe dai ya zo ya kawo mana waina da miya da kuma dukunu.Bayan mun ci ne suka hau aikinsu,cikin ikon Allah komai ya tafi daidai ɗaki sai ƙamshi yake.Daga nan kuma suka wuce kasuwa,suka bar ni a nan ina raba ido ina kallon kayan.

Ina nan zaune ya shigo,na dube shi ina turo baki.Ticket biyu ya miƙo min ya ce “ ga shi ki ajiye musu”

“Wai kana nufin gobe za su tafi?”

“Eh zaman mi za su yi”

“Amma Yaya wannan kamar kora da hali ne fa”

“Tun kafin mu tawo suka ce kwana biyu za su yi”

“To ai kwanansu ɗaya”

“Zan kawo gas sai ki ɗora girki” ya faɗa yana mai ajiye tickets ɗin kan kujera ya fice.Ina nan cike da tsoron da tun a gida na yi ƙoƙarin binne shi ,amma yanzu ya dawo daram.A haka ya zo shi da wani abokinsa suka haƙa min tukunyar gas ɗin,ga kuma uban cefane duk sai na ruɗe don ban taɓa girki mai yawa irin wannan ba.

Abokin nasa ya fita daga cikin luguna,a shagwaɓe na ce “ saboda Allah ya za a yi na yi girki ni ɗaya?”

Jawo ni yayi jikinsa ya ce “ don Allah ki cire sakalcin nan ki yi girki mai daɗi zuwa an jima abokaina za su zo”

Ai kuwa na saka masa kuka jin wani zance har da bubuga ƙafa,rarrashina ya soma yana ƙara min ƙargin gwiwa tare da faɗa min abin da zan fara yi.Muna a haka rungume da juna aka buɗe murfin kewayena,har ta yi baya sai kuma Yaya Khaleed ya ce “ ah shigo mana” sai ya janye jikinsa daga gare ya fice bayan ya amsa gaisuwar matar ba za ta wuce shekara ashirin da bakwai ba.

Da murmushi kan fuskarta ta ce “ maƙwabciyarki ce,kewayena ne na can ƙarshe sannu da zuwa ya baƙunta?”

“Alhamdullah shigo mana” na faɗa .

Ta ce “ a'a dama dai na leƙo ne na yi miki sannu da zuwa,na ji daɗi sosai da na ji kuna Hausa halan yʻar maraɗi ce ke?”

Na girgiza kai na ce “ a'a Zinder”

“Allah sarki ni kuma maraɗi,Allah ya bada zaman lafiya da zuri'a ɗayyiba”

Na sunne kai tare da amsa wa da “ Amen ”

Har za ta fice sai kuma na ce “ don Allah in babu damuwa ki taya ni girkin nan ban taɓa yi ba”

“Babu komai bari na canza kaya to”

Ba ta wani jima ba ta dawo,a tare muka wanke kajin tasss sannan ta saka a tukunya ta zuba ruwa ta kunna gas ta ɗora.Ta yanka albasa mai yawa ta saka kayan yaji,yayin da ni kuma na ɓare tafarnuwa na wanke atarugu na saɓa.Yʻar ƙaramar cokali ta sa ta ɗiba ta zuba a tukunyar,sannan muka hau gyaran karas,dankalin turawa da kuma albasar da za a yi miyar.

Tukunyar kajin ta sauke tana mai cewa “ ina mai?”

“Ai kuwa babu,kuma banda waya ballantana na kira shi.Yanzu ne suka tafi sayen Garar ”

“Ok bari na ɗauko ina da shi” ta faɗa tare da fita ta ɗauko nata,haka ta soye kajin muna ta hira abin mu.

Can sai ga yʻan sayen Gara sun dawo,sai a lokacin muka ɗora tukunyar shinkafa.

“Oh muna ta aiki ban tambayi sunanki ba?” na faɗa ina dariya.

“Shafa'atu ” ta bani amsa.

“Ni kuma Baseerat ” ni ma na sanar da ita sunana,kafin mu ɗora hira daga inda muka tsaya labarin Yamai ne take bani da irin yadda ta ci wuya farkon zuwanta don ba ta iya yarensu ba.

Sai bayan sallar la'asar muka ida girki ,na zuba mata nata miya daban ,shinkafa ma haka.Na zuba muka ci sauran kuma na juye cikin manyan kuloli,sai na je na yi wanka.

Bayan sallar magarib suka tattara komai nasu wai za su wuce gidan mota ,ina kuka ina ƙari wannan abokin Yaya Khaleed ɗin ya ɗauke su da mota.Can uwar ɗaka na shige na kwanta,kaina ma ke yi mini ciwo.Ina jin shi ya shigo amma na yi banza da shi,samana ya zo ya kwanta yana min raɗa a kunne kafin ya miƙar da ni “ mu je ki yi wanka ki shirya yanzu za su iso” duk yadda na so turjewa amma sai da ya tilasta min yin wani wankan,mai kawai na shafa na saka wata shadda irin ta jikinsa.Hijabi na ɗora a kai na ɗauki turare zan fesa ya shigo ya karɓe ,“ga su nan za su shigo ki fito falo sannan ki nutsu ban son shagwaɓar nan”

“To ka bani na fesa”

“Tun da mahaukaci ne ni ko? Kin ga mu je” ya ja ni zuwa falo tuni kuma abokan nasa sun gaji da sallama sun shigo.

Nan suka soma tsokanarsa suna cewa “ hankali ya kwanta SEERAT ta zo Yamai ” ya ɗan dube ni,da sauri na shiga gaishe su suka amsa.Sai na rikice ganin duk kusan ni suke kallo,na yi saurin riƙo hannun Yaya Khaleed ganin shi ma zai bi ayari ya zauna cikinsu.Murya can ƙasa-ƙasa na ce “ don Allah ka mayar da ni can ƙurya ɗaki”

“Ki nutsu mana ,ki je ki kawo musu ruwa” kamar na fasa ihu haka na ji,dakyar na iya sakin hannunsa na nufi table inda na ajiye ruwan da kofofi tun tuni .

“Matsalar auren ƙwaila kenan,Khaleed ka rasa wacce za ka auro sai baby? Wannan ai ba ta wuce raino ba” muryar wani abokinsa ta daki kunnena.

“Kai Shereef haka kake komai Khaleed zai yi sai ka kushe shi muddin dai bai nemi shawararka ba”

“Ai kuwa kusan duk manyan abokai haka suke fa”

“Ni kuwa ina cewa in akwai ƙanwarta na yi kame irin mai bi mata ɗin nan,ka ga nan da shekaru biyu sai a kawo min abata ”

“Kai ma rainon kake son yi kenan ?” da sauri na juyo jin muryar abokin nasa tun na farko da ya soma magana,wanda ake cewa shine babban abokin mijina mai suna Shareef.Ai kuwa muka haɗa ido sai na ga yana yi min wani kallon mai saman ruwa,da sauri na ci gaba da aikina na zuba ruwan a kowanne kofi.Sai na yi tsaye ina tunanin yadda zan bi na bai wa kowa,sam banda wannan juriyar a shagwaɓe kuwa na ce “ Yaya” tamkar ɗaukewar ruwa haka falon yayi shiru duk suka maido hankalinsu gare ni,yayin da fuskar SHAREEF ta yi baƙi ƙirin muna haɗa ido na sa ransa ya ɓace.

Yaya Khaleed ya taso ya zo kusa da ni,“ mene ne SEERAT?”

Idona suka ciko da ƙwalla na ce “ kaina ke yi min ciwo sai nake jin kamar wani kusa da ni yana zuga ni akan na kunyatar da kai”

Ya wani jawo ni ya manna a ƙirji yana duban bayana kafin ya ce “ Shuraim don Allah zo ka ɗauki tray ɗin nan ka basu ruwa”

Wanda ya kira da Shuraim ɗin ne ya zo ya ɗauki ruwan,ina kallon ya bai wa kowa ya sha amma banda SHAREEF don bai karɓi kofin ba.Da sauri na ɓoye fuskata a ƙirjinsa ina tambayar kaina ‘ shin mi na yi wa bawan Allahn can yake jin haushina?’ banda amsa.

Yaya Khaleed ya ja ni muka koma tsakiyar falo ya ɗan saki murmushi ya ce “ ku yi haƙuri Madam ba ta jin daɗin jikinta ne har yau da gajiyar biki ga kuma ta mota ,sannan ga dadaɗan girkin da ta yi muku” sai suka hau shewa suna baban love.Daga nan ya ja ni zuwa ɗaki,kan bed ya shimfiɗar da ni ya tofe ni da addu'o'i sannan ya fice ,na lumshe ido ina tunani iri-iri.

A can falo kuwa Khaleed na fita abokansa suka ci gaba da tsokanarsa,Shuraim ne ya zuba musu abincin dakyar Shareef ya ci shi ma don kar ace yana yi wa aminin nasa hassada ne.Bayan an ci an sha sai suka buge da yin hira,kaf cikinsu babu mai aure Khaleed ne ya soma.

Ɗaya daga cikinsu ne ya ce “ to mun ci abincin gidan Khaleed saura na gidan wa?”

Shuraim yayi murmushi ya ce “ ƙila Shareef don a yadda suke gasar juna ina jin ba zai iya haƙuri ba shi ma zai ɗauko tasa amaryar” duk sai kowa ya maida dubansa ga Shareef ɗin wanda ya kasa cewa komai,saboda tunani birjit da suke masa yawo a kai.Khaleed ya ɗan murmursa ya ce “ in sha Allah muna hanya za mu baku mamaki,kun san halin abokina komai nasa special ne kamar dai shi”

Duk suka tuntsire da dariya ,don duk kowa ya san halinsa da tseko in abu ya burge mutane to shi in ya zo kushe shi zai yi.Sannan ra'ayinsa tamkar na Aljanu ne ya sha banban da na kowa,da za su tafi suka soma tsokanar Khaleed suna cewa “ daga yau dai wani zai cire samartar shi”

“Wa ya sani ma tun tuni ya cire ɗin”

“Kai yadda amarya take garas ɗin nan ban ga alama ba,sai dai ko yau hahaha”

“To me za a yi wa wannan ɗin saboda Allah? In mutum yayi ma mi zai ji? Ai sai dai raino” Shareef ya faɗa yana dariya,Khaleed dai bai ce komai ba don tun ranar da ya nuna masa hoton SEERAT har izuwa yau bai taɓa jin ya yabe ta ba.

Shuraim ya ce “ yʻan shilla ai su ake yayi,amma ko da yake ban yi mamaki ba ra'ayinka daban da na mutane.Khaleed a kirawo Madam mu yi sallama ko?”

“Ta yi bacci ku bar ta haka nan ta huta” cewar Khaleed nan ɗin ma sai da aka samu masu yi masa iskanci,duk suka ajiye abin da suka fi ƙarfi na kyautar amarya amma banda Shareef a haka yayi musu rakiya duk suka fita ƙofar gida.

“Wai yau ba za ka zo majalisa ba ne?” cewar Shareef ganin Khaleed bai da niyyar bin su don tuni wasu har sun ɗauki abin hawansu.

Shuraim ya ce “ kai ma ta ya zai tafi ya bar yʻar mutane ita ɗaya? ”

“Don na ga jiya a tare muka cika dare” cewar Shareef yana son basar da damuwarsa.

Shuraim ya ce “ jiya ai akwai waɗanda suka rako ta,ɗazu kuma na mayar da su can gidan Bus ka ga zo mu tafi mu ida sauke haƙin da ke kanmu”

“Wane haƙi kuma?” Shareef ya tambaya .

“Mu sayo kaza da fruits mana” Shuraim ya faɗa .

Khaleed dai bai ce komai ba,su uku ɗin abokan juna ne amma ya fi kusa shi da Shareef haka kuma sun fi saurin samun saɓani , Shuraim ɗin ne ke shirya su .Mota suka shiga suka tafi,yayin da shi kuma ya koma ciki.Yana shiga kuwa ya tarar SEERAT na bacci,wurin da suka ɓata ya share ya goge ya fesa turare sai ya zauna yayi shiru yana tunani.Tsawon lokaci kafin su dawo, TV ce Shareef ya sayo sabuwa dal wurin da aka tanada don ɗora ta ya ajiye ta yana cewa “ ga nawa tukuicin na

amarya” Shuraim ya ajiye ledojin hannunsa tare da cewa “ zuwa gobe in sha Allah sai a kunna mu gani”

“Wace gobe kuma bari dai na haɗa na kunna yanzu” haka Shareef ya kunna tv ta kuwa kawo daram, Khaleed ya soma yaba kyawunta da yadda take fitar da hoto kafin kace wani abu Shareef ya san yadda ya ja su da hira har suka zube kan kujeru ana kallo ana dariya har ƙarfen biyun dare ta buga,Shuraim ne ya farga da sauri ya miƙe yana cewa “ subahanallah ashe dare yayi sosai,Shareef tashi mu tafi” kamar ya caka masa wuƙa haka ya ji don takaici saboda shi bai ƙi su kwana a falon ba,zama ya gyara ya ce “ kai na ƙi na tafin ɗin sai sauri kake sai ka ce kai ne angon”

Khaleed dai murmushi yake duk da ƙasan zuciyarsa ya so kasancewa da SEERAT amma ya bai wa kansa haƙuri da rareashin muradinsa da cewa akwai gobe.....

Nan free page na book 3 ya ida mai so za ta biya 500 ta wannan account ɗin 6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank sai ki turo min da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .
```

_____

BOOK3

7_8

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Cike da takaici da ɓakin ciki Shareef ya bi bayan Shuraim suka bar gidan.Sai a lokacin Khaleed ya ja wata sanyayyar ajiyar zuciya.Da ɗan saurinsa ya wuce bedroom ya zauna kusa da ita,cikin bacci na ji ana shafa ta na buɗe ido da kyar na yi tozali da yaya Khaleed,ya sakar mini murmushi tare da cewa “ tashi ki ci abinci” kamar ya san yunwar nake ji kuwa,don tunanin kaɗaici bai bari na ci abincin ba.Na

tashi zaune ina kallonsa,“ je ki kuskure baki bari na ɗauko” sai ya fita ni kuma na sauka daga gado na shiga toilet na wanko baki da fuskata,ko da na fito ban gan shi ba sai na nufi falo na same shi yana juye kaji a plate .Kan capet na zauna ya ajiye tray gabana,shi ma ya zauna muka fara ci sai da na ƙoshi sannan ya bani madara na sha.Na miƙe har zan shiga bedroom na tsinkayo muryarsa “ ki yi wanka ki canza kaya kafin ki kwanta” “ to” na amsa kafin na shige na cire kaya na faɗa toilet sai da na yi wanka sosai sannan na fito,bayan na tsane jikina na shafa humura na ɗan mirza mai kaɗan kafin na zaɓo kayan bacci na saka .Ina shirin haye bed ya shigo “ kin yi alwala ne?” na girgiza kai ya ce “ to zo mu yi” a tare muka shiga muka yo alwalar da muka fito ya ja mu Sallah bayan mun gama yayi mana addu'o'i sosai kafin ya soma yi min tambayoyi,na sunne kaina don kuwa ban yi wani karatun addini ba.

Bai ce komai ba ya tashi ya shiga toilet,babu jimawa na soma jin saukar ruwa da alamu wanka ne yake yi.Bed na haye ina tunani bacci ma ban ji,na lula sosai a duniyar tunani kafin na ji damshin ruwa a bayana.

Yaya Khaleed ne ya rungume ni,daga shi sai towel da dukkan alama yana fitowa daga Toilet ɗin nan yayo tsinke.Ido na ƙara lumshewa ina sauke numfashi jin halshensa a kunnena yayin da hannunsa ke shafar ko ina na jikina.Cikin ƙanƙanan lokaci gyaran da Mama ta yi min ya soma aiki,yadda yaya Khaleed ke jan numfashi da yanayin yadda yake fitar da sautin jin daɗi da zaƙuwarsa su suka haɗu suka saukar min da kasala wacce ta hana ni wani kataɓus na barsa ya dinga yin yadda ya so da ni.Sai da ya soma yin addu'a ne na ɗan yunƙura zan tashi murya na rawa na ce “ Yaya Khaleed tsoro nake ji”

“Ba zan yi da ƙarfi ba my SEE..R...AAAH!” ya furta tare da haɗe bakinmu,na rumtse ido saboda azabar da ta ratsa ni sai dai babu damar yin ihu ya toshe bakin ,sai hawaye da suka soma yi min zuba . Haka yaya Khaleed ya ci gaba da budirinsa kamar minti goma wayarsa ta soma ringing ɗin wata waƙar abokina.Sama da sau biyar kiran na shigowa yana tsinkewa kafin Khaleed ya miƙa hannunsa dakyar ya jawo wayar da tunanin babu lafiya tabbas kar a je ko hatsari suka yi,yana karawa da kunne Shareef ya balbale shi da masifa “ wani abun ana kiran ka ne amma don wulaƙanci ka ƙi ɗauka? Kai ba ka kira mu ba don jin in mun sauka lafiya ni na kira amma ba ka ɗauka?” sarai na ji abin da ya ce ɗin don har yanzu bakinmu na manne da na juna,Yaya Khaleed yayi ƙarfin cire bakin nasa a wannan karon ta yiyu don ya mayar masa ni kuwa kamar jira nake na soma kukan da ya hana ni ina cewa “ ina jin ciwo don Allah ka bari haka nan! Ni dai ka tada ni na gaji” ina furicin ne ina ɗan

dukansa tare da ƙoƙarin ture shi,ina jin dakyar yake ba Khaleed haƙuri wanda da dukkan alamu yayi suman wuccin gadi tsabar baƙin ciki.Khaleed ya jefar da waya yana cewa “ SEERAT don Allah ki taimaka min na samu nutsuwar nan” tamkar wani yaƙin sojoji haka Yaya Khaleed ya yi min tuni na fahimci so yake ya gamsu don ya samu ya kira abokinsa,duk da ina cikin azaba amma sai da na ji takaici .

Bayan komai ya lafa ne Khaleed ya jawo wayarsa sai ya ga ashe har yanzu kiran na tafiya.

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un! Shareef dama ba ka kashe ba?” ya furta yana mai kara wayar a kunne,sai a daidai wannan lokaci Shareef ya kashe kiran .Da kuma Khaleed yayi ƙoƙarin kiransa sai aka ce wayar a kashe,duk abin da yake ina kallonsa.Sai a lokacin ya ɗauke ni zuwa toilet,babu bahon wanka wannan yasa dole da shower muka yi.Shine ya canza mana zanen gado ya shirya mu cikin wasu kayan baccin sannan muka zube kan bed sai baccin gajiya, washegari tuni muka makara sallar asubah a nan gida ya ja mu sannan ya fita ya ɗora min ruwan zafi.

Tsakiyar ɗaki ya ajiye ƙatuwar roba,ina kuka ina ƙari yayi min wanka tare da gasa ni sosai.Kamar wata yʏar yaye na kwaɓe fuska na ce“ yunwa nake ji”

Plate ya ɗauka ya wanke fruits tare da yankan min,haka na soma ci da sauri har sai da cikina ya cika.A nan kan kujera na zube ina bacci yayin da Yaya Khaleed ya fita wankin zanen gado,ko da na farka kan bed na tsinki kaina.Yana kwance a gefe yana bacci ,na kai hannu na shafi fuskarsa sai na ji zafi rau.Ya buɗe ido yana kallona,“ kin tashi?” na jinjina masa kai .Ya tashi zaune tare da ɗaukar wayarsa,bayan yayi yʏan danne-danne ya kara a kunne “ Assalamu alaikum Shuraim don Allah ka zo ba mu da lafiya ni da Madam” ina jin lokacin da abokin nasa yayi yʏar dariya kafin ya ce “ ina zuwa yanzun nan bari na shiga pharmacie na sayo alluran” bayan nan ya kashe kiran sai ya jawo ni ya ɗora a cinyarsa,“ kina jin zafi har yanzu?” yayi min tambayar yana sunsunar gefen wuyana,hawaye suka zubo min shaaa ba tare da na basa amsa ba a haka ya dinga kissing ɗina yana gode min a kan darenmu na jiya mai cike da ɗumbin tarihi.

Kamar minti talatin haka sai ga kiran Shuraim ɗin,hijabi ya ɗauko ya saka min kafin ya je yayi masa isa.Suna shigowa na sunne kai don na ji Shuraim ɗin na cewa “ yau dai dole ka bari a yi ma allurar nan don kusan duk saurayi sai ya ji abin nan a ranar farko da ya san mace”

Yaya Khaleed ya zauna kusa da ni yana cewa “ ita dai nurse ai ba za ta ji tsoron allura ba”

“Ita ƙarin zan saka mata ai,sannu Madam ”

Sai a lokacin kawai na gaishe shi,ƙarin ruwan ya saka min yayin da nake kallon ikon Allah yadda sam Yaya Khaleed ya ƙi tsayawa a yi masa allurar,na ce “ kawo na yi masa irin simple wacce ba ta da zafin,kai ba ka iya ta ba ko?” Shuraim ya jinjina kai ya ce “ tun tuni nake son koyon ta amma kin san ai jami'an tsaro ne babu ruwansu da wani zafi sai dai shagwaɓaɓen mijinki”

Allurar na karɓa na yi masa tsaf kuwa ya zauna har na ida masa ,sai a lokacin Shuraim ya soma yi masa Iskanci “ wato ƙato da kai an yi ma wayo”

“Na ji! Nemo min dambu don Allah ” cewar Khaleed, Shuraim ya amsa da “ toh” kafin ya fice.Daga nan bacci ya kwashe ni ban ƙara sanin abin da ya faru ba ko da na farka har an cire min ƙarin ruwan,Yaya Khaleed ya matso kamar mai jiran na tashi ya ce “ ga ruwan ɗumi can ki yi wanka ,zuwa ƙarfe biyu su Shareef za su zo” ambaton sunansa sai na ji raina ya ɓace a take kuma mafarkin da na yi da shi ya faɗo min,na ɗan saki murmushi kafin na miƙe na shiga bedroom.Kayan jikina na rage,sannan na shiga Toilet ɗin sai a lokacin yaya Khaleed ya shigo ɗauke da bokin ruwan zafi.Sai da ya ƙara wasu kafin ya bar ni na yi wanka,bayan na gama na fito na shirya cikin doguwar riga ta atamfa na yi ɣar kwaliyya.

Na fito da zumar wanke kwanukan jiya sai na ga tuni an wanke,da mamaki na ce “ Yaya wai da kanka ka yi wanke-wanke?”

“Eh me yake don na yi? Kar ki manta duk sanadina ne kike wannan tafiyar”

“Wace tafiya?” na tambaya da mamaki,sai ya soma nuna min na yi kukan wasa ina rumtse ido tare da jin kunyarsa.

“Ki kula da kan ki zan fita” ya faɗa tare da yi min kiss a goshi,“ a dawo lafiya ango SEERAT ”

“Iyeee babyna an girma har an fara kalaman manyan mata” ya faɗa yana dariya tare da ficewa.

Tsintsiya na ɗauka na ƙara share ɗakin da kuma nan filin kewayena,na goge na fesa turare sannan na saka na wuta .Sai a lokacin na yi tsaye gaban tvn da ban san yaushe aka kawo ta ba,na ɗan taɓe baki ina cewa “ Ni da ma ba wata gwanar kallo ba” sai kuma na yi zaune tare da yin shiru ina tunanin abin da muka yi jiya sai dariya nake ni ɗaya,daga can bakin ƙofa Shafa'atu na miƙe na je na buɗe mata .Kwanukan jiya je ta maido min,na karɓa tare da gaishe ta .

“Zan fita unguwa ne sai na dawo” ta faɗa .

Na ce “ to Allah maido ki lafiya”

“Amen amarsu,yau ba ki girki ne?”

“Bai ce na yi ba” na bata amsa .Ta waro ido ta ce “ to sai ya ce ki yi? Ai kawai ke ce za ki shirya masa ”

Na yi yar dariya na ce “ to bari na yi” a haka muka rabu,ni kuwa abubuwan buƙa na ɗauko na ɗora girkin shinkafa fara da miyar kifin gwangwani.Saura ƙiris na gama miyar aka soma kiran sallah ,na rage ƙargin gas ɗin na wuce can ɗaki na shiga toilet sai da na yi wanka na ɗaura alwala.

Ina fitowa na samu Yaya Khaleed zaune gefen gado,“ sannu da zuwa har ka dawo?”

“Eh na dawo sai kuma na tarar kin bar gas a kunne”

“Miyar ba ta ida ba ne”

“To ai kashewa ya kamata ki yi in kin fito sai ki ƙara kunnawa don babu kyau barin gas a kunne sai abin da ka ɗora ya ƙone”

“To in sha Allah zan kiyaye gaba” na furta don kuwa na gane kuskure ne.Ya jawo jikinsa ,na kuwa haye cinyarsa ya ja dogon hancina yana murmushi kafin ya ce “ rufe idonki” na mayar masa da martanin murmushin kafin na rufe kamar yadda ya buƙata,kawai sai na ji ya jawo hannuna ya ɗora mini abu.Da sauri na buɗe su na yi tozali da kwalin waya,ban san lokacin da na rungume shi gam ba tare da sakar masa kiss ko ta ina shi kuwa sai dariya yake ƙyalƙyatawa gwanin sha'awa.

“Don Allah muna jiranka” aka faɗa daga can falo,ya tsaya da dariyar da yake ya ce “ ki yi sauri ki shirya ga baƙin nan sun zo”

Na jinjina kai tare da nufar dressing mirror na shafa mai da hoda da kuma kwalli sai man leɓe.Wani farin less na ɗauko na saka tare da ɗan fesa turare,sai na ɗauki mayafi na yafa kafin na fito falon.Idonsa ƙurrr a kaina hakan yasa har sai da na ɗan razana,“ baby kin ga matar da Aboki zai aura nan” muryar Yaya Khaleed ta katse ni daga kallon abokinsa Shareef.

Na juya inda yake nuna min ina sakin murmushi,wata cikakkiyar budurwa na gani a zaune fara ce tasss amma bai farin bai ɓoye muninta ba.Tana da laguɓaɓen ƙaton hanci da wasu ƙananan ido kamar kifi,sannan kumatunta tamkar wacce aka baiwa busar algaita haka suke suntum da su wanda tsabar cikar su ne ya ƙara sa idonta suka ƙanƙance.

“Ina wuni anty?” na furta da murmushi.

“Alhamdullah! Ya baƙunta? ” ita ma ta amsa cike da fara'a,na ce “ an gode Allah ” sai kuma na je na kawo mata ruwa.

“Ita kaɗai za ki ba ruwan banda ni ?” Shareef ya furta cikin sanyin murya,har sai da na yi mamaki.

“Hubby in na sha ai kamar na sha ne amma bari na zuba ma” cewar ita budurwar tasa tare da zuba masa a kofi.A yadda na lura ni ya so na zuba masa,dakyar ya karɓa ya sha.

Yaya Khaleed ya ce “ Ramatu fatan dai za ki kula da abokina yadda ya kamata dube shi yadda ya shagwaɓe fuska ”

Sai suka sa dariya shi da ita,ni kuwa Shareef ɗin na kalla sai na ga ashe shi ma ni yake kallo.

“In dai ɓangaren abinci ne wannan banda matsala,kullum tumbina sai kwashi dadaɗan girki ɗaya ɓangaren dai ne ba a sani ba to tun da an ce lukataye sun cika raki ” Shareef ya faɗa ,da sauri na ga Ramatun ta sunne kai a nan na fahimci mi yake nufi.

Yaya Khaleed ya ce “ ai ba daga nan take ba,kai dai Allah sa mu dace.Seerat kawo abinci”

“To” na furta ina mai fita waje,don zuba abincin.Daga inda nake ina jin lokacin da Shareef ke cewa “ Aboki ina fa mamakin yadda yarinyar can ta ɗauke ka”

“Aboki Ramatu na jin ka” cewar Yaya Khaleed.

“Tun jiya na faɗa mata ta rage ƙibar nan don ina son mace mai juriya kar ƙibarta ta hana mu cin amarci”

Na taɓe baki a zuci na ce ‘ shege ɗan iska ’ miyar na ƙara kunna wa wuta sannan na koma gefe sai bayan ta yi daidai ne na kashe na zuba abincin.

Tun da na shigo idon nasa ma yanzu na kaina,na zabga masa uwar harara kafin na ajiye tray ɗin.Shareef ya sakar min murmushi kawai ,na fita na samu wani ɗan madaidain kwano na zuba wa Shafa'atu abincin Allah na gani shaf na manta da ta fita sai kawai kuma na nufin lungunta na ƙarshe kamar yadda ta sanar da ni.Wata mace na gani wacce ba ita ba ta shiga kewayen,ban kawo komai a raina ba na yi tunanin ko baƙuwa ta yi.

“Assalamu aleykum!” na ji muryarta daga bayana,na juya sai na ga Shafa'atu ce ta shigo gidan da murmushi ta zo daidai inda nake a tsaye tana cewa “ kiran Isama'il na gani ya fi goma kuma da na kira ya ƙi ɗauka shine na dawo ko ajiyar da ya bani ce yake son zuwa karɓa,zo mana” ta faɗa tare da ja na daidai ƙofar kewayenta ta cike da mamaki nake kallon yadda ƙofar ke manne da kwaɗo amma na yi shiru ban ce komai ba, “ a rufe fa na bar ɗakin yanzu haka shi ya dawo ya barsa a haka...” sauran maganar ce ta yanke ganin mijin nata ya fito daga shi sai gajeren wando.

“Shafa'atu mi kika dawo yi gida?” ita ce tambayar da yayi mata.Ba ta kai ga basa amsa ba wata baƙar mage ta fito daga ɗakin idonta kawai na kalla na fahimci mutum ce ta ɗauki siffar kawai sai na gyara tsayuwata.Magen ta yi tsalle ta haye katanga,da sauri na riƙe mata bindi na jawo amma shegen nauyi ne da ita.

“Wace ce wannan?” mijin nata ya tambaya hankali tashe , Shafa'atu kuwa ba ta ce komai ba sai da ya sake maimaita tambayar ta basa amsa da “amaryar gidanmu ce”

“Matsafiya dai! Kin ga don Allah ki sake ta na yi miki alƙawari wannan ce shigowar ƙarshe.Shafa'atu ce ta sako magen nan” ya faɗa hankali tashe,ita kuwa sanin yadda mijinta ke da mugun son mage yasa ta ɗauka normal mage ce.

“BASEERAT sake ta don Allah ” ta furta sai a lokacin na saki bindinta ta yi tsalle kuwa ta faɗa kewayen tsakiya wanda daga shi sai nawa.

Kwanon abincin na ajiye mata tare da ficewa ina jin raina na azalzala,abin da na fahimta duk mutanen da nake abin kirki da su sai an samu masu cutar da su.Yanzu maƙwabciyata wacce jininmu ya haɗu tun kafin a yi nisa na gano ainahin maƙiyanta,kiciɓus muka yi da maƙwabciyata ta tsakiya wacce sai yanzu ne kawai na ganta.Ta buɗe ƙofar sashenta ,abun mamaki kayan matar da na gani za ta shiga lungun Shafa'atu sune a jikinta.Ido cikin ido muke kallon juna da ita,na sani sarai ita da kanta ta fahimci na san ita ce magen nan.

Sashena na yi tsinke nan na tarar da su suna ta cin abinci Shareef sai kushe ni yake yana cewa “ abokina ba za ka sanin daɗin aure ba sai ranar da ka auri cikakkiyar mace wacce ta san ciwon kanta,amma ka ga yan 15 zuwa 17years ɗin nan ko tsarkin kirki ba su iya ba” ina shiga daidai ya ɗauki kofin lemun zai sha na motsa hannuna na hagu kofin ya suɓuce masa lemun ya zube ga fararen kayansa.Na yi dariya na ce “ sai kace dai wani baƙauye?”

Yaya Khaleed da Ramatu ma suka tuntsire da dariya hakan ya ƙara sa ran Shareef ya ɓace kawai sai ya miƙe ya bi ta gabana ya fice.Suka mara masa baya su biyu suna faman kiran sunansa,don iya mugunta ni ma na fita na laɓe yana daf da buɗe ƙofar fita daga gidan na sa murfin ya motsa da mugun ƙarfi ya buge goshinsa yadda ya fitar da sautin azaba ya fi komai faranta min fiye da faɗuwar da yayi.Na yi amfani da wani Siddabaru da ni kaina ban san ina da shi ba,na yi furicin da iya shi kaɗai zai na ce “ raggon maza” daga inda Shareef yake kwance ya ɗago kai ya dube ni,na tuntsire da dariya ina kallon ƙaton abu da ya fito masa a goshi na bugewar da yayi.Kofar kewayena na jawo ina murmushi juyowar ga da zan yi tsudum na ga saukar mage a gabana baƙa ƙirin da ita ga ta kuma kamar uwar giwa,har sai da na ji wani das.Ban ida daidaita nutsuwa ta ba ta yo tsalle ta haye jikina,amma duk uban girmanta ba ta kai ni ƙasa ba wuyanta na riƙe gam yayin da ita kuma ta soma yafita jikina da akaifunta.Bakinta ta buɗe tana shirin haɗiye ni sai

kuma na ji ta fasa ƙara tare da faɗuwa ƙasa na waro ido ina kallon cikinta mai ɗauke da wuƙa,wanda ba kowa ya ɗaba mata ita ba sai Yaya Khaleed.Ta saki wani mahaukacin ihu wanda ya kusa girgiza gidan,a nan take kuma ta rikiɗa ta zama mutum.

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un ! Khaleed mi nake gani?” muryar Shareef ce ke faɗar haka yayin da kuma Shafa'atu da mijinta su ma tuni sun iso lunguna, Isama'il ya ce “shikenan ta kashe ta” sai ya nufi matar yana kiran sunanta “Sumayya? Sumayya?” sai kuma ya zare wuƙar jikinta

Jiniyar motar yɗan sanda kawai muka ji ba tare da an san wanda ya kira su ba,sai dai Shareef ne ya fita yayi musu iso sai aka rasa wa za a kama .Aka tafi da Yaya Khaleed da kuma mijin Shafa'atu,duk da na lura Shareef ni ya so a damƙe.

“Don kar ka tafi Yaya” na faɗa hawaye na zubo min,“zan dawo gare ki ƙanwata kar ki damu” shine furicin Yaya Khaleed ina ji ina gani aka tafi da shi yayin da ita kuma Sumayya aka cicibeta zuwa asibiti wuƙar da aka yi kisan kuma a wani farin ƙyalle aka naɗe ta.

Ina shigowa ɗaki na tarar da Bafulatana zaune a hakimce kan kujera tana sakar mini murmushi,a nan take na fahimci hakan yayi mata daɗi na je rai ɓace zan shaƙe wuyanta amma sai na ji hannuna cikin iska kamar ban riƙe komai ba.Duk da haka ban haƙura ba ƙara kai mata farmaki da hannu ɗaya ta yi wani yarfa ni gefe kaina ya bugu da ƙarfa table jini ya soma yi min tsiyaya,na ɗago kai ina kallonta.Murya a hassale ta ce “sai ki fara shirin mission ɗinki ta gaba,idar da ita ne kawai zai sa Yayanki ya dawo akasin haka kuma wallahi zai tabbata a rufe” tana gama furta min ta ɓace ɓat.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755
```

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

9_10

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Rasa abin da ke yi min daɗi na yi,duka kwana ɗaya da tarewa a gidan miji amma har na fara fuskantar ƙalubale.Ina nan a durƙushe ina nazarin madafa sai ga Shafa'atu ta shigo,wani irin haushi take bani wato saboda ita ne Yaya Khaleed ke can rufe,na kuma gane ba kowa ne ya cakawa Sumayya wuƙa ba sai Bafulatana amma ta ƙaƙabawa mijina saboda kawai na ceci Shafa'atu.

“Jini na yi miki zuba BASEERAT bari na taimaka miki ” ta furta cikin rawar murya tare da nufo ni,na yi saurin dakatar da ita ina cewa “ kin ga ban so,ki faɗa mini abin da ya kawo ki .Ina jin ki me cece damuwarki?” na yi mata tambayar ina ɗago idona da na ji suna yi min masifar zafi,ban san mi ya firgita ta ba sai kawai na ga ta yi baya tare da dafe saitin zuciya.

“In ba ki shirya sanar da ni dukkan matsalolinki don Allah ki fita ki ban wuri” wannan karon ma cikin zafin rai na faɗa .

“Kamar yadda na faɗa miki sunana Shafa'atu,ni ɗin ƴar asalin Maradi ce aure ne ya kawo ni nan.Tun aurena da Isma'il ban taɓa fuskantar wata matsala ba sai da muka dawo nan gidan,tun a ranar farko ya dake ni wanda ban san dalilin hakan ba .Duk abin da zan yi sai ya ga kuskuren shi,a haka na samu ciki na farko a ranar da na sanar da shi a ranar ya nemi kwanciya da ni ban musa ba don haƙinsa ne.Washegari ko da na tashi cikin jini na tsinci kaina,na ci kuka sosai kafin na haƙura in taƙaice miki zancen sau wajen biyar ina samun ciki da zarar Isma'il ya kusance ni sai ya ɓare shi ma tun bai damuwa har ta kai da ya soma” sai ta yi shiru,ɗan jinjirin cikinta na duba kafin na ce “ shi yasa yanzu kika ɓoye masa kina da ciki?” ta jinjina mini kai idonta na kawo ruwa.

“Yayin da yake mu'amalar aure da ke ba ki jin komai?”.

“Ban jin komai amma muddin na shaida masa ina da ciki in yayi amfanin da ni tamkar ana jawo hanjin cikina da ƙugiya haka nake ji,don fita hayyacina ma nake yi sai washegari kawai nake tuna abin da ya faru”

Na taɓe baki na ce “ duk da kin fahimci cewa shine silar kashe ƴaƴanki amma kika ci gaba da aurensa,ban ma san mi yasa ake so na taimake ki ba.Mutane dayawa sune silar matsalar da ke mamaye da duniyarsu,mutum na cutar da ke amma kin zauna kina aurensa ”

Ta zube a gabana ta ce “ ina sonsa ne sosai don ni ce na fara furta masa kalmar so,sannan iyayena ba wani ƙarfi ne da su ba hatta kayan ɗaki Isma'il ne yayi min su.In na koma gida zan ƙara musu nauyi kuma ba lallai a samu wani da zai aure ni ba”

Cike da takaici nake kallon ta kafin na ce “ wato kema kina ɗaya daga cikin matan da ke jahiltar zaman ZAWARCI? Wato duk irin masifar da kike ciki kin zaɓe ta akan ki yi ZAWARCI? Faɗa min mene ne amfanin baɗi ba rai? Auren da zai yi silar rayuwarka ai barinsa shi ya fi alkhairi.Dube ki yadda ruhinki ya takure saboda fuskantar miyagu amma ke hankalinki kwance.”

“Wallahi ba kwance yake ba,ko ranar nan da na je asibiti sai da likita ya ce min jinina ya hau”

“Shine zai kashe da yawan mata,kutun namiji ba.Miji na ƙumsa miki baƙin ciki iri-iri amma kuma kina tsoron rabuwa da shi,da wannan ɗin zai fake ya yi ta azabtar da ke tun da ya fahimci tsoron hakan kike”

“Baseerat har yanzu yarinya ce ke,ba ki san ƙalubalen da ke tattare a cikin ZAWARCI ba shi yasa kike faɗar haka” ta faɗa a ɗan dake.Na dube ta cikin ido na ce “ yanzu kenan in na fahimta kin zaɓi ci gaba da zama da Isma'il a kan ki koma gidanku? To yayi je ki in mahaifarki ta saki ta yadda ba ki iya ɗaukar ciki sai ya tsotse naki jinin kin ga ƙarshen ƙauna kenan masoyi ya cinye masoyiyarsa”

“Wai kina nufin Isma'il maye ne? ”

“Ko ma dai ba shi ba ne wakilin mayyar ne,tun da ita yake ba kaf yayanki.Ban san dalilin da yasa ya haɗa hannu da ita ba har yake sadaukar da yayansa gare ta ba,amma ƙila ke kin sani”

“Ni kaina ban sani ba,amma yanzu don Allah mene ne mafita?”

“Dole sai na ji ta bakin shi mijin naki” na faɗa tare da miƙewa na wuce bedroom jiri na ɗiba na.Toilet na yi tsinke na tsaya ƙarƙashin shower tare da kunna shi,ruwa suka soma dukan fuskata a sannu a hankali na soma jin raɗaɗin na tafiya haka wurin da ya fasa yana haɗe kansa.Daga ƙarshe wanka na yi tunani fal zuciyata,da na fito na ɗauki wayar da Yaya Khaleed ya bani,sai na ga akwai layi ciki haka kuma ya saka min lambobin yan gidanmu.Ina tsaka da dubawa na ji ihun Shafa'atu daga falo,da sauri na fita ina cewa “ lafiya?”

Jikinta na rawa ta ce “ ji..jininki ne da ya zuba zan goge amma kin ga ya ƙi fita ,ƙarshe kuma sai na ji kamar ma yana tafasa ”

Ruwa na ɗebo cikin tafin hannuna na zuba daidai wurin,a take jinin ya ɓata kamar ma ba a taɓa halittar shi a wurin ba.Na juya zan tafi ta jefo min tambaya “ wace ce ke?”

“Ke ya kamata na yi wa wannan tambayar,saboda a duk lokacin da mutum ke cikin matsalar da ta shafi maita a kallo ɗaya nake gane shi amma ke banda ke” ina gama faɗa na shige ɗakina sai na tarar da Bafulatana a tsaye tana jera min turaren nan da Madam Rakiya ta bani.

“ Muddin kina kusa da Khaleed power ɗinki ba za ta taɓa aiki yadda ya kamata ba, SEERAT ki sani ban zaɓe ki matsayin wakiliya ba sai da na tabbatar za ki iya.Akwai aiki jajajur a gabanki amma na ga sai sanyin jiki kike,har da wani faɗawa soyayya hum!”

“Amma ai kin san aure shine burin kowace ƴa mace ko? Sannan shi yaya Khaleed ɗin mi yayi miki?”

“Ba ki san waye shi ba ko? To ki sani Khaleed ɗa ne ga sarki Waleed,ambaton sunansa kawai ya ka san zuciyar miyagu ta buga.Shi ɗin Sadaukin yaƙi ne,mai farautar dukkanin wani matsafi ko wani nau'in maita.Laƙaninsa shine kaifi ɗaya,muddin ya kama mutum ko kaɗan bai basa damar guduwa .Zo ki shafa turaren nan yanzu za a zo ɗaukar ki”

“Amma ki ci gaba da bani labarin mana” na faɗa da sauri ina mai ƙarasawa kusa da ita,“ bakina ba zai iya ba ke ce da kan ki za ki nemo tarihin mijinki,saboda sakalci yasa har yanzu ba ki nemo amsar tambayar da kike son sani ba”

“Wace amsa kenan?” ba ta bani amsa ba sai tafin hannuna da ta kamo ta shafa min wani turare,daga nan ta ɓace.Na ja numfashi kafin na shirya cikin riga da zane na atamfa,daga can waje kuwa na soma jin sallamar Shuraim.Hijab na ɗora kafin na fito,tuni Shafa'atu ta amsa masa,gaishe ni yayi tare da cewa “ na zo na tafi da ke ne”

“Zan bi ku don Allah ” ita ma ta faɗa da sauri.

Komai ban ɗauka ba in baya ga key ɗin rufe ɗaki,bayan mun fito waje da ni da ita duk bayan motar muka shiga ya tuƙa mu.Tafiya muka soma yi sosai kafin mu hau gada,da sauri na dubi gefen window jin muryoyi na gaishe ni.Ruwa ne na gani masu bala'in yawa sai gudana suke,na sauke madubin mota ina shaƙar ƙamshinsu har izuwa yanzu kuma ina jin sautin muryoyin wanda na yi imani aljanun ruwa ne.Idona a lumshe suke ,ban buɗe su ba sai da muka sauka daga kan gadar.Ta madubi Shuraim ke kallona wanda ban san na mine ne ba,a haka muka isa police station ɗin.Shi yayi mana iso har can ciki,Shareef na zaune cikin kayan yʻan sanda sai cika takardu yake.

“ Amma ai ka san yanzu ba lokacin ziyara ba ne ko?” shine abin da ya faɗa yana mai tashi tsaye.

Shuraim ya ce “ kar fa ka manta Khaleed ɗan sanda ne,sannan har yanzu ba a tabbatar shi ya aikata laifin ba ko a'a zargi kawai ake”

“Amma ai a kewayensa aka tsinci matar ko? Kuma ma dai ko mine ne ka san ba za mu taɓa tauye haƙin kowa ba sannan ba za mu saɓa dokar aiki ba,lokacin ziyara bai yi ba don haka sai su jira waje” Shareef ya faɗa yana min wani kallo da na kasa fassara na mine ne.

Shuraim ya dube ni kafin ya ce “ Baseerat ku zauna nan ina zuwa” ya nuna mana wani banci,muka zauna kuwa shi kuma ya wuce can saman bene.

Ban taɓa sanin cewa Aboki zai iya hassadar amininsa ba sai yanzu,kawai ido na zura wa Shareef da ke ta faman cika takardu abin da na lura yana matsayi sosai a wurin sauran yʻan sanda cike da girmamawa suke gaishe shi.Shafa'atu na yi min hira amma ban ajiye hankali ba ballantana na san mi take cewa,burina guda na hukunta Shareef .Ina cikin wannan tunani kuwa na hango cinaka na tafiya,da sauri na fito da hannuna na hagu na jawo cinakar kusa da ni.Sai da na mayar da su kusan ashirin

kafin na watsa su a jikin Shareef duk suka shige cikinsa,daga nan na lumshe ido na soma basu umarnin cizonsa lokaci guda.

“Innalillahi!” ya furta da mugun ƙarfi,sai na buɗe idona ina kallonsa.Ya miƙe zumbur yana cike baki wato yana so ya jure ne amma na hana yiyuwar hakan na sa cinakun na da ƙalla masa cizo ya saki ihu ya fara tsalle-tsalle hakan ya jawo hankalin sauran polices ɗin suka shigo suna tambayar lafiya.Tuni ya cire riga ,na saki murmushi ganin duk fatar jikinsa ta yi ja ni kuwa hakan zuciyata ta yi ƙal da ita tsabar farin ciki.

Cinakar gasken wacce ba ta tsafi ba ita ce kawai ya samu nasarar fitarwa,sauran kuwa ido ba su ganinsu ballantana a cire.Kafin wani lokaci Shareef ya fita hayyacinsa , waɗanda suka fara yi masa dariya sai suka soma tausaya masa.

“Baseerat ki dakata da abin da kike ya isa haka” cewar Shuraim yana mai zuwa kusa da ni,ban san wa ya faɗa masa ni ce ba amma ko da na ji ya faɗi haka na san da tabbas to yana da tabbacin ni ce ɗin kawai sai na fitar da cinakun.

Shuraim ya ja ajiyar zuciya ya ce “ taso mu je” har Shafa'atu ta miƙe amma ya tsayar da ita.Na bi bayansa har muka isa wani ɗaki,shi ya saka key ya buɗe ƙofar sai ya tsaya ni kuma na shiga da sauri tare da zuwa jikin Yaya Khaleed na rungume shi ina kuka.

“Lafiya duk ka cire kaya? ?” na tambaye shi ganin daga shi sai gajeren wando,amsa yake bani amma sam ban ji sosai ba sakamakon idona da ya sauka kan sarƙar wuyansa.

Tambarin da ke jikin sarƙar sak irin ta tsuntsuwar nan,wato abin da na lura tambarin masarauta ne. ‘ kenan mahaifin Khaleed sarki ne? To mi yasa Ammy Habibah ta rabu da shi ? Mi yasa ko sau ɗaya ban taɓa jin ta bamu labarin dangin mahaifin Yaya Khaleed ba?’ na tambayi kaina a zuci.

“Ya dai mi kike tunani?” Yaya Khaleed ya tambaye ni.

“Babu komai,yaushe za ka dawo gida?”

“Sai in matar nan ta warke,wallahi SEERAT ba ni ne na caka mata wuƙa ba ni ma ina shigowa na ganta a cikinta”

“Na sani Yaya amma shi mijin Shafa'atu yana ina? Tare muke da ita”

Daga can bakin ƙofa Shuraim ya ce “ Baseerat fito ya isa haka nan”

“Ki kula min da kan ki sosai kar ki sanar da Ammy cewa ina nan a rufe” ya furta tare da yi min kiss.

Ina hawaye haka na fito Shuraim ya rufe ɗakin,wani ɓangaren ya ƙara nufa da ni mai warin ƙattai kamar zan yi amai.Mijin Shafa'atu yasa aka fito da shi daga cikin raga sannan ya bamu wuri,“kina da minti goma”

Na dube shi da mamaki,yanzu ni da mijina duka ko minti biyar ba mu yi ba amma ya bani har goma don na zatan da wani banzan.

“Bani labarin ranar farko da ka kama haya ,mi ya faru?” ita ce tambayar farko da na yi masa.

“Babu komai,kawai dai mun haɗu da Sumayya ne,sai na yi ta kallonta saboda yanayin shigar da ta yi ta burge ni.A lokacin da na shiga sashen da na kama ina duba ko ina sai ta shigo ta kawo min ruwa,ni kuma na karɓa na sha saboda girmamawa a matsayinta na hajiyar da ke da gidan”

Da mamaki na katse shi “ dama gidanta ne?”

“Eh nata ne! To ni dai tun da na sha ruwan nan sai na ji kamar jikina ba nawa ba,tamkar yadda ɗa ke tsoron uwarsa haka na ji ” sai kuma yayi shiru ya sunne kai ,na jinjina kai na ce “ daga nan sai ta neme ka kuka aikata masha'a,tun daga lokacin kuma sai ka bar jin daɗin mu'amala da Shafa'atu wannan ya saka kuka ci gaba daga inda kuka tsaya eh dama ita zina garɗi ne da ita ballantana mai sirki da tsafi.To ka sani ta saka maka MACIJIN CIKI (MRS SADAUKI) ne duk in matarka nada ciki shi zai dinga cinye yaron ,sannan duk da ka san da cewa Sumayya hatsabibiyar bokanya ce haka ka ci gaba da yin mu'amala da ita”

Ya fashe da kuka kamar ƙaramin yaro kafin ya ce “ don Allah ki taimaka min ki cire min macijin nan”

“Lokaci yayi mu je!” cewar Shuraim ,aka mayar da shi a raga mu kuma muka fito waje ta wata hanya.Tsaye na yi ina kallon farfajiyar wurin,na ɗan saki murmushi kafin na ce “ yalaɓai wane ne kai? Na san DA WALAKIN (Saadiya Abdulrazaq) tun da har ka kawo ni nan”

Shuraim ya saki murmushi mai sauti karin ya ce “ ni ba kowa ba ne amma ina da baiwar duba irin ta mafarki haka,tun kafin na haɗu da Khaleed na gansa a mafarki wannan yasa ko da ya zo ban wani ci wuya wurin gane shi ba.A irin hirar da muke yake bani labarinki da irin abubuwan da kika yi,sai na ji lokaci yayi da zan kawo ƙarshen hajiya Sumayya.Hatsabibiya ce sosai ta ƙware wurin Maitar tsafi,duk waɗanda suka shiga haya gidanta babu wanda ba ta mu'amala da mazajensu a ƙarshe kuma ta dinga cinye yaransu walau waɗanda aka haifa tun tuni walau kuma waɗanda ke ciki.Ni ne na kama wa Khaleed hayar gidan kuma ga shi alhamdullah komai na tafiya kan tsari”

Na ce “ amma hakan da ka yi ba ka ganin kuskure ne? Inda fa ta baiwa Khaleed ruwan da take bai wa mazajen sai ya kenan?”

“Zai amayar da su ne na sani! ”

“Mi yasa ka ce haka?”

“Saboda muddin Khaleed ya ci abu mai gubar tsafi yana maido shi ne”

“Wa ya faɗa ma?”

“Ni ne na gano haka,saboda muddin ....” sai kuma yayi shiru yana waige-waige.

Na saki murmushi kafin na ce “ na fahimta! Amma shugaban nan naku bai da imani ko kaɗan,duk wannan tashin hankalin da ya binne na mene?” na yi masa tambayoyin ina kallon farfajiyar wurin da take ta fitar da hayaƙi kusan ko ina.

Ya ɗan yi ƙasa da murya ya ce “ mahaifin Shareef ne”

Na waro ido,ya saki murmushi ya ce “ mu je” sai muka dawo inda muka bar Shafa'atu,tana ganinmu ta miƙe .Can inda ya ajiye mota muka nufa yanzu ma baya muka zauna ya soma tuƙa mu,mun yi nisa sosai kafin ya ce “ in sha Allah zuwa gobe zan kawo miki uniform ɗin makarantarku,Khaleed ya ce kuma na kai ki asibitin da za ki ci gaba da stage ”

“Allah ya kai mu” na furta,sai da ya tsaya ya saya mana fruits sannan ya ajiye mu gida muka yi godiya muka shiga ciki.A sashena ta zauna,ita ce ta yi mana girki muka ci sam ko da wasa ban soma amfani da waya ta ba.

Da dare Shafa'atu ta kasa tafiya sashenta wai tsoro take ji,nan wurina ta kwana.

Washegari tun da safe kuwa na gasa jikina da kyau sannan na yi wanka na shirya tsaf.Abin da Shafa'atu ta haɗa na ci,ina nan sai ga Shuraim ya zo haka ta laƙe min muka tafi tare.

Wata babbar asibiti ce ya kai ni,tun a bakin ƙofa gabana ya bada rasss saboda tarin aljanai da kuma mabiyansu da suka yi min maraba.....

Assalamu alaikum,mata da yɗan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yɗan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

11_12

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi
```

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

A cikin asibitin wuri guda ne ya fi ɗaukar hankalina don a can ne na ga duhun inuwar nan dayawa wacce ke mini nuni da Aljanu ne.Ba ko ina ba ne sai wurin da mata ke wanki da kuma shanyar kaya,ƙafata har ƙaiƙayi take wurin isa sai na ga kusan duk wankin kayan jini ne suke irin in mace ta haihu kaya sun ɓace.Na lumshe ido tsawon daƙiƙa biyu kafin na buɗe su na zube su kan matar da take ta faman yin wanki tana rera ƴar waƙa da alamu jika ta samu,inuwa sama da ashirin suke jiran ta zubar da ruwan su sha.

“Mama in kin tsame kayan kafin ki zubar kice Bismillahi” na furta,da sauri ta ɗago tana kallona kamar yadda inuwoyin suka yi.

“To yʻata” ta faɗa ,ban gusa ba sai da ta zubar da ruwan farkon a gabana tare da ambaton sunan Allah.Na saki murmushi tare da yin gaba ganin sun kasa shan ruwan ,sam na manta tare nake da Shafa'atu sai da na ji ta ce “ to mene ne kuma ya faru a can?”

Na juyo na sakar mata murmushi kafin na bata amsa da “ kin san da cewa ko maye bai fi aljani son jini ba? Wannan yasa suke zuwa duk wani wuri da ya shafi zubar da jini,dama kaɗan suke jira su kai farmaki shi yasa ake so a kowane lokaci in za ka soma wani aiki ka fara da Bismillah amma Musulmi da dama suna sakacin nan”

“In kina magana sai na ji kamar ba sautin muryarki ba ne,kuma zantukanki sun girmi shekarunki ” cewar Shafa'atu.

Ban ce da ita komai ba har muka isa ofishin shugaban likitar,sai da na nemi izini kafin na shiga ciki.Bayan na gaishe shi ne na yi masa bayani,nan yake cewa “ ai jiya ne duk malaman jinya suka ida koyon aiki yanzu makarantarku za ki koma” godiya na yi masa tare da fitowa.

Likitocin asibitin sai wani kallo suke yi min kamar dai yadda na ga shugaban nasu na yi .

“Ya kuma haka? Inda sun gama ai na san Shuraim ba zai kawo ki nan ba” cewar Shafa'atu bayan na sanar da ita abin da ke faruwa mun nufo ƙofar fita.

“Na sani sarai da munafurci ne yasa ya kore ni saboda yana tsoron na kawo masa cikas,kin ga asibitin nan duk ahalin MAFIYA(my next book in sha Allah) ne cikinta ,bai san ni babu ruwana da Aljanu ne ba”

“Wai da gaske? Amma mi yasa ba ki maganin Aljanu ?”

“Aljanu da maita abu biyu ne mabanbanta,ki gane mana.Twin ɗina BASHEER shine ke harakar su ”

“Kice dukkan ku ƴan baiwa ne”

“Kai ba wata baiwa sai wahala duk an bi an tauye mini rayuwa saboda da ta wasu” na faɗa ina mai tsayar da taxi,Shafa'atu ce ta sanar da shi inda za mu je kafin mu shiga.Gida muka dawo,ita ta fita ɗora girki ni kuma na fara aiki da wayata.Lambar Ammy na kira muna fara gaisawa kuwa ta ce “ ina Khaleed kwana biyu bai kira ni ba”

“Wallahi sun tafi wani ƙauye mission ina ga kuma babu network a wurin,ina Mama?”

“Ta tafi kitso da lalle”

Na yi ƴar dariya na ce “ kamar wata amarya dai,Mama ce za ta yi lalle?”

“To ai amaryar ce,wani soja za ta aura in sha Allah gobe ake ɗaurawa”

“Wai Mama ce za ta yi aure?” na tambaya da ƙarfi,Ammy ta rufe ni da faɗa har da min gori ba a yin auren ni na yi.A haka dai na kashe wayar.

#GIDAN SAKEENATU

Tamkar wata asibiti haka masu bayar da magani suke shige da fice a kullum dangane da ciwon Ma'idah.Sai dai har yanzu babu canji ta bar faɗa musu cewar

aljanar ruwa ta zo ta tafi da Heesham.Kullum Sakeenatu cikin kuka take Nafisa ce ke bata ƙarfin gwiwa ,yanzu ma ta zo gidan nata ne sun saka Ma'idah gaba wacce ke ta faman dube-dube a ɗakin.

“Ina ga ya kamata a dakatar da masu bada maganin nan,a koma yi mata na Alƙur'ani zalla kawai tun da shi waraka ne akan dukkan matsaloli” Nafisa ke faɗar haka.

Sakeenatu ta ce “ to babu matsala,amma kafin ki tafi ki yi mata ruwan addu'o'in ta sha ta yi wanka”

“To bari na yi mata” cewar Nafisa tana mai tashi ta shiga kitchen ta ɗauko ƙaton bokiti mai murfi.Sai da ta yi alwala sannan ta zo ta soma karatun Alkur'ani a cikin ruwa tana karanto duk ayoyin da suka sawwaƙa.

Sama da minti talatin kafin ta ida,kofi ta cika wa Ma'idah ta bata ta sha.Babu jimawa bacci ya ɗauke ta,Nafisa ta dubi Sakeenatu ta ce “ yarinyar nan har aljanu ba za ta rasa ba”

A cikin baccin da Ma'idah ta samu sai ta tsinci kanta can ƙasan ruwa tare da Heesham,kuka yake yana neman agajinta tare da sanar da ita mugun ayyukan da ya dinga yi a doron ƙasa.Heesham ya kasance tantiri bai ajiye komai ba sai neman mata,matan ma sai masu aure a cewar shi hakan ya fi sirri ko ciki ya fito bai da matsala.Dalilin da yasa Surabiyya ta tafi da shi can ƙasan ruwa kenan don rage mugun iri a doron duniya,a cikin mafarkin take cewa “ na rabu da kai na har abada,babu ni babu kai.Ka tsaya nan ka ci gaba da rayuwarka ni zan koma duniyarmu sannan kar ka sake zuwarmu cikin mafarki ko tunanina ” daidai nan ta farka da tasbihi a bakinta.Ɗakin babu kowa sai ta miƙe ta je ta yi wanka ta canza kaya,duk wani ƙunci da damuwa sun kawar mata ba ta jin matsalar komai a tattare da ita.

Falo ta fito ta tarar da mahaifanta,ta gaishe su tare da yin zaune cike da nutsuwa ta sanar da su mafarkin da ta yi ba ta ɓoye komai ba.Nafisa wacce ta fito daga kitchen ta ce “ dama da yawan mutane suna samun sauƙi ne ta cikin mafarki,kamar yadda wasu kuma ake cutar da su ta mafarkin ta hanyar basu abinci ko kuma maƙiyi yayi nasara cutar da su.Duniyar mafarki nada matuƙar muhimmanci a rayuwa wannan yasa ake son mutum ya dinga lura da irin mafarkan da yake yi don sanin inda rayuwarsa ta dosa”

Ma'idah ta yi murmushi ta ce “ anty Nafisa na gode sosai da addu'o'in da kika bani na sha in sha Allah za su zame mini ruwan sha,in sun ida sai na yi wasu ”

“Hakan shine daidai,in son samu ne ki dinga gamawa da wanka”

Haka suka zauna suna hira Nafisa ta dinga bai wa Agali labarin Mamuh da kuma yƴar uwarta,sannan kuma da wasu labaran da suka shafi ban al'ajabi a haka ne har suka sako zancen FA'IZA .

Nafisa ta ce “ wai ya zancen yƴar aikinki?”

“Wallahi banda labarinta amma in sha Allah zan je har gidansu na duba” cewar Sakeenatu.

“Yanzu in zan koma zan bi ta gidansu,baiwar Allah ita ma sai da ta shiga cikin baƙin tarkon Mamuh ”

“Ai kuwa da kin kyauta na san yanzu ta yi aure har da yƴaƴa ”

Haka kuwa aka yi da Nafisa za ta tafi sai da ta fara zuwa gidansu FA'IZA ,a tsakar gida ta tarar da ita tana suyar awara yayin da mutane suka yaɓe ta suna saya.Kallo

guda Nafisa ta yi mata ta ji wani irin tausayinta ya tsargar mata ,duk uban kyawun nan na FA'IZA da kuma farar fatarta duk sun rage tsabar wahala.

“Awarar za a baki?” FA'IZA ta faɗa tare da ɗagowa da idonta da suke zubar da hawaye tsabar hayaƙin da ya turnuƙe wurin,Nafisa ta ce “ ba ki gane ni ba? Ƙanwar Sakeenatu ce wacce kika taɓa aiki gidanta”

FA'IZA ta waro ido tare da tashi daga kan kujerar da take,sai da ta je ta wanke fuskarta kafin ta ce “ wallahi ban gane ki ba, Allah sarki ashe kina nan? Ke kin yi aure ko? Ina anty Sakeena?” ta jero mata tambayoyin yanayin fuskarta na canzawa.

Nafisa ta zauna kujerar da ƙanwar Fa'izar ta kawo mata kafin ta ce “ eh wallahi! Anty Sakeena ta rabu da Abbas yanzu mahaifin Ma'idah take aure ”

Ta washe baki ta ce “ Allah sarki anty Sakeena,Ma'idah ai yanzu an zama yaran mata ko na ce ma dai uwaye tun da ba yau ba ne”

Nafisa ta dube ta da kyau kafin ta ce “ ke ba ki yi aure ba ne?”

Mai son kuka an jefe shi da kashin awaki mi zai yi? Kawai sai FA'IZA ta soma hawaye tare da cewa “ ban yi ba har yanzu ,kin ga Mamana ma ta rasu ni ce ke kula da ƙannaina,bari na zubo miki awara” ta yi gaba ba tare da ta jira ta ji ta bakinta ba.

Nafisa kuwa waya ta ɗauko ta kira Sakeenatu tana kuka ta yi mata bayanin halin da ta tarar da FA'IZA ,ita kuma ta ce tana zuwa.Ta kashe kiran tana ƙarewa gidan kallo a ko ta ina talauci ne ke magana sai dai babu ƙazanta,awarar ta kawo mata ta karɓa tana godiya.

FA'IZA ta zauna ta soma bata labarin tun bayan rayuwarsu ,a cikin labarin babu na dadi yadda tun saurayinta da ya so aurenta to babu wanda ya taɓa cewa yana sonta.

Nafisa ta yi ɗan murmushi ta ce “ dukkan jarabawa daga Allah take ,ki ƙara haƙuri in da rabon za ki yi auren za ki yi har ki haihu ”

FA'IZA ta ɗan murmursa ta ce “ na gode anty na jima ban samu wanda yayi min magana mai dadi ba irin ta yau”

Suna nan zaune suna hira sai ga Sakeenatu ta shigo ita da Ma'idah,tsabar murna FA'IZA rasa inda za ta sa kanta ta yi.Ita ma Sakeenar sai da ta tausaya mata,da za ta tafi ta bata kudi sannan ta shaida mata in tana so za ta iya zuwa ta ci gaba da yin aiki gidanta.

Wannan ita ce babbar damar da FA'IZA ta samu,tun washegari ta soma yin aiki a gidan Sakeenatu inda take samun albashi fiye da biyu ɗin waccan tun na farko.Sun canza yanayin tsarin komai nasu ita da ƙannanta,yanzu abinci suke yi na saidawa kuma sosai suke cin riba.Sannu a hankali hasken FA'IZA ya dawo haka ma kyawunta.Kafin ta soma aiki sai ta yi wanka ta canza kaya,duk da kuwa tana yin wani a gidansu.

Cikin sauri ta shiga toilet ta soma saɓe jikinta,yau ma kamar kullum haka Agali ya laɓe jikin ƙofar yana leƙen yadda FA'IZA ke wanka.Farar fatar jikinta ta fi komai fizgarsa,har yawu yake hadiya tsabar jaraba.Ita kuwa sam ba ta san yana kallonta ba har ta gama ta yi ɗaurin ƙirji ta fito,turus ta yi tana kallonsa wanda shi kuma shagalar da yayi sosai cikin shauƙi yasa bai farga ba.

“Ina kwana yalaɓai?” ta furta tana ƙanƙame zanenta.Agali bai amsa ba sai mayen kallo da yake bin ta da shi,da wani mugun sauri ta raramo hijabi ta saka tana kallon yadda yanayinsa ya canza.

“Ki dafa min shayi ki kai min ɗakina” ya furta tare da fita,ta bi bayansa da ido tana cewa “ Allah gani gare ka kar ka jarabce ni da abin da ba zan iya ɗauka ba” sai kuma ta fashe da kuka a zuci ta ci gaba da cewa ‘ wato don ya ga na yi jinkirin aure shine yake dubin yar iska ce ni tuni na watse da titi, Allah kar ka nuna min ranar da zan bari wani namiji ya kusance ni’ dakyar ta iya kimtsa kanta ta canza kayan aiki,shayin ta dafa masa amma ta ƙi kai masa a cewar ta in ya matsu zai fito ya nema.Da wannan ta ci gaba da hidimar gabanta har ta kammala komai ta ajiye kan dianing,ƙarfe tara cif Sakeenatu ta fito daga ɗakinta cikin shirin zuwa asibiti.Kan kujera ta zauna ta zuba abinci ta soma ci tana duba wayarta,Agali ya fito ransa a ɓace ya zauna kusa da ita ya soma cin na plate ɗinta.

“Ya dai lafiya ?” ta tambaye shi.

“Da dama dai ” sai ya ja tsuki ya miƙe tare da cewa “ a kawo min shayi” ya faɗi haka ne sanin a kullum FA'IZA ke kai masa shi.

“Dama ba ka sha shayin safen ba? Fa'izaaaa?” ta ƙwala kiranta ,baiwar Allah ta fito da saurin ta tana mai cewa “ na'am anty”

“Ki kai wa Baban Ma'idah shayinsa”

“Ni kuma?” ta furta ba tare da ta sani ba.

“Eh kullum ai ke kike haɗa masa ko? Ko da matsala ne?”

Ta girgiza kai ta ce “ dama ai ga shi nan tun ɗazu na haɗa”

“To ɗauka ki kai masa”

FA'IZA ta ɗauki tray ɗin mai ɗauke da kayan haɗin shayin da kofofi ,ba don ta so ba haka ta shiga ɗakin nasa ya na ganinta ya miƙe yana yi mata wani kallo mai cike da ƙasƙanci.

“Na yi miki kama da wanda za ki wulaƙanta? Daga ke har ahalinku nawa kuke? In na ga dama zan iya ɓatar da ku ko ba ki san waye ni ba?” Agali ke faɗa cikin rashin mutumci.

Jikinta na rawa ta soma basa haƙuri,kafin ta dire tray ɗin kan table,babu kunya ballantana tsoron Allah Agali ya zura hannunsa cikin rigar FA'IZA.Da sauri ta yi baya amma ya damƙo ta ya riƙe gam,idonta na shatatar da hawaye haka ya ci gaba da shafar jikinta yana sauke numfashi kafin yayi cilli da ita kamar wata ƙaramar yarinya.

Da gudu ta fito sai ta tarar tuni ma Sakeenatu ta fice sai Ma'idah wacce take breakfast a tsaye da alamu ta makara.Kitchen ta koma ta ci gaba da kuka,tare da ɗaukar alƙawarin ba za ta sake tsoma ƙafarta a gidan nan ba.....

Assalamu alaikum,mata da yɾan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciya kuma jajirtaciyar mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga ƙasar Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

13

PAID book ne,500 via 2670215530

ZULFAU YAHAYA Ecobank DM +22795045822

Tun da FA'IZA ta koma gida duk sai ta takure wuri ɗaya,sosai take takaicin abin da Agali yayi mata.Hatta ƙannanta sai da suka lura da hakan,don ko abincin da ta kawo yau su ɗaya suka ci ba kamar kullum da suke ci har da ita ba.

A wannan daren bacci sai ya ƙaurace wa idonta,da zarar ta rufe ido Agali take gani yana taɓa sassan jikinta.Sai kusan asubah ta samu baccin ya sace ta,kuma shi ɗin ma ba mai daɗi ne ba don cike yake da abubuwan tashin hankali.A taƙaice dai da firgici ta farka ,wanka ta soma yi kafin ta gabatar da sallah.Tana nan zaune kan sallaya ɗaya daga cikin ƙannanta ta shaida mata ana buƙatar wasu kuɗin jarabawa a makaranta,hankalinta ne ya tashi don aikatau da take yi ne rufin asirinsu.Hatta makarantar da ta mayar da wasu ƙannan nata bayan su Sakeenatu sun zo ne ta mayar da ita a aiki,kai kawai ta jinjina tare da cewa “ to ki ce za a kai” sai kuma ta yi zungum kamar ba za ta tashi ba amma ta aro jarumta ta shirya tsaf cikin shirin zuwa aiki .

Yau sam ko da wasa ba ta shiga toilet domin yin wanka ba,tana zuwa gidan ta soma shara ta goge ko ina sannan ta ɗora shayin ƙaddara da kuma abincin breakfast.

Tana tsaka da yin aikin ta ji an tabki mazaunanta,ta zabura haɗi da juyowa da sauri nan ta yi arba da Agali daga shi sai gajeren wando.Jikinta ya ɗauki kyarma,wanda kuma wannan tsoron shine ya bai wa Agali samun wata dama .Ƙofar kitchen ɗin ya rufe gam har da murɗa key,ƙasa yayi da wandonsa yana nuna mata jikinsa cike da shaƙiyanci yake cewa “ na san ai kin saba ganinta iri-iri a yadda kika tsofe ɗin nan a gida babu kalar namijin da ba ki sani.Zo ki yi min zan biya ki maƙudan kuɗi kuma babu wanda zai sani”

Banda hawaye babu abinda ke sauka daga idon FA'IZA,ko ƙwaƙwaran motsi ta kasa , Allah na gani yau karon farko da ta taɓa ganin halittar namiji babba .Da sauri ta rumtse ido gam hawaye na ci gaba da yi mata shatata,tana cikin haka ne kuma ta ji shi kusa da ita.A dole yake son yin mu'amala da ita,butar da ta ɗora kan wutar gas ta ɗauko da mugun sauri tare da zuba masa ruwan zafi a ƙafafu.Agali yayi wani ihu tare da saurin buɗe kitchen ɗin ya fita,direct ɗakinsa ya wuce yana jin zuciyarsa na ƙuna.

Abun ka da farar fata tuni ƙafarsa ta yi ja jawur kuma wurin ya fara danno ruwa alamun ƙunar dai sai ta fito.Likita ne shi babu buƙatar a sanar da shi komai dangane da lamarin ƙuna,magani ya duba ya sha wanda ya kamata tare kuma da shafa magani.Tsawon minti goma yana a zaune kafin ya ji ciwon ya lafa wata yar ƙaramar allura ya ɗauka ya cika ta da ruwan magani,ransa a ɓace ya koma kitchen ɗin sai ya tarar ba ta nan direct sai ya wuce ɗakinta wanda aka ware mata domin ajiye abubuwanta ko kuma in tana son yin wanka.

A zaune ya tarar da ita ta haɗe kai gwiwa tana kuka,tana jin motsi kusa da ita ta ɗago ta yunƙura za ta tashi kenan yayi saurin danne ta.Duk yadda ta so ƙwatar kanta kasawa ta yi saboda ƙarfin namiji da na mace ba ɗaya ba,allurar yayi nasarar caka mata a damtse ta saki ƙara a haka tana ji tana gani ya ɗura mata ruwan a jikinta.

Sannu a hankali ta soma jin jikinta na mutuwa tamkar wacce ba ta da rai,Agali ya koma gefe yana yi mata murmushin ƙeta kafin ya ce “ sama da mace goma na yi wa wayo sai ke ce mai taurin kai za ki kawo min cikas? Ita kanta uwar ɗakin naki ta

wannan hanyar muka san juna” yana furicin ne tare da raba ta da suturar jikinta,ido kawai ta rumtse don su kaɗai take iya sarrafawa.

Da ƙarfin tuwo dai Agali yayi mata fyaɗe wanda da ace ya san abin da zai faruwa da shi da tabbas ko da wasa ba zai yi kuskuren aikata hakan ba.

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un !” ya ji muryar Sakeenatu daga can bakin ƙofa wacce dawowarta kenan daga asibiti a can ta kwana,da ta shigo gidan ƙaurin ƙonewar girki ne ya tarbe ta wannan yasa ta shiga kitchen ta kashe gas ɗin.Ta buɗe ƙofar ɗakin FA'IZA don yi mata faɗa akan barin gas kunne sai kuma idonta suka yi mata mugun gani ta tarar da mijinta akan yar aikinta suna aikata masha'a.

Furucinta shine ya kusan saka zuciyar Agali bugawa,domin a duniya babu wacce Allah ya jefa masa mugun ciwon sonta irin Sakeenatu.

Da sauri ya janye jikinsa daga na FA'IZA ya mayar da guntun wandonsa ya biyo bayanta,a zaune ya tarar da ita dirshen kan tile tana kuka sai ya rasa ta ina zai soma bata haƙuri.

“Ƙaddara ce Keenat! Wallahi ba yin kaina ba ne kuma ita ce ta ja ra'ayina” Agali ya furta,ta ɗago ta dube shi da jajayen idonta kafin kuma ta miƙe a zafafe ta koma ɗakin FA'IZA .A yadda ta shiga da zafin rai nufinta ta ci mutumcinta amma halin da ta tarar da ita ne yayi mugun tayar mata da hankali.Tamkar an kunna pampo haka jini ke zuba a ta jikin FA'IZA ,hankali tashe ta kara yatsunta kusan hancinta sai ta ji ba ta numfashi.

Ta fasa wani uban ihu tana cewa “ na shiga uku ya kashe ta” sai kuma ta soma bata duk wani taimako amma ga banza,hatta shi kansa Agalin sai da ya bada nasa agajin amma amsa guda suka samu FA'IZA ta mutu babu sauran numfashi a tattare da ita.

Idon Sakeenatu ne suka ƙeƙyashe hawayen suka tsaya cak,cikin wata irin murya take jerowa Agali tambayoyi “ kace ita ta ja ra'ayinka? Wannan ko mahaukaci ya gani ya san fyaɗe ka yi mata.Ka san mi hakan ke nufi? Ka san mene ne wannan? Laifi biyu,ga na fyaɗe ga na kisan kai a matsayinka na likita mai ceto rayukan mutane wane irin hukunci kake gani ya dace da kai?” bai iya bata amsa ba sai kuka da yake yi wiwi yana roƙon ta rufa masa asiri,wanda kuma sautinsa ne ya jawo hankalin Ma'idah wacce fitowarta kenan daga ɗakinta.

Turus ta yi tana zarar idanuwa yadda ta ga FA'IZA cikin jini da kuma furicin da mahaifiyarta ke ta faman nanata wa yasa ta ɗan fahimci wani abu,ta rufe ƙofar da sauri ta fita a guje kamar wata mahaukaciya haka take gudu saura ƙiris a kaɗe ta amma cikin ikon Allah ta samu adaidaita ta shiga tare da sanar da shi police station za kai ta.Har zuwa wannan lokacin Ma'idah ba ta yi kuka ba,abun da ta gani kawai ke juya kwanyarta .Suna isa ta dire ko kuɗin ba ta biya ba ta shiga ciki,sai a lokacin ta ji wasu hawaye na zubo mata masu zafi.Cikin kuka ta soma yi musu bayanin abin da ke faruwa,cikakkun minti biyu ba a ƙara ba aka ɗauke ta cikin motar ƴan sanda suka isa gidansu.

Ita ke gaba suna take mata baya har ɗakin FA'IZA ,sam Sakeenatu ba ta firgita ba da ganin ƴan sanda don ko da ace Ma'idah ba ta kira su ba ita kanta ba za ta taɓa barin jinin FA'IZA ya tafi a banza ba.Sai da suka yi wasu ƴan ɗauke-ɗauke na hotuna kafin a tafi da gawar FA'IZA wacce zuwa yanzu duk illahirin jinin jikinta ya ƙare kaf.Agali kuwa tuni an tisa ƙeyarsa an wuce da shi,dakyar Sakeenatu ta iya lalubo wayarta ta kira Nafisa ta ce kawai ta zo gidanta.A yadda ta ji yanayin muryar ƴar uwarta sam sai hankalinta ya ƙi kwanciya ta fasa zuwa makaranta ta nufo gidan,a jungum ta tarar da su kowacce ido suntum da alamu sun sha kuka.Ita Ma'idah sai da ma Sakeena ta saka mata ƙarin ruwa.

“Zan iya sanin meke faruwa a nan?” cewar Nafisa.

Tamkar ta ƙara rura mata wutar da ke azalzalar zuciyarta kawai sai ta ƙara fashewa da matsananci kuka tana cewa “Nafisa na tsani kaina,kullum cikin ganin masifu iri-iri nake.Auren farin na haɗu da sharrin mayyar suruka yanzu kuma ɗan iskan miji,ko da yake ma laifina ne ai na san da fasiƙi ne amma na aure shi”

“Me ya faru don Allah?” Nafisa ta sake tambaya hankali tashe, Sakeenatu kasa bata amsa ta yi saboda numfashinta da ya danne zuciyarta,sai Ma'idah ce cikin kuka ta ce “Daddy ne ya yi wa FA'IZA fyaɗe kuma ta mutu”

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un ! Ya Rabb in dai bacci nake ka yi gaggawar tashe ni daga wannan mummunan mafarkin.Wace Fa'izar? Wai Agali ? Fyaɗe kuma?” sai ita ma ta soma kuka.

“Yʼan sanda sun tafi da shi,ita kuma an wuce da ita asibiti sun ce zuwa gobe za su zo su tafi da mu domin yi mana tambayoyi” wannan karon Sakeenatu ce ta faɗa tana wani irin huci,dakyar Nafisa ta aro jarumta tare da ɗauko kofin ruwa ta karanta Fatiha ƙafa bakwai ta bai wa antynta ta sha ,domin Suratul Fatiha na maganin duk cutar zuci.

Ita ma cikinsu ta zauna duk suka yi jungum kowa da abin da yake tunani kafin kuma wani abun ban al'ajabi ya soma faruwa,bango ɗakin Agali ne ke tsagewa da kansa yayin da ya soma rushewa dukkan bulo na bajewa.Duk wani abu da ya shafi kwalba kuwa ji kake rasss yana tarwatsewa,hatta TV da ke manne a bango haka ta zama gari liƙis babu shiri suka ari na kare.....

Jummah MUBARAK.Ga posting ɗinku na gobe

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁 Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

14

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉
```

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Dakyar Sakeenatu ta ƙara shiga ɗakin ta ɗauko musu abubuwan buƙata ita da Ma'idah.Tuni dai ɗakin Agali ya zube iya shi kaɗai,mai gadi babu yadda bai yi ba wurin bata haƙuri amma haka ta ja yꞌarta da ƙanwarta suka bar gidan.

Mama baiwar Allah kasa cewa komai ta yi,duk da tana tausayin Sakeenatu amma haka ta daure ta ce “ su kuma ƙannan Fa'izar fa kun sanar da su?”

“Tukuna dai Mama,sai yꞌan sanda sun gama bincike” cewar Nafisa .

“Ya kamata a sanar da su tun da haƙi ne,sannan ya zama dole gare ki Sakeena ki ci gaba da kula da su.Sannan ki shaidawa dangin ɗan iskan mijin naki,ko da yake ma babu buƙata don kashe shi za su yi ”

Sakeenatu wacce idonta suka kumbura suka kuma yi ja ta dubi Mama tare da yin wani murmushi wanda ya fi kuka ciwo kafin ta ce “ Mama har yanzu ba ki san waye Agali ba,ai wannan shari'ar babu inda za ta je za su sake shi.Na sani sarai family ɗinsa nada ƙarfin iko a Nijar babu wani haƙi da za su ƙwatar wa FA'IZA .Allah dai ya jiƙanta ya kuma nuna mana ranar hisabi” sai kuma ta fashe da kuka dukkansu babu wanda bai zubar da hawaye ba,ita Ma'idah a ƙarshe ma sai da aka yi mata allurar bacci.

Nan Nafisa ta wuni tare da su kafin ta wuce can gidansu FA'IZA ,ashe tun tuni yan sanda sun kawo girgiza gidan yadda ta tarar ana ta koke-koke yasa ta fahimci tuni sun san da mutuwar ma.Gidanta ta wuce cike da jimami,haka ta kwana cikin wannan zullumi kamar dai yadda su Sakeena ke ciki .

Tun washegari da safe Sakeenatu ta je can police station ta amsa tambayoyi game da Agali ,ko kaɗan ba ta yi ƙoƙarin ɓoye ko da gaskiya guda ba ce .Ita ma Ma'idah an yi mata tambayoyi,sai a lokacin kuma yan sanda suka bada izinin bai wa dangin FA'IZA gawarta.

Da Sakeenatu ta je gidan makoki suka soma zaginta tare ci mata mutumci amma ko kaɗan ba ta ji ciwo ba,duk wani abu da ya kamata sai da ta yi shi.Tun daga abinci har ruwan da za a sha,ganin dai da gaske ba ta goyon mijinta sai suka sassauta tsanar.Tuni kuwa an kai FA'IZA gidanta na gaskiya,yanzu abin da ya rage kawai shi ne zartar da hukunci wanda yan uwanta suka yi tsaye daram kan cewa ba su yarda da duk wani hukunci in ba na kisan Agali ba.

An zaman Shari'a sau biyu a kotu,mahaifiyar Agali ita ce kan gaba wurin ɗaukar masa lauya duk da kuwa da farko Agali ya amsa laifinsa amma yanzu fafur ya ƙi.Jami'an tsaro kuwa ganin shari'ar na ta ƙara girma yasa suka haɗa takardun suka miƙa su can babban birnin Yamai.

#GIDAN DADDY

Cikin ikon Allah Safeenatu ta ƙara samun mijin aure,babban mutum ne don ya kusa kai wa sa'an Daddy.An ɗaura aure amarya ta sha ƙunshi da kitso,sosai kuma Ammy ta yi mata gyara kafin a yi mata rakiya zuwa gidanta.Ita ɗaya ce a gidan sauran kishiyoyinta ma nasu gidan daban, wannan yasa ba ta fuskanci matsalar komai ba.Cikin farin ciki suke mu'amulantar junansu duk da kuwa ba wata zurfafiyar soyayya ce take masa ba amma suna zaman lafiya cike da fahimtar juna.

#YAMAI

Yau kusan sati guda da aka rufe Yaya Khaleed,duk yadda nake ta ƙoƙarin kawar da damuwa abun ya cuttura.Ga dai abubuwa dayawa da ke jirana waɗanda ni ce zan warware su amma sam abun ya fita raina,kullum sai Bafulatanata ta fito min amma haka za ta yi surutunta ta ɓace.

Yanzu ma ina kwance ina kallon hotunan Mama na ranar walimar aurenta kawai kamar daga sama na ji muryarta “ SEERAT mi kike nufi? Tun yaushe na nuna miki duk abubuwan da za ki yi ta mafarki? Ba za ki yi ba ne ko me ?”

A hankali na ɗago na dube ta kafin na mayar da dubana ga wayata,sululu na ji wayar ta fita hannuna ta koma kan table.

Na tashi zaune babu tsoro ko shakka na ce “ ba fa zan sake yin komai ba sai kin maido min mijina,na gaji da wannan halin kullum ni ke yi wa mutane hidima sam banda lokacin kaina haba!”

“Amma ai bayan wuya sai daɗi”

“Ba fa zan yi ba,kin ga karɓi sarƙarki ita ma ban so” na faɗa ina ƙoƙarin cire sarƙar a wuyana amma tamkar a tare aka haifo mu ta ƙi fita.

“Zai dawo ! Tun da hakan kike so ai shikenan!” tana gama faɗa ta ɓace .

Na je na ɗauki wayata na ci gaba da dannawa, Shafa'atu ta yi sallama ta shigo tare da ajiye min abinci a gabana.

Haushi ta bani sai nake jin duk a kanta ne mijina ke cikin matsala,na ja tsuki tare da tashi na shige bedroom na ƙyale ta nan.Kan bed na haye na soma kuka kamar yau ne aka kawo ni ina amarya.

Sama da awa ɗaya nake kwance duk abubuwan da suka faru da ni suna dawo min ina mai ci gaba da yin hawaye.

“ SEE...RAH!” na ji sautin muryarsa kamar a mafarki,na zabura na tashi zaune ina kallon Yaya Khaleed ya jingina ga katanga kusan ƙofa.Hannuwansa ya buɗe min,da sauri na diro daga kan bed ɗin na je na shige jikinsa.

A tare muka sauke ajiyar zuciya kafin ya lalubo bakina ya soma yi min kissing mai tsayawa a rai.Tsawon lokaci yana shayar da ni yawunsa kafin ya ja ni izuwa bed,shi ya zauna sannan ya ɗora ni kan cinyarsa sai ya tsura min ido.

Sajensa da ya soma fitowa na soma shafawa ,murya na yɤar rawa na ce “ Yaya...Na yi kewarka...kuma...kuma ” sai na yi shiru.

Ba tare da yayi magana ba ya ja zip ɗin rigata ta atamfa yayi cilli da ita kafin ya ƙurawa ƙirjina ido na wani lokaci kafin ya lumshe ido.Hawaye na ga suna yi masa zuba,muryarsa ba ta fita sosai ya ce “ ina sonki SEERAT ! Na yi kewarki fiye da kalmar keya,a kwanakin da na yi ba tare da ke ba ji nake kamar shekaru ne.Wallahi duk a takure nake a can,ga tsananin buƙatarki da nake.Haka nake kwana cikin kaɗaici sai dai na yi ta tuna daron farkonmu a haka nake samu na yi mafarki in ɗan samu sauƙin wutar feeling ɗin da ke dabaibaye da ni ” magana yake cikin haƙiƙanin gaskiyarsa daidai saitin zuciyarsa sai wani bugawa yake.Da hannu na soma goge masa hawayen,yana buɗe ido kuma sai na tsaya muna kallon juna tsakiyar ido .

A hankali ya ɗora kansa tsakiyar ƙirjna yana sauke numfashi kafin ya dinga bin ko ina nawa yana sumba.Yau salon wasannin daban suke,kan bed ya shimfiɗe ni bayan ya cire zanen jikina ya bar ni daga ni sai pant.Rumfa yayi min da ƙirjinsa ya soma yi min raɗa a kunne ta zazzafan kalaman soyayya masu ɗauke da kalmomi na tsantsar jin kunya,ido kawai na lumshe ina jin wani abu na tsarga min.Ya zautar da ni sosai ta yadda ban ma san lokacin da ya cire tasa suturar ba,da farko kuka na soma yi masa kafin kuma na yi shiru da ya soma bi na a hankali.

Sama da minti talatin kafin ya mu dawo hayyacinmu,kan ƙirjinsa ya ɗora ni yana cewa “ yunwa nake ji My Zuma”

Shiru kawai na yi ban basa amsa ba,don ni ma yunwar nake ji tamkar babu hanji a cikina.Sukutata yayi zuwa toilet,dakyar na iya tsayuwa kan ƙafafuna muka yi wankan muka fito muka shirya.Hannuna cikin nasa muka fita falo,gabana ya faɗi rasss ganin Shareef zaune kan kujera fuskar nan tasa a murtuƙe.

Yaya Khaleed ya saki hannuna yana cewa “ abokina yaushe ka zo?”

Sai da ya kalle ni kafin ya ce “ na kai minti ashirin,ina zuwa can Shuraim ke sanar da ni ai an ce a maido ka gida kuma matar ta tashi ta sanar ba kai ne ka cake ta ba”

Khaleed ya saki murmushi ya ce “ eh wallahi ai tuni shi ma wancan a sake shi ko?”

“Ban sani ba ni ma,ita matarka ba ta san ta gaishe da mutane ba?” Shareef ya faɗa yana tsure ni da ido,na kawar da kai gefe ina jin takaicinsa.

“Baby zo ki gaishe shi mana ” cewar Yaya Khaleed.

“Yunwa nake jiii!” na faɗa a shagwaɓe kamar zan yi kuka ina kwaɓe fuska,da sauri ya iso gare ni.Abin da na fahimta shagwaɓa na zautar da Yaya Khaleed,tun kafin walimar aurenmu muddin zan dinga yi masa shagwaɓa to sai ya keɓe da ni.

Cike da iya shege na ci gaba da yin shagwaɓar ina wani ririƙe shi,shi kuwa bawan Allah sai ƙoƙarin hana kansa yake shiga shauƙi yana daidai nutsuwarsa.

Na ɗan faki idonsa na saci kallon Shareef sai na ga kuwa mu yake kallo,cikin ƙirjin Yaya Khaleed na shige tare da fashe masa kuka murya ƙasa-ƙasa na ce “ ni yunwa nake ji,kuma ni mu ci abinci mu koma ɗaki wajen kwana nawa ba mu yi abin nan ba? abin da aka ce wuni guda ake ana abu ɗaya shine amma kai ka kwaso abokinka kuka zo”

Wannan karon kuwa sam Khaleed kasa controling kansa yayi,muryarsa tuni ta canza ya ce “ Baby ki yi haƙuri yanzu zan nemo abincin sai mu ci ,da gaske kina son mu yi second round?” a yadda na lura ma kamar ya manta Shareef na nan.Ni kuwa

tsabar rigima irin tawa yunwar ma ji na yi ta ɓata,kamar wacce aka yi wa allurar shaƙiyanci na soma shafarsa har wurin da bai kamata ace na taɓa ba tun da na san dai ba mu biyu ne ba a ɗakin.

Wani sauti Yaya Khaleed ya fitar ya soma mayar min da martani,jikinsa har rawa yake.Da ido ɗaya nake kallon Shareef ya miƙe ya fice,na ɗan janye ina cewa “ mu ci abinci Yaya” na faɗa da ɗan ƙarfi.

Yaya Khaleed ya dube ni da rikatatun idonsa ya ce “ wallahi yanzu ban jin ta,duk kin susuta ni ” ya faɗa yana ƙoƙarin kai hannu jikina amma na yi saurin janye wa na buɗe plate ɗin da ke kan table.Abincin da Shafa'atu ta girka ne,haka na zauna na soma ci amma shi sam ya kasa ci.Fahimtar fa abin da yake nufi yasa na ji tsoro don na gaji sosai,sai na yi masa tuni da Shareef na ce “ wai ina abokinka?”

Shi ma da dukkan alamu ya manta da shi,kai ya dafe kafin ya ce “ duk laifinki ne Baby ”

“To ka kira shi mana ,ko kuma ka je wurinsa”

Wani kallo ya tsaya yi min wanda yasa na haɗiye yawu muƙut,sai kuma na soma cin abinci a hankali amma duk wannan ba ta fishe ni dare ba don kuwa tarkon da na ɗana ni ce da kaina ya damƙe,sai da Yaya Khaleed yayi second round ɗin nan.Sai da ya gamsu hankalinsa ya kwanta ya fita ya sayo mana kaza da soyayen dankalin turawa sai kuma fruits,sosai na ci na ƙoshi har sai da na yi mamakin kaina shi kuwa Yaya Khaleed daɗin haka ya ji.

A tare muka wuni manne da juna sallah kawai ke raba mu,sai bayan sallar asar sannan ya fita shi ma bai wani jima ba ya dawo.Duk yadda na so na yi mana girki hanawa yayi,da dare shirya wa muka yi tsaf muka tafi restaurant cikin motar Shuraim don shi ya zo ya ɗauke mu.

A bakinsa ne muka ji cewa wai Shareef yayi fushi ya zo gidanmu mun yi masa wulaƙanci.

“Mene ne kuka yi masa don Allah? Wallahi har da kuka yayi fa,ya ce kun yi masa wulaƙanci amma bai faɗa min ba ya ce na tambaye ku ” Shuraim ya faɗa yana murmushi.

Khaleed ya girgiza kai kawai,yana ganin Shareef da daraja fiye da tunani duk wata hanya da za ta kawo musu saɓani yana guje ta.Sam bai damu ba don an ce masa yayi fushi don ya san da dama abokin nasa bahaggon mutum ne.

“Please ka sanar da ni,ko na tambayi matarmu?” yayi furicin yana kallona Yaya Khaleed ya girgiza min kai alamun kar na sanar da shi,dama ko bai ce ba ai ba zan sanar ɗin ba tun da ina jin kunyarsa.

Haka muka ci abincin muka soma yin hira duk da ni jefi-jefi ne nake tsoma bakina,sai da dare yayi sosai sannan muka baro wurin.Shuraim ya sauke mu ,a yadda na ga haske a sashen Shafa'atu na fahimci yau dai ta haƙura ta zauna ɗakinta.Muna shiga na ɗumama ruwa muka yi wanka,ni da nake tunanin bacci za mu yi sai Yaya Khaleed ya fahimtar da ni shi wannan aikin ladar ya fi komai yi masa daɗi sannan a wannan daren ne na fahimci mijin da na aura.

Washegari ko da na farka duk jikina ciwo yake,shine ya haɗa mana ruwan wanka .Bayan mu yi sallah na fita na haɗa abin breakfast sannan na zo na shirya cikin uniform ɗin makaranta,shi ma tsab ya shirya cikin kayan yɘan sanda .Muna cin abinci na ji suna waya shi da Shuraim yana cewa ya zo ya ɗauke mu.

Bayan ya ajiye wayar na ce “ Yaya kai ma ka sayi mota mana ,ya fi a ce kullum sai ka jira abokinka ”

Ya ce “ SEERAT ina na ga kuɗin sayen mota? Su ma da kike gani duk yayan masu kuɗi ne, musamman ma Shareef.Ki taya ni addu'a na samu kuɗin saya mana gida kin ga sai mu huta da yawon haya”

Na ce “ yawwa dama ina son mu tashi daga gidan nan wallahi”

“Abin da ya zama dole,ina mu ina haya gidan mayya”

Na tuntsire da dariya na ce “ mun fi ƙarfinta can ta ci kanta”

Murmushi kawai yayi,sai da Shuraim ya zo sannan muka fita.A baya na zauna yayin da shi kuma Yaya Khaleed ya zauna kusan direba.

Har cikin harabar makarantar Shuraim ya shiga tare da yin parking,Yaya Khaleed ne ya fito ya buɗe min yayi wani tsaye ƙiƙam ya tare min ƙofa.Na ziro ƙafa na fito dakyar,na turo baki na ce “ to ka matsa na wuce ko?”

“Ki kula min da kanki” yayi furicin yana saka min kuɗi a tafin hannuna,kafin ya koma mota yana kallona.Na ɗan yi baya,sai da motar ta fita daga harabar makarantar sannan na wuce ajinmu sanda sau ɗaya kawai na taɓa shigarsa.

SHAREEF

Tsakanin ƙiyayyar SEERAT da kuma sha'awarta sai ya rasa wane ne yake yi mata.Shi dai abu guda ya sani,tun can farko ya fi son ace duk abin da Khaleed zai yi ya zama a tare su biyu suka yi shi sannan ya nemi shawarsa kafin aiwatar da komai.Tun jiya da abin ya faru ya kasa sukuni,duk da ya shaidawa ɗaya abokin nasa cin mutumcin da su SEERAT suka yi masa amma har yanzu yana jin takaici da raɗaɗi a azuciya,wanka kawai yayi ya zube cikin luntsumemen gadonsa ya lumshe ido yana ƙiyasta abubuwa da yawa a ransa ga shi nan shi da SEERAT suna kissing da sauransu.Ya ja tsuki yana jin haushin kansa,a fili ya furta “ na tsane ki! Sai na yi silar cilla rayuwarki cikin ZAWARCI wallahi sai ya sake ki kawai hankalina zai kwanta.Shi ma munafiki ɣar ficiciyar yarinya yake ɗauki ya kasa tsaye ballantana zaune,tsabar jaraba daga fitar da shi har neme ta mtsww !” ya ja dogon tsuki tuna irin sautin da kunnuwansa suka zuƙo masa a jiya.Tsabar takaici ya ɗauki wata kwalba mai ɗauke da furanni ya tarwatsa ta ga ƙasa ta fashe,an yi katari kuwa Daddynsa ya shigo ya same shi cikin wannan hali.....

Assalamu alaikum,mata da ɣan matan garin Agadas.CHAFA'ATU MAKE-UP fitacciyar kuma jajirtaciya mai koyar da kwalliya iri-iri.Ta yi tattaki tun daga Nigeria ta zo nan Nijar a garin Agadas domin horar da masu buƙatar koyon kwalliya,ɗaurin kallabi.Wannan horar wa da za a yi za ta kwashi kimanin sati biyu ,kuɗin koyo jika ashirin ne (20.000f).Ga masu buƙatar ƙarin bayanin za su iya kiranmu kai tsaye ta wannan lambar 88584336 ,ko kuma ku tuntuɓe mu lambarmu ta WhatsApp 09041604348 .

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

15_16

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍
```

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Mahaifin Shareef yayi saurin isa inda yake yana mai tambayarsa “ lafiyarka kuwa Shareef? Wannan ɗin duk na mene ne?”

“Babu komai DADDY wata yarinya ce ta ɓata mini rai amma komai ya wuce ,zan shiga wanka zan same ka can wurin aiki” Shareef ɗin ya faɗa tare da tashi ya nufi toilet.

Daddynsa ya ce “ ai kuwa dai ka yi sauri ka isa akwai wani case da aka turo mana daga Zinder wani ya yi wa yar aikinsa fyaɗe kuma ya kashe ta”

“Fyaɗe da kisa duk lokaci guda? Amma wannan an yi riƙaƙen ɗan iska,bari na yi sauri na yi wanka” yana gama faɗa bai jira cewar mahaifinsa ba ya shige Toilet ɗin.Bahon wanka ya cika ya shige tare da yin lamo,haka wani banzan tunaninsa yake kawo masa ‘ ina ma ace kai da SEERAT ne cikin ruwan nan tana saman ƙirjinka kuna wanka?’ ya ja tsuki a fili in akwai wacce ya tsana a duniya a yanzu to bayan SEERAT take.Cike da takaici yayi wanka ya fito,kamar marar rai haka ya shirya cikin kayan yan sanda ya ɗora hulla tare da feshe jikinsa da turare sannan ya fito yana tsamin rai.

Ko breakfast bai tsaya yi ba ya wuce harabar gidansu ya ɗauki motarsa,yanzun ma yana tuƙi tunanin SEERAT na kawo wa kwanyarsa farmaki har ya isa can wurin aikin nasu.

Motarsa da ta Shuraim kusan lokaci guda suka shigo,sarai ya gan su amma sai ya wani share su bai tsaya ba ya wuce ciki yana hurar hanci.

Shuraim yayi dariya yana duban Khaleed da ya rufe murfin mota ya ce “ abokina wannan karon fa ka yi ƙololuwar fusata amini”

Khaleed ya saki murmushi ya ce “ za mu shirya ai” sai su ma suka wuce ciki,gaishe da Ogan nasu suka yi kafin su ma su ƙame wuri guda suna sauraren faɗan da yake yi wanda in da sabo ya ci ace sun saba Daddyn Shareef irin shuwagabin nan ne da sam ba a yi musu daidai,kullum cikin yi wa na ƙasa da shi masifa yake kuma duk suna mugun tsoronsa in ka cire Khaleed wanda sam gubar tsafin Daddyn ba ta kama shi ba.

“Za a kawo mana wani ɗan iska yau abu na farko da za ku yi shine ku tabbatar ya amsa laifinsa kafin safe,ban so a yi kuskure ko ɗaya ina son ganin cewa wani station ɗin tamu ita ce ta fi kowacce stations da ke Yamai fatan kowa ya fahimta?”

“Eh Yalaɓai!” suka amsa a tare,shi kuma ya ce “ in sauran sun zo ku sanar da su,ku kuma yɓan uku ku zo ina son ganin ku ofis ɗina” yana gama faɗa yayi gaba yayin da su Khaleed ke kallon Shareef da ya nemi kujera ya zauna alhalin sarai ya ji abin da shugaba kuma mahaifinsa ya ce.

Shuraim ne ya je ya ɗauke fayil ɗin gaban Shareef yana mai cewa “ sai ka bari in mun amsa kiran oga sai ka ci gaba da aikin rainin hankali kawai,an ce maka nan gidanku?” sai kuma yayi gaba ya take wa Khaleed baya,shi ma bai da zaɓi haka ya miƙe ya isa.

Daddy ya zuba musu na wani ɗan lokaci,kafin ya ce “ Shuraim za ka iya faɗa mini meke faruwa a nan ?”

“Eh to yʻar matsala ce kawai ƙarama Daddy shine fa suke ta yin fushi kamar wasu yara” cewar Shuraim wanda a yanzu shi ne a tsakiyar abokan biyu.

Daddy ya girgiza kai ya ce ,“ dama na san tun da na ga Shareef cikin fushi to tabbas ɗaya daga cikinku ne ya samu saɓani da shi amma don shashanci ya ce min wata yarinya ce.Ku yi niyya ku biyun nan kuma ku fitar da matan aure kafin sabuwar shekara don wallahi mission zan tura ku ta wata biyu,kuma in kun dawo kun soma zuwa ta wata guda kenan a haka ne za ku san ciwon kanku.Ku fita ku ban wuri” ya faɗa yana hararen su.Har sun kai bakin ƙofar ya ce “ kuma don Allah kar ku shirya ku yi ta zama a haka kun fi kyau”

A tare su ukun suka saki murmushin da ba su shirya ba,Shareef ya bangaji Khaleed da za su fita har na mai buguwa da ƙofa.“Da wani baƙi nasa sai ka ce tukunya ”

“Eh na dai ji ai ya fi ace ina da fari irin na zabaya(Albino)” Khaleed ya mayar da martani cikin raha,Shuraim ya ce “ wato ba ku ɗauki shawara Daddy ba hahaha! Kai abin nan bai yi min daɗi ba zan ƙara komawa bare a cikinku ” nan ma duk sai suka hau dariya tare da soma yin hira kai kace ba su ne suka shiga suna tsamin rai ba.

Shareef ya zauna kan kujera yayin da su kuma su biyu suke a tsaye, tattaunawa suka soma akan case ɗin da ke jiransu yau kowa na faɗar albarkacin bakinsa kafin kuma su rabu zuwa aikin da ya kamata.

Wuraren ƙarfe biyun rana motar yʻan sandar Zinder ta dira a station ɗin,fitowa suka yi da Agali har zuwa tsakiya ofishin.Khaleed ya karɓi fahil ya shiga dubawa yayin da kuma Shuraim ya je ya sanar da oga criminal ya iso.Tsawon lokaci kafin ya fito tare da bai wa yaransa umarni a wuce da Agali ɗaki na musamman a kuma kula da shi.

Cikin ƙanƙanen lokaci wurin ya ɗauki ihun Agali don dukansa suke yi kamar Allah ya aiko su,amma saboda taurin kai ya ƙi amsa laifin.

Yʻan uku suka shiga ragar da aka aje Agali farar fatarsa ta yi baƙi saboda buguwa.Ido Khaleed ya tsura masa kafin ya ce “ mene ne yasa ka aikata babban zunubi haka? Ka san hukuncin zalunci a wurin Allah kuwa? Shine kuma kake ci gaba da ƙaryata wa kan cewa ba ka aikata laifin ba,kana tunanin akwai lauyan da zai kuɓutar da kai ne ga shari'ar da ta shigo hannun oganmu? To ka makaro ka fara lissafin kwanakinka da za ka yi a duniya don kashe ka za a yi”

Cikin kuka ya ce “ don Allah ka taimaka mini ka sa a yi min sassauci wallahi ba da niyyar kashe ta na yi ba”

Khaleed ya saki murmushi tare da dakatar da ɗaukar da yake da abin naɗar sauti,ya ce “ madallah da bayar da amsa daga bakinka, za mu tura ka can kotu mu gabatar da recodin nan domin yanke ma hukuncin ɗanyen aikin da ka aikata ”

Agali yayi shiru yana kallon Khaleed kafin ya ce “ ka san wane ni ? Ka san su waye iyayena? To ina mai tabbatar maka da sai na fita daga hannunku banzaye” Khaleed ya ɗauke shi da wani gigitacen mari yana shirin kai masa naushi Daddy ya shigo yana mai dakatar da shi .

“Ku ƙyale shi bai da laifin komai,kai kuma taso ka biyo ni” Daddy ya faɗa kafin ya fice,dakyar Agali ya miƙe yana layi har ya bi bayansa ɗin.

Cike da mamaki Khaleed ya dubi abokan nasa sai ya fahimci su tuni sun yarda kan cewa eh bai da laifin.Duk yadda ya so kwatanta musu sun ƙi ganin abin da yake son nuna musu a ƙarshe ma Shareef cewa yayi “ ka ga tun da ka ji Daddy ya ce ba mai laifi ba ne to kawai haka ɗin ne,kuma kai ɗin ai shaida ne akan duk wata Shari'a da Daddy ya faɗi haka har abada ba za a yanke hukuncin da ba shine ra'ayinsa ba”

Shuraim ya ƙara da “ eh tabbas kuwa zancenka haka ne,Khaleed kawai ka share dama dai ina ce Daddy ne ya bamu umarnin gudanar da case ɗin nan to yanzu kuma tun da ya janye ai shinenan”

“Haka ne!” shine kawai abin da ya iya faɗa ,haka suka ci gaba da sha'anin aikinsu ba wai don ya gamsu ba.

SEERAT

Tun da na shiga aji na zube jikin banci na soma jin bacci,duk a gajiye nake dole ce ta saka ni zuwa makarantar.Daga inda nake na hango Bafulatana tana yamutsa fuska,“ ai mijin naki ya dawo ko? Da shegiyar jarabarsa kike tunanin za ki iya cimma burinki? Ai sai ki gani tun da kin ƙi saurare na” ta faɗa .

Takaici ne ya rufe ni na maida fuskata ɗaya ɓangaren amma tun tuni ita ma ta dawo nan ɗin tana mai ci gaba da yi min dariya amma ban kula ta ba .Da ta gaji ta tafi don gaban kanta,duk wani darasi da aka yi mana ban wani gane shi ba dama-dama ma wanda aka yi bayan mun dawo daga shan iska na ci abinci da ruwan sanyi.Sai ƙarfe uku na maraice muka tashi,a gajiye na tsayar da taxi ta kawo ni gida.Nan ɗin ma ba hutu ba ne girkin dare na ɗora bayan na gama na ɗora ruwan ɗumi na yi wanka na shirya,ana shirye-shiryen kiran sallar magrib Yaya Khaleed ya dawo daga aiki.

Sannu da zuwa na yi masa tare da haɗa masa ruwan ɗumi na wanka,ko da ya fito tuni an soma kiran sallah.Jallabiya ya saka ya wuce masjid ni kuma na yi tawa a gida,bayan na gama na ɗauki uniform ɗinsa zan wanke kenan ya shigo yana wani rungume ni.

“Zan wanke ma kaya ne” na faɗa .

“Ki ajiye har ki fara wanke ni please ” ya furta.

Na yi murmushi mai ɗan sauti na ce “ kamar ba yanzu ka yi wanka ba? Mu je na zuba ma abinci”

“A'a ni ke nake so mu je ki ji da ni in mun gama zan ci abincin daga baya”

“Yaya Khaleed don ka bar ni haka Allah duk a gajiye nake,yau ma da na je makaranta ban yi wani abun kirki ba” na faɗa kamar zan yi kuka .

Kayan hannuna ya karɓe ya zubar kafin ya ja ni izuwa ɗaki,wasu hawayen tausayin kaina ne suka zubo min.Duk yadda yayi ƙoƙarin na basa haɗin kai ƙiyawa na yi

saboda ban so,shi kuma bai fasa ba haka ya mu'amulance ni ina ta kukan azaba sam abin babu armashi.

Na yi tunanin zai rarrashe ni ne amma sai ya janye jikinsa na wani ɗan lokaci kafin ya sake zuwar min a karo na biyu.Wannan kam kasa yi masa biyayya na yi na tashi da mugun ƙarfi har ina shirin faɗuwa a ƙoƙarin sauka daga bed,ya cabko ni tare da banƙare ni ina kuka ina ƙari ya biya buƙatarsa kafin ya shige toilet ya bar ni nan kwance.

Da ya fito ɗin ma bai min magana ba ballantana rarrashi kaya kawai ya saka ya fice zuwa falo ya kunna tv tare da ƙure volum ƙila don kar ma ya jiyo sautin kukana.

Dakyar na iya tashi ba je na tsarkake jikina,ɗaure da towel na fita can waje na ɗora ruwan zafi bayan sun tafasa na juye su a bokiti na koma can toilet na gasa kaina da kyau sai na ji ɗan dama.Alwala na ɗauro sannan na fito,doguwar riga na saka da hijabi na gabatar da sallah isha'i.

Da na fito falo ba ya nan sai plate ɗin da ya ci abinci,na zauna na zuba ni ma na ci ina tausayin kaina domin kuwa shekaruna sun yi ƙarancin ɗaukar nauyin buƙatar Yaya Khaleed.Ba don tun kafin a yi walimar aurenmu na san shi da shegen ƙulafuci da fitina ba,tabbas da zan iya cewa sharrin Bafulatanata ne.

Ina nan zaune ya shigo shi da Shareef,raina ne ya ɓace wato shikenan abokinsa kullum sai ya zo nan.Tsabar fitina kuma idonsa ƙurrr a kaina,na juye kai kamar ban gan su ba ina mai kallon bango.

“ Ki je ki saka hijabi Baby sai ki dawo ku gaisa ke da Shareef” na ji muryasa a cikin kunnena har da zama kusa da ni.

“Ba zan saka ba,ni da gidana babu wanda ya isa ya takura ni yana hana ni shan iska,in hira za ku yi kuna iya fita can tsakar gida nesa da ni ” na yi furicin tare da tashi na fita don wanke hannuna.

“ SEERAT wai lafiyarki ? Meke damun ki?” na ji muryar Yaya Khaleed a bayana,na ajiye butar kafin na juyo muna facing juna na ce “ lafiyata lau! Ina ka taɓa ganin kullum abokin miji sai ya zo? Akan wane dalili?”

Bayana ya soma dubawa sai na fahimci wato tunaninsa baƙar halittar nan ce ke hure min kunne,ya ƙanƙance ido ya koma sak Yaya Khaleed ɗina na kafin aure sai kuma na ji tsoronsa ya kama ni.

“Kenan cikin hankalinki ne kike faɗa min son ranki don tsabagen raini? Baseerat wallahi ki shiga hayyacinki in ba so kike na yi mugun baki mamaki ba.Wuce mu tafi” na fashe da kuka tare da maƙe kafaɗa na ce “ ku zauna ku biyun ni zan yi zauna a nan ɗin”

Bai ce komai ba ya shiga ɗaki ya kuma fito riƙe da hijabina,da kansa ya saka min tare da ja na muka koma.Sam Shareef bai canza fuska ba sai ma tsokanar Khaleed da ya soma “ abokina ina ga bayan aikin yʻan sanda kana iya koyar da ƙananun yara karatu na san za ka fi ma ƙware wa ta wannan fannin” sai kuma ya ƙyalƙyace da dariya yana kallona,wato ni ce yarinya abin da yake nufi kenan.

“ To ya na iya sai haƙuri ka san har yanzu akwai ƙurciya a tattare da ita” Yaya Khaleed ya faɗa yana kallona,na turo baki gaba ina hararsa.

“Hum! Wannan raini har ina? Yanzu Khaleed mace ce ke ma haka kai kuma kana wani sakin murmushi?” Shareef ya faɗa ,da alamu abun ya sha masa kai.Bai ce masa komai ba sai ma zaunar da ni da yayi kan kujera ya zuba ruwa a kofi da kuma abinci a plate ya ce “ ci abinci don Allah ka bar Baby haka nan ta huta,wallahi duk ka firgita ta tsoronka fa take”

Ni ya kalla yana min kallon nan mai ayar tambaya ‘ wai haka ne?’ da sauri na kawar da dubana ina jin kamar na shaƙe shi don takaici,da yake bai da zuciya haka ya ci abincin da ni ce na girka.

“Tumatur ɗin kamar bai soyuwa ba,ana jin zaƙin magi Hajiya kin kuwa soya miyar nan da kyau?” Shareef ya faɗa wanda hakan yasa na yi saurin kallonsa,cike da gyatse na ce “ ai miyar ma ban dafa ta ba sam,da ruwan sanyi na haɗa ta”

“Ai kuwa na ga alama shi yasa sam girkin bai yi daɗi ba ,wannan ai ko yaɗar shekara biyar tana iya yinsa.Dubi shinkafar ma fa ta kwaɓe kamar wani tuwo”

Idona na ji sun ciko da ƙwalla,ba wai tsokana ta ba ce yake kamar yadda Yaya Khaleed ke tunani a'a ƙona min zuciya ce yake saboda na ji haushi.Murya na ɗan rawa na ce “ Yaya wai miyar ba ta yi daɗi ba?” kai ya jinjina ya ce “ eh to ba sosai ba” kamar shigar mashi haka na ji furicin kaina ne na ji ya sara kamar wacce aka yi wa allurar hauka haka na fasa wani uban ihu tare da yin tsalle na cakumi wuyan Shareef na ware dukkan ƙarfina na soma dukansa ,Yaya Khaleed ya ɓanɓare ni tare da banƙare ni ya soma yi min karatu sai fizge-fizge nake ina jin muryar Shareef na cewa “ innalillahi! Khaleed ka auro wa kanka masifa wato iskokai ma gare ta?” sai kuma ya fice da sauri.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via
```

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yɗan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

17_18

Sai da Yaya Khaleed ya sha fama kafin ya samu na yi shiru,na koma gefe ina kallonsa ina sauke ajiyar zuciya.Shi ma ido ya tsura min ,kallo ne mai cike da ma'noni dayawa wasu na fassara wasu kuma na kasa saboda sai shi kaɗai ne ya san ma'anar su .Miƙe wa na yi na shige bedroom na zube kan gado ina jin haushin Shareef ,ban san wace hanya zan bi ba don ganin na raba shi da mijina ba na yi tunanin iri-iri amma ban cabko wanda yayi daidai ba.

Daga bayana na ji ya kwanta tare da rungumo ni,a tare muka sauke ajiyar zuciya.“ Ki yi haƙuri babyna,Shareef tsokanar ki yake fa shine ranki ya ɓace har kika gayyato min yɗan tsatsubanki” ya ƙarashe faɗa yana murmushi mai sauti,shiru na masa ban ce komai sai da na ji ya soma wasa da jikina.

“Yaya ban so ka bari!” na furta tare da riƙe hannunsa da ke kan cikina,da sauri na lumshe ido jin yana lasar kunnena tare da yi min wasu abubuwa.Tsawon lokaci kafin ya birkita ni ina kallon sama,idonsa ya saka cikin nawa yana wani ƙanƙance wanda

hakan yasa na ji abubuwa na cika min kwanya tare da shiga shauƙi.Sumba ya soma yi min,can ya tsaya tare da yin magana cikin rawar murya “ me yasa ba ki dinga mayar min da martani?” ban ce koma ba sai murmushi.

Ya cire rigar jikinsa ,ya kwanta kan bayansa yana mai jawo ni a ƙirjinsa wasa na soma yi da sarƙar wuyansa wacce taɓa ta da hannun hagu ya haifar min da ƴar zabura kamar wacce lantarki ya ja .“ Mene ne?” ya tambaye ni,“ babu komai” na basa amsa ina mai kai bakina kan nasa yayin da kuma na jimƙe sarƙa wuyansa cikin tafin hannuna na hagu.Tamkar na kunna kaset haka na soma jin tarihin Yaya Khaleed.

Sarki Waleed shine mahaifinsa miji ga gimbiya Zahra'u sha ƙudum mahasada,jajirtaciyar ƴar gwagwarmaya ce ciwon idon matsafa.Ta kafa tuta da tarihi a BAƘAR DAULA(Ameera Adam) wacce bayan tsafi da shirka ba su ajiye komai ba.Wanda silar haka ne matsafan yankin suka haɗa ƙarfi da ƙarfe suka yi silar haukata ta bar masarautar cikin dare tare da ɗanta Khaleed wanda a yanzu shi suke farauta su kashe domin tuni sun ƙara yin nasara akan ɗaya jigon nasa wato mahaifinsa,sun kwantar da shi matsananciyar jinya wacce ke buƙatar ganin manyan malamai domin warware ta.

Yaya Khaleed ya soma karanto addu'ar keɓantuwa da iyali yana mai gyara mana kwanciya hakan yasa sarƙar ta bar cikin hannuna.Aka cewa da kiyon da ya karɓe shi,a lokacin da Yaya Khaleed ke ta ƙoƙarin ganin ya sama mana kyakkyawar fahimtar juna da ƙauna,ni kuma burina shine na ƙara cabko sarƙar wuyansa na jimƙe garin yin haka ne yasa na cire sarƙar daga wuyansa ta dawo hannuna.

Fatseee! Ƙwan lantarki ya tarwatse yayin da kuma gadon da muke kwance ya soma wani irin motsi yana shirin kayar da mu.Ba wani dare ne ba amma hakan ɗakinmu ya turniƙe da wani irin duhu irin na damina ,cak ya tsaya da abin da yake ni kuma da sauri na lalubo wuyansa na soma kiciniyar mayar masa da sarƙarsa saboda

rugugin tafowar matsafa kusa da mu da na soma ji kunnuwana na zuƙo mini.Amma tamkar wata musaka sai na kasa ɗaura wa,Yaya Khaleed ne ya taimaka min sarƙar ta ɗauru na ja wani numfashi tare da rungume shi jin komai ya dawo normal na bar jin sawun tawowarsu sannan duhun ya rage hasken falo ya shigo ɗakinmu.

Bayan mun yi wanka ne Yaya Khaleed ya fita ya sayo sabon ƙwan lantarki ya saka.Na fara ƙoƙarin shiga bacci ya ce “ karatun fa? Ko babu lesson ɗin da za ki yi?”

“Na gaji! Gwara na yi baccin kar gobe in na je aji na kasa ɗaukar darasi” na faɗa ina mai kwanta wa.Yaya Khaleed yayi min wani kallo kafin ya ce “ mi zai hana ki yin darasin? Ina ce ma jiya kin yi bacci sosai”

“Eh rabi da rabi ba,ka manta ka hana mu saƙat motsi kaɗan ka manne min,ni fa har sai da ka bani tsoro na yi tunanin ko Bafulatanata ce ta hura ma wutar sha'awa ”

“Wace Bafulatana ? ”

Shiru na yi na ɗan wani lokaci kafin na ce “ sai da safe Yayana ”

“A'a sai dai in na tashe ki domin kula da ni”

“A'a wallahi ban so”

“Ni ina so”

“To ai yanzu mun yi”

“In an jima ba yanzu ba ce”

“Don Allah ka bari Yaya,kar ka tashe ni” bai ƙara cewa komai ba har na yi bacci,nan ɗin ma mafarkin masarautar na soma.Fitinar Yaya Khaleed ce ta katse min baccin,sam ban yi tsammanin cewa zai tashe ni ba duk yadda na so bijire masa amma haka nane mini kamar mayen ƙarfe.Ina kuka ya sukuce ni zuwa toilet,ina shirin komawa bacci na ji ana kiran sallah dole na tsaya sai da na gabatar sannan na kwanta.

Cikin bacci nake jin muryarsa wai na tashi na yi shirin makaranta,“ Ni fa ba zan je ba”

“Tashi za ki yi Malama ” ya faɗa tare da zaunar da ni zaune,wani haushi ne ya rufe ni na soma kuka wiwi sam gani nake Yaya Khaleed bai tausayina ai kuwa sai ya tabbatar da zargina ya soma yi min faɗan da yasa dole na je na yi wanka na zo na shirya.

Muna fita waje sai na ga yau Shareef ne ya zo ɗaukar mu,shi ya buɗe min gidan baya kafin ya shiga gaba.Ta madubi muka haɗa ido Shareef,ban gaishe shi ba haka shi ma bai ce min komai ba sai labari da ya soma yi .

“Zuwa gobe zan tafi Say ka fara shirin haɗa mini gift ɗin tarben amarya” Shareef ya faɗa yana murmushi.

Khaleed ya ce “ ma sha Allah ka ce yʻar fillo za ka auro? Amma dama ka san mutane a can ?”

“Eh Daddyna a can ne asalinsu nan aiki ne ya kawo shi”

“Abokina kana iya zama da Bafulatana ƙauye kuwa?”

“Wa ya faɗa ma ƙauye ce? Duk Nijar akwai inda ya fi can kyau da tsaruwa? Ka kuwa san irin yadda Allah ya azurta su da dukiya da kuma kayan more rayuwa”

“A'a in auren naka ya tashi za mu je ai ”

“Ai kuwa nan kusa ne”yayi furicin yana kallon madubi muka haɗa ido ,na zabga masa uwar harara kafin na kawar da kai.A daidai ƙofar makarantarmu yayi parking,na ƙi fita sai da Yaya Khaleed ya buɗe min ƙofar,duk da ban ganin Shareef amma na tabbata idonsa na kanmu hakan yasa na riƙe hannunsa na soma zuba masa rigima tare da ƙorafin ƙila ma yau in na je baccin zan ta yi.Mun kusa minti goma kafin ya bani kuɗi na karɓa shi kuma ya shige mota,yau dai da ɗan dama ban yi bacci a aji ba sai dai jefi-jefi ina yin tunani akan labarin Yaya Khaleed a yanzu na sani ba Ammy ce mahaifiyarsa ba amma ban san ta yaya aka yi ya zo nan ɗin ba.Yau ma muna sauka daga makaranta na shiga taxi zuwa gida,ko da na zo ƙofar gidan na tarar duk an shimfiɗa tabarmi da alamu zaman makoki ake yi.Ina shiga ciki na fiddo key don buɗe ƙofar kewayena sai ga Shafa'atu ta fito tana cewa “ dama tun ɗazu ke nake jira”

“Ga ni lafiya?” na faɗa don yanzu ina kiyaye saka kaina a matsala.

“Hajiya ta rasu mai gidan nan,tashi za mu yi ƙarshen satin nan za mu koma gida kafin nan za a yi wa Isma'il karatu dangane da abin da ya faru”

Na taɓe baki na ce “ yanzu a hakan za ki ci gaba da zama da shi?”

Ba ta kai ga bani amsa ba ya fito yana kiranta,da sauri na shige kewayena na ja ƙofa na rufe.Ina buɗe daki na cillar da jakar makaranta sannan na shiga wanka ,bayan na fito ne na ɗora girki na ci na ƙoshi.

Sai bayan sallar isha'i Yaya Khaleed ya shigo a cikin wani yanayi na haɗe rai wanda ya wanzar min da tsoronsa.Da na gaishe shi ma dakyar ya iya amsawa,abinci ma da kansa ya zuba ya saka TV a gaba yana kallo duk sai na ji babu daɗi na je bedroom na canza yanayin shiga ta na saka kayan da ya fi so.Ina fitowa na je na zauna kan cinyarsa a shagwaɓe na tambaye shi “ wai don Allah laifin me na yi?” kamar jira yake yi ya soma yi min ihu cikin kai “ abin da kike yi kin kyauta kenan? Abokina ma ba za ki iya gaishe shi ba? Sannan yau ina lura da ke a cikin mota sai hararen shi kike laifin mi yayi miki? In yanzu yayi aure ya kawo matarsa ta yi min abin da kike masa za ki ji daɗi ne? Amma ba laifinki ba nawa Shareef yayi gaskiya saboda ina sake miki fuska ne” yana gama faɗa ya ture ni ya fice ya bar gidan.

Tun ina jiran dawowarsa har na gaji na ja ɗaki na rufe,kan kujera na kwanta dakyar bacci ya ɗauke ni.Kiran sallah ya tashe ni,shaf na manta da abin da ya faru na wuce toilet na yi wanka sai da na fito ne na lura Yaya Khaleed bai kan gado wato ba gida ya kwana ba.

Da na buɗe ƙofa sai na ga babu ma alamunsa,sai na ji duk zuciyata ta ƙiya na koma ciki ina ta kuka.Ashe ban ma soma ba har biyun rana babu ko mai kama da shi ne,haka na wuni sukuku kamar kazar da ƙwai ya fashewa a ciki.Dakyar na iya yin girkin dare,na zauna jungum ina zaman jiransa,sai dai yau ɗin ma bai kwana ba wayarsa kuma a kashe.Washegari bugun ƙofarsa ya tashe ni,na buɗe masa ya shigo a yanayinsa kawai na lura daga daji yake na ja ajiyar zuciya tare da cewa “ Barka da zuwa”

“Yawwa” ya amsa tare da nufar bedroom,na take masa baya tare da taimaka masa ya cire kayan jikinsa duk da kuwa sai hurar hanci yake ban damu ba har toilet na yi masa rakiya na taya shi wanka bayan ya fito kuma na basa abinci,yana ci yana kallona har ya ida.

Kamar wasu baƙin juna haka duk muka yi shiru,a dole ni ma na soma kallon TV daga bisani kuma na shige bedroom.Wayata na ɗauka na soma tunanin lambar ƙawata Maryam cikin ikon Allah na samo ta daidai,tana jin muryata ta gane hira

sosai muke inda take sanar da ni cewa tana ta ganin canji da ta soma amfani da man zaitun da sauran.

“Ƙawata ya amarci?” ta tambaye ni tana dariya.

Na saki murmushi mai sauti na ce “ to ga shi nan da dama dai ba daɗi ba wuya ”

“Har yanzu ba ki saba ba kenan?”

Ban bata amsa ba don ban ga amfani yin hirar sirrin shimfiɗar aurena ba sai na canza zancen “ ya makaranta kuna ta zuwa duk na yi kewar Zinder ”

“In na haihu ai za ki zo”

“Ciki gare ki ?”

“Eh ina ta laulayi ”

Na ce “ ƙila dama can aljanin jikinki ne ya hana haihuwar,to Allah ƙara lafiya kin ji ko kuma ki ci gaba da amfani da maganin”

“In sha Allah kuwa ,wai....” da sauri na yanke kiran ba tare da na jira jin abin da za ta ce ba sakamakon Yaya Khaleed da ya zo yayi a tsaye a gabana yana faman cire kayan jikinsa.

Gadon ya hauro ba ummm ba a'a ya soma shafa ta,takaici ya rufe ni sai kawai na fizge zan sauka amma ya cabko ni tare da saka ƙarfi ya karɓi haƙinsa,kwana biyun da bai yi a gida ba sai da yayi nasu su ma.Washegari ma da zai tafi aiki sai da ya maimaita ya kuma fice ya bar ni ina kuka, kwata-kwata sai na ji na tsani auren.

Tun daga wannan lokaci rayuwarmu ta koma wata iri,ba mu yin hira ni da Yaya Khaleed tsakaninmu na yi abinci na basa ya ci ya ƙoshi sai kuma ya hau turmusa ta.Ɓangaren Shareef kuwa ya ɗauke ƙafarsa a gidanmu,sai dai kamar wani saurayi da budurwa kullum cikin kiran Yaya Khaleed yake a waya suna hira da dariya.Wani

sa'in ma muna kwance kan bed yake kiran nasa haka shi kuma zai ɗauka, ni kuma sai dai na maida fuska ga bango na yi ta kuka.

Tsawon sati guda currr kenan ban je makaranta ba kuma Yaya Khaleed bai matsa min ba sai na ga kamar ma ya ji daƒin haka.Ina zaune ina kallonsa yana shiryawa muna haɗa ido yayi saurin kawar da kai,kafin ya ce “ Shareef zai kawo budurwarsa zan kawo kaji ki yi musu girki irin na ranar farkon zuwan ki yayi daƒi sosai,sannan ki nutsu ita ɗin ba wata babba ba ce ƙila ma kin girme ta ki kula da kyau ban son a samu matsala har su koma”

Idona na ji sun ciko da hawaye na ce “ Yaya Khaleed yanzu hakan da kake yi min ka kyauta? Dube mu kamar wasu baƙi babu hira ,babu komai da muke yi na romantic komai kamar na dabbobi in kana da buƙata ne kawai kake neman sulh...” mugun kallon da yake jifa na da shi yasa na haƒiye sauran maganar.

“Kenan faɗa muka yi ban sani ba? Wato so kike na dinga sake miki fuska kina raina ni ? Dama Shareef ya faɗa saboda ina biye wa shiriritarki ne yasa kika raina ni kike min iskanci iri-iri ”

“Kenan shi ya baka shawarar ka canza min? Shawarar mugun aboki kake bi?” na tambaye shi hawaye na zubo min shaaa a kumatu,irin kallon da na jima ban gani ba Yaya Khaleed ke aiko min mai cike da tausayina da kuma ƙaunata.Sai ya fice ba tare da ya amsa min ba,sai da na ci kuka na gaji kafin na yi aikin gida.

Kamar yadda ya faɗa ɗin ya kawo kajin na gyara na yi komai,wuraren ƙarfe biyar na maraice suka iso.Wata kyakkyawar Bafulatanata ce mai shegen kyau kana ganinta

ka san iyayenta Naira ta gama jiƙa su,dukkan jikinta kuɗi ke magana agogon hannunta kawai a bar kallo ce.

Ta ci uban ado kamar yar tsanar zinare,bayan sun zauna na gaishe su cike da ladabi Shareef kawai ya amsa ita kuwa tun da muka haɗa ido take haɗe rai tana wani cin magani .

Na je na kawo musu ruwa na zuba musu,da Shareef zai karɓar kofin har da wani shafar hannuna yayi yana sauke ajiyar zuciya.Na yi saurin ja da baya ina hararensa,kafin na zauna kusa da Yaya Khaleed ai kuwa sai budurwar ta sunne kai.

“Aboki ka fa san amarya akwai ta da kunya da dai kun ɗan matsa da junanku ” cewar Shareef .

Khaleed yayi murmushi tare da tashi ya canza wuri,muka haɗa ido da Shareef ya sakar min murmushin gefen baki ya tsure ni da ido yana min tambayoyi irin ‘ ya kika ga wasar? Yanzu kin yarda da ina iya juya mijinki? Kin fahimci cewa ina da matuƙar tasiri ?’ cikin muna kallon juna ne na soma jin kukan kyankyaso a cikin kunnuwana hannuna na kawai na soma sarrafawa ina nemo kyankyason cike da son ɗaukar fansa na so cilla shi a rigar Shareef sai na mayar da su da yawa ta yadda zai yi ihu amma sai na ji an tare hanyar faruwar haka.Sai a lokacin na janye idona muka kuwa haɗa ido da budurwarsa wacce a yanzu ta bayyanar da ɓoyayyar siffarta ta matsafiya.

Na janye idona tare da fasa abin da nake shirin yi ɗin,“ abincin ma ba za a kawo mana ba sai mun roƙa?” SHAREEF ya faɗa ,da sauri na miƙe na je na kawo,sai kuma na shige bedroom ina ta tunanin ina kuma ya kwaso waccan budurwar mai shegen hatsari amma banda amsar tambayar.

Sai da za su tafi ne na fita don yi musu sallama,“ ba za ki yi wa amaryata kyautar komai ba?”

Cikin gajiya da salon raininsa na ce “ eh ba zan bayar ba ɗin,ba dai amaryarka ba uwar amarya....”

“Keeee! ” Khaleed ya min tsawa,sai kuma ya dubi Shareef “ abokina mu je” haka suka fice ni kuma na zauna zuciyata na suya.Da ya dawo haka ya tisa ni gaba yana faman yin faɗan banda haƙuri kuma banda kunya har da bada misali da ita budurwar Shareef ɗin wai tsabar kunya kasa cin abinci ta yi,daren nan dai ba mu yi shi cikin daɗi ba.

Washegari da ihun Yaya Khaleed na tashi,akan kaf kayansa na zuwa aiki sun yi dauɗa ban wanke ba.Ni kuwa cike da mamaki nake dubansa don kuwa dukkansu sai da na wanke na goge.

“Allah Yaya Khaleed na wanke su...” hannu yasa ya buge min baki har sai da ya fasa abin da na kasa jura kenan na ɗaga masa murya tare da nuna shi da yarsa ina cewa “ wannan shine na farko kuma na ƙarshe da za ka sa hannu ka dake ni,ba a haifo ni ba don wani ƙaton banza ya dinga jibga ta ba.Kaya ne na wanke su kuma ai niyyata ce yasa nake wankewa to daga yau ban sake yi ka wanke da kanka”

“Eh lalle wuyanki ya isa yanka Baseerat ni Khaleed yau Ni kike nuna wa da yatsa?”

“Eh ɗin ubana ne kai?”

Ya wato ido ya ce “ rashin kunyar taki har ya kai haka? Kin kuwa san matsayina a wurin ki?”

“Ina ce dai miji ne,kuma miji ba uba ba ne ballantana nace ban iya rabuwa da kai”

“Alamu sun nuna kin gaji da aurena ”

“Eh in kuma ka ji haushi sai ka sake ni”

“Ai na ga alamun haka ,kuma in ba ki bini sannu ba wallahi kin kusa kama layin zawarawa ”

“To sai me? ZAWARCI ai ba gare ni farau ba ga iyayenmu muka gani”

Zuwa wannan lokacin na san na ƙure Yaya Khaleed kawai ya ɗauke ni da mari har biyu yana cewa “ wato da Ammyna kike ? Ita bazawara ? Ki na ji na SEERAT ki haɗa kayanki ki bar min gidana tun da iskancin naki ya wuce ni ya kai har ga uwar da ta kawo ni duniya”

Sai ya watso min kuɗi “ ki je ki shiga mota ta ƙarfe tara in kuma kin isa sai ki wuce gidan matar aure ba wurin bazawara ba” yana gama faɗa ya fice.

Wani irin tsoro ne ya dirar min,sai yanzu nake ganin laifina da na biye masa.Ina kuka ina ƙari na kwashi kuɗin,tsinke ban ɗauka ba iya wayar hannuna kawai na fita da ita.Sai da na rufe ko ina kafin na je na shiga taxi zuwa gidan Bus .Na ciri takardar ƴan balaguro,sai da na yi wajen awa ɗaya kafin motarmu ta tashi .Kuka na soma yi ina tuna ranar da za a kawo ni nan,aure duka wata ɗaya amma ga shi miji ya kore ni silar mugun aboki .

Dakyar na iya samun abin da na sakawa cikina,sai bayan sallar magarib motarmu ta kai Zinder.Kalaman Yaya Khaleed suka dawo min sai da na auna su da kyau sannan na fahimci mi yake nufi,wato kar na je gun Ammynsa na tafi gun Mama.

Sai da na saka kati sannan na kira Mama,ko gaishe ta ban yi ba na ce “ Mama wace unguwa kike?”

“Ban gane wace unguwa nake ba?”

“Ina Zinder ne yanzu na shigo”

“Lafiya? ” ban bata amsa ba sai kuka da na fashe mata da shi,“ kina gidan wacce Bus ?” dakyar na sanar da ita,an ɗauki lokaci kafin ta zo ta ɗauke ni.

Kanzil ba ta ce min ba har muka isa gida,nan na ga gidanta mai shegen kyawu.Wanka ta umarce ni na je na yi,bayan na gama ne kuma na soma neman kayan da zan saka banda.Zanenta na ɗaura na saka hijabinta,abinci ta zuba min na ci na ƙoshi sannan ta nemi ba'asi kamar pampo haka na soma zuba babu abin da na ɓoye mata har baccin da nake yi a makaranta da kuma barin zuwa da na yi .

A gabana ta ɗauki waya ta kira Ammy ta sanar da ita ,amma da alamu ma kamar tun tuni ita Ammyn ta sani duba da yanayin da take bata amsar a daƙile.

Mama ta aje wayar tana cewa “ SEERAT ki faɗa min gaskiya da gaske ya dake ki? A yanayin yadda na ji Goggo da alamu Khaleed ya sanar da ita kuma ina ga ke ce mai laifin”

Hawaye kawai na soma gogewa,muna a haka sai ga mijinta ya shigo.Na gaishe shi cike da ladabi ya amsa cikin kamala,Mama ta yi masa bayanin cewa ni ce yarta amma ba ta sanar da shi matsalar da ta kawo ni nan ba.

Wani ɗaki Mama ta kai ni,bayan na yi sallah na haye katifar sai baccin gajiya.Tsakar dare yunwa ta tashe ni ,haka na fita domin samawa kaina abinci amma ashe rabon na yi mugun ji ne.A yanayin sautin da ke fitowa a ɗakin Mama na fahimci komai,sai mamaki nake yadda mijin nata ke faɗar abubuwa masu cike da abun kunya.Jikina har rawa yake na shiga kitchen na zuba abincin,cikin sauri na ci na ƙoshi na sha ruwa na koma yanzu ma da na ratsa ta falo haka na yi ta jin sautinsu.

Da na koma ɗaki sai bacci ya ƙaurace wa idona,wata irin kewar Yaya Khaleed ce nake ji babu abin da nake buƙata irin na samu kaina a tare da shi.Na haye katifa tare da curewa wuri guda,da na duba waya ƙarfe ukun dare moments ɗinmu da shi duk ya dawo min da yanzu ina gida muna second round ne saboda mijina jarumi ne.Haka na yi ta tunani har bacci ya ɗauke ni mai cike da mafarkinsa, washegari sai na ji kunyar Mama sai nake ganin kamar za ta gane na ji sirrinsu amma a haka muka wuni tare da ita lokaci zuwa lokaci ina kama ta tana kallona da na tambaye ta lafiya kuma ba ta sanar da ni ba.

Sati guda currr na yi a gidan Mama ko sau ɗaya Yaya Khaleed bai kira ni ba,haka ita ma Ammy yayin da kuma Mama ta ce mu zuba musu ido mu gani.Duk dare na Allah sai na tashi cin abinci saboda azababiyar yunwa ,kwana biyun da mijin Mama bai gidan cikin hankali kwance na yi shi amma da zarar girki ya dawo hannunta sai na ji abin da ya fi ƙarfin kunnena.

Yau ma girkin Mama ne kamar yadda lissafi ya bada,tun safe ta fita kasuwa ina zaune muna waya da ƙawata Maryam nake ce mata “ wallahi feeling ya sha mini kai kin ga kuma har yanzu ba su maganar komawa ta ɗakina ”

Ta ƙyalƙyace da dariya ta ce “ to fa nan yaji ne kika yi,ina to da auren ne ya mutu? Kin ga wannan ma na ɗaya daga cikin ƙalubalen da zawara ke fuskanta,lokacin da kina budurwa ba ki san namiji ba hankalinki kwance yake saɓanin in kin taɓa aure kina ZAWARCI.Ke ma da laifinki a ciki ba ki tsaya kin yi dogon bincike ba kika kwaso jiki kika dawo,ni na fi zargin ma budurwar Shareef ɗin tun da kin ce matsafiya ce ba ki tunanin ko ita ce ta haɗa muku tuggu?” Maryam ta faɗa kasancewar na kasa jure baƙin cikin da nake ciki na sanar da ita damuwata

Shiru na yi na soma nazari tabbas sai yanzu na fahimci haka,“ zan ƙara yin dogon nazarin amma don Allah ki faɗa min abin da zan sha don na bar jin feeling kin san Allah ji nake kamar na yi fifike na je Yama....” ban ji shigowarsa ba sai ganinsa na yi tsakiyar falo.

Da sauri na ce “ ina kwana Abba ?”

“Lafiya lau Bas baby,ina Mamar taki? ” Alhaji ya faɗa yana murmushi.

“Ta tafi kasuwa” na basa amsa.

“Tun ɗazu?”

“A'a ba ta jima da fita ba”

“Toh! Toh! Ki kawo min ruwa masu ɗan sanyi don Allah ” sai yayi gaba ya shiga ɗakin Mama.

Kitchen na shiga na ɗauko gorar ruwa da kuma kofi ,na yi sallama bayan ya amsa sai na shiga.Da sauri na sunne kai ganinsa babu riga,na ajiye ruwan ina shirin tafiya sai na ji yana cewa “ mijinki soja ne ?”

Da mamakin abin da ya kawo tambayar na juyo amma yadda yayi mugun ƙure ni da ido yasa na yi saurin gyaɗa kai,ya washe baki ya ce “ ah dole! Ai akwai su da iya lammura wai! Wai”

Ni dai fitowa na yi na bar masa ɗakin,ban kuma ɗauki abin da muhimmanci ba na wuce ɗakina.Ina ƙoƙarin maida wa Maryam kiran aka turo ƙofa ,na ɗaga kai sai na

ga Alhaji ne da sauri na miƙe ina cewa “ wani abu kake buƙata? Ko abinci? Bari na je na haɗa”

“Eh to abincin ne sai dai kuma ban sani ba ko na samu”

“Jira na je” na faɗa ina ajiye wayar na je zan fita amma ya ɗan tare hanya da zan wuce har sai da jikinmu ya gogu da na juna.Kitchen na shiga na haɗa masa indomie,ina jin muryarsa yana cewa “ in kin gama ki kai min ɗakin Mamarki zan shiga wanka”

Ina tsaka da girkin Mama ta dawo,na yi mata sannu da zuwa ta bani kayan da ta sayo min har da mangoro na karɓa yawuna na tsinkewa ko wanke shi ban yi na ɗauki guda ina sha.Mama ta yi murmushi ta wuce ɗakinta,ina shiga kitchen na sauke indomie na koma ɗakina da tunanin Mama za ta zo ta zuba masa.

Wunin ranar haka na ta shan mangoro wanda ya fi min daɗi irin mai tsamin nan,abinci ma ban ci na wani kirki ba.Da dare kafin na shiga ɗaki sai da na zuba wani a kula na wuce da shi gudun kar na fito tsakar dare.Bayan na yi wanka na shirya na haye kafita na ɗauki wayata ina kallon hoton Yaya Khaleed da wannan bacci ya ɗauke ni.

Numfashina ne na soma jin yana ƙoƙarin tsayawa ,ina buɗe ido na ga mijin Mama Alhaji ne ke ta ƙoƙarin kissing ɗina.Ban san inda na aro ƙarfin ture shi ba,jikina na rawa nake kallonsa yayin da shi kuma ya soma raba kansa da sutura yana cewa “ ki zo mu rufa wa juna asiri babu wanda zai ji har Mamarki,kin ga tana can tana bacci na saka mata magani har mu yi mu gama ba za ta tashi ba” ƙofa na nufa da gudu sai na ji ta rufe gam da key,Alhaji ya nufo ni gadan-gadan nan muka shiga zaga ɗaki har Allah yasa na ɗauki wayata ina cewa “ wallahi zan kira yan sanda in ka matsa min” ban rufe baki ba kiran Yaya Khaleed ya shigo wayata a karon farko kenan tun bayan zuwana.Hannuna na rawa na soma ƙokarin ɗaukar kiran sai na ji Alhaji ya cabko ni wanda yayi daidai da jan yatsana da na yi kan screen na ɗauki kiran.

“Wayyo Yaya za a min fyaɗe ” na furta da ƙarfi cikin muryar kuka .....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

19_20

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😉
```

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Yana ƙoƙarin haɗe bakina da nasa sai dai irin girgizar da ɗakin ya ɗauka yasa ya sake ni don dole,tamkar jirgin leda haka ɗakin ke juyawa kafin window ɗin ta buɗe da ƙarfi.Da idona na ga wannan tsuntsuwar,wata irin bangaza ta yi wa Alhaji da fufukenta na hagu yayin da kuma ta jawo ni da na dama daga nan ban sake sanin abin da ya faru ba sai ganina na yi kwance kan gado,gadon kuma na ɗakina ga Yaya Khaleed yayi tsaye kaina ya harɗe dukkan hannuwansa.

Ido na lumshe na sake buɗe su,eh tabbas gaske dai ne.Na fara ƙoƙarin tashi zaune da sauri ya zo ya jawo ni jikinsa,haske na ga yana fita daga cikin rigarsa a haka ma ina iya ganin tambarin masarautarsu da ke ta bada hasken zanensa kuma ya fito raɗau.

Cikin ido nake kallonsa masu ɗauke da ɗimbin tambayoyi, kyakkyawan masauki yayi min a ƙirjinsa yana shafar bayana.Sai yanzu na lura da alamu ma har wanka yayi min ya canza min kaya,a hankali na soma yi masa kuka bai ce min komai ba sai wutar lantarki da ya kashe a yau za su gwagwanji ƙauna wacce alƙalamin MRS SADAUKI yayi kaɗan ya rubuta ta.

Da za a tambaye ni zan iya cewa wannan daren ya fi yi min daɗi sau dubu kan darenmu na farko ,ba don komai ba sai don ya kafa tarihi ne mai ɗumbin yawa .Yaya Khaleed ya zama gwarzo kuma Sadaukin zuciyata,sosai yau yayi matuƙar ƙoƙari wurin shayar da ni zumar ƙauna wasu abubuwan ban ma san da su ba sai a yau kuma a karon farko ya kai ni fagen ƙarshe wanda kowacce mace ke fatan zuwa saboda muhimmancinsa da kuma zallar lagwaden shi.

Kan ƙirjinsa na haye ya ja mana blanket ba don niyyar yin bacci ba sai don mu baiwa juna labarin irin yadda muka yi kewar juna,duk da gangar jikinmu da ruhi tuni sun fahimta amma faɗar ma a baki tana da nata muhimmanci.

“ Duk abin da nake yi miki fa da sanina nake yinsa,duk da shawara Shareef ce amma ni ban yi don cutar da ke ba .SEERAT a kaf abokaina na fi son Shareef sai dai na fahimci yana yi min hassada ba wai tun a gare ki ba a'a komai ne in zan yi sai ya kushe shi.Ina so ki kawar da kai ga duk abin da zai yi miki ko da yake yanzu zai rage tun da yayi aure”

“Har an yi auren?” na katse shi,sai da yayi dariya kafin ya ce “ wai ba,kuma ko sati guda ba su yi ba da sanin juna amma har ya aure ta”

“Ai auren gida ne ko?”

“A'a wallahi,auren kece raini ne yayi.Saboda a ce matarsa ta fi tawa shine ya je can Say ya nemo Bafulatanar nan”

Shiru na yi ina tunani ‘ ko dai na sanar da Yaya Khaleed matar abokinsa matsafiya ce?’

“Na sani ai ba sai kin faɗa min ba” na ji muryarsa,“ kamar fa a zuci na yi magana”

“Kina kwance kan sarƙa ta kuma” ya bani amsa.

“Kana da power ne Yaya Khaleed?”

“Eh yau dai na soma ganin zahiriya,tun bayan tafiyarki na shiga ƙunci na kaɗaici da na kira Ammy na shaida mata komai shine tace min in na kira ki Allah ya isa na jira in lokacin dawowarki yayi zan kira ki ,to kullum haka nake fita a gari in yi ta tunani ina shawagi.Yau kawai sai na ji ana raya min kina cikin matsala kawai sai na kira ki ,ina cikin wannan tashin hankali domin kin ɗauka amma ba ki magana sai ihu neman taimako sai kawai ganin tsuntsuwar nan na yi ta dira a gabana.A daidai kuma wannan lokacin sarƙar wuyana ta fita ta koma a wuyan tsuntsuwar, SEERAT yadda dai kika san wani jinnu haka gangar jikina ta koma haƙi na shiga jikin tsuntsuwar.Duk da ina a siffarta amma tunani nawa ne,haka na soma shawagi sararin samaniya har na isa Zinder na je na ceto ki”

Hasken ɗakin na kunna ina mai tashi zaune ina dubansa,shi ma yayi zaunen tare da cewa “ SEERAT wannan ɗin ma duk tsafi ne na sani,masarautarmu nada wutar sha'ani da kuma haɗari.Su tsafin nasu mai haɗe ne da ayoyin Alkur'ani,da su ne suke amfani sai su juya su.Kin san duk aikin da za a saɓawa Ubangiji sosai ya fi tasiri.Ban san wa ya ƙyarƙyari sarƙar nan ba amma koma wane ne matsafi ne,sai dai ban san dalilinsa ba na baiwa Anna ita”

“Wace ce Anna?” na jefo masa tambayar ina kafe shi da ido,“ ta rasu tun ina ƙarami,malamata ce ta farko kafin kuma na koma ga ta biyun wato Ammy ”

Na saki murmushi don na fahimci zuwa yanzu Yaya Khaleed ya san da Ammy ba ita ce ta haife shi ba,amma yana jin kunyar faɗar wata ce uwarsa.

Ya jawo ni a jiki yana mai cewa “ kin ga zo ki kwanta gobe fa asibitinku ta ce za a tura ku ƙauyuka domin gudanar da examen ɗinku na ƙarshe za ku yi wata uku”

Na turo baki ina cewa “ ni fa ban son zuwa ƙauye”

Yayi murmushi ya ce “ kin san da kuwa garin su Fatima za a kai ku wato Say ”

“Wace ce Fatima?”

“Matar Shareef ”

Daga nan ban sake ce masa komai ba muka yi shiru a haka bacci ya ɗauke mu, washegari bayan sallar asubah sai da Yaya Khaleed ya kai ni shimfiɗa muka ƙara kwasar ɗumbin lada kafin mu shirya tsaf.

Yau Shuraim ya zo ya ɗauke mu,muna tafe suna hirar walimar bikin Shareef inda Shuraim ke cewa “ kamar dangin Mayu yan matan amarya duk suka cinye naman rago wajen biyu suka bar mu da lemu, wannan abu na ban takaici har yanzu ”

“Ai kunyar da Shareef ke kurin matarsa nada ita a ranar sai ta shayar da shi giyar mamaki,dubi don Allah yadda ta yi ta rawa tana yarfa hannu” sai suka ƙyalƙyace da dariya.

Da muka isa can makaranta sai muka tarar ana ta loda trollyn ɗalibai,Yaya Khaleed ya ce “ wai ana nufin in sun tafi sai an yi wata uku su dawo ko me?”

“Eh mana! Tun farko sai da na so na tambaye ka ita SEERAT haka za ta je babu kaya? Sai kuma dai na yi shiru” cewar Shuraim.

“To mu koma a hadɗo,amma abokina ka san dai an shiga haƙina ko? Ni dai a tafi da ni”

Shuraim ya ɗan rage murya ban mi ya ce ba na dai ga Yaya Khaleed na kallona ta madubi,a hanya ya saya min abinci ya ce na ci ban kawo komai a raina ba na ci na ƙoshi.

Da muka isa gida na sha ruwa sannan ya taya ni zaɓar kaya bayan mun gama ne ya wani langwaɓar da kai “ ki zo ki ɗan sallame ni kin ga yanzu in kin tafi shinenan sai an ɗauki lokaci ”

Na ɓata rai tare da soma gunguni,“ don Allah ni dai mu je kar a tafi a bar ni ”

“ haba SEERAT ɗina ki tausaya wa Yayanki mana” haka yayi ta min dadɗin baki har na yarda bayan mun gama muka yi wanka muka sake sabon shiri.Sai da ya ɗauki waya ya kira Shuraim sannan ya zo ya ɗauke mu,ko da muka je makaranta tuni motocin farko sun tafi ashe garuruwa ne za a watsa mu na yi tunanin duk a can Say ɗin za mu je.

“Zan je ƙarshen week na kai miki abubuwan buƙata,kin ga wasu nan Shuraim ya sayo miki.Ki kula da kanki banda zama da yunwa ,ki dinga tofe min cikina da addu'a na ji an ce garin akwai Mayu da yawa” Yaya Khaleed ke faɗa har da saka hannunsa cikin hijabina yana shafar ƙasan marata.

“Yaya Khaleed ana kallonmu fa,ka bari don Allah ” na faɗa ina son janye masa hannu,idonsa ya tsura min waɗanda tuni sun canza kala murya can ƙasa yake cewa

“ don Allah mu koma mota, Allah SEERAT zan yi kewarki sosai ke na ga kamar murna ma kike .Cikin jikinki duk ya ƙara miki...”. Bakinsa na toshe saboda yadda yake maganar nan ni ma tsuma ni yake ,kiss yayi min kafin ya bani kuɗi masu yawa sannan ya ja ni har izuwa motar da za mu shiga.

Shuraim wanda ke tsaye tun ɗazu ya ce “ har an saka kayanta”

“Na gode sosai Allah saka da alkhairi Allah ya biya ka da gidan aljanna,sannu da hidima” na faɗa ina sunkuye kai, Shuraim ya ce “ bai komai yi wa kai ne”

Yaya Khaleed ya ce “ a'a ka faɗi gaskiya ka ce saboda ɗanka ka sayo mata”

Da sauri na ɓoye a bayansa cike da kunya,haka suka yi ta tsokana ta har lokacin tashin motarmu yayi.Dakyar na shiga muka tafi,garin bai da wani nisa sosai awa biyu muka yi a hanya muka isa.

Kamar yadda dai Yaya Khaleed ɗin ya faɗa garin Fulani ne sannan kusan kaso ashirin ɗinsu duk Mayu ne.Abokan aikina duk kowacce sai shafa turaren tsari take,da alamu kowa ya san da zancen .A bakin hanya muka tsaya wasu suka sayi abin da suke so kafin a kai mu masauki,wani ƙaton gida ne mai ɗakuna daban-daban.

Mu mata ɓangrenmu daban haka su ma mazan,kowa ya kai kayansa ɗaki sai a lokacin na buɗe abubuwan da Shuraim ya saya min na ci biscuits da chocolat kafin na buɗe trolly na fiddo zanen gado na shimfiɗa kan yaɗar ƙaramar katifar kwancin mutum ɗaya.Sosai na yi baccin gajiya,da na farka miss call na gani barkatai ciki kuwa har da na Mama,ita na fara kira tana ɗauka na ji ta saki ajiyar zuciya kafin ta ce min “ duk abin da Goggo Habibah ta sanar da ni gaskiya ne?”

Duk da ban san mine ne ɗin ba haka na amsa mata da eh ɗin,mun yaɗar hira kafin na yi mata sallama.Yaya Khaleed na kira muka sha hira na soma basa labarin garin,bayan nan na je na yi wanka na yi sallah sai kuma duk muka fito nan harabar gidan kasancewar akwai bishiyoyi.Hira sosai muka yi cikinsu ni ɗaya ce baƙuwa

amma a haka na saki jiki,waɗanda suka kawo gas sune suka ɗora mana girkin dare muka ci muka ƙoshi nan ma muka hau hira kafin mu kwanta.

Washegari tun da safe duk muka soma shiri don yau ne za mu shiga asibitocin garin Say ɗin,muna nan muna tsaka da shiryawa muka ji jiniyar ambulance.

Da sauri duk a soma fita amma ni sam ban fito ba saboda ina duba farar rigata ta likitoci,dakyar na ganta sai na tsaya fesa mata turare.Daga nan inda nake ina jin muryar wani mutum mai zafin zuciya yana cewa “ kun tabbata dukkanku ne nan babu wacce ta tafi wani wurin?”

Muryar wacce muke ɗaki guda na ji mai suna Ayshatu tana cewa “ a'a baƙuwa tana ɗaki”

Saka farar rigar tawa yayi daidai da shigowar wani jajirtacen namiji mai cike da zati ga tsayi ga jiki ga kuma kayan sarauta.

Maimakon ya dubi fuskata kamar yadda nake kallon tasa a'a ido na ga ya tsurawa wuri guda a jikina,ni ma sai na kai dubana a wurin .Haske na ga yana fita daga cikin aljihuna,na kai hannu na ciro abin da ke ƙyallin ba komai ba ne face kuɗin da wata mata ta taɓa bani tun a Zinder da na ceto ɗanta.

Ban ga tawowar shi ba sai ganinsa na yi a gabana,hannunsa yasa ya ɗauke kuɗin da ke kan tafin hannuna kafin ya ce “ biyo ni ” in na ce ban ji tsoro ba to tabbas na yi ƙarya jikina na rawa na take masa baya,sai na ga hatta motocin da ke a wurin na alfarma ne ina ganin tambarin masarautar su Yaya Khaleed a jiki sai na saki murmushi a zuci na ce ‘ an zo wurin!’

Ashe ban sani ba mutumen nan na ankare da ni,sai jin tambayarsa na yi “ mi kike yi wa murmushi?”

“Babu komai” na basa amsa.

Bai ce komai ba sai wani dogari ne ya soma magana “ kamar yadda tsarin yake duk wasu sabbin likitoci da aka kawo nan garin ana zaɓar wasu daga ciki domin yi wa masarauta hidima to a wannan karon mun ɗauki mace guda za mu kai ta masarauta,da izinin shugabanku ga shi nan Dr Jamal”

Babu wanda ya kawo komai a ransa haka duk aka watse,dogarin ya matso kusa da mu yana mai cewa “ yalaɓai ka tabbata ita ce?”

Bai basa amsa ba sai ni da ya kalla,sai an yanzu na ga hoton fuskar Yaya Khaleed akan tasa.

“Ka buɗe mata mota ta shiga” ya bada umarni,“ an gama shugaba” sai ya buɗe min ƙofa amma sai na ji taurin kaina ya motsa na ce “ ina za a kai ni ?”

Mutumin nan ya murmusa ya ce “ masarauta mana matar yarima Khaleed”

Sai da na ji wani rasss,amma ban san mi yasa ba na basar na ce “ wane ne kuma haka ?”

“Ni ɗin ƙane ne ga gimbiya Zahra'u uwa ga Yarima Khaleed zan so ki fara girmama ni tun yanzu don ni surikinki ne ba abokin wasa ba” yana gama faɗa yayi gaba,haka na koma ɗaki na ɗauko jaka ta da wayata sannan na fito na je na shiga motar da tun ɗazu aka buɗe min ƙofar.

Wani irin ƙamshi haɗi da gumin motar suka saukar min da nutsuwa,gudu ake kamar za a tashi sama har muka isa ga wani ƙaton gini mai ƙatanga doguwa kai kace ginin gidan fir'auna.Tun daga manyan get har izuwa shuke-shuken wurin za ka fahimci kuɗi ne ke ta magana.

Motar da nake ciki na shigowa masarautar tsuntsuwar nan mai kai mana ziyara a can Zinder ta dira a gaban motar tana wani irin kuka wanda ya game kaf illahirin Masarautar,ya kuma jawo hankulan mutane.

Yanzu ma dogari ne ya buɗe min ƙofa,kasa fita na yi kawai na tsurawa baƙar turɓayar ido wacce aka jiƙa ta da jinin tsafi na al'umma .

“Wace ce kuma wannan?” muryar wata mata ta daki kunnena,sai a lokacin na ɗago ido na dire su kanta ta ɗan ja baya tana aiko min da kallon tsana.

Ban damu ba na sauko da ƙafata ta dama ta fara taka ƙasar masarautar,wani iska ne ya taso ya turniƙe wurin tamkar yadda in an yi shara ƙazanta ke kawar wa to haka turɓayar ta zama tasss duk baƙin nan ya bi iska.Na ida fitar da gangar jikina na tsaya kan ƙafafuna,sannan haka kawai na ji na motsa hannuna na hagu kamar mai korar ƙuda sai iskan ya tsaya cak.

“Sunana nurse SEERAT na zo nan ne domin duba lafiyar mai martaba!” na faɗa ina mai kallon matar wacce har zuwan yanzu ban san wace ce ita ba.

“Mu je” cewar mutumin nan yana nuna min hanyar da zan bi,ina gaba yana take min baya har muka isa cikin wani ƙayatacen falo mai cike da kayan alatu,tamkar wacce ta san gidan haka nake bin lungu da saƙon wurin har na isa gaban wata ƙofa,sai na yi tsaye.

Muryarsa na ji yana cewa “ ina Yarima Khaleed fatan yana lafiya?”

Na juyo na dube shi kafin na ce “ na faɗa maka ban san shi ba”

Ya murmursa ya ce “ buɗe ƙofar ki shiga” babu wani tunani na sa hannun hagu na buɗe ƙofar,daga can bayana ya ce “ wannan ƙofar mutum uku ne kawai ke iya buɗe ta,na farko ni,na biyu Yarima Khaleed na uku kuma sai matarsa!” jin abin da ya ce yasa na yi saurin jawo ƙofar na rufe na ce “ dama a buɗe na tarar da ita ai,yanzu kuma ga shi ta koma ta rufe gam ka ga na kasa” na yi furicin tare da tura ƙofar da hannuna na dama.

Sai ya ce “ to ai hannun hagu za ki sa sai ki buɗe” tsuru-tsuru na yi ina kallonsa,abin da na fahimta dai ya gama sanin bayanina.Buɗe ƙofar na yi na shiga,nan ɗin ma yana da kyau sosai an ƙawata shi sosai haka na yi ta tafiyar har na isa kusa da wani gado na alfarma inda wani dattijo ke kwance idonsa ruf kamar mai bacci amma kuma ba baccin yake ba saboda magana da na ji yayi min,“Uwais ka samo yarinyar kuwa?”

“Eh yalaɓai ga ta nan a gabanka ” cewar Uwais wanda sai a yanzu ne na san sunansa.

Dattijon ya buɗe idonsa yana kallona na wani lokaci kafin ya ce min “ ina Yarima Khaleed?” sai da na dubi Uwais ɗin kafin na ce “ wane ne shi?”

“Ka ce min kuma ita ce?”

“Eh ita ce mai martaba,tana tattare da gurbin baƙin ruhi a jikinta har yanzu shine yake wasa da kwanyarta” Uwais ya faɗa tare da takowa kusa da ni,hannuna na hagu ya kamo har zan fizge amma yayi min riƙon tsiya,daidai ƙirjin mai martaba ya ɗora hannun na saki ihun azaba saboda tartatsin wutar tsafi da ya soma huda tafin hannun nawa.

Jikin Sarki ne ya ɗauki wata irin rawa har gadon na jijiga,Uwais ya ƙara danna hannuna da ƙarfi nan bakin mai martaba ya buɗe.Wani siririn baƙin maciji ya soma fitowa daga bakinsa yana shiga rigata direct kuma cikin sarƙar wuyana ce yake tsinke.

Sama da minti biyar kafin a samu dukkan macijin ya fita,na yi baya da sauri cikin gajiya zan zube Uwais yayi saurin taro ni yana min sannu.Kan kujera ya zaunar da ni sannan ya kawo min madara na karɓa hannuna na rawa na soma sha.

“Sarki Waleed na yaƙi da matsafa amma kuma bai yarda cewa tsafinsu zai iya kama shi ba,sun yi masa zagon ƙasa na fitar da gimbiya Zahra'u daga masarauta domin raunata imaninsa da wannan suka yi amfani suka haɗa kai da gimbiya Layya aka nakasar da shi,sannan kuma ita ce ke kawo malamai domin neman masa magani amma kuma sai aka ci gaba da ciyar da su da gubar asiri” Uwais ya faɗa cike da takaici.

“Wace ce Gimbiya Layya?”

“Wacce kika gani ɗazu,ita ɗin yarsa ce ta farko wajen haihuwarta mahaifiyarta ta rasu gimbiya Zahra'u ce ta riƙe ta”

“Amma ai sarauniya ya kamata a ce mata ba gimbiya ba”

“Ita ta mayar da shi a gimbiyar,babban burinta shine hawa karagar mulki.Domin biyan buƙatarta shine ta sadaukar da jinin mijinta sannan kuma ta yi aƙawarin zama a haka babu aure har ƙarshen rayuwarta”

“Amma tana da yara?”

“Ba ta taɓa haihuwa ba,hatsabiyayar bokanya ce da kike ganinta babu abin da ta iya sai tsafi ” cewar Uwais .

Na ce “ amma wannan ɗin ma duk tsafi ne muke,ƙofar ɗakin nan ma fa da tsafi ake buɗe ta”

“A'a ba tsafi ba ne,alƙaluman ruhaniya ne.Ba mu muka nemi taimakonsu ba haka kuma ba su ɗora mana sharuɗan komai ba.Yanzu dai duk mu bar wannan maganar ki jawo Yarima Khaleed a izuwa nan,ke kaɗai ce kawai za ki iya yi masa iso ba tare da an samu matsala ba”

“Ni kuma ? Saboda me?”

“Saboda ruhinsa korarriye ne daga wannan masarauta,gimbiya Layya ta yi tsafin da muddin tana numfashi Yarima Khaleed ba zai taɓa hawa karagar mulki ba wanda kuma hawan nata shine zai sa sihirin jikin mai martaba ya fita duka”

“Amma yanzu mine ne kenan na fitar masa?”

“Kambun maita ne wanda suka saka masa, MACIJIN CIKI mai kashe dukkan macen da sarki ya aura domin kar ya samu wani magajin”

Shiru na yi ina jin ƙiyayyar gimbiya Layya na ratsa ruhina.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .
```

_____

BOOK3

21_22

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi □ Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku□□□ muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni’ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta □ mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal □□

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu.....

Uwais ya je ya ɗauko min kundin hotunan ahali ya miƙa min,page ɗin farko sunan masarautarsu ce a rubuce da babban baƙi.Ta gaba kuma hoton kakan Yaya Khaleed ne da matarsa sai kuma ɗan ƙaramin yaronsu wanda tuni na fahimci mai martaba Waleed ne,wata page ɗin na buɗe sai ga hoton wata kamilalar mata cikin shigar sarautar .

“Anna kenan mahaifiyar Yarima Khaleed ” cewar Uwais, da na yi gaba sai na ga hoton Khaleed ɗin tun yana ɗan shekara biyar haka amma kamanninsa na nan har yanzu,na saki murmushi ina shafa hoton tare da addu'ar Allah sa yaron da zan haifa yayi kama da shi.Haka na dinga kallon hotunan ɗaya bayan ɗaya har na gama na rufe na ce “duk sun yi kyau,amma mi yasa ban ji ko sau ɗaya ka tambaye ni ita Anna tana ina?”

Ya murmusa kafin ya ce “mun san da cewa ta rasu! Saboda akwai wani daɗaɗen sirrin masarauta da yake mallakinta ne ,tun ranar da ta sa ƙasa ta bar gidan da ya fito yayi kuka ya koma bai sake fitowa ba sai ranar da ta mutu ya fito ya zubar da jajayen furanni,rana ta gaba kuma shine ranar zagayowar haihuwar Yarima Khaleed,to daga nan ne kuma ya dinga fitowa lokaci zuwa lokaci .Ranar aurenku da Khaleed ma har naman bikin ya kawo min na ci”

Ido na tsura masa kawai ina kallo har ya gama magana,na ce “amma wannan ɗin ma duk tsafi ne ko?”

Ya miƙe tsaye tare da cewa “eh to ta wata hanya za a iya fassara shi da tsafin,yayin da kuma in muka ɗauki tarihin ruhaniya za mu ce wata baiwa ce da duniyoyin biyu ke cuɗanya da junansu.Yanzu dai tashi na kai ki ɓangaren da za ki zauna,in sha Allah zan koma na tawo miki da dukkan kayanki”

Ni ma tashi tsayen na yi ina mai cewa “a'a ba zan zauna a masarauta ba domin akwai wasu ayyukan masu muhimmanci da zan gudanar,sannan Yaya Khaleed ba zai taɓa tako ƙafarsa a nan ba a tsalle ɗaya dole dai sai mun samu kyakkyawar fahimta.Sannan ina so a karon farko na karya wannan canfin na cewa dole sai Yaya Khaleed ya hau karagar mulki mai martaba zai samu lafiya,ka yarda da ni wannan abubuwan da suke faruwa daga ɗazu zuwa yanzu duk na yi su a mafarki kawai maimaici nake gani”

Shiru yayi yana kallona na wani lokaci kafin ya ce,“amma sai nake ganin kamar fitar ki cikin masarauta akwai matsalar tsaro,domin za ki iya fuskantar hare-hare daga magauta”

Na murmursa na ce “domin wanan harin kawai nake son na koma can masaukin ɗalibai,saboda tabbas ban zo nan ɗin ba sai don shi kuma a shirye nake na yaƙi duk wani taƙadirin matsafi da ƙananun mayun garin nan”

“You are the best!” ya furta yana murmushi kafin ya ƙara yi min iso kusa da gadon da mai martaba ke kwance yana bacci.Na yi tsaye ina kallonsa cike da tausayi,wayata na ɗauko domin yi masa hoto amma sai na ga wasu baƙaƙen ruhi a zagaye da shi waɗanda sam ba su iya ɓoyewa Camera ba.Yi na yi kamar ban gansu ba na ɗauki hoton ,kuma dukkansu sun fito jikin hoton hakan kuma yayi min daɗi.

“Mu je” ya faɗa tare da yin gaba na take masa baya,shi ya buɗe ƙofar.Bayan mun fito ne yake cewa “sama da kwana bakwai kenan sarki bai rintsa ba sai yau”

“Ai dole ya kasa bacci saboda macijin cikinsa da jinin mutane yake rayuwa,tun da ya bar auren matan shine ya koma cin hanjin cikinsa da kuma jininsa”

“Uwais!” muryar gimbiya Layya ta karaɗe falon,a tare muka juya ni da shi muna kallon ta tana can daga saman bene.

Cike da ƙasaita ta fara saukowa tana mai cewa “wane mataki ne ka taka a masarautar nan da za ka shure dokata haka? Tun yaushe ka fara zartar da hukuncin

ban sani ba? Wace ce wannan yarinyar? Sam ban yarda da ita ba,ka ce nurse ce mai kula da mai martaba ina za ta je kuma yanzu? Ko ita ta fi sauran duk likitocin da suka yi yayin duba mai martaba ne?”

Ba tsoro ballantana fargaba na ce “ sarauniya Layya na yi tunanin tun a bakin ƙofa mun gane junanmu kin san ni kamar yadda ni ma na fahimci ma'ajiyar ruhinki,kar ki wani ɓata wa kanki lokaci wurin kawo kanun labarai kai tsaye ki je da gundirin labarin.Mi kike son sani? Jikin mai martaba ? To ya samu bacci bayan wani dogon bincike da na yi masa na gano yana ɗauke da macijin ciki na basa magani yanzu haka bacci yake,sai me kike son sani kuma ?”

Tsoro ne ya bayyana a yɼan ƙananun idonta masu ɗauke da maganar da na fahimci mi take cewa ‘ kar dai ɗan ƙaramin kiyashin da na raina ya gallabi rayuwata ta yadda zan kasa zama ɗam!’

Daga can saman benen kuma wata mata ta soma saukowa ita da wata matashiyar budurwa wacce ta fi ni girma a jiki sannan a shekarun ma ina tunanin haka.

Gaban gimbiya Layya suka zo suka yi tsaye ,uwar ce ta ce “ mun gama ranki shi daɗe”

Gimbiya Layya ta dubi Uwais tana wani murmushi kafin ta ce “ za ku ci gaba da zama a can sashena kuna yi min hidima,ai sanin kanku ne ku ɗin baƙin haure ne a wannan masarauta ku ba jinin sarauta ba ne,don haka kowa ci ladar kuturu dole yayi masa aski”

“Abba don Allah ka yi magana ni dai Allah na gani ba zan iya zama a sashen can ba” budurwar ta faɗa tare da zuwa da gudu za ta rungumi Uwais amma gimbiya Layya ta wani hura iskan bakinta budurwar ta tsaya cak kamar gumki.

Na waro ido ganin tsafi ƙarara babu sakayawa a gaban kowa kuma,sai na ga gimbiya Layya ta saki murmushi tana kallona kafin ta ce “ Uwais ka iya faɗa wa yɼarka masarautar nan tawa ce,kai ɗan shan miya ne kawai saboda an auro Yayarka

wacce ba a ma san jinsin mutum ce ko aljan ba,ko da yake yanzu ta zama tarihi.” tana gama faɗa ta sake hura iskan ga jikin budurwar sai a lokacin ta motsa.

Uwais ya ce “ Latifa wuce can sama,zan mayar da nurse in na dawo zan shigo na same ki” tana kuka ta ruga da gudu ta haura sama yayin da kuma ya watsawa matar harara wacce nake tunanin matarsa ce,ita ma barin wurin ta yi.

“Ka faɗa wa ungulu ta koma gidanta na tsamiya,domin gidan rama ba nata ba ne” gimbiya Layya ta faɗa .

Kai tsaye na amsa mata da cewa “ kar ki taɓa tunanin ɗan ƙaramin siddabarunki zai tsorata SEERAT! Wannan ɗin ba komai ba ne a wurina face wasa yara, ki sa a ranki kuma ni ce nan zan ruguza baƙar tawagarki ta matsafa” ina gama faɗa na ware tafin hannuna na hagu na cilla ta can sama sannan ta bugu ga ƙarfen bene har goshinta na fashewa.

Da sauri Uwais ya nufo ni yana cewa “ don Allah ki rabu da ita,tana da ciwon kwanya ne ita ɗin mahaukaciya ce fa ko ba ki lura da hakan ba tun ɗazu”

Na yi wata dariya na ce “ au haba? Sai yanzu na lura ka san ba kasafai ake gane haukan mutum uku ba,attajiri,malami da kuma sarki to ita ma ka san basarakiya ce ta matsafa” ina gama faɗa na saka idona cikin nata tare da yi mata murmushin ƙeta, Uwais ne ya ja ni muka fito.

Wannan karon da kansa ya karɓi key zai yi draving ɗina,sai bayan mun fita daga cikin masarauta sannan na ce “ amma mi yasa na ga kamar duk kuna tsoronta?”

“Ba kama ba ce haka ɗin ne,kaf masarautar yanzu ƙarƙashin ikonta muke.Ni ne mai ɗan sauƙi saboda ina ɗauke da abubuwan sirri na mai martaba,ciki kuwa har da sarƙar wuyansa wacce ke bani damar shiga sashen da yake a yanzu.”

“To amma mi zai hana kai ka hau karagar mulkin kafin Sarki ya samu lafiya?”

“A'a bana buƙata gaskiya,Yarima ne ya cancanci kujerar ba ni ba.Amma na tambaye ki wannan abun da kika yi wa gimbiya Layya mine ne shi?”

“Ni kaina ban sani ba kawai dai na san ina iya sarrafa hannuna na motsa abubuwa da shi”

Ya ja numfashi kafin ya ce “ amma kin san da yau sai sun yaƙe ki ko?”

“Eh na sani! Yanzu haka na matsu ka sauke ni akwai da wacce nake son yin magana”

“Ki kira ta izuwa nan mana”

“A'a ba za ta zo ba”

“Saboda me?”

“Kana ɗauke da sarƙa mai hoton tambarin masarauta”

Ya saki murmushi kawai kafin ya ce “ kin san mene ne ainihin asalin tambarin nan?”

“A'a sai ka faɗa ”

“To gimbiya Zahra'u ce ta fitar da shi,ita wacce kike ikirarin kina son ganinta za ku yi magana Yayar mahaifiyar Khaleed ce.Ita ce babba sannan Zahra'u ni kuma autansu,tun muna yara ra'ayoyinmu suka sha banban da na juna musamman yadda ita Bintu take da mugun son abin da ya shafi tsatsubai ni kuma da gimbiya Zahra'u bar mu da tilawar Alkur'ani wanda hakan ashe yana baƙanta ranta ba tare da ta san dalili ba sai ta shiga zana hoton wani tambari wanda shi ɗin ya kasance ashe na wata masarautar jinnu ne,a lokacin da ta nuna wa Zahra'u ita ma sai ta zana wannan ɗin wanda yake ɗauke da sarƙar wuyanmu daga nan suka fara rigimar cewa na wa ya fi kyau.Ana cikin haka ne wani iska mai ƙarfi ya taso ya mamaye duk illahirin farfajiyar wurin,a gaban idonmu wani abu mai kamar inuwa ya bayyana yayi sama da Bintu wato Bafulatanarki,yayin da mu kuma aka cilla mu gidan sarki Hasheem mahaifin mai martaba a lokacin shi ke mulki .Tambarin Zahra'u shine abu na farko da ya ɗauki hankalinsa da ya tambaye ta nawa za ta sayar masa sai ba ta ce komai ba sai kuka da take yi,ni ne na yi masa bayanin abin da ya faru jin haka sai ya zuba malamai aka soma karatun Alkur'ani yayin da kuma ɗaya ɓangaren ya sa aka yi amfani da tambarin gimbiya Zahra'u matsayin na masarauta.Kwana uku da ɓatan Bafulatanarki sai aka tsince ta a ƙofar masarauta,sama da sati biyu kafin ta farfaɗo mun yi murna sosai sai dai sam ba ta yin magana” yana kawo wa nan sai yayi shiru.

Na ce “ amma iyayenku fa?”

“Duk sun rasu”

“To kenan Bafulatanata fatalwa ce?”

“Eh kusan haka ne tun da esprit ɗinta ne ke yawo”

“Mi ya jawo hakan ?”

“Ta auri wani mutum ne a nan garin tana tsananin sonsa amma kuma cutar da ita yake har dukanta yake,wata rana tsautsayi yasa ya dake ta ashe aljanin da ya taɓa tafiya da ita har yanzu yana jikinta kawai sai ta ɗirka wa mijin uban duka har sai da ya suma shine a ƙarshe ya sake ta”

Shiru na yi kawai ina nazari maganganun sa,sam ban yarda da su ɗari bisa ɗari ba,amma tuni ya kawo ni gida sai na fita ina yi masa sallama.Ko da na shiga ciki mutanen da na tarar tsiraru ne duk sun tafi aiki,kan yɝar katifata na haye sannan na kira Yaya Khaleed.Sai da na jera wajen kira biyar,a na shidda ne ya ɗauka.

“Shine sai yanzu ka ɗauka” na faɗa a shagwaɓe.

Ya ce “ ki yi haƙuri babyna, wallahi abubuwa ne sun yi yawa.Wata shari'a ce aka yi munafurci ya yi wa yɝar aikinsa fyaɗe a ƙarshe ya kashe ta amma a haka tsabar zalunci ka tauye haƙin yarinyar aka basa gaskiya saboda iyayensa nada kuɗi,to amma kin san me?”

Da sauri na ce “ a'a sai ka faɗa ”

“Wallahi ya haukace ! Sai hauka yake yana faɗar sunayen yɝan matan da ya lalata”

Na saki murmushi na ce “Alhamdullah! Shi yasa ba kowanne mahaukaci ne ya kamata ya bamu tausayi ba,wani Allah kaɗai ya san mene ne silar haukan nasa.Ita ainahin wacce ya yi wa fyaɗen tana ɗauke da baƙin iska wanda ya aure ta shekara da shekaru,shine ya haukata shi amma kai abun ya bada citta ” na faɗa tare da yin dariya sai na ji an kwaikwayi dariyar tawa cikin muryar ɓeraye.

Shiru na yi ina baza ido amma ko alamun ɓera ban gani ba don babu wasu kaya sosai a ɗakin ballantana na ce a can ya ɓuya.

“ SEERAT ? Kina ji na?”

“Eh Yaya ina ji” na faɗa tare da ƙoƙarin saita nutsuwata sai dai abu ya cuttura saboda ina ji a jikina kamar ana ankare da duk wani motsina,duk sai na tsargu.

“Yaya zan kira ka daga baya” na furta tare da kashe kiran ,kamar wata mahaukaciyar na ce “ to ina sauraren ku me kuka zo nema wurina?” shiru babu amsa sai labulayen ɗakin da suka soma kaɗawa,yayin da ƙwan lantarki ya soma wasar yara ya kunna kansa ya kuma kashe kansa.

“ Ah to na fahimta wasa kuka zo yi ashe to ku ci gaba in kuna da magana bayan hakan sai ku taɓo ni” na faɗa tare da saka airpix a kunne,hoton mai martaba kuwa Ammy Habibah na turawa shi duk da kuwa ina cikin fushi da ita.Kamar wacce ke jirana dama ina turawa ta buɗe,sai kuma ta kira ni video call kamar ba zan ɗauka ba sai kuma na ɗaga.Sai da wayar ta kusan kubce min saboda ban shirya ganinsu ba,wasu babaƙun fuskoki ne suka bayyana a screen ɗin wayata dukkansu suna zaune a bayana sun zagaye ni.....

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3

23_24
```

Ina ƙoƙarin kashe kiran amma Ammy Habibah ta dakatar da ni,“ su wane ne suka kawo miki ziyara SEERAT? ”

Ban kai ga bata amsa ba na ji an shaƙe min wuya a dole na saki wayar domin ƙwatar kaina,amma ina tuni sun yi min ƙawanya ta ko ina sai duk na rasa yadda zan kuɓutar da kaina kamar ƙuda a cikin ƙullun waina.

Idona har wani lummm suke tsabar yadda nake jin azaba ta ko ina,sai kuma na ji tsit kamar cirar ƙaya komai ya tsaya.Na riƙe wuyana da dukkan hannuwana ina jawo numfashi,kamar daga sama nake jin muryarsa “ SEERATna???” sai kuma ya tallabo ni ya rungume ƙam a ƙirjinsa,dakyar na ƙoƙarta na ce “ Yaya Khaleed zan mutuuu!” bai ce min komai ba sai bakinsa da ya ɗora kan nawa ya dinga shayar da ni yawunsa waɗanda suka zame min tamkar maganin waraka.

Ras na dawo normal,na janye jikina daga nasa ina kallonsa kafin na ce “ ya aka yi ka zo nan alhalin ba mu daɗe da ida waya ba kana Yamai?”

“ SEERAT na sha faɗa miki duk wannan abin da kuke kira baiwa duk sharrin sheɗanu ne da fatalwa,in na ce miki ga taƙamaimai hanyar da na bi na zo nan to na yi miki ƙarya.Ni dai kawai na san na ga tsuntsuwar nan kuma sai na tsinci kaina a nan,haka zuciyata ke faɗa min wai kina cikin matsala”

Na lumshe ido ina zancen zuci ‘ tabbas dakwai banbanci tsakanin mutanen da na yaƙa a can baya da kuma su gimbiya Layya da tawagarta! Mene ne suke taƙama da shi? Duk ƙarfin tsafi ne ko me? ’ na tambayi kaina ba tare da kuma na samo amsoshin ba na ware idona ga Yaya Khaleed.

“ Meke faruwa SEERAT? Ji nake kamar yanayin iskan garin ya sha banban da na saura”

Shiru na yi ban basa amsa ba saboda bayyana Bafulatanata a can bakin ƙofa ta yi wata tsayuwa da fararen kayanta tana kallona.Ni ma ido kawai na zuba mata,can ta gaji ta ce “ za ki kirawo Basheer domin wannan ba aikinki ba ne nasa ne,ke ɗin wurin ajiyarsu kawai kike da.Ki tabbatar duk kin kwashe su kin zuba su a sarƙar wuyanki kar ki manta a cikin masarauta akwai mutum ɗaya mai fuska biyu naki ne gano kowane mutum ne” tana gama faɗa ta fice,daidai nan kuma wayata ta ɗau ruri.

Na jawo na duba sai na ga sunan Ammy na yawo kan screen,da sauri na ɗaga sai na ji ta ja wata doguwar ajiyar zuciya tana mi cewa “ Alhamdullah! In sha Allah zuwa gobe muna shigo wa ,yanzu haka tuni na haɗa kayana zan zo”

“Ku tawo tare da Basheer ” na faɗa da sauri.

“To babu damuwa” sai kuma ta kashe,jikin Yaya Khaleed na je na shige ina jin wata irin kasala ga kuma yunwa .

“Yunwa nake ji” na faɗa wasu guntayen hawaye na zubo min.

Rigata ya ɗaga ya soma shafa cikina,bai kai ga yin magana ba muka ji tsayuwar mota kafin kuma sallamar Uwais.Da sauri na tashi zaune ina cewa “ Yaya Khaleed don Allah ka ɓuya ban so su san ka zo” sai dai ko kafin na rufe bakina Uwais ya shigo hankali tashe,a tare muka miƙe .

“Masarauta ta hargitse suna can sun tada bori suna kiraye-kirayen sunan aljanai” Uwais ya faɗa kamar zai yi kuka idonsa ƙurrr kan Yaya Khaleed wanda shi ma ɗin Uwais yake kallo.

“Ka zauna zan je na dawo” na faɗa ,Yaya Khaleed yayi min wani kallo irin tun da mahaukaci ne ni.

“Mu je” ya furta yana yin gaba, da sauri na biyo shi ina mai cewa “ Yaya Khaleed don Allah kar ka je wallahi kashe ka za su yi,mutuwa za ka yi don Allah ka tsaya” na kamo hannunsa hankali tashe don tuni duk an nuna min komai a mafarki muddin ya shiga masarauta to yayi ban kwana da duniya.

“Waɗanda suka nuna miki hakan ki faɗa musu sun yi ƙarya” Yaya Khaleed ya faɗa tare da buɗe mota da kansa ya shiga ,ni ma a dole na shiga dafe da zuciya.

Kamar Uwais zai tashi sama haka yake gudu,ina son yi wa Yaya Khaleed tambayoyi amma bai bani fuska ba.Muna isa masarautar sararin samaniya ya ɗauki wani launi mai matuƙar firgitar wa,duk wani matsafi da ke wurin sai hankalinsa ya dawo gare mu.

Karon farko kenan da na ji tsoron tunkarar mugu saboda waɗannan ɗin siffarsu ma kawai abar tsoro ce,bayan Yaya Khaleed na ɓuya ina mai ciro sarƙar wuyana.Daga inda nake a laɓe nake jin sautin muryarsa yana karanto ayoyin tsari da kuma na yaƙar duk wani matsafi.

“Ku zo mu shiga daga ciki” cewar Uwais,har mun bi bayansa sai kuma muka tsaya cak sakamakon wani iska da ya turnuƙe wurin,wata dunƙulalar guguwa ta tawo tun daga sama har ta dira ga ƙasa.

Na waro ido ganin Basheer a tsaye cikin wasu kaya kamar na mafarauci.Gimbiya Layya da maƙarabanta duk suka yi baya suna waro ido ,“ Yaya Khaleed ka shiga daga ciki mai martaba na neman agajinka,kai kaɗai ne ke iya yin wannan aiki ni kuma ka bar ni da SEERAT ”

“A'a ba ta da wani ƙarfi,zan shiga da ita” cewar Yaya Khaleed.

Da sauri na ce “ ka shiga kawai za mu yi aikin tare da Basheer” sai na saki murmushi ganin karon farko mafarkina bai zo daidai ba duk an sauya shi a zahiri,Uwais ne ya ja hannun Yaya Khaleed suka shiga ciki.

Na matso na yi tsaye bayan Basheer ina cewa “ ta ina za mu soma?”

“Ki yi min shiru Malama kar ki ɓadda min lissafi” Basheer ya katse ni yana mai ci gaba da karanto wasu sunaye waɗanda na tabbata na jinnu ne,sannu a hankali kuwa na soma ganin irin inuwar nan na cika masarautar.

“ Wannan ɗin cin amana ne mai girma Shakal! Sam wannan bai dace da tsarin mulkin duniyar ɓoye ba,kai ne da kanka ka shimfiɗa mana dokoki yanzu kuma shine za ka karya su ? Mene ne laifinmu don mun nemi adalci?” gimbiya Layya ta faɗa tana zarar ido .

Basheer ya buɗe baki ya soma yin magana sai dai sam ba muryarsa ce ba ta wani tsoho ce,“ Layya kar ki manta aljani bai da gaskiya,cin amana wannan shine babban jigonmu.Kin yi min alƙawarin bani abubuwa dayawa amma ko ɗaya babu wanda kika cika,ɗan ƙaramin tambarin ma kin kasa sauya wa to ina ga ƙona duk wasu takardun tarihi.Wacce ke da burin canza tambarin masarautar nan yanzu ta ce ba ta da muradi don haka kashe ki zan yi” yana gama faɗa ya jefa mata wata ƴar ƙaramar ƙusa da ya fitar daga bakinsa,sai dai tun kafin ta cake ta cikin tawagarta wani ya tare ƙusar ta huda ƙirjinsa ya faɗi ƙasa a mace.

Hankali gimbiya Layya ya tashi,tsoron mutuwa ya fito kan fuskarta ƙarara.Duk yadda Basheer ya so kashe amma abu ya cuttura,cikin wata irin murya ya ce “ SEERAT yi amfani da tafin hannunki ki ruguza min taronsu ” ko bakinsa bai rufe ba kuwa na aiwatar .

Tamkar fankon gyaɗa haka duk suka watse suka yi sama cikin iska sai a lokacin ya samu ya caki gimbiya Layya ta zube ƙasa dafe da saitin zuciya,Basheer ya ce “ yi sauri ki jaye ta ki adana ta cikin sarƙarki kafin ta fara aman powerta” ban san dalilin

duk saka mutane a cikin sarƙar ba,amma haka na cilla wa gimbiya Layya ita nan kuwa kifin ya haɗiye ta.

Gefe na koma ina kallon yadda Basheer yake fatattakar matsafan da suka yi fito na fito,sai bayan ya gama kawai ya zube ga ƙasa .Da sauri na nufe shi ina mai jijiga shi dakyar yake ware idonsa waɗanda suke canza kaloli kamar hawainiya.

“Ruwaaa!” ya furta kamar ransa zai fita,bai ko rufe bakinsa ba sarƙar hannuna ta soma feshin ruwa,da na duba sai na ga kifin nan ne ke amansu.

Sai bayan ya sha ruwan ne sannan ya karɓi sarƙar hannuna ya soma kaɗa ta kamar majaujawa,abun mamaki duk gawarwakin da ke zube a ƙasa suka soma tashi sama suna bin iska tamkar hayaƙi haka suka ɓace.

Bayan ya gama ne ya miƙa min na mayar da ita a wuyana,sai a lokacin muka shiga daga ciki.Duk yadda Basheer ya so bin bayana domin mu shiga part ɗin da mai martaba yake amma abu ya cuttura ya kasa ƙetara ƙofar.

Da mamaki nake dubansa na ce “ ka shigo mana”

Ya girgiza min kai yana nuna min saitin zuciyarsa wacce ta kumbura.Ban san lokacin da na saki ihu ba,Basheer yayi baya zai faɗi amma na taro shi.

Uwais da Yaya Khaleed suka fito suna tambayar ba'asi,na sanar da su.Sai na ga yanayin fuskar Uwais ya canza,“ mene ne?” na jefo masa tambayar.

“Sai haƙuri gaskiya,ina ga sarki Shakal na son janye ɗan uwanki izuwa waccan duniyar.”

“Akan wane dalili?”

“Saboda a cikin jikinsa ya girma,Basheer ba zai taɓa dawowa normal ba muddin ya zauna a wannan duniyar.Wannan kumburin na zuciyarsa ba komai ya haifar masa da shi ba sai musulman aljanan da ke gadin sashen mai martaba,su ɗin sun kasance abokan gaban sarki Shakal in ba ki manta ba na baki labarin tambarin gimbiya Zahra'u da kuma na Bafulatanarki,to ita kanta gimbiya Zahra'u tana ɗauke da aljanai amma su ɗin musulmai ne kuma tambarin masarautar nan ainahin nasu ne”

“Duk ku bar zancen tambarin nan don Allah ku yi tunanin yadda za sama masa lafiya,a duk duniyar nan babu wanda ya isa ya yi maka wani abu sai da yardar Allah don hakan zancen tambarin gimbiya Zahra'u da na wata Bafulatana duk bai shafe mu ba.” Yaya Khaleed ya faɗa tare da tsuguno ya ɗora hannunsa ga goshin BASHEER,yana soma yi masa karatu zuciyar ta soma yin motsi sosai yayin da kuma ya soma shure-shure.Mun shagala sosai akan Basheer na ga kamar mutum ya shiga sashen sarki da sauri na nufi ɗakin,“ dakata! ” na furta ganin wata mace hannunta riƙe da wuƙa sai ta juyo jikinta na kyarma sai ta yi wani ihu tare da ɗaga wuƙar ta yo kaina.

Kamar an kunna ruwan pampo haka wani haske ya fita daga goshina ya ɗaure ta tamau.Ihu ta soma tare da kiran sunan Uwais,“ SEERAT mi kike haka?” na ji muryarsa daga bayana.

“Kar ka tausaya mata,ta kashe ɣar cikinta yanzu kuma jinin mai martaba take son sha” na furta daidai nan kuma sarƙar wuyana ta jawo matar Uwais kai kace mayen ƙarfe har sai da ta zuƙo ta sannan ta haɗiye ta.Da sauri kuma na yi baya ina jin tamkar ana yi min magana a cikin kai “ mission ɗinki ta cika SEERAT congratulations akan wannan jajircewa” luuu na yi saboda fitilun idona da suka ɗauke ɗif,ban ƙara sanin abin da ya faru ba daga nan kawai na tashi na tsinci kaina a gadon asibiti ga kuma ahalina kewaye da ni duk murmushi kan fuskarsu.....

```MRS SADAUKI✍```
```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

BOOK3

25-26

Ammy Habibah ce ta matso kusa da ni tana cewa “ ya jikin naki SEERAT?”

“Da sauƙi alhamdullah! Yaushe kika zo?”

“Tun shekaran jiya”

“Kenan kwana biyu na yi a nan gadon asibiti? Ina Basheer?” na tambaya da sauri tuna halin da na bar shi.

“Yana can gidan mai magani,ana yi masu ruƙiya” ta bani amsa cikin jimami.

“Ruƙiya kuma?”

“Eh aljani je jikinsa,har ma yayi magana amma ya ƙi fita wai sai ya cika masa burinsa na zama sarki .Ke kuma fa ya labarin ita Bafulatanar ?”

Shiru na yi ban ce komai ba sai Yaya Khaleed da nake ta kallo wanda har yanzu bai motsa ba sai kallona da yake.

“Seerat faɗa mini ya kuka rabu da ita?” Ammy ta sake tambaya ta.

Na ja ajiyar zuciya ina tuna doguwar tafiyar da na yi wacce take tamkar a duniyar mafarki,amma kuma zahiri ne ruhina ne ya tafi can.

“Ta kai ni duniyar su sannan ta umarce ni kan na cire sarƙar wuyana na jefa cikin kogi,da na jefa sarƙar sai na ga duk mutanen da na ɗura a ciki sun fito suna ihu tare da neman agaji amma babu mafita aljanan ruwa haka suka dinga cacakarsu suna cin naman jikinsu.Daga ƙarshe kuma ta kai ni na yi ziyara ga jaruman da suka taka rawar gani,an nuna min Ayodele wata babbar jaruma ce mai magana da gawa ita ma ɗin dai ta yi gwagwarmaya wurin kai ƙarshen mayu,sai wata Siren mai suna Sarah ita ma ta yi yaƙi ne da matsafa”

Ammy Habibah ta ja ajiyar zuciya ta ce “ madallah tun da dai a ruwa kika jefar da sarƙar shikenan hankalina ya kwanta ba za a ƙara yaudarar wani da ita ba da sunan baiwa”

Na saki murmushi na ce “ ai kuwa Bafulatana ta ce ita wannan sarƙa za su juya ta cikin salo na daban,sannan tuni ta sanar da ni akwai wani tsarkaken ruhi da zai samu sarƙar nan ta yadda zai kawo ƙarshen MAFIYA a duniya”

“Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un !” Ammy Habibah ta furta tare da zama tana dafe ƙirji,“ lafiya ya na ga kin tsorata? Ina ce dai ni ma na yi zama da sarƙar ” na furta tare da shafa wuyana wanda a yanzu babu komai.

Ammy ta kamo tafukan hannuna ta ce “ SEERAT dukkan miyagun da sarƙar nan ta haɗiye to suna ɗauke da power mai ƙarfi,ya kike ganin in an haɗe power Mamuh,Goggo Hajara,Rahamu, shugaban makarantarku,gimbiya Layya da duk sauran da ba a ma san iyakar su ba? In an haɗe su wuri guda ya zamana mutum ɗaya ne ke da ƙarfin juya wannan power me kike gani zai faru?”

Tsoro ne na ji ya kama ni,har zan yi magana na tsinkayo muryar Yaya Khaleed na cewa “ babu fa ruwana da shi,ina ce tun jiya na sanar cewa muna asibiti cikinku akwai wanda ya zo ne? Sai yanzu za ka wani kira ni kana cewa wai Shareef bai da lafiya,ita matar tasa mene amfaninta?” sai kuma yayi shiru,ban ji abin da aka ce masa ba na dai ga ya miƙe tsaye yana cewa “ mayya ce? To kai ya aka yi ka gane ita mayya ce? Bari ma gani nan zuwa”

Ambaton sunan mayya sai yasa na ji wani karkashi tare kuma da tuna zancen Bafulatana a duniyar mafarki lokacin da ta karɓe sarƙar wuyana sai na tambaye ta shi kuma tambarin goshina fa da na tafin hannuna? Sai ta bani amsa da saura ƙiris su fita amma akwai guntun aikin da zan yi.

“Yaya Khaleed ka tafi da ni” na furta ina dirowa daga kan gado,ya yi min wani mugun kallo kafin ya fice ai kuwa na take masa baya.Sai da na fito a farfajiyar asibitin na fahimci cewa ashe nan ɗin Yamai ne ba can Say ba,Yaya Khaleed mota ya buɗe ya shiga mai ɗauke da tambarin masarauta,na saki murmushi tare da yin amfani da hannuna na hana motar tashi har sai da na fita na nemo taxin da zan shiga sannan na saki motar tasa.

Kamar yadda na cewa mai taxin haka ya dinga bibiyar Yaya Khaleed har ya isa wani wuri ya ɗauki Shuraim sai kuma aka yi gaba,haka na take musu baya har muka isa ga gidan da motarsu ta shiga.

Mai taxi kuwa ce masa na yi ya jira na fito zan basa kuɗin,kawai sai na shige.

Tun a tsakar gidan nake jin kakarin mutuwa wanda ba komai ya haifar da haka ba sai don an damƙe kurwarsa.Su Yaya Khaleed tuni sun shige falon,ni kuwa bakin ƙofa na yi tsaye ina hangensu ta yar ƙofar da suka manta ba su rufe ba.

Iyayensa na gani ,mahaifin Shareef sai zarar ido yake da dukkan alamu shi yasa meke damun ɗan nasa ita kuwa Uwar ba ta sani ba.

Na shagala sosai wurin kallon abin da ke wakana sai jin wani abu mai santsi ya taɓa ƙafata,a hankali na kai dubana ƙasa sai na ga wani maciji ɗan siriri jikinsa sak irin na capet ɗin da ke can shimfiɗe a tsakiyar falo.

Cikin ɗakin macijin ya shiga,zuciyata ta tsananta bugawa don na fahimci wannan ɗin ba maciji ba ne.Ai kuwa ban tsaya wani jinkiri ba na shige ɗkin na yi tsaye,duk da ina jin idon kowa kaina amma hakan bai sa na bar dubana ga ƙasan capet ɗin ba.

Neman macijin nake amma ya saje da capet,dakyar na iya gano shi ta hanyar jajayen idonsa.Ta kai bakinta za ta caki wuyan Shareef na yi saurin ware tafin hannuna,tamkar mai saman ruwa haka na rabo macijiyar daga jikin ƙasa.

A lokaci guda duk suka fitar da sautin tsoro da kuma mamaki,yayin da kuma munafukar matar Shareef ta soma juye-juye tana son sauka ƙasa domin cimma burinta na kashe shi amma na ƙi bata dama so nake na tona mata asiri ta dawo a siffar mutane.

“Ki rabu da ni ” ta furta cikin muryarta raɗam.Shareef ya zabura ya tashi zaune,na saki murmushi na ce “ ki mayar masa da semence ɗinsa da kika kwashe,da kuma kurwarsa”

“Ba zan yi kunya biyu ba” ta furta tare da ƙarawa jikinta tsayi domin cizon Shareef amma mahaifinsa ya tare ta same ga hannu yayi baya yana ihu.A lokacin ne kuma na matsa mata lamba na soma cutar da ita ina cacaka mata ƙayoyi a jikinta,jurewa ta soma yi tana yin wani gurnani sama da minti goma kafin ta rikiɗa ta zama mutum jikinta duk ko ina a hude tana fitar da jini .

Banda kukan nadama babu abin da Shareef ke yi,gefe guda kuma Shuraim ya ɗaure hannun ogansu.Na ƙarasa na kwance ƙyallen ina mai cewa “ a'a don me za ka ɗaure masa? Barsa gubar ta ratsa jikinsa ya ji irin raɗaɗin da mutanen da aka yi wa kisan gilla suka ji,a ƙarshe kuma ya take haƙinsu ta hanyar amfani da ikonsa da kuma tsafin da malaman tsibo ke yi masa”

Dattijon ya dube ni,duba irin na ƙeƙe da ƙeƙe kafin ya buɗe baki dakyar ya ce “ wallahi na yi nadama na tuba ki yi min rai na yi miki alƙawarin zan daina komai”

Na saki murmushi ina mai kai hannuna daidai saitin shatun haƙoran macijin,duk gubar da ta shiga ta fita daga jikinsa ya dawo daram.Sai a lokacin kuma na ƙara komawa wurin matar Shareef wacce na dabaibaye da haske ta kasa motsi,“ ki yi abin da na ce sai na bar ki da halinki ” na furta ina mai gyara tsayuwa.

Ƙwala-ƙwalan idonta ta zuba min kafin ta ce “ don me yasa kike son ceton mutumin da kullum bai da buri sai na ganin ya cutar da ke ya ɗunguza ki a inuwar ZAWARCI?”

“Mayar da alkhairi akan sharri shine ɗabi'ar mutanen kirki, wannan ba damuwa ba ce.Abin da na sani shine kawai hassada ga mai rabo taki ce,ya yi ya gama! Yadda bacci ya bar ido haka zai bar SEERAT ” na faɗa tare da samun kujera na zauna .

“Amma kin bani mamaki gaskiya,a sanina duk wani wanda ya samu dama irin taki yana juya duniyarsa ne da mugunta amma banda ke.Ki sani Shareef ba mutumin kirki ba ne,ya shiga garinmu ne da zumar samo matar aure mai kyau wacce dukkan abokansa za su yarda cewa tasa ta fi ta Khaleed kyau.Wannan ne yasa na aure shi ba don ina sonsa na sai don nuna masa ba dukan ƙyalƙyali ne gwal ba,a bayan wani kyawun akwai ɓaƙin hali.Tun ina ƴar mitsitsiyata nake sarrafa tsafi da maita,ko sau ɗaya ban taɓa jin sha'awar dainawa ba sai yanzu da na gamu da ke.Zan mayar masa da semence ɗinsa wato masarrafar ƙwayoyin haihuwarsa sai dai ki sani ba lalle ne ba ya martabarsa ta ɗa namiji ta dawo ɗari bisa ɗari ko yaya ne sai ya samu raunin sauke haƙin iyali” tana gama faɗar haka ta buɗe bakinta ta soma amayar da wani abu mai kamar hayaƙin wuta,haka ya dinga zageye Shareef wanda nadama ta aura. Tsawon lokaci kafin komai ya tsaya,ta dube ni ta ce “sai kuma wannan cutar ta maita ya za a yi na daina?”

Na ce “gidan Sarkin Mayu za ki je shine zai miki magani” na furta tare zuwa gare ta na soma warkar da ciwukan da na ji mata.

Sai a lokacin na dubi Yaya Khaleed na ce “ka yi haƙuri mijina,ina ganin daga yau SEERAT za ta koma normal kamar yadda kake so”

Sai ya sakar min murmushi.

Baban Shareef ya ɗauki magana,“haƙiƙa komai yayi farko to tabbas zai zo ƙarshe,na ga aya har da hadisi babu abin da zan ce miki sai godiya.Kai kuma Shareef maza je ka zo ka neme ta gafara ita da mijinta kuma daga yau kar na sake jin wani abu ya shiga tsakaninku da Khaleed”

Ido na tsurawa Shareef wanda ya zube gabana yana bani haƙuri,a ƙwayar idonsa kuma tsantsar nadama ce wacce uwar bari ta sa ya ji ta.Haka suka je suka rungume junansu shi da Khaleed,matar gidan ce ta kawo min abinci na ci sannan ta bani hijabi na luluɓe jikina don ban fito da shi ba.

Sam ba mu ga fitar matar Shareef ba sai kiran ujila da mai gadi ya shigo yana yi “an kaɗe Madam yanzu da ta fita ina ga ma ta sheƙa”

Duk a tare muka fita,ai kuwa ta mutu ɗin don babu alamun rai a tattare da ita.Asibiti muka nufa duk da haka,sai a lokacin na tuna na bar Ammy Habibah cikin zullumi.Tana ganina ta zo ta rungume ni tana sauke ajiyar zuciya ta ce “alhamdullah! Komai ya zo ƙarshe ko? To ke ma za da buƙatar a yi miki ruƙiya”

Na yi ɗan murmushi na ce “wai Ammy fushin mene ne na ga Yaya Khaleed na yi da ni ?”

“Saura ƙiris cikin jikinki ya ɓare shine dalili,mu je ki kwanta zuwa gobe za mu koma Say”

Da muka zauna ne na ce “Ammy bani labarin zuwan ki a Say,me da me ya faru?”

Ta ɗan saki murmushi ta ce “abubuwa masu daɗi mana,jikin mai martaba na daɗa sauƙi saboda ayoyin Alkur'ani da yake sha yake kuma wanka a bisa umarnin jajirtacen mijinki,Khaleed ɗana” sai ta yi wani murmushi har hawaye na zubo mata,sai ta ci gaba da cewa “kin san da cewa gorin da kika yi min ya zo ƙarshe?”

Na waro ido na ce “wane gori kuma na taɓa yi miki Ammy?”

Ta yi min daƙuwa ta ce “au kin manta kin ce gare ni kika gaji ZAWARCI? ” da sauri na rufe fuska da tafin hannuwana ina dariya.

Ta ce “shakirar yarinyar,to zan auri mai martaba Waleed” da sauri na buɗe fuskar cike da farin ciki na ce “ki ce na zama yar sarki”

“A'a matar sarki dai don lokaci yayi da Yarima Khaleed zai hau karagar mulki” furucinta yayi daidai da shigowarsa ya ce “don Allah Ammy ki bar faɗar haka,ni dai a mu koma gida tun da ta samu lafiya”

“A'a da saura sai ta gama shan allurai ”

“Allah Ammy ta samu lafiya yanzu nan ta gama wasa da maciji,ni dai a bani matata” ya faɗa yana wani yi min kallon da yasa har sai da na ji yanayin shauƙi,da sauri na sunne kai ina jin zuciyata na bugawa da ƙarfi.

“Khaleed ka fita idona na rufe,ina ce dai ka ji abin da likita ya ce ko? A barta ta huta kar a takura ta.Wai ma ba ka ce min ka ga ƙawar Safeenatu ba tana ina?”

“Tana cikin asibitin nan,yaɗarta babu lafiya tun bayan da ta ga mahaifinta ya haukace”

“Allah sarki Ma'idah tana ganin rayuwa” cewar Ammy Habibah tana mai miƙewa ta ci gaba da cewa “wane ɗaki take?” lambar ya faɗa mata,tana fita ya jawo ƙofa ya rufe har da saka key.....

ASSALAMU ALAIKUM

Mata masu abun dadi

Zuzeam ventures takawo muku babbar gara basa

Duka akan 6500 ki daure ki mallaki naki kar dama ta wuceki Garabasa gara basa 😁□□□□□ Mutun goman farko da goman 2 Zuwa goban 3 da suka siya promo dimmu na 6500na Kaza rabi Ciccibi Gumba 2 Gari 7in1 Tsimi 2 sunada kyauta abubuwa kamar haka 1.Matsin ba a Fira da wando sa mai gida kukan dadi 1k Matsin maganin infection 500 matsin kaska 500 Matsin dare daya wanka goma 1k Total total gift 3k😁 Kiyi kokari ki kasance aciki Garabasa kan garabasa Da 6500dinki ki

mallaki kayan da ko 13k Bata bakisu zakisha dadinki oga ya more har kyauta saikin samu insha Allah *08144015291* Maman yasmeen takuce 😍

Wa.me/+2348144015291 For more information say hi Ina uwar gida da Amaren bayan sallah zuzeam empire tashirya tsaff dominku muna gyaran ciki muna saida kayan gyaran jiki dilka sabulu dadai sauransu

DAHUWAR KAZA

Kin taba cin *DAHUWAR KAZA 5in1* wato *Ni'ima, Matsi, Chikowa, MAllaka, da Karin soyayya*

Duk me buqata TAYIMUN magana ta Pvt *Akwai kyauta mai tsoka ga mutun 5 da suka fara siya*

INA MASU JEGO DA AMARE

Karku bari wannan dama ta wuceku

08144015291

Zuzeam ventures

ASSALAMU ALAIKUM Mata ga wani sirri mai abun mamaki amma mata aji tsoron Allah kada ayi amfani da wannan dama kijuya mai gidanki yanda bai kamata ba amfaninshi shine a tafin kafar ki kawai zaki shafa lokacin kwanciya zakiga daukar hankali wurin mai gida amman don Allah karki juyashi yanda bai kamataba amana ce na baki 08144015291. 1500kacal

Munada kaya kala kala wanda bazasu faduba kedai kidau number kimin magana ngd

Maganin karin kiba

Maganin nono da hips

Rage tunbi da kiba

Infection set

Sabon budurci set

Niima set

Basir set

Matsi mallaka

Amarya set

Uwar gıda set

Mai jego set

Dadai sauransu

```MRS SADAUKI✍```

My book is only 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,ko kuma katin MTN na 500₦ yan Nijar kuma carte airtel ko Moov ta 500f sai a turo da shaidar biya ta WhatsApp +22795045822,in kin san ba ki biya kuɗin karatu ba kar ki karanta min littafi domin mallakina ne .

_____

BOOK3
```

The END

Da sauri na miƙe ina cewa “ Yaya Khaleed kana dai ganin ko wanka ban yi ba don Allah ka bari har mu koma gida ” hannuna ya kama ya kai ni Toilet ɗin,na yi tunanin ni ɗaya zai yi wa wankan amma sai na ga shi ma ya cire nasa kayan .Wanka ne muka yi mai cike da shauƙi da zallar ƙauna,na sha jin ana cewa irin haka rayuwar aure ta fi armashi in ruwa na dukan mutum amma ban yarda ba sai yanzu.

Tamkar cirar ƙaya haka na ji abin a tsakiyar goshina lokacina da Yaya Khaleed ya kai bakinsa kan goshina ya na kissing.Haka ma ya yi da tafin hannuna,kafin ya koma gefe ya ta kelaya aman wani abu baƙi ƙirin wanda ko makawa babu gubar tsafi ce.

A halin yanzu da nake tsaye ina dubansa babu abin da zan iya don na dawo normal mutum duk na rasa komai nawa.Tsawon lokaci ya ɗauka yana aman nan kafin ya miƙe ya zo gare ni,wani wankan muka yi kafin mu fito.Kayan jikinmu muka maida sai kuma muka hau hirar abubuwan da suka shuɗe waɗanda a yanzu tabbas na yarda harakar asiri ne da tsafi babu wata baiwa.

“Amma Yaya Khaleed ita Ammy me yasa ba za ka cire mata nata power ba?” na jefo masa tambayar.

Ya ce “ ita fa iskokanta ne ke sanar da ita komai,ita nata ba sabon abu ba ne ana samun irin wannan abin wurin mutane da dama.Wasu an fi nuna musu abu a mafarki,yayin da wasu har a zahiri”

“To amma ta ya mutum zai bi ya rabu da su?”

“Dole sai ya tashi tsaye ya nemi maganin jinnu ta wannan hanyar ce kawai aljanun za su barsa,ko kuma in sun nuna masa abin sai ya ƙaryata jinnu na jin haushin haka daga wannan ne sai su rage faɗa musu.”

Na ja ajiyar zuciya na ce “ to ai kuwa za mu yi wa Ammy magana ita ma ta nemi magani”

Yayi murmushi ya ce “ ai ba ta so ta ce abar ta da kayanta, Basheer dai shi yana can ana yi masa magani.In ya samu lafiya zan saka ku makarantar islamiyya ku biyun don fitar da duhun jahilci ”

Na soma kukan shagwaɓa na ce “ ai a addininmu cewa aka yi in mace ba ta da ilimi kar miji ya kusance ta”

Fuska ya haɗe wannan yasa da sauri na shiga hankalina,ƙofar aka bubuga ya je ya buɗe Ammy ta shigo ita da Shuraim nan fa aka zauna aka soma yin hira .Likita ya shigo ya bani takardar sallama,Ammy ta ce “ ku zo ku duba Ma'idar ”

Yaya Khaleed ya ce “ don Allah Ammy mu je ” harara ta yi masa wannan yasa dole muka shiga ɗakin,baiwar Allah tana rakuɓe tana shan ayaba duk ta rame.

Shuraim kuwa ido ya ƙura mata yana kallo har sai da kowa ya lura,da muka fito ya kasa haƙuri ya ce “ abokina ya kuke da waccan ɗin? Da na ga ko ranar da aka yi musu shari'a kana ta kula su”

“To wannan ɗin bazawara ce,kuma ma dai kusan za ku kai shekaru guda” cewar Yaya Khaleed.

Ammy ta ce “ to sai me? Ita bazawara ba mutum ba ce? Ka ga in kana sonta je ka karɓo lambarta ni nan zan tsaya ma har komai ya tafi daidai”

Shuraim ya sosa ƙeya yana murmushi kafin ya ja hannun Khaleed su koma ciki,ba su wani jima ba suka fito suna dariya .Sai bayan mun shiga mota ne Yaya Khaleed ke bamu labarin yadda aka yi“ kasa fa magana yayi sai ni ne na karɓo bayan na yi wa mahaifiyarta bayani”

“To tonan min asiri”

“To ai gaskiya ce,wai ya zancen mayyar Shareef?” sai kuma suka tuntsire da dariya kafin Shuraim ya basa amsa da “ tuni an kira danginta ai suna can za ku sallace ta,ai maganin mai ruwan ido da ɗan hassada kenan .Kana ganin Oga tuni ya bani umarnin na je na tone abubuwan da ya binne ”

“Ai Shareef gadon mugunta ce yayi,Allah dai ya kyauta ”

Haka suka ta yin hirarsu,ina saurarensu na yi lamo a jikin Ammy na yi tunanin gida za mu je sai na ga ya ɗauki hanyar Say.Har sai da na yi bacci na farka ba a kai ba,haka na zauna na yi ta ƙarewa garin kallo har muka isa masarauta.

Da ihun Basheer muka ci karo,da sauri na shige gaba jiki na min rawa.Kwance na tarar da shi dogarai duk sun danne shi yayin da malami sai karatu yake zubawa,aljanin kuwa sai ƙara jadadda maganarsa yake ba zai fita ba.Sai da ya galabaita sosai sannan ya yarda ya fice bayan ya karɓi kalmar shahada,tuni shi kuwa BASHEER ya ɓingire da bacci.

Ɗauke shi suka yi suka mayar da shi ɗaki,daga nan wurin mai martaba muka je yana zaune yana sauraren sautin ƙira'a a cikin wani MP3 .Duk muka gaishe shi da jiki ya amsa cikin sakin fuska, Khaleed ya je ya rungume mahaifinsa yana murmushi kafin kuma su yi mana sallama shi da Shuraim su koma can Yamai

★Bayan sati biyu da zuwan Ammy aka ɗaura aurenta da mai martaba ,a kuma wannan rana ce yayi murabus daga kujerar mulki juyin duniya aka da Khaleed amma ya ƙi hawa a dole aka baiwa Uwais riƙon ƙwarya na karagal mulki.

A can Zinder aka yi ɗaurin aure amma biki kuma a nan aka yi,ɗaiɗaikun danginmu sun zo ciki kuwa har da Mama wacce sai a yau ne na ji ashe aurenta ya mutu.

Ina zaune kusa da ita take ce min “ Alhaji fa na can tension ta buge shi ba hannu ba ƙafa tun ranar da ya so yi miki fyaɗe,ban san mene ne ya gani ba amma sabatu iri-iri haka yake yin su har da cewa ya tsane ni na je ya sake ni dama da ZAWARCI na fi dacewa rabon a yi ne yasa shi aurena ”

A yayin da Mama ke maganar fuskarta sai ta canza,na yi ƙasa da murya na ce “ Mama in sha Allah ai za ki yi aure har ma ki hai...” sallamar Uwais ce ta katse min ƙarshen zancen,da sauri Mama ta miƙe za ta bar wurin shi kuwa sai wani kallo yake yi mata .

“Sarauniya SEERAT zo kin yi baƙi” ya furta.

Na ce “ mai girma mai martaba shine kuma da kanka za ka zo kira na?” na faɗa tare da fice wa na barsa da Mama ban sn me suka tattauna ba.

“Gimbiya Safeena na ce don Allah a bani damar nan na gwada sa'a ta”

Safeenatu ta haɗe rai ta ce “ na faɗa ma ban gama idda ba,kuma a ko wane irin lokaci mijina zai iya mayar da ni tun da saki ɗaya ne”

Ya murmusa ya ce “na sani amma ba na fatan hakan ya kasance domin ke ɗin matar manya ce ba ta tsofi ba” wani kallo ta yi masa kafin ta ɗauke kai,duk yadda ya so ta yi masa magana mai daɗi amma hakan bai samu ba dole ya shafa mata lafiya.

Su Yaya Khaleed ne da Shuraim da Shareef,a mutumce duk muka gaisa na lura har yanzu Shareef na jin kunyata.

Kayan marmarin da aka zube a gabansu na kalla yawuna suka tsinke,na dubi Yaya Khaleed cikin ido tuni kuwa ya fahimci me nake so ya ɗauko ya miƙa min na karɓa na soma sha.

“ Abokina ko mun yi ajiya ne?” Shareef ya faɗa yana dariya.

Shuraim ya ce “ ai kuwa dai little Princess za a haifa mana ka ga sai na yi ta biyu da ita”

Shareef yayi masa dukan wasa ya ce “ Allah ya sawwaƙa na bayar da yata ga tsoho can ka iya da Bazawararka”

Khaleed ya ce “ cewa ake Baz hahaha! «

“Ko ma dai me za ku ce sai na aure ta,yo ai dama an ce sun fi sanin makashin aure”

Gyaran murya na yi kafin na ce “ ni dai a bari har na gusa ”

Shareef ya ce “ ni ma ki samo min ko baz ɗin ce na angonce don wallahi ba zan zauna a gwabro ba”

Shuraim ya ƙyalƙyace da dariya ya ce “ a'a bazawari zaka ce ko ka manta cikin zawarci kake?”

Duk muka dara har shi Shareef ɗin kafin Yaya Khaleed ya ce “ wato har maza ma ana cewa suna zawarci?”

“I sosai mana ! Ka ga kamar abokina sakin wawuya ce ” haka suka dinga tsokanar junansu gwanin sha'awa,ina zaune gefe ina kallonsu da lokacin cin abinci yayi na je na bada umarni bayi suka zo suka kawo.

#SAKEENATU

Tun daga ranar da FA'IZA ta mutu har izuwa yau ba ta taɓa kwanciya bacci ba sai ta yi mafarkinta tana roƙon ta don Allah ta kula da ƙannenta .Wannan yasa sam ba ta yi ƙasa da gwiwa wurin tallafa musu ba,masu karatun har makarantarsu ta je ta bayar da lambar da za a dinga kiranta in ana buƙatar wani abu.

Sauran kuma makarantar koyon ɗinki ta saka su domin su koya ta yadda za su tsaya da ƙafarsu ,don yau da gobe sai Allah duk da ba ta fatan ranar da za ta gajiya .

Bayan Shari'a Ma'idah ta kwanta jinya,ita ta kula da ita yayin da dangin ubanta suka biya kuɗin komai.Daga lokacin da Shuraim ya nuna yana son ta kuwa sai dangin Agali suka fara bar masa nauyin kula da ita duk don su ga in zai iya,shi kuwa ya nuna musu cikkaken namiji ne sai ɗawainiya yake da ita.

Ba wata hira suke yi sosai ba,ko a waya in ya kira ta iya gaisuwa da kuma tambayar jikinta kawai yake yi.Wani sa'in ne yake haɗawa da nasiha,a ƙarshe kuma sai ta fashe masa da kuka har yayi mata sunan wasa da mai saurin kuka.

Tun da manyan suka shiga lamarin aka soma yi wa Ma'idah gyaran jiki,sosai ta yi kyau sai dai akwai rama saboda tunanin tsohon mijinta da kuma na mahaifinta wanda a halin yanzu ba su san inda igiyar hauka ta kai shi ba.

Ana gobe walimar bikin Ma'idah Abbas ya zo gidansu Sakeenatu,har cikin falo aka yi masa iso.Shiru ta yi tana sauraren jawabinsa,“ Keenat wallahi tun bayan rabuwarmu babu sallah ƙwaya ɗaya da na taɓa yi wacce ban roƙi Allah ya maido min ke cikin rayuwata ba,ina sonki sosai ke shaida ce .Ki ɗauka duk abubuwan da suka faru matsayin ƙaddara ne,ki bani dama don Allah na ƙara zama mijinki”

“To sai na yi shawara, sannan ni ma ai ka san ina sonka sai dai a halin yanzu hankalina ba kwance yake ba ga bikin Ma'idah ga kuma abubuwan da suka yi ta faruwa a rayuwata”

“Haka ne , Allah shige mana gaba”

“Amen”

Sai da suka taɓa hira kafin su yi sallama.

★YAMAI

Wani irin katafaren gida na gani na faɗa mai Martaba ya saya wa Yaya Khaleed,sai da aka ƙara sabunta shi sannan aka zuba mana sabbin kaya.Waɗan can tsofin kuma aka sayar aka saya min mota da su,motar da Yaya Khaleed yayi tsalle ya dire kan ba zai bari na hau ba sai dai a nema min direba.

Kamar wata sabuwar amarya sai da Ammy da wasu bayi suka yi min rakiya zuwa sabon gidana wanda babu ce kawai babu.Sosai na yi murna har da taka rawa,a ranar ko agwagwa albarka wurin wasa da ruwa.Haka na dinga shiga bahon wanka ina camɓal-camɓal a ciki har sai da Yaya Khaleed ya soma yi min faɗa .

An zuba min masu yi min hidima har mace huɗu,ga mai gadi da direba amma tsabar tsiyar gumi haka yake saka ni shiga kitchen wai ya fi son girkina .

Yanzu ma girkin nake suna taya ni har muka kammala,wanka na je na tsala na caɓa kwalliya.Bayan sallar magarib ya shigo yayi wanka ya shirya cikin wasu blue suit har da shace kai tare da soma ɓarin turare.

Kasa haƙuri na yi na ce “ wai ina za ka je?”

“Wurin partyn Shuraim mana ” ya bani amsa kai tsaye.

“To amma ai tun shekaran jiya aka yi bikin ko?”

“Eh! Jiya aka kawo amarya,yau kuma taron taya murna da police suka shirya”

“Amma mu da aka yi bikinmu ba a yi wannan ba”

“Eh ni ne nan na hana saboda ina da kishi ba zan bari a kalle min mata ba”

“To na ji! Bari na kawo ma abinci”

“Ina sauri in na je can zan ci” ya faɗa yana ɗaura agogo,da sauri na je na tsaya a gabansa na ce “ wallahi babu inda za ka je”

Cak ya ɗauke ni ya ɗora tsakiyar gado,yayi min kiss a goshi ya ce “ sai na dawo” yana gama faɗa ya fice.Na bi shi da kallo ina jin wasu hawaye na zubo min kafin na miƙe da sauri na biyo bayansa.

A gaban idona ya shiga mota na dubi tafin hannuna ina cewa ina ma ace har yanzu ina da power da tabbas sai na tsayar da motar nan na hana ta tashi,haka na koma ciki ina hawaye.Duk kwalliyar da na yi da wahalar girki sun tashi a banza,ƙawata

Maryam na kira don ita ce na ware matsayin ƙawar shawara,kamar wata uwata tana ɗaga wa na fashe mata da kuka wiwi kafin na koro mata bayani ta shiga yin wani murmushi mai sauti kafin ta ce “ SEERAT abin da ba ki sani duk yadda namiji ya kai ga son ki to akwai ranar da sai ya baƙanta miki rai,ke ce kike ganin wannan a laifi shi kuwa a wurinsa sam ba wata matsala ba ce don bai tsaya cin abincin da shine ya fitar da kuɗinsa aka dafa.Sannan bari na faɗa miki wani sirri,ba kowanne lokaci ba ne mace za ta nuna sarautarta ba .Misali kamar yau da take ranar walimar babban abokinsa ta ya ke ma kike tunanin za ki hana shi fita kuma ya biye miki? Inda dai kamar fita ce zuwa majalisa ko kuma wani yawo da suka shirya su da abokansa waɗannan duk za ki iya yin gadara a matsayinki na yɨa mace ki hana shi fitar”

“To na ji tun da kin shigar masa,yanzu yana can yana kallon yɨan mata fa” na faɗa wasu ruwan hawaye na sake zubo min.

Maryam ta tuntsire da dariya ta ce “ ke fa duk tsiyar mace ba za ta iya hana mijinta kallon Mata ba,Allah na tuba yo ko matar indiya namiji ya aura wallahi in ya fita sai ya kalli wasun.Kawai dai ki yi addu'a in ma kishiyar ce Allah sa ta gari ce ba irin namu ba da suka asirce mana mazaje”

Na ce “ wai kishiyarki?”

“A'a fa matarsa dai ko ba ki da labarin na bar gidan? ”

“Innalillahi saboda me? Inda kin yi zamanki ko ba komai kana ɗakinka ya fi gaban iyaye”

“Wallahi gwara gidan iyayena da gidan habibi, ke tsabar ɗiyan iskanci fa shi da matarsa suka dinga yi min abubuwa iri-iri wai fa sai abin da ta ce ake zartar wa a gidan har da hana ni zuwa makaranta”

Na ce “ Maryam anya kuwa ba aljanin kanki ba ne ke juya miki kwanya? Ya zancen maganin kina amfani da shi?”

“Na bari,ke ni fa ban san daɗin aure ba hakan ma ya fiye min kwanciyar hankali ɗan cikin da na samu ma ɓarewa yayi”

“Duk sharrin jinnu ne ki nemi magani,in ba haka ba zai dinga zubar miki da cikin kenan ko wani auren kika yi don da alamu ke naki aljanin mai barin a yi aure ne haihuwa ce bai so”

“ SEERAT yar baiwa! Amma kin ji daɗinki fa komai kin sani na ɓoyayyar duniya” ban kai ga bata amsa ba kuɗina suka ida ,na ajiye wayar tare da shiga toilet na wanke fuskata.

★ A wurin diner kuwa sosai aka ƙawata komai ,dangin amarya da na ango da kuma abokai sai hidima ake yi.Komai yana tafiya kan tsari,Shareef ya koma can gefe yana kallon yan mata amma sam bai jin irin wannan yanayin nan da yake shiga in ya ga mace da wannan tsoron ya zauna wuri guda har aka gama aka mayar da amayar gidanta wanda aka cika tanƙam da dukiya .

Khaleed da Shareef har tsakiyar falo suka yi wa Shuraim rakiya kafin kowa ya kama gabansa.Da sallama ya shiga ɗakin, Ma'idah bazawara ce amma tamkar wata budurwa haka take wani noƙewa.Dakyar ta yarda suka yi wanka a tare,yau ma sai da ya sake jan su sallah suka yi yan ciye-ciye kafin ya ja su shimfiɗa.Da farko ta soma jin kunya amma da ta ɗauki caji dolenta ta soma mayar masa da martani,a nitse suka yi komai cikin kwanciyar hankali .Da asubah haka suka shiga wanka tare Shuraim sai wani manne mata yake ita kuwa Ma'idah duk wata sauran damuwarta duk ta kau,bayan sun yi sallah ya soma koya mata karatu kafin kuma ta shiga kitchen shi kuma ya shige ɗaki yana shat.

★A ɓangaren Basheer kuwa sai da ya sha ayoyin Alkur'ani yayi wanka da su kamar ba gobe sannan hankalinsa ya dawo jikinsa.Haka zai zauna yayi ta tunanin abubuwa wasu yana sane wasu kuma jinsu yake kamar a mafarki don ba cikin kansa ya aikata su ba.Kusan kullum sai sun yi waya da Hawa'u wacce ta mutu cikin sonsa duk da a yanzu shi a ɓangaren Baseer ɗin gani yake ta yi masa girma tun da ta girme masa amma a haka yake biye mata suna amintar mai cakuɗe da soyayya.Burin zama sarki kuwa raɗam yake a zuciyarsa,kuma haka yake sake jadadda wa Hawa'u shi kusan kullum.

★★★

“Zo mu zauna zo mu saɓa” waɗannan abubuwan biyu na koye su ne tun ranar da Maryam ta yi min nasiha,wannan yasa ko a ranar da Yaya Khaleed ya dawo ban nuna masa ɓacin rai ba sai ma kulawa ta musamman da na basa wacce a washegarin ranar ne kuma ya kai ni makaranta domin ci gaban karatuna wanda da farko ya so katse igiyar numfashinsa.Farin ciki da nutsuwa sune suka wanzu a familyna,hankalinmu kusan za mu ce duk a kwance yake ,yɤar tangarɗa da muke ciki bai wuce yadda Mama ta shafa kwallin rashin mutumci tare da hawan kujerar ZAWARCI ta ƙi sauka.Juyin duniya mun haɗa baki wurin rarrashinta akan ta amince da auren sarki Uwais amma ta ƙi,a cewar ta ba ta da rabo a zaman aure miji guda ne ta aura ɗan mutumci wato mahaifinmu bayan shi ta yi aure biyu waɗanda gwara babu su,don haka babu wanda zai ci gaba da yi mata ƙirgen gidajen da ta yi aure.

Wannan ƙoƙon barar na Uwais ya kwashe tsawon watanni shidda kenan amma ta ƙi karɓarsa,sai yau kamar daga sama ta ce ta amince farin cikin da na shiga ya haifar

min da naƙudar wuri tun kafin lokacin haihuwar yayi .Ban wani ci wuya na haifo yʻata yʻar mitsitsiya da ita,don tsabar ƙarantarta sai da aka saka ta cikin kwalba.

Ammy tuni ta kawo girgiza asibitin ita da masu yi mata hidima,wata kula ta musamman ta soma bani ko motsi na yi sai ta tambaye ni me nake so .Shi kuwa Khaleed ya kasa zama kusan kowanne lokaci yana asibitin haka ba kunya zai wani manne min sai in Ammy ta yi masa faɗa ,sai da muka yi sati guda currr kafin a sallamo me mu.

Kaka ita ce yʻar tsaron biƙi,ita da Samira ta zo wacce sam auren da ta yi a idona ban ga ya karɓe ta ba.A ranar da ƙawata Maryam ta zo kowa sai da ya san aminiyata ce,girki na musamman aka yi domin tarben ta.Haka muka yi ta shirme,in na ɗauki Princess zan shayar da ita sai Maryam ta yi ta ƙyalƙyata dariya ta ce “ oh wai yau SEERAT ce ke ban nono” Samira ta kama mata har sai da suka ban haushi na ce “ sai ku yi ta dariyar tun da mahaukata ne ku”

Maryam ta ce “ eh mun....” sai kuma ta yi shiru saboda shigowar su Yaya Khaleed,ina ganinsa na nufe shi ina turo baki na ce “ gwara da Allah ya kawo ka zo ka hukunta min Maryam da Samira na kawo ƙararsu”

Yayi murmushi ya ce “ sai dai ban fiye yin Shari'a ba,amma ga Shareef nan sai yayi musu kin san ya ƙware wurin alƙalanci”

Na dubi Shareef ɗin da ke kallon Maryam na ce “ Papan Princess a zo a yi mana shari'a”

Maryam da ke can gefe ta ce “ ko? Ke ga matar ɗan sanda shine kike yi mana gami,to ni soja zan aura ”

Yaya Khaleed ya ce “ Maryamu soja kuma? Ko dai a cikin mota wani yayi gaba da zuciyarki”

Ta yi dariya ta ce “ wasa fa nake Yayanmu,amma ina ni ina soja Allah sawwaƙa ”

Na ce “ ah to in sha Allah shi za ki aure”

“Bari na je na kawo musu ruwa ya fi wannan surutun naki da nake saurare,in auri soja na kai shi ina” sai ta min harara,na yi murmushi don na gane abin da take nufi.

Jaririya Khaleed ya ɗauka ya soma tofe ta da addu'o'in da ya saba kafin ya miƙawa Maryam ita wacce ta kawo musu ruwa.Shareef uban iya yi sai cewa yayi “ Madam mu gan ta” ta je za ta basa ita kenan na fito ina cewa “ wai ni kam Papan Princess ba ka taɓa bani cigiyar matar aure ba?”

Ya ɗago yana cewa “ eh haka ne matarmu”

Na ce “ na baka Maryam ga ta nan sai a bamu sadaki”

Ta harare ni ta ce “ tun da wani buhun dankali ne ai dole ki ce kin basa”

“To na karɓa ,sadaki kuma mijinki ne zai biya” cewar Shareef .

Haka muka dinga yin raha Maryam na wani sharewa kamar ba ta so alhalin kuwa munafukar tuni ta kamu,bayan fitar su ne na bata labarin tsohuwar matar Shareef .

Ta ce “ Allah sa ma raggon namijin ne kin ga shikenan mun yi anko” muka hau dariya.

Abu kamar wasa sai ga Shareef ya dawo da dadare,sun yi hira sosai ta fahimta tun da dukkansu sun taɓa yin aure sun fita daga sawun yara.Daga nan soyayya ta ƙullu kullum sai ya zo sun yi hira ko ya ɗauke ta da mota su zaga gari , wannan lamari ya fi komai yi min daɗi musamman da ya zamana ita ma matar Shuraim na santa.

A ranar suna yarinya aka raɗa mata Zahra'u amma muna kiranta da Princess,mun yi anko mu uku iri ɗaya ni,Ma'ida da kuma Maryam kamar yadda su ma abokan mazan suka yi.

Sai ɗaya ga biki Mama amarya ta zo ganin jikarta,na ɗora bori kan sai na tafi shan kunu amma Yaya Khaleed ya hana a dole na zauna domin kare igiyar aurena,wacce muhimmancinta da darajarta bazawara mai fuskantar ƙalubalen rayuwa ce ta fi kowa saninta. A shekaruna na fahimci cewa da yawan mutuwar aure mu mata muke jawo shi,abin da bai zama dole ba mu ce sai mun yisa saboda kawai mun kwankwaɗi giyar al'ada.

ZAWARCI ba za a kira shi illa ba kai tsaye sai dai za a iya ce masa babbar makaranta ce wacce ke koyar da darasi iri-iri,yana da azuzuwa marar misaltawa waɗanda in aka ce za a buɗe aji guda kaɗai zai iya ɗaukar shekara guda ba tare da an gama bayaninsa ba.Wani sa'in yinsa shine masalha ƙunci da muke ciki,yayin da kuma ɗaya ɓangaren gwara zaman gidan mijin da fito wa ka dawo gaban iyaye.

ALHAMDULLAH !!!

A nan kawo ƙarshen littafina na ZAWARCI,wanda shi dai wannan jigo yana da faɗi mai girman gaske wanda na ɗauka shine na maƙiyan da suke son dole su ruguza rayuwar auren ka domin ka zauna cikin ƙuncin zawarci wanda gwara a ce tun farko baka taɓa auren ba da wani zarwacin.Kamar yadda na sha faɗa yau ma zan sake maimaita wa a yadda na tsara labarina a nan ne kawo ƙarshensa don na warware duk abin da na ƙulle,in kuma akwai wanda yake ganin da buƙatar a saka wani abun to na ba kwanyarsa dama ya ci gaba da tunanin yayi ma kansa ci gaba

Waɗanda suka karanta min book ba tare da kun biya sisi ba kuna da zaɓi biyu ƙofa a buɗe take don sauke haƙi 500 via

6042551755

Hassana ibrahim

Keystone bank,in kuma na biyun kuka ɗauka babu matsala.

Chamsiya Laouali Rabo□□